بسم الله الر حمن الر حيم.

*______________________________*

* 💧💦RUWA DA KANKARA⛈⛈*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The notion}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp

*________________________________*

*PAGE ONE*

********************

Wani dattijo ne tafe akan keken shi, da ciyawa a bayan kariyar sa wadda ya daure da igiya, yana ta sauri saboda yana so ya k'arasa gida, saboda hadarin dake barazanar tasowa, ga wani duhun damana da ya mamaye fadin sararin samaniya.

Aiko duk saurin shi na son yaje gida kafin afara ruwan, sai da suka fara sauka tareda wani iska mai karfi dake kadawa, ya karawa keken shi gudu yana tafe yana sharce ruwan dake zuba akan fuskarshi.

Tun daga nesa yake jiyo sauti kamar na kukan jariri, acikin al'jabi ya k'ara kasa kunnuwan shi, saboda yana so ya gasgata abunda kunnuwanshi suka jiyo masa, acikin fargaba yake tafiya saboda jin kukan yana k'ara kusantoshi, sai raba ido yakeyi domin ya ganema idanunshi abunda zuciyarshi ta tabbatar masa.

Karaf idanunshi suka hango masa wani k'aton kwali dake ajiye acikin ciyayi, inda ko tantama babu acikinshi ne wannan kuka na jariri yake fitowa.

Gabanshi ya k'ire ya fad'i, ba shiri ya tsaida keken shi ya sauko, tareda furta kalmar:

"INNALILLAHI WA INNA ILAIHIRRAJI'UN YA HAYYU YA KAYYUMU BI RAHMATIKA ASTAGISU, A'UZU BI KALIMATILLAHIT TAMMATI MIN SHARRI MA KHALAKA"

Bai tsaya anan ba har saida yayita jero addu'o'i yana shafe jikin shi, sannan ya tunkari inda kwalin yake ajiye, acikin jarumta ya saka hannu ya bud'e kwalin bakin shi d'auke da bismillah, da sauri yaja baya ganin abunda ke ciki, alokaci d'aya aka tsuge da ruwan sama masu k'arfi, har ya juya acikin sauri da nufin yaja keken shi ya bar dajin.

Aiko jinjiri ko jinjirar dake cikin kwalin ta kara k'wallah wani kuka saboda ruwan saman dake sauka acikin kwalin suna jik'a masa/mata jiki, da sauri dattijon ya waigo yana k'ara maimaita addu'a acikin zuciyarshi da bakin shi.

Da hanzari ya dawo ba shiri, ya k'ara zurawa jinjirin/jinjirar idanu, alamu duk sun nuna a bayyane cewa mutum ce/ne, amma ganin farin da tsantsar kyawon halittar ya sakashi jin tsoron kar fa ace diyan aljanu ne, azuciyarshi yace:

"Nayi niyyar taimako don Allah koma menene Allah Ubangiji ya kare ni da sharrin dake ciki"

Aikuwa duk wani tsoron da yake ji ya gushe azuciyarshi, acikin kuzari, yayi bismillah ya saka hannu ya d'auko abunda ke cikin kwalin, ya aza akafad'arshi, ba shiri jinjirin/jinjirar yayi shiru tareda sauke wasu ajiyar zuciya ajere da juna.

Yana kai idanunshi acikin kwalin, yaga kud'i ajere k'asan kwalin, sanadiyyar towel d'in dake shimfid'e aciki da ya janye a gefe d'aya yayin d'auko jinjirin/jinjirar, da sauri dattijon ya maida jinjirin/jinjirar acikin kwalin ya rufe, aiko ba shiri ya k'ara k'walla wani kukan, jiki yana rawa dattijon ya kinkimi kwalin ya azashi agaban kekenshi sannan ya gyara mata zama ya fara lula gudu, duk da k'arfin ruwan dake sauka, acikin k'warewa yaketa balbala gudun, hannunshi d'aya rik'e da kwalin d'aya yana tuk'a keken, wanda har izuwa lokacin jinjirin/jinjirar bata daina kukan ba.

Tofa dandano daga abunda ke cikin littafin:

*RUWA DA KANKARA*

Akafta🙊

Nice dai taku har kullum :

D/Auta 👌🏻

بسم الله الر حمن الر حيم.

*___________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA🌧️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The notion}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp

*_____________________________________*

*ASSALAMU ALAIKUM DA FARKO INA MIKA SAKON GAISUWATA AGAREKU TAREDA SAKON TAYA JUNA BARKA DA SALLAH ALLAH YA MAIMAITA MUNA*

*PAGE TWO*

********************

Jiki yana rawa dattijo yakai k'ofar dan madaidaicin gidanshi,bayan waige waige da yakeyi don yana jin tsoron tuhumar 'yan unguwarsu, ba shiri ya sauke ajiyar zuciya, ya godewa Allah da wannan ruwa da ake tayi kamar da bakin k'warya, wanda k'arar saukar ruwan ya hana ajiyo sautin kukan jinjirin/jinjirar.

Abakin k'ofar gidan ya ja burki, Wanda a kallo d'aya zaka gano gidane irin na rufin asiri, amman fa akwai babu a gidan,  duba da yanda k'ofar shiga gidan ta kasance ta langa langa duk ya hunhunde ya taso wanda idan bakayi a hankali ba yayin shiga gidan tsaf langa langar zai yage maka kayan dake jikinka.

Da dubara ya sauko hannushi d'aya rik'e da kwalin da jinjirin/jinjirar  yake ciki wanda duk ya jik'e sharkaf, saboda ruwan da ake ta tsulawa har izuwa lokacin, yayinda shima jaririn/jaririyar har izuwa lokacin bata daina kukan ba, amman ga dukkan alamu  daga yanayin kukan da yake ko take ta gaji sosai,  saboda tasha kuka har muryarta ta dusashe.

ya samu ya jingine keken, sannan ya ciro kwalin dake gaban keken ya rungume da hanzari ya fada gidan a sukwane kamar anjefo shi.

Kai tsaye ya wuce wani d'an madaidaicin d'aki, yayin da iya kulu dake baiwa akuyoyinta k'asari ta bishi da kallo baki asake, tana mamakin kukan jaririn da tajiyo, haka kawai zuciyar ta tabuga ba shiri, da sauri ta d'auraye hannunta ta nufi d'akin da taga ya fad'a,  jin sautin kukan jaririn muraran ya k'ara kid'imeta.

Ba shiri ta afka d'akin ko sallama babu domin ta ganewa idanunta abunda ke faruwa, da sauri wata tsohuwa dake zaune tayi tagumi tareda wannan dattijon suka bita da kallo.

Ido abud'e iya kulu tace:

"Malam me nike shirin gani?"

Da sauri tsohuwar ta katseta da cewa:

"To tonanna maza kiyi sauri kiyi shela har mak'ota su ji, tunda ke ba'a sirri dake"

Jiki asanyaye iya kulu ta rakub'e gefe tareda tsurawa masu kallo in ta kalli malam ta kalli Dada 'yar tsohuwa, tanason taji ba'asin abunda ke shirin faruwa.

Dattijon nan mai suna malam wanda ga dukkan alamu,  wannan tsohuwar itace mahaifiyarshi, duba da yanda kamar su ta fito abayyane.

Ya saukar da ajiyar zuciya tareda cire tagumin da yayi, ya duk'a ya d'auko jinjirar dake cikin kwalin ya rungume ajikinshi, tareda sauke ajiyar zuciya, jinjira kam saboda sanyin da ya ratsa jikinta, da sauri ta ratsa kuka, ba shiri  Dada ta karbeta hannunu malam ta janyo zane ta goyeta tana jijjigata tana bubbuga bayanta,  tun tana kukan har taji gumin goyo tayi bacci.

Iya kulu dai tana tsaye sai rabon idanu takeyi, Malam ya k'ara sauke ajiyar zuciya ya fara yimasu bayanin yanda akayi ya tsinto ta.

Iya kulu ta rafka salati da k'arfi tace:

"Yanzu malam haka kawai kaga d'iya acikin daji an jefar kai kaje ka kwaso muna jaraba ka kawomuna acikin gida, muna zaman zamanmu ka jaza muna hitina, yanzu in d'iyar aljanu ce fa?, shikenan kasa mu shiga uku"

Dada saboda hararar da take yimata,  kamar idanunta su fad'o,  amman duk da hakanan sai da iya kulu takai k'arshen maganarta, malam ya d'auke kallonshi daga kanta yace:

"Ko aljanar ce nayi niyyar taimako don Allah kuma bazan fasa ba, saboda bazan iya ganinta acikin wannan  halin ba, ace in kasa taimakon 'yar jinjirar Allah ba, bazan tab'a yafewa kaina ba, idan har ban taimaketa ba, ki kwantar da hankalinki za'ayi cigiyar iyayenta, idan ansamesu sai mu basu 'yarsu salun alun, don ga dukkan alamu wannan 'ya bata k'ananun mutane bace, duba da yanayin shigarta, sannan da wad'annan mak'udan kud'in da na sameta tareda su"

Jiki yana rawa inna kulu ta zaro ido tace:

"Kud'i? Kud'i fa kace malam"

Malam ya tabbatar mata, sannan yace da ita ta bud'a kwalin ta gani, aiko jikinta yana b'ari ta bud'a da sauri ta d'auki kwalin ta rungume baki har kunne tace:

"Bari inje in b'oye su malam tun kafin 'yan unguwa su gano munada wad'annan kud'ad'en a gidanmu su samu abakin duniya"

Da hanzari Dada ta karb'e kwalin tace:

"Ta ina suka zamo kud'inmu?,  waya baku?, daga ganin sarkin fawa sai miya tayi zak'i, to gani nan bari nan saboda bamuda hak'k'i da wad'annan kud'in har sai anje wurin mai unguwa abunda duk yace shi za'a bi, saboda gudun abunda zaije ya dawo kafin agano iyayen yarinya su karb'i 'yarsu"

Iya kulu ta b'ata fuska tace:

"Dada fa kowa ya samu ta kanshi yakeyi, yanzu saboda Allah sai ad'auki wad'annan zundumayen kud'i akaiwa mai unguwa, haka kawai ya cenye su ya barmu sake da baki, kura da shan bugu gardi da kwasar kud'i"

Dada ta rik'e baki tace:

"'yar kuluwa wallahi kiji tsoron Allah ki rage son kud'i, tun kafin su halako ki abanza"

Iya kulu ta fita fuu alamun ranta ya b'ace, don tasan k'arshen abun in ta biyewa Dada ranta ne kawai zaiyita b'aci akan hakan, malam dai ya bita da kallo ya girgiza kai, saboda inda sabo ya saba da ganin rikicin da yafi haka tsakanin Dada mahaifitarshi da Iya kulu matarshi.

Muje zuwa mutanena🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️

Akafta😝

Taku ce har kullum

D/Auta👌🏻

[8/22, 1:55 AM] Auntyna: سم الله الر حمن الر حيم.
*___________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA🌧*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The notion}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*_____________________________________*
*HAPPY EIDUL FIDHIR FOU YOU ALL MY FAN'S💃🏻👍🏻*

*PAGE THREE*

*********************

Malam ya maido da kallonshi akan dada yace:

"Idan an d'auke ruwa zamuje mu kaita wurin mai unguwa, domin abada sanarwa koda Allah zaisa adace asamu iyayenta"

Dada tayi shiru na d'an wani lokaci,  sannan ta sauke ajiyar zuciya tace:

"Ban tari numfashin ka ba, amman jikina yana bani wannan 'yar ba'a yankin nan namu take ba,

akwai lauje acikin nad'in da yayi jagora wajen ya rabata da mahaifiyarta, don ga dukkan alama bawai gama garin yanda ake jefar da yara bace, akwai wata sark'ak'iyar da tayi tsanin wannan bak'ar aika aikar, domin na tabbata duk inda iyayenta suke insha Allahu, suna cen acikin tashin hankalin neman ta ruwa k'ok'o "

Malam ya nisa sannan yace:

"To ke Dada su nemeta akan mi? bayan sun nuna daman cen neman maraba sukeyi da ita, idan akayi la'akari da kud'in da aka saka tare da ita, ana nufin an baiwa wanda ya tsinceta ladar tsintuwa kenan?".

Malam ya k'are maganar acikin jin haushin, wad'anda sukayi wannan ta'adi, tareda janyo kwalin kud'in ya fara fiddo dasu awaje, saiga wata farar takarda aninke, ta jik'e sharkaf da ruwa tayi laushi, da sauri ya d'auko ta ya fara bud'a ta da dubara, don gudun kada ta yage, sannan 'ya harhad'a d'an guntun bokon shi na yak'i da jahilci, ya fara karanta abunda ta k'unsa abayyane domin Dada taji yace:

"Assalamu Alaikum
Wannan jaririya ayau kwana hud'u da haifuwarta, diyar sunnah ce gaba da bayanta, ga kud'i nan a kula da ita sosai arik'eta amana.

Bakin dada yana rawa tace:

"Maganar ka gaskiya ce Ayuba, don haka dole ne mu kaita wurin mai unguwa domin mu cire kanmu a zargin 'yan wannan gari namu, sabo.... "

Kafin ta k'are maganar jaririyar ta fara mutsu mutsu tana son tayi kuka, da sauri Dada ta kwanto ta daga goyon da tayi mata, aiko yarinya ta fara saka hannu abaki tana tsutsa tana bud'ar baki sannan ta saka kuka, Dada ta kalli malam tace:

"Nono take nema kuma gashi ana wannan ruwan ina za'a je asiyo mata madara?".

Malam ya shafa goshin sa sannan ya tashi tsaye jikinshi yana rawa yace:

"Bari inje in gani in d'an liti yana shagon shi in siyo mata madara sai abata"

Dada tayi hanzarin fad'in:

"Wannan madara ba itace ake baiwa jarirai ba, ka jira zuwa gobe idan Allah ya kaimu, sai kaje birni ka siyo mata, saboda madarar da ake baiwa jarirai daban take, na ganta ana baiwa yaran gidan Alhaji murtala, don kasan uwar batada isashen nono"

Malam ya dawo ya zauna acikin damuwa yace:

"To yanzu Dada me zaa bata tasha ne?,tunda  gashi tana jin yunwa?"

Dada ta yunk'ra ta tashi tsaye tana girgizata sannan tace:

"Akwai yanda za'ayi, kira man 'yar kuluwa, tazo ta tatso muna nonon Akuyarta da tayi sabuwar haihuwa, sai abata, amman yanzu idan kace kaje birni a yanzu to yaushe zaka dawo ne?, gashi yamma tayi sosai,  gara dai abari gobe ido yana ganin ido sai kaje ka dawo a mutunce"

Malam ya zaro ido yace :

"Dada yanzu kina ganin ba wata matsala, a nonon akuyar idan an bata?"

Dada tayi murmushi tace:

"Da akwai matsala da tuni kai ne ka fara fuskantar ta, saboda kai ka fara sha kafin ita, gashi kuma Har yanzu ba abunda ya sameka"

Malam yayi murmushi sannan yafita yana cewa:

"Yau tsohon tarihin ya tashi kenan?"

Dada tana dariya tace:

"To wa ya janyo tashin ba kai ba"

Malam ya fito yaje rumfar da akuyoyin iya kulu suke ad'aure, sannan yace da wani yaro wanda bai wuce shekara takwas ba yace :

"Kai garzali je kira man iyarka"

Aiko saigata ta fito tana cin magani sai kumbure kumbure takeyi, malam ya kalleta yace:

"Dauko man kofi mai kyau ki kawo, zan tatso nonon akuya ne abaiwa yarinyar"

Iya kulu ta washe baki tace:

"Yawwa malam na nawa kakeso in tatso maka?"

Jikinta yana rawa ta d'auko kofin ta fara tatso nonon har saida yayi rabin kofin sannan ta rufe ta mik'a masa baki har kunne tace:

"Kawo hamsim na raga maka don sani da sabo"

Malam ya karb'i kofin kota kanta bai bi ba ya koma d'akin dada ya kai mata, aiko tasa d'an k'aramin cibi ta fara bata nonon, yarinya kam sai sha takeyi har sai da ta k'oshi sannan ta b'ingire tana ta baccin ta hankali akwance sai maida numfashi takeyi acikin natsuwa, Dada ta maida ta abaya ta goya, ta d'auko towel d'in da aka tsinto ta dashi ta lullub'eta, sannan ta janyo zanenta da take yafawa ta yafa ta kalli malam tace:

 To yanzu muje wurin mai unguwar tunda ansamu ruwan sun tsaya kafin su dawo"

Malam ya d'auko kwalin suka fito, iya kulu tana barandar ta atsaye taga fitowar su, da sauri ta k'araso awurinsu tace:

"Yanzu da gaske kai kud'in zakuyi?, munaji muna kallo ayi muna sama da fad'i dasu?"

Dada ta galla mata harara sannan tace:

"A'a barmaki za'ayi ki tusa su agaba kiyi ta kallo tunda gadon gidan ku ne"

Iya kulu ta b'ata fuska ta kalli malam tace:

"Nidai bani Hamsin d'in kar ka mance"

Malam ya kalleta don baya buk'atar tada jijiyoyin wuya yace da ita:

"Kin biyoki"

Suka fita suka barta, sai ga garzali aguje ya biyosu yana fad'in:

" Baba ina zakuje?,  ina zuwa"

Dada tace:

"Zo muje shalelena, inda dai wancen mai kan mangwaron ne da ko k'ofar takashi bazanje dashi ba, halin uwarshi kaf shi ya kwashe"

Tofa ita iya kulun🤣🤣🤣

Akafta😜

Taku ce har kullum

D/Auta 😅
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: .سم الله الر حمن الر حيم
*______________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The notion}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*________________________________________*
*BARKA DA SALLAH MY FAN'S ALLAH YA MAIMAITA MUNA*

*PAGE FOUR*

******************

Dada yar tsohuwa agaba malam  da Garzali suna biye da ita suna tafe suna tattauna matsalar har k'ofar gidan mai unguwa.

Ba tareda b'ata lokaci ba  suka samu damar ganin shi,  bayan sun k'are gaisawa ne,  malam ya fara koro jawabin abunda ke tafe dasu, gabaki d'aya d'akin kowa jikinshi yayi sanyi k'alau,  da jin wannan badak'alar da ta faru acikin garin nasu, mai unguwa yayi gyaran murya sannan yace:

"Ina jaririyar?"

Dada ta ta ciro yarinyar daga goyon da tayi mata, wanda sai alokacin duk wad'anda ke d'akin suka gano da d'iyar abayanta, saboda baccinta takeyi sharkaf,har da su ajiyar zuciya alamun taji dad'in goyon.

Malam ya karb'i d'iyar ya mik'awa mai unguwa, Mai unguwa ya k'ura mata kallo na tsawon lokaci yana nazari, sai ga hawaye suna kwaranya akan fuskar shi, saboda ta bashi tausayi sosai,  kasancewar shi mutum mai tsananin tausayi, saboda yanda ya ganta fara jajir babu d'igon baki ajikinta kyakkyawar yarinya son kowa k'in wanda ya rasa, don rashin imani irin na mutanen mu,  ace ad'auke ta akaita daji a yadda, tamkar an yaddo kashi, afakaice ya share hawayen shi, sannan ya mik'awa Dada ita yayi gyaran murya ya fara magana kamar haka:

"Malam Ayuba"

Malam yace:

"Na'am ranka shi dad'e"

"Yace naji duk abunda ka fad'a ina takardar da kace ka gani acikin kud'in"

Malam ya ciro takardar ya mik'a masa,  mai unguwa ya baiwa wani wanda yake wurin yace ya karanta masa yaji, saboda shi mai unguwa baiyi boko ba,tiryan tiryan aka karanto takarda, mai unguwa yace:

"Malam Ayuba zaka iya rik'e wannan yarinya a hannun ka?, ko zaka barta ahannu na ne har zuwa lokacin da za'a sami iyayenta?"

Malam ya kalli Dada, tayi masa umurni da ido, atake ya d'au hannu yace:

"Zan iya rik'eta a hannu na ranka ya dad'e har zuwa lokacin da aka samu iyayenta"

Mai unguwa yaji dad'in furucin malam yace:

"Alhmdllh na amince dakai ayuba tun ba yau ba shiyasa ma ban musa wannan takardar da kace ka gani aciki ba,  saboda amanar ka ce ta saka har ka bayyana kud'in aka san da akwaisu, nasanka mutum ne kai mai gaskiya da rik'on amana, saboda haka na amince da zata samu kula sosai a wurinku, Allah ubangiji ya taya ka rik'o, kuma ya baku ladar taimakon da kukayi"

Duk d'akin aka had'a baki da cewa:

"Ameen"

Mai unguwa ya bada umurnin akawo goro a rarrabawa mutanen dake d'akin, akayi kamar yanda ya buk'ata,  sannan ya kalli malam yace:

"Wane suna kakeso asawa 'yarka?"

Malam yaji dad'in wannan karamci na mai gari,  baki awashe yace:

"Ina son asa mata suna IZZATU"

Mai unguwa yayi murmushi sannan yace:

"Daga yau an rad'awa 'yarka suna izzatu,sannan kud'in kaje dasu kaci gaba da kula da ita kamar yanda aka umurta, gobe sai kuzo da ita akaita asibitin birni aduba lafiyar ta, sannan abata magunguna irin nasu na jarirai,  sai a azata akan madarar da d'orata akanta adinga shayar da ita, insha Allah zamu shiga binciken su wanene iyayenta,   Allah ya rayata akan tafarkin musulunci Allah ya zamo gatan ta damu baki d'aya"

Gaba d'aya akace "Ameen"

Daga nan taron ya watse su Dada suka fito, bayan sunyi sallama da mai unguwa, suna tafe Garzali ya kasa hak'uri yace"

"Dada ita wannan jaririyar yanzu a gidanmu zata zauna?"

Dada tana murmushi tace:

"Ko baka so ta zauna gidan in maida masu da yarinyar su?"

Garzali yayi saurin fad'in :

"Cab ai ni dada naso ma ace iyarmu ta haifeta wallahi da naji dad'i, baturiya a gidanmu, ai kina bani ita in d'auketa ko Dada?"

Ya k'are maganar acikin tsantsar farin ciki, Dada tana masa dariya tace:

"In kana son inbaka ita ka d'auka,  to dole sai ka bada nera biyar"

Garzali yayi tsalle yasha gabanta yace:

"Zan baki in d'auki d'iyar indiyawa wallahi"

Ba Dada ba har da malam sai da yayi murmushi yace:

"Daga turawa sai indiyawa to sai munji gaba kuma k'ilan ta koma ta larabawa"

Firar da sukeyi kenan har suka shigo gida, iya kulu tana ganin su ta ajiye aikin da takeyi da sauri ta sha gabansu tace:

"Allah dai yasa bai karb'e kud'in ba"

Dada ta harareta tace:

"To mutu kud'i bai karb'i ko k'wandala ba, yanzu ke nawa kikeso abaki naki kaso tun kafin su k'are"

Iya kulu tasan halin Dada tas bak'ar magana ce ta buga mata, shiyasa nan take tayi kalar tausayi ta kalli malam tace:

"Bani Hamsin d'in asiyo ma awaki na dussa"

Malam ba musu ya saka hannu aljihu ya mik'a mata nera d'ari yace:

"Ki ajiye hamsin har da na gobe"

Ya wuce abinshi ya barta anan tsaye sororo da nera d'ari a hannu, tana tunanin me yake nufi, ta watsar da zancen ta koma kan aikinta.

Dada dai tana k'ara yab'awa iya kulu magana ta barsu anan ta shigewar ta ad'akin ta, Malam ya shigo cikin d'akin da sallamarsa, sannan ya ajiye kwalin yace:

"Ga kud'in nan ki ajiye hannunki"

Dada ta girgiza kai tace:

"A'a je ka ajiye su ahannunka, duk lokacin da ake buk'atar wani abu sai ka bada"

Malam ya duk'a ya raba kud'in uku ya saka kashi d'aya a aljihu, ya tura mata kashi biyu yace:

"Ki ajiye a hannunki saboda tsaro"

"Dada tace to Ubangiji Allah ya bamu ikon rik'on wannan yarinya tsakani da Allah, amman ka sanar da 'yar kuluwa abunda ake ciki"

Akafta😅

Takuce

D/Auta 👌

بسم الله الر حمن الر حيم.

*______________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The notion}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp

*________________________________*

*PAGE FIVE*

******************

Malam yana fita Dada ta fito itama, ba tareda tabi ta kan iya kulu ba, ta fara kici kicin aza ruwan zafi, da sauri iya kulu tazo tana baiwa Dada hak'uri akan taje ta zauna ita zata aza ruwan zafin, Ba musu Dada ta bar wajen, tareda fad'in:

"Wanka za'ayiwa Izzatu, idan sunyi zafin ki kawo man d'aki"

Iya kulu ta bita da kallo acikin mamakin jin sunan yarinyar da taji abakin Dada, saboda suna ne na d'iyarta da ta haifa, wadda watan yarinyar hud'u a duniya tace ga garinku nan, sanadiyyar rashin lafiyar da tayi ta fama da ita kafin ta rasu, gashi yarinyar ta shiga zuciyar kowa agidan, tun daga kanta iya kulu bata sake haihuwa ba, ko b'atan wata bata sake yi ba shekara hudu kenan da rasuwar izzatun, amman har izuwa lokacin bata fidda tsammani ba, akan cewa zata sake samun wata izzatun
sai gashi kwatsam yanzu izzatun ta fad'o daga sama.

Agurguje ta gangand'a kara da guntu guntun itace, ruwan sukayi zafi ta juye ruwan ga wani

bokitin karfe, ta had'a da katuwar roba takaiwa Dada ad'aki, sannan taje ta d'auko tsohuwar ajiyar ta,  da take ta tsimi da tanadi, wato  kayan jarirai na mata set biyu ta kawo ta ajiyewa Dada agefen gado, sannan tace:

"Ga kayanan idan anyi mata wankan asaka mata, amman fa d'ari hud'u na sayi d'aya, d'ayar kuma d'ari uku da hamsin, idan an had'a kud'in gaba d'aya zasu kama d'ari bakwai da hamsin, sai abada d'ari bakwai d'in na yafe hamsin"

Dada dake kici kicin cirewa izzatu kayan dake jikinta,wanda tunda iya kulu ta fara magana bata fasa abunda takeyi ba, aikin gaban ta kawai takeyi, har saida taji ta dire zancen ta, sannan ba shiri ta d'ago fuskarta ta kalleta,  bakin ta yana rawa tace da ita:

"Kibar kayanki ai ba rok'ar ki  akayi ba ko?,  balle ki fara yiwa mutane wani lissafin ki cen na shirmen da kika saba"

Tana k'are zancen ta fara yiwa izzatu wankan acikin natsuwa tareda k'warewa, tana wanketa lungu da sak'o.

Iya kulu ta b'ata fuska tace:

"Dubi kayan dakyau  Dada masu kyau ne fa, ayi hak'uri asiye mata su kawai, saboda zasuyi mata kyau sosai"

Dada bata koma bi takanta ba har ta k'are yimata wankan, sannan ta saka zane ta goye ta, tana k'ok'arin fitar da kayan,ne, iya kulu tayi saurin kwashe kayan ta fita dasu, saigata ta dawo da garwashin wuta acikin wani kasko ta ajiye, Dada ta saukar da izzatu ta fara yimata gashin cibiya,  sannan ta kalli iya kulu da kyau tayi murmushi tace:

"Da zaki ajiye son kud'inki 'yar kuluwa to da kinji dad'in rayuwar ki, amman ina kullum abu sai gaba gaba yakeyi, Allah ya jik'an 'yar dubu, don itakam batada son kud'i irin naki"

Iya kulu ta tashi tsam ta fara tafiya zata bar d'akin,  fuskar ta kicin kicin saboda maganganun da Dada take yab'a mata ba k'aramin zafinsu takeji ba, Dada ta kira sunan ta, ta waigo, sannan tace :

"Kinbar kayanki, ko kin barmata kyauta ne?"

Da sauri tace :

"Na zaci an siye mata ai?"

Dada tace :

"Tafi da kayanki, insha Allah gobe zaaje asiyo mata wasu"

Iya kulu ta duk'a ta d'auki kala d'ayar da tace ta siye d'ari hud'u, sannan tace:

"Ga kala d'aya nan asaka mata"

Dada tace :

"Yafi maki dai kam, kiyi don Allah koda zaki samu lada"

Iya kulu ta fita tana takaicin rashin siyen kayan da Dada batayi ba, acikin zuciyarta tace;

"Malam ne zai biya ai, don ni ba mai cin kayana abanza, sai dai in wuta bal bal ce za'aci, inaji ina gani ga kud'i dami guda, abani hak'k'i na ankasa saboda kawai inyi magana, asani abakin duniya, to wallahi dole ne abiyani kud'in kaya na, dari ta uku bazata tafi a iska ba, dank'ari bazata sab'u ba don kuwa yasin zasu saiman dussar kwana biyar in baiwa akuyoyi na"

Idanunta arufe saboda b'acin rai, ba zato kawai taji tayi karo da malam, da sauri ta fara borin kunyar cewa:

"Ai kayan zasuyi mata kyau gaskiya, ni ko d'ari biyu ma aka bada ba komi"

Oh ni dije🤔

Akafta👍🏻

D/Auta ce👌🏻

بسم الله الر حمن الر حيم.

*___________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA🌧*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The notion}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*________________________________*
*BARKA DA SALLAH MY FAN'S ALLAH YA MAIMAITA MUNA*

*PAGE SIX*

*********************

Malam ya kalleta da kyau, saboda yasan iya kulu ciki da bayan ta, batareda ya bi kan maganar ta ba yace:

"Ina su Garzali ne?"

Iya tayi saurin saita natsuwarta tace:

"Shi yana wajen Dada, Abu ko yana d'aki, ai tunda aka fara ruwan sama ya fara bacci har yanzu bai tashi ba"

Malam ya fara tafiya yace:

"Ki tadashi dai kinsan ba kyau baccin marece"

Iya kulu tana tsaye har sai da taga shigewar sa ad'akin Dada, hannun ta agaba sannan ta sauke k'atotuwar ajiyar zuciya tace:

"Wai Allah ya soni baiji ba, da na jawo wa kaina jangwam"

*SHIN WAI SU WANENE WADANNAN AHALI?*

Malam Abdulkadir jelani mai almajirai, shine ainahin sunan Baban malam Ayuba, mijin mairo wadda kuka fi sani da suna Dada, wanda mutane suke kiranshi da sunan malam jelani, kasancewar shi babban malami, wanda yayi suna acikin garinsu da kewayen shi, saboda almajirai da ake kawo masa yana karantar dasu.

Yayi hidima sosai ga addini alokacin rayuwar shi, wanda har manyan dattijai na garin duk yana basu karatu acikin gidanshi, wanda har izuwa yanzu wannan tarihi bai goge ba acikin zuciya da idanun mutanen garin, saboda ahalin yanzu malam Ayuba shima malami ne masani akan harkar addini, don dattawan garin masu ra'ayin neman sani akan karatun su, to awajenshi ne suke d'aukar karatu, asati sau  biyu ne sukeyin zaman .

Malam jelani matarshi d'aya ce ta aure wato mairo, yana da 'ya 'ya biyu rak da Allah ya albarkace shi dasu, wato Malam Ayuba da hurere, wadda ake yiwa lak'abi da suna hure, wad'anda su kad'ai ne suka rayu amatsayin 'ya'yansu, saboda matsalar da Mairo (Dada)take ta samu awurin haihuwa, da ta samu ciki ya lalace.

Wanda alokacin aka canfa aljanu ne suke shanye abun d'an cikin cikin, saboda yanda malam jelani har maganin aljannu yana badawa, shiyasa mutane suka canfa hakan, ganin  da ta sami cikin sai yak'i tsayawa, ak'arshe ma haihuwar ta d'auke d'if aka barsu tareda yaransu biyu Ayuba da hure.

Ayuba yayi aure da iya kulu wadda ake kira da suna 'yar kuluwa, alokacin ganiyar budurcinta, suma Allah ya albarkace su da yara biyu Garzali da Abubakar, sai izzatu da suka haifa wata hud'u  ta rasu, tun daga kansu har zuwa yanzu tsit,  ko b'atan wata.

Hurere kuwa itama tayi aure da yaranta hud'u biyu maza biyu mata, don ko yanzu cikine da ita yau ko gobe,  inna hure kenan itama kunji labarinta.

*DANGANTAKAR DADA DA IYA KULU*

Dada da mahaifiyar iya kulu uwa d'aya uba d'aya suke, wadda ake kira da suna halima amman ana yimata lak'abi da sunan ('yar dubu).

Yar dubu ta rasu wajen haihuwar 'yar kuluwa, ta barta tana jaririya ahannun Dada, itace ta rik'eta har zuwa girmanta, saboda kiriniyar 'yar kuluwa da mugun son kud'inta,  yasa Dada tashin hankali ba kad'an ba, alokacin da girma ya fara zo mata samari sukayo mata caaa, amma ita kam ba wanda yayi mata acikin su, don ita ayuwarta, tafi son ta auri mai kud'i, shiyasa gaba d'aya samarin k'auyen nasu ta rena su.

 Saboda ganin k'awarta da suka taso atare, wani alhaji abirni yazo ya aureta, shiyasa ta k'wallafa ranta akan bata auren kowa sai mai kud'i, itama ta fantama yanda k'awarta takeyi, musamman in tazo k'auyen ankawota da mota, suje suyita shafa motar suna k'auyanci, tayita rok'on k'awar tata akan ta nemo mata miji d'an birni itama tayi aurenta acen itada k'auyen sai dai idan zata wuce ta hango shi,  aiko suka kitse magana atsakanin su, batared sanin kowa ba 'yar kuluwa tabi k'awarta abirni cen inda take aure.

Hankalin su Dada ya tashi, gari ya d'auka kulu ta b'ace, sai cen aka ji labarin tabi k'awarta abirni, jiki yana rawa iya tasa aka kaita har cen gidan na k'awar tata, ta taso k'eyar ta suka dawo

k'auyen su, bayan tasha duka ba na wasa ba ahannun Dada, saboda takaicin hakan yasa ta nemi alfarma awurin  dangin baban ita kulun.

  Akan tana son ad'aurawa Ayuba aure da ita kulun, saboda tana jin tsoron abunda zaije ya dawo,na aibi ga rayuwar kulu, domin yanda tasawa zuciyar ta k'aunar kud'i, zaiyi wuya idan ta k'ara girma ashawo kan matsalar,  alokacin ko bacci takeyi, mafarkin kud'i takeyi.

Ba tareda sanin Ayubaba bale kulu aka d'aura auren su, da yake shi ayuba mutum ne wanda yasan darajar iyaye ko afuska bai nuna yaji haushin auren ba, duk da ba ita yaso ya aura ba, amman yayi biyayya ya rungumi 'yar  uwarshi kulu sukayi ta zaman auren su,  duk da botsare botsaren da kulun ke yimasa, bai fasa kyautata mata ba, har izuwa yanzu lokacin da suka hayayyafa, iya kulu bata saduda  da son kud'in ba, har saima abunda yaci gaba.

*To kunji tarihin su sai adawo gundarin labarin 🏃🏻‍♀️wanda shine mak'asudin wannan littafi mai suna RUWA DA KANKARA*

Ci gaban labari

Malam ganin yanda Dada ta shirya izzatu tsaf tareda maida mata da sock's d'inta da hularta da aka tsinto ta dasu.

Farin ciki kwance akan fuskar malam yace:

"Rik'o man 'yata garzali, kabi ka kanainayeta, kamar wanda za'a k'wacewa ita"

Garzali yana murmushi ya taso ya mik'awa Abba y'ar, sannan yace:

"Da ka ganta ni zaka maida wa ita ko?, ba dada ba"

Malam yayi murnushi yace:

"Hannun amsa ai hannun mayarwa"

Dada tayi dariya tace :

"Dani kake zancen yaro, bayan ka mance da marairecewar da kayi ne a yanzu,  akan in baka ita nak'i, to gobe ko zan baka ita yaro kasani sai in kana da nera goma"

Garzali yayi saurin saka hannu ya karb'e izzatu a hannun malam yana dariya yace:

"Allah ya soni na d'auketa har da na goben, kinga goma ta sai ta huta"

A haka sukayi ta barkwancin su Garzali da Dada, suyi fad'a sudawo su shirya, malam dai

iyakacin shi murmushi idan sunyi abun dariya, har zuwa lokacin da iya kulu ta k'are abinci, anan ta kawo masu suka baje sukaci abincin su.

Hadari ya k'ara had'uwa aka yita malala ruwan k'ank'ara gundum gundum gwanin ban firgici, domin kuwa atarihi kaf basu tab'a ganin irin wannan al'ajabi ba, su malam suka rud'e sai zuba addu'o'i sukeyi, garzali da Abu kam kuka reras suka sha,  saboda tsoro, ita kanta iya kulun,  sai da tazamo tamkar wata sabuwar balaraba saboda salati da hailalar da takeyi.

Sai kace ba itace mayyar kudin nan ba😹🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️

Taku ce

D/Auta👌🏼
*💦RUWA DA KANKARA🌨️*

*NA HADIZA D/AUTA*

بسم الله الرحمن الر حيم

*_______________________________________*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*_________________________________________*

*PAGE SEVEN*

********************

Itama kanta jaririya izzatu sai kuka takeyi, Dada tana ta lallashinta tana kiran:

"Tsarki ya tabbata ga ubangijinmu,  wanda yake sauko muna wad'annan RUWA DA KANKARA, lalle ke 'yar baiwa ce, samunki alkhairi ne awurinmu, Allah ya bamu ikon rik'on ki da gaskiya"
Su malam sukace: "ameen"

Haka dai akayita ruwan k'ank'arar guma guma, anraba dare ana ruwan sannan ahankali suka fara ragewa har suka tsaya cak, zuwa lokacin iya kulu da su Garzali har sunyi bacci, amma Dada da malam suna tsaye kai da fata sunata addu'o'i tareda jinjina girman wannan iko na Ubangiji,.

Bayan komi ya lafa Dada tace da malam "suje d'akunansu su kwanta, saboda gobe zasuyi sammakon zuwa birni domin sukai izzatu asibiti domin aduba lafiyarta"

Haka ko akayi Malam ya tada iya kulu suka ja yaransu suka fita tareda yiwa junansu sai da safe.

Bayan fitarsu Dada ta sauke izzatu ta lallab'a ta kwantar da ita, tareda tofeta da addu'o'i, sannan ta rab'a agefenta ta d'an gincira, aiko ba shiri bacci mai nauyi ya d'auketa.

Asubar farin izzatu ta tada Dada daga barcinta mai dad'i da takeyi, ta hanyar kwantsama kukan da tayi tayi, dole Dada ta farka ba shiri.

Da dubara ta samu tayi sallah, sannan ta
dawo hidimarta, akayi dai dai malam ya shigo domin ganin meke faruwa, saboda yaji kukan izzatu,haka kawai yakejin son yarinyar tamkar shine ya haifeta, da sallamarshi ya shigo idonshi akan izzatu yana yiwa Dada barka da safiya.

Bayan sun gaisa ne Dada tace dashi:

"atatso nono aba  izzatu tasha saboda yunwa ce ta tada ita daga bacci"

Malam jikin shi yana rawa ya fito, bai ko bi takan iya kulu ba yaje ya tatso nonon da zafinshi yakai aka bata, sai da tasha ta koshi sannan ta koma bacci, hankalinsu ya kwanta.

Malam yana shirin fitowa d'akin ya had'u da iya kulu ta  fito tana kiciniyar had'a wuta, domin ta aza ruwan zafin da za'a yiwa izzatu wanka, malam yace da ita:

"Na tatso nono anbaiwa izzatu tasha"

Iya kulu tayi saurin d'agowa daga hurin wutar da takeyi da bakinta tace:

"To ai kuma ba'a bada kud'in ba ko anbiyo ne?"

Malam ya kalleta sororo sannan yace:

"Na jiya da na baki asusu nace ki saka su halan?, yanzu ke don Allah tun da sassafe zaki saka mutane d'aga jijiyoyin wuya, to daga yau ma ta daina shan nonon sai ki dinga kasa shi a kasuwa kina saidawa idan kinso, amma nikam babu ni aciki"

Yana k'are maganar ya wuce abinshi zai shige d'akinsa, iya kulu ta bishi da kallo tareda murgud'a baki ta fara gungunin cewa:

"Mutum da abunsa bazaiyi tambaya ba?, waya saya mun akuyoyin?, ai da kud'in adashe na ne da nikeyi na sayi kayana, don haka bazan tab'a lamunta aci da hak'k'ina ba, ko don kai ke bani kud'in zubin adashen,  shiyasa zakayiman gadara, to ai kyauta ka bani ba ranko aciki"

Bayan ta k'are 'yan surutanta sannan tayi saurin biyar shi abaya tana bashi hak'uri, saboda ta fahimci ransa ya b'aci akan hakan, baija zancen da tsauri ba yace da ita: "taje bakomi".

Sannan ta fito ta nufi d'akin Dada domin ta dubo ya suka kwana.

Bayan sun gaisa ne taje ta juye ruwan zafin ta kawo akayiwa izzatu wanka, sannan Dada ta shafeta da man kad'e tas sai k'yalli takeyi, ta k'ara shiryata ta goyeta.

Saiga Garzali ya shigo kamar an jefoshi, yana mutsu mutsun idanuwa, sai rabasu yakeyi domin ya hango izzatu, amman bai ganta ba, acikin tashin hankali yace :

"Dada ina izzatu yanzu shikenan ank'waceta ta tafiyarta bazamu sake ganin ta ba?"

Acikin mamaki Dada da iya kulu suka bishi da kallo, ganin yanayin kallon da suke yimasa yasa ya gasgata mafalkin shi ya fara kuka yana sanbatun cewa:
"Yanzu shikenan sun karb'eta don mugunta"

Da dai Dada ta fahimci inda ya dosa, tayi saurin cire lullub'in zanenta da ta rufa wanda shi ya hana shi yaganta a goye, aiko yana ganinta kafin Dada tace wani abu yayi saurin washe bakin shi yace:

"Laa ashe basu tafi da itan ba"

Dada da iya kulu suka tuntsure da dariya, Abu dake bayanshi, saboda ya biyoshi yaji me ya firgitashi acikin  bacci, jin abunda yake fad'a ayanzu shiyasa yaji haushin sa,  don shi sam yarinyar batayi masa ba,  ba shiri ya buga tsaki yabar d'akin, Dada ta gallawa k'ofar da ya fita harara tace:

"Kai kam duk wanda yaga girmanka sai yaga fad'in rai, bak'in hali k'arara tun kana d'an k'aramin ka to ina ya ka girma?, Allah dai ya shiryeka amman kam akwai aiki"

Iya kulu ta b'ata fuska tace:

"Zai daina ne ai"

Dada ta kalleta tareda yimata wani kallon reni tace:

"Daman aike baki so aga laifin d'anki, kuma dole ne a nuna masa kuskurensa ko don gobe ya gyara, don in har aka barshi da tarbiyar ki,  kece zaki kwana aciki inya girma,  donmu alokacin ma bamu araye bale muga kayan takaici"

Iya kulu ta zunb'uro baki ta fitowarta, Dada tace:

"Ai komi da Abu yakeyi gado yayi awurinki, bai yar ak'as ba, don haka daga ke har shi Ubangiji Allah ya shirye ku"

Bayan sun karya ne suka fara shirin zuwa gidan mai unguwa domin ahad'a su wad'anda zasuyi masu jagora zuwa  birnin, aiko daga zuwan su ba wani tsaiko daman su kawai ake jira suka lula sai asibitin birni.

Bayan duk wasu gwaje gwaje da akayiwa izzatu an tabbatar batada matsalar komi, amman sun rubuto mata magungunan da za'a rik'a bata tanasha, masu inganta jiki, sannan an fad'a masu madarar da zasu dinga bata wacce take d'auke da wasu sinadaran da nono yake d'auke dashi.

Malam ya nemi alfarmar wata nurse da ta rakashi yaje yayi ma izzatu siyayyar abubuwan da zata buk'ata, aiko ba musu ta d'auki excuse suka  garzaya sai wani babban shago, nurse d'innan ta zage damtse tayita lodowa izzatu kaya, tun daga b'angaren sutura da pampas, da madara hatta kayan wasa idan ta k'ara girma duk saida ta d'auko, malam dai iyakacin shi ido, duk da yana da 'yar wayewarsh dai dai gwargwado,  amman kam wasu kayan ko ganinsu bai tab'a yi ba balle yasan me akeyi dasu.

Bayan sun gama siyayyar ne, nurse d'in tayi masa bayanin duk wani abu da ya shige masa a duhu, malam yaji dad'i sosai yayi mata godiya, sannan suka dawo inda su Dada suke jiransu, ganin uwar siyayya ledaodi manya manya ya saka Dada tambayar malam akan cewa "duk me ya siyo har haka?".

Malam yace: "Ta jira idan sunje gida zai yimata bayani"

Nurse d'innan tayi masu sallama zata tafi, Dada tace da ita:

"Dawo 'yar nan, kigayamuna sunanki, ko don mu k'ara yimaki godiyar irin wannan hidima hk"

Ta dawo tana murmushi tace:

"Suna na Aisha"

Dada tayi murmushi ta fara yiwa nurse Aisha wak'a tace:

"Sannunki shatu shatulle,   indo A'i farar d'iya, baki aure k'auye kisha wuya, daga birni sai babban gari, sai ko wani babban malami,  koko wani babban attajiri"

Indo an wasu🤣🤣🤣

Akafta😜

D/Auta ce👌🏻

بسم الله الرحمن الر حيم

*____________________________________*

*⛈RUWA DA KANKARA💦*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp

*______________________________________*

*PAGE EIGHT*

********************

Aiko BA shiri nurse Aisha ta washe baki har kunne, saboda taji dad'in wak'ar da Dada tayi mata, aiko ta samu wuri ta zauna sai fira ta b'alle atsakaninta da Dada,har zuwa lokacin da izzatu ta fara kukan neman abinci, Dada ta kalli Aisha tace:

"Na shigesu ni mairo, ko ina zan sami nonon akuya inbaiwa wannan yarinya?"

Aisha ta zaro ido awaje tace:

"Nonon meye?"

Dada acikin tabbatarw tace da ita:

"Nonon Akuyoyi"

Aisha tayi murmushi tace:

"Jirani minti biyu inzo"

Aiko saigata ta dawo da Flack's na ruwan zafi da cup da spoon  ta ajiye agaban Dada,  sannan ta bud'a ledodin siyayyar ta fiddo da gwangwanin madara d'aya don guda uku aka siye, saboda tazarar dake tsakanin k'auyen SU da garin.

Sannan ta fiddo fida babba taje ta wanko ta tas, sannan ta zuba madarar akofi ta tsiyaya ruwan zafi dai dai madarar ta jujjuya,har saida ta hade gaba d'aya, sannan ta juye madarar afida ta rufe.

Dada dai da sauran wad'anda ke wurin, sai binta da kallo sukeyi, acikin mamaki dada tace:

"Yanzu shikenan za'a iya bata tasha ahaka ba sai in dafa awuta ba?"

Aisha tayi 'yar dariya tace:

"Haka akeyi akullum idan za'a bata yanzu ad'an jira ta rage zafi sai abata"

Aiko farin ciki ya wadatu afuskokin su gaba d'aya, musamman Dada da malam da suka if kowa shiga damuwa akan kukan da izzatun takeyi, suna tunanin yanda zasuyi, saiga mafita asauk'ak'e Allah ya kawo masu.

Aiko saboda kukan da izzatun takeyi, Aishar ta d'ebo ruwan sanyi akofi ta jefa fidar madarar

tana juyawa, minti k'alilan madarar ta huce aka bata sai zuk'a takeyi, kamar ta saba sha, kafin kace me har ta shanye fidar gaba d'aya, sannan tayi gyatsa sai bacci.

dukansu sunyi mamakin madarar da tasha, shiyasa aka sake kad'a mata wata madarar, koda zata falko kafin suje gida.

Sukayiwa Aishar godiya sosai sannan suka mik'e zasu koma k'auyen su, anan ne Aishar take tambayar a'ina suke, dada tayi mata bayanin sunan k'auyen da suke zaune, nurse Aisha tayi mata alk'awali duk lokacin da ta sami dama zataje har k'auyen ta dubo izzatu, saboda yarinyar ta shiga ranta sosai ta burgeta.

Dada taji dad'i sosai tayi ta yimata adduar gamawa lafiya,aiko da ita Aishar aka sakawa su Dada kayan su amota, daga nan sukayi sallama, akan sai watarana, suka rabu acikin kewar juna.

Tafiyar da bata gaza minti arba'in ba itace ta kawo su d'an k'aramin k'auyen su, kai tsaye aka wuce dasu Dada har gidan mai unguwa, bayan sun k'are yimasa bayani abunda ya wakana acen asibiti, suka nuna masa siyayyar da akayowa izzatu, ya jinjina masu sosai tareda saka albarka acikin duk wani nufi nasu na alkhairi akan jinjira marainiyar Allah izzatu.

Bayan sun k'are ne mai unguwa ya saka aka jidi kayan nik'i nik'i aka kai masu gida tun kafin su K'arasa agidan.

Suna shiga suka iske Iya kulu tayi fillah fillah da kayan ak'ofar d'akinta sai kallo takeyi, inta duba wannan at ajiye ta d'auko wani har takai kan gwangwayen madarar da aka siyowa izzatu, ta d'aga gwangwanin tana kallo sai jujjuyashi takeyi, saboda tana son ta k'ara tantance shin miye aciki, ta girgiza taji k'arar garin madarar dake aciki yana sukuf sukuf, batareda tunanin komi ba ta saka hannu ta b'alle murfin, saiga wannan 'yar silbar takarda dake rufe da bakin gwangwanin.

Ba shiri ta b'urmama farcen ta atsakiya aiko sutuf ya fad'a kasancewar akaifarta da take da itace tayi saurin walshe takardar, aiko bata tsaya wata wata ba ta yage takardar gaba d'aya ta jefar, ta saka hannu ta kwaso madarar ta kai abaki zata afka saiga sallamar Dada da Malam sun shigo, aiko ba shiri ta guma madarar, sannan ta jawo murfin gwangwanin ta rufe tana k'ok'arin maida kayan acikin ledodin.

Baki asake Dada ta bi iya kulu da kallo, saboda gaskiyar ma taxi mata yawa, malam kam k'arasowa yayi ya dinga tama ta suna maida kayan, Dada saboda haushi kasa magana tayi ta shigewarta d'akinta.

Malam yana ganin shigewar Dada, iya kulu ta kawo hannu zata d'auki wani tissue ta mayar leda, da sauri ya bangaje ta, ba shiri ta fad'i ak'asa warwas, aiko madarar dake bakinta ta dunk'ule mata mak'oshi ta sark'e, ta fara tari ido suka gwalalo awaje sai nuni takeyi da hannu akan ya taimaka mata da ruwa.

Malam kam yana k'are maida kayan, ya nufi d'akin Dada yabarta anan tana neman agajin abata ruwa, ya fahimceta kar amma yayi banza da ita ya tafiyarsh, acikin zuciyarshi yana cewa:

"Indai hak'k'i ne to kad'an kika gani"

Da rarrafe taje wurin tukunyar ruwanta, ta kandamo tayi masu muguwar zuk'a aiko saigata da k'walla k'ara tace:

"Wayyo wuyana!"

Saboda yanda ta had'a ruwan sukayi muk'ut suka fad'a da k'arfi tareda dunk'ululun madarar da ya tsaya mata amak'oshi, saiga su Garzali sun dawo inda ta aikesu.

Da sauri Garzali ya k'araso idonshi akanta yace:

"Iya lafiya idanunki sukayi ja haka?"

Iya kulu ta had'iye miyau tace:

"Bari kaidai d'an nan,  kwad'ayi da dad'i amman akwai wahala idan rana ta b'ace aka rutsa da mutum"

Sai jin muryar Dada tayi tana fad'in cewa:

 "Ai dama ance duk wanda ya hau motar kwad'ayi,  to ba inda zata saukeshi sai tashar wulak'anci, duniya dai ce ta ishi kowa riga da wando, wanda bai zo bama jiranshi takeyi"

Iya kulu tayi sum sum ta fad'a d'akinta, saboda ita kanta bata ji dad'in riskarta da akayi ba, amman dai kam taji dad'in madarar ba kad'an ba, shiyasa afili ta furta cewa:

"Anji kunya ansha dad'i"

Tofa😹😹

Akafta😝

D/Auta ce 👌🏼

[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*______________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA🌧️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*________________________________________*

*PAGE NINE*

*********************

Dada ta k'walla mata kira, sai ga iya kulu ta fito jiki ba kuzari, don tasan yau kam ta jawo wa kanta jangwam, Dada ta galla mata harara tace:

"Duk da kinga kayan tun kafin a nuna maki, amman kizo ki k'ara gani saboda bayanin da ayuba yake yimani akan yanda za'ayi amfani da kayan ne ya rikice ni, nace bari in kiraki kizo kiji kema don k'ila ke kifini ganewa, don nikam ba duka na fahimta ba"

Garzali yana k'yalla ido yaga Dada, aiko sai gashi da jin wani farin ciki ya mamaye sa bakinshi yana rawa yace:

"Laa ashe kun dawo Dada?, ina izzatun?"

Dada tayi masa nuni da hannunta, sannan tafara tafiya domin ta koma d'akinta, wanda kafin ta isa har Garzali ya rigata kaiwa a d'akin.

Iya kulu tana biye dasu a baya ranta fess, don atsamaninta Dada ta mance da abunda ta aikata.

Tana shiga ganin izzatu ahannun malam yana bata madara,  ga Garzali da ya kasa ya tsare yana rik'e da hannunta, yana kallon yanda take zuk'ar madara a lokaci d'aya  taji wani b'acin rai ya ziyarceta,  batasan lokacin da tayi tsaki azuci ba, saboda jin takaicin wannan rawar k'afar da sukeyi da jaririyar,  sai kace malam shine yayi silar kawota a duniyar.

Dada ta dinga nuna mata, malam sai bayani yakeyi dallah dallah kamar yanda nurse Aisha tayi masa bayani, iya kulu sai gyad'a kai takeyi, tamkar wata k'adangaruwa.

Bayan malam ya k'are bayanin ne iya kulu ta kalli tulin kayan ta kalli izzatu, sannan tace:

"Yanzu duk wad'annan tulin kayan na wannan jinjirar yarinyar ne?"

Dada ta harare ta sannan  tace:

"To ai kud'in ta ne ba ko k'wandalar mu aciki, saboda haka idan kina da kud'in kema ki kawo, sai gobe aje ayo maki siyayyar da tafi ta jinjirar"

Iya kulu tab'ata fuska tace :

"To ai abun bai kai cen ba,  ki gafarceni"

Dada tace:

"Madarar fa itama bazaki siye irinta ba?, ki dinga cika hannu kina afkawa abaki, tunda nasan kinji dad'in ta"

Aiko iya kulu sai ido suka rena fata, don tasan Dada tsaf da bugun gorar ta, shiyasa ta fita d'akin salun alun batared ta koma cewa k'anzil ba.

Amman fa abun nasu ya fara b'ata mata rai gaskiya,  saiga sallamar kande mak'ociyar ta, ta karad'e gidan gaba d'aya,  saboda kande mace ce mai d'aga murya idan zatayi magana, batasan ta sassafta halshenta ba yayin magana, duk inda take muryarta ce zata sanar da zuwanta.

Tana zuwa tayiwa kanta mazauni,  ta hanyar janyo kujera 'yar tsugunno ta zauna,  idanunta akan iya kulu acikin mamakin ganin yanayinta tace:

"Kefa lafiya?, ko keda Dadar taki ne, yau ma kuka hau sama?"

Iya kulu tayi mere tace:

"Ke ko wata tsintacciyar mage ce aka tsinto aka kawo muna acikin gida"

Kande ta dafe baki tace:

"Ashe dai zancen da nakeji yana ta yamad'd'i agari gaskiya ne?"

Iya kulu tayi mata wani kallo tace:

"To yanzu kinji dimun ai jiya aka tsinto ta anata zuba ruwa da k'ank'ara, yanzu haka an saka mata sunan izzatuna"

Kande tace:

"Lalle wagga 'ya ta zama 'yar gaban goshin, a'i da anbarta da sunan ta na yanka RUWA DA KANKARA,  don shine yafi dacewa da d'iyan shegun da ake haifa ana yardawa"

Iya kulu ta zaro ido awaje tace:

"Rufawa kanki asiri kar Dada ta jiyoki, ance fa ba shegiya bace da ubanta"

Acikin mamaki kande tace:

"To ku taya kukasan ba shegiya bace ba?, to kenan kunsan iyayenta ko?"

Iya kulu tace:

"Acikin takardar da aka tsince ta atare da ita ne aka rubuta,  cewa ba shegiyabace"

Kande ta mere baki tace:

"Kuma ku har kun amince?, cab da sauran ku wallahi, yanzu harda shi malam yanzu ya gasgata wannan shirmen?, to bari kiji koda shegiyar ce da gaske baza'a fad'a arubuce ace itace ba, don idan ba hakan ba me zaisa a jefar da ita haka kawai?"

Iya kulu tayi tagumi, tareda zurfafawa azurfin tunani, musamman da ta tuno da kud'in da aka sako acikin kwalin, aiko anan take zuciyar ta ta gasgata zancen kande, wani sabon b'acin rai ya ziyarceta, fuska ahad'e tace:

"Indai da gaske  shegiyar ce, to wallahi ban yafewa hidimta mata da nayi ba, kuma da sannu sai nayi sanadin da zata bar gidan nan, tunda ba da kud'in ubanta ne aka ginashi ba"

Kwatsam sukaji maganar Dada asaman kansu tana cewa:

Inajin ai kema da kike zaune agidan bada kud'in naki uban aka ginashi ba, balle kiyi ik'irarin fitar da wata a gidan"

Ta juyo da kallonta ga kande mai cike da takaicin Allah ya wadaran naka ya lalace tace:

"Ke kuma kande wallahi kiji tsoron Allah ki tuba agareshi, akan k'ulle k'ullen munafuccin da kike bi gida gida kinayi, saboda kin bar baya gaba ake wa gudu a turke ki acikin d'iyanki kiji kunya, sannan zancen ki kira wata shegiya bai taso ba ma, saboda shi shegen ai a tsakanin ma'aurata ake samunshi ko kin manta in tuna maki?"

"Sum sum Kande taja k'afafunta tabar gidan talkaminta a hannu"

Saboda tasan halin Dada yanzu ne zata bayyana mata yanda akayi aka haife uwarta ma balle ita, saboda ita kande kullum acikin danbacewa sukeyi da mijinta, sannan akullum furta kalmar saki abakin shi ba wani abu bane, sai dai in basuyi fad'a ba, don wannan sananne ne duk lokacin da sukayi fad'a mak'ota sai sun gaji da jin kalmar ya saketa, amman da sun shirya sai aci gaba da auren ayita hayayyafa.

Har saida 'yan unguwa suka kai k'arar zaman auren su a wurin mai unguwa, bayan an natsu kowa yayi bayani sai aka gano ba aure atsakanin su, saboda yaran da take dasu da yawa sai akace ya barta tayi zaman yaranta, amma kwatsam sai ga wani ciki ya b'ulla a jikinta, abunda ya zama cecekuce ak'auyen, aka fito za'ayi masu ature, dak'yar aka samu rigimar ta lafa, adalilin yarinyar cewar da tayi cikin kwanci ne, ya dad'e ajikinta sai alokacin ya tashi acewarta fa.

Dada ta dawo da kallonta ga Iya kulu tace :

"Ke kuma sakarya da bakida hankali, sai Ki tsaya biye kande, tana shirya maki tuggun da zai rufta dake "

Iya kulu ta fara gungunin cewa :

"Ai gaskiya ce ra fad'a idan har da gaske ba shegiya bace, wane daliline zai saka iyayenta su jefar da ita, ai don suna gudun aga abun kunyar da suka aikata ne"

Tana dire zancen ta ta fisgi buta ta fad'a bayi, Dada ta bita da kallo acikin k'unar zuciya tace:

"Ke kam 'yar kuluwa da ana canza hali da na canza maki naki, kidon kiji dad'in zaman duniyar da kowa saboda inhar mune yau, tofa ba mu bane gobe, akwai rai akwai mutuwa, wadda komi sonka da k'aunar duniya dolene sai a barta, fatanmu kawai ubangiji ya yafe muna kurakuranmu"

Malam dake fitowa yace "Ameen"

Dada ta share k'wallar da ta zubo mata akan fuska ssboda tausayin  rayuka biyu, bak'in halin ' Iya kulu, da rayuwar da izzatu zata tsinci kanta aciki anan gaba, idan har ba'a samu iyayenta ba.

Malam yana hango baba tana kuka, ranshi inya kai million to duk sun b'ace, duk da tsananin hak'uri irin nasa, 'yar kuluwa tana fitowa daga bayin ba'a tantance ba sai jin k'arar mari sukaji har sau biyu, iya kulu ta dafe kumatun ta da suka sha marora, tareda kwantsama kuwa, acikin fushi malam yace:

"Muddin kika sake yin abunda ya saka uwata kuka, to wallahi sai na  cire maki hak'oran gaba"

Dada ba shiri ta k'araso akusa dasu tace:

"K'yaleta ayuba ai itama ta haifa, indai duniya ce tafi iccen bagaruwa jima, adai juri zuwa rafi watarana tulun zai fashe, aure dai ne ko bayan raina ban yarda ka ace ka saketa ba, ka barta taci gaba da cin albarkacin zumunta, ko don darajar zumunci"

Ahaka dai ranar gidan dukansu suka kwana, a tsakanin su ukun kowane da abunda suke sak'awa acikin zuciyoyin su,yayin da  iya kulu k'iyayyar izzatu tay mata tsaye a k'ahon  zuciya, wanda taci alwashin ita ko izzatu d'aya ne zai zauna a gidan don bazata so ta k'ara k'yalla ido ta hango ta ba, duk ta hanyar da zata bi sai taga izzatu tabar gidan ko don kwanciyar hankali agidan, tunda gashi ba'aje ko ina ba ta fara zamar mata matsala.

Allah sarki izzatunmu😢

😔😔😔Bance akafta ba

D/Auta ce
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*___________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA🌧*

*NA HADIZA D/AUTA*

*PAGE TEN*

*********************

Koda safiya ta waye Dada bata jira iya kulu ta aza ruwan zafin wankan izzatu ba, tana k'are sallahr asuba taje ta d'ora ruwan zafin, sai da suka tafasa sannan ta fara cika flack's da ruwan ta kai ta ajiye, saboda yawan shan madarar da izzatu take yi akai akai, ta dama mata wata madarar sannan ta jefa a cikin ruwan sanyi domin tayi saurin rage zafi, sannan taje ta d'ebo ruwan zafin tayi mata wankanta, tareda yimata gashin cibiya, tasha madarar ta k'oshi sannan ta koma baccinta.

Har ta k'are 'yan guntayen ayukanta na yau da kullum, da takeyi ta koma tana lazuminta, amman iya kulu bata zo yiwa Dada ina kwana ba, duk da rashin ganin ta ya damar da Dada sosai, amman ta share taci gaba da lazuminta hankali akwance.

Malam da Garzali sun dawo masallaci, suka zarce d'akin Dada domin suji ya suka tashi, bayan sunyiwa juna ina kwana ne Malam yake baiwa Dada hak'uri akan abunda ya faru jiya, Dada tace:

"Ba komi ai komi ya wuce fatanmu kawai Allah ya fahimtar da ita ta gano gaskiya"

Garzali ya nufi inda izzatu take kwance zai d'aukota, Malam yayi masa kashedi akan kar yaje ya tada ita daga bacci, ya barta har sai ta tashi da kanta, sannan yaje ya d'auketan, Garzali ya b'ata fuska ya koma gefe ya rakub'e, Dada ta kalleshi tayi murmushi tace:

"Daina fushi mutumina indai izzatu ce, taka ce na baka ita kyauta, don nasan ko bayan raina, kaine wanda zaka tsaya kai da fata akan rayuwar ta, saboda shi ayuba ba kullum ne zai dinga kasancewa agidan ba,don haka ba komi ne zai sani na abunda ke faruwa agidan ba, amman kai jikina yana bani inhar dakai to izzatu ba zatayi maraici ba"

Dada ta share hawayenta, Malam jikinshi yayi sanyi, wata damuwa ta mamaye zuciyar shi, acikin sanyin murya yace:

"Insha Allahu bazaki mutu ba har sai kinga girman uzzatu, kin auradda ita da hannun ki, matuk'ar ba iyayenta suka bayyana ba suka karb'i abussu"

Dada tayi murmushi tace:

"Zanso hakan ta kasance ayuba, amma kasan da cewa ba komi ne kake so ba, kuma har ka samu ya tabbataba, musamman ita mutuwa saboda rashin tabbas d'inta akeso akoda yaushe kayita tunata kana ambatonta, don gudun shagala, saboda tana kusa damu a kowane taku da mukeyi tana biye damu abayanmu, lokaci kawai take jira kamar walk'iya haka zata rik'e ka gam, shikenan sai ashafe babin mutum acikin doron k'asa, shiyasa akeson kayita ganin tamkar yanzu ne zaka mutu ba sai anjima ba, saboda rashin tabbas irin nata"

Ba malam ba har Garzali dake sauraren su, sai da jikin shi yayi sanyi, don shi malam jikinshi ya mutu murus, saboda yana jin tsoron kada ace, Dada wasiyya ce take bar masu, murya asark'e Malam yace:,

"Hakane Dada amman kinji ance, ka nemi duniya kamar bazaka barta ba, haka ma ka nemi lafira itama tamkar yanzu ne zaka barinta, fatanmu kawai Allah ya bamu rai da lafiya, kuma yasa mu cika da imani, idan lokacinmu yazo"

Garzali ya taso yazo ya lafe ajikin Dada ya lafe, Dada ta shafa kanshi tace:

"Allah yayi maka albarka, ya dafa maka acikin lamurranka na yau da kullum, ubangiji ya d'auka ke ka,  ya kareka da sharrin mutum da aljan"

Tana fad'a sunata amsawa da : "Ameen "

Malam jiki asanyaye yayiwa Dada sai anjima,  sannan ya fita yaje ya shirya kafin lokacin fitar sa yayi,  saboda akwai kasuwar da yakeso yaje yaci aranar.

Garzali ya k'urawa izzatu dake ta baccinta hankali akwance idanuwa, wanda ko k'iftasu baya so yayi, saboda kawai baya so ya d'auke kallon shi daga kanta, Dada tana kalle da shi, tayi murmushi acikin zuciyar tayi ta sak'awa abubuwa da yawa, wanda take hange da wuya hakan ta kasance idan ba tsananin rabo ne ya gitta ba, ba shiri ta sauke ajiyar zuciya tace dashi:

"Tashi kaje ka d'auko muna furar cen kazo musha, ko kai baka fara jin yunwar ba ne?"

Garzali ya tashi ba musu yaje ya d'auko furar,  suka fara sha a cikin hikima ta fara ta bashi labarai na ban tausayi, da jarumta,ak'arshe ta bashi na ban dariya, anan sukayi ta firar su suna dariya, har lokacin da uzzatu ta falka daga bacci.

Iya kulu kam tana d'akinta ta k'ule, sai cin faman cin magani takeyi, ita ala dole anb'ata mata,

shiyasa yau ko zazafen tuwon da zatayi kowa yaci akarya kasa azawa tayi, bak'in halinta sai nuk'urk'usar ta yakeyi, ta sak'a ta kwance, shi kawai take tayi, har sai da malam ya dawo daga d'akin Dada sannan ta mik'e zata fito, aciki ciki tayi masa ina kwana, shima ya amsa irin yanda tayi masa, bayan shigewar shi ta d'aga kafad'a alamar ko ajikinta.

Da taso kar taje d'akin Dada, amman dai ta hak'ura ta shiga abakin k'ofar ta tsaya ta gaidata, Dada kam ko kallo iya kulu bata isheta ba, tayi banza da ita kamar bata jita ba, har sai da Garzali yace:

"Dada fa iyata tana ta gaidaki "

Sannan Dada ta kalleta fuska ahad'e tace:

"Ai da kin rik'e gaisuwarki, don ni banga amfanin da zata yiman ba"

Iya kulu ta turo baki,  kamar wata k'aramar yarinya, sannan aciki ciki tace:

"Nidai kiyi hak'uri  tunda har kinga  na b'ata maki"

Dada tayi mata wani kallon tafi bani wuri sakarya tace:

"Ko 'yar dubu ta dawo duniya, zaki iya yimata haka ballanta ni da ban haifeki ba, renon ki kawai nayi, don haka kije kiji da halinki, nidai fatana akullum Allah ya ganar dake gaskiya ki shiryu ki gyara halayenki"

Iya kulu ta fita fuu tana gungunin cewa:

"Ni halina agyare yake"

***

A haka rayuwa taci gaba da shurawa, yau fari gobe bak'i a tsakani iya kulu da Dada 'yar tsohuwa, yayinda iya kulu take neman duk wata hanya da tasan zata raba izzatu da gidan, amman Dada tayi tsayin daka awajen kare izzatu da jikinta da manyan addu'o'in da take ta tofe ta dasu, kamar wadda aka sanar don izuwa wannan lokaci duk wata hidim ta izzatu itada Garzali suke yinta, ba ruwan iya kulu da sabgar izzatu, hakan yayiwa Dada ciyo, amman kuma taji dad'in faruwar hakan, kodon kare lafiyar marainiyar Allah,tayi b'ul b'ul abinta saboda madarar ta karb'eta sosai, duk bayan sati take shanye gwangwani uku, farinta ya k'ara fitowa, gashinta ma duk da Dada tasa reza ta aske shi tass amman kafin kace me ya k'ara cika kanta fam, gashi bak'i sid'ik tamkar ka saceta ka tsere.

A zuwa lokacin labarin izzatu ya bazu acikin k'auyen, mutane sai turuwar zuwa ganinta sukeyi, Dada kam data fahimci zuwan ba na Allah bane, sai ta kame abutta ta goye ram, akullum goye

take sai idan za'a bata madara asauketa, amman kam ko madarar takesha taji sallamar 'yan ganin k'wam to zata katse bata madarar ta goyeta ta lullub'eta da zane shif shif.

Dadar mu ta mutunci🤣🤣🤣

Akafta💃

D/Auta ce👌🏻

[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*___________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*_____________________________________*

*PAGE ELEVEN*

*********************

Watan izzatu uku agidan,  amma idan ka ganta zakace tayi wata biyar, saboda yanda madarar ta karb'eta tayi k'iba tayi fari, tamkar d'iyar indiyawa,  shiyasa Dada da malam suka k'ara k'aimi

wajen tofeta da addu'o'in tsarin jiki.

Gashin ta anannad'e acike fam, Garzali kam aikin shata ya same shi, domin kuwa shine mai shace kan akullum akayi mata wanka, Dada tayi ta yimasa fad'a wai kada yasa kanta yayi ciyo.

Akwai ranar da inna hure tazo gidan da jaririyarta itama da bata wuce wata biyu ba, mai suna Amina, ta iske ana diramar shatar kan atsakanin su, tayita dariya tace da Dada:

"Gyara ne fa ake yimata Dada, ko bakiso 'yar taki ta fito ne"

Dada tace:

"Ba wani gyara ni aske mata gashin ma zanyi, ko don ta huta da wannan K'ulafuci na Garzali, aikin kenan akullum sai kace ibada"

Aiko Dada ta d'auko reza ta aske kan tas, sannan tace;

"Shikenan yanzu anhuta, kafin dai wata sumar ta fito ai kanta zai sarara da fisgar da yake sha"

Tana k'are maganar ta waiga gefen da Garzali yake azaune, taga wayam bashi awurin, ta dawo da kallonta akan inna hure tace:

"Ke hure ina kika ganar man Garzali, bansan fitar shi ba, Allah dai yasa ba fush....."

Kafin takai k'arshen zancenta ne, suka jiyo sautin iya kulu tana ta fad'a tana dukan Garzali, da sauri dukansu suka fito awaje, domin su ganarwa idanunsu abunda ke faruwa.

Ita ko iya kulun bata daina dukanshi ba har sai da inna hure ta tureta ta janye Garzalin, da gudunshi yaje wurin Dada ya ruk'unk'umeta yana kuka, acikin jin haushin dukan da Iya kulu tayi masa, Dada takai dubanta afuskarshi tace:

"Me kayi mata ne, har da zata yimaka irin wannan dukan? "

Garzali yana sheshekar kuka yace:

"Wallahi banyi mata komi ba, wai don ta ganni ina fushi ne, ta tambayan me akayi nace mata aski kike yiwa izzatu, shine ta fara dukana, kuma tace in na k'ara tab'ata sai ta yankeni ta cire mani kai tayi ferfesu ta cinye"

Dada saboda jin haushin iya kulu k'anzil bata ce ba, taja hannun Garzali shigewarta ad'aki, inna hure ita ta tsaya maidawa iya kulu martani, suka fara sa'insa Dada ta fito tace da inna hure ta daina biyeta, saboda ita masifa ce ke cin zuciyarta, abokin yi take nema abarta da halinta shine zai horata, aiko bud'ar bakin Abu k'anen Garzali sai cewa yayi:

"Wallahi iyata ba masifaffiya bace, ke wayafiki masifa... "

Kafin yakai k'arshen zancen shi inna hure tasa hannu ta kwad'a masa mari, Dada kam bulala tasaka ta zaneshi tas, iya kulu ta fara masifa akan donme za'a dakar mata yaro, aiko fad'a ya rincab'e atsakanin inna hure da iya kulu, da abu yayi tsamari sai ga dambe ya kacame atsakanin su, Dada ta tsawatar inna hure ce kawai taji maganar ta ta daina, amma ita iya kulu sai zillo takeyi sai ta daki inna huren.

Dada tana kuka tace da inna hure ta d'auki 'yarta ta tafi gidan mijinta ta k'yaleta, aiko ba musu ta goye 'yarta tazo zata fita, iya kulu ta fara cin mutunci tana cewa:

"In dai akan wannan tsintacciyar magen ce ake yiman cin kashi acikin gidan, to aci gaba kar afasa, wallahi bazan tab'a son d'iyar shegu ba, haka kawai wata k'atuwa taje ayi mata cikin shege, ta duk'a ta haifo y'arta shegiya ace ni inzo inyi mata reno akan mi?, wallahi bazata sab'u ba, da inyi haka ai gara inje inyi sharar gidan karuwai a birni ana biyana, nasan aikin kud'i ne nikeyi akwai ribar da na samu, amman wannan ba lada bale la'ada, haka kawai inyita wahala abanza"

Inna hure zata maida martani iya ta kad'a ta tabar gidan, sannan ta juyo ta kalli iya kulu da guntayen hawayen ta mak'ale acikin idanunta tace:

"'yar kuluwa ban tab'a tunanin rashin hankalinki yakai har haka ba, amman inason ki fad'a man, shin ita wadda kike kira shegiya, kina da tabbacin cewa da gaske shegiyar ce?, wallahi ki kiyayi bakinki, don gudun ki d'aukarwa kanki abunda baki iyawa, izzatu dai koda shegiyar ce, ai inajin batada hak'k'in kowa sai wanda ya d'auki nata hak'k'in ire irenki ya d'orawa kanshi, saboda haka kisani tunda bakyajin maganata, idan kika sake kiranta shegiya da kaina zanje gidan mai unguwa ingaya masa irin cin fuskar da kike yiwa marainiyar Allah"

Iya kulu ta rikice ta fara borin kunya tana fad'in :

"Yo inba shegiya ba, a'ina aka tab'a haifuwar d'iyan sunnah aje ajefar, nidai ko a tarihi bantab'a ji ba"

Dada ranta ya k'ara zafi, jikinta yana rawa ta d'aga murya tace:

"Ita wadda ta fara fad'a maki cewa d'iyan shegu kawai ake jefarwa, ki tambayeta ita shegunta nawa acikin yaranta?, izzatu ko d'iyar magajiyar karuwai ce, aduk inda ta fito tafi k'arfin matsayinku daga ke har kanden munafuka, idan har Allah yasa rayayya ce har acikin gidannan iyayenta zasu zo nemanta, jikina yana bani izzatu d'iyar manyan mutane ce, zakuyi danasani idan har wannan rana tazo kuka gano gaskiya"

Kande dake lab'e ajikin katangar da ta raba tsakanin gidajensu, ba shiri ta duk'e daga katangar

da ta haye turmi ta lafe tana kallon abunda akeyi, ashe ita Dada ta hango kanta shiyasa tayi wannan habaicin.

Dada ta maida kallonta agefen katangar tace:

"Ahaka za'a k'are tsohuwar algunguma, kidaina lafewa ajikin katanga ki fito ki zagayo kigani da kyau, in akwai abunda kika k'ara yin tanadi, ki isar dashi kafin ki tafi, don kinga wannan da kika k'ulla yayi tasiri munafuka mai bacci da idanuwa d'aya"

Dada kam ta b'alle marfin fad'anta,  baji ba gani har saida wani mak'ocinsu yayi sallama ya bata hak'uri,  sannan ne tayi shiru fad'an ya lafa,  musamman da taji kukan izzatu.

Iya kulu kam shiru tayi, saboda tuno mak'udan kud'in da aka tsinci izzatu tare dasu, wad'anda ta gansu ido cikin ido ba labari aka bata ba, jikinta sanyi k'alau ta shigewarta d'aki tana tunanin cewa:

"Oh ni kulu tabbas da gaskiyar Dada, don wannan yarinya daga ganinta wanda yayiwa uwarta cikinta ba k'aramin attajiri bane, watak'ila daya d'irka mata cikin shegen ta haife, suka sako kud'in akwali tareda 'yar suka jefar, to idan haka ne, ai ni bawai son 'yar zasuyi ba bale suzo neman ta, kai wallahi nikam bazan iya wahalarwa d'iyan shegu ba cab gaba gaibu shegiya mai ido atsakiya kai sai warai warai takeyi dasu, kamar tsohuwar mayya"

Yinin ranar Dada tayi shine,  acikin b'acin rai d'a damuwar abunda iya kulu tayi, sannan da tarin tausayin izzatu da ya mamaye mata zuciya.

Koda malam ya dawo haka ya risketa da damuwa, yayi ta tambayarta amma tak'i sanar dashi abunda ya faru, saboda batason wata sabuwar hayaniya, domin tasan shi sarai duk da hak'urinsa idan yaji,  bazai k'yale iya kulu ba, tana gudun wani sabon fad'an ya k'ara tashi, shiyasa tayi gum,  amma bakinta bai daina yiwa iya kulu adduar shiriya ba.

Kwanaki sai shurawa sukeyi,sati yazo ya wuce, wata ya danno kai, shekara tazo ta wuce, kamar wasa saiga izzatu da shekara biyu, izuwa lokacin, ta iya tafiya, ko ina tana zuwa, acikin gidan, Duk da Dada bata barinta zuwa b'angaren d'akin iya kulu, amman yaro da k'urciya har acikin d'akinta take shigewa tayo mata b'anna, itako ba kunya zata saka hannu ta bubbugeta ta turota waje, idan Dada taji kukanta ta fito tayi ta fad'a, amman bai hana gobe ma iya kulun ta zaneta idan ta k'ara shiga d'akin.

Ga Abu k'anen Garzali shima sai cin zalinta yakeyi, har jira yakeyi tayi masa abunda zai daketa, Garzali ko ya rama mata su kacame da dambe, iya kulu tazo ta shigarwa Abu ba kunya, ita ko Dada tayita fad'a.

Dada ta fara ciyo wasa wasa,  sai ga  ciyo ya kwantar da ita magashiyyan.

😳😭

Ba akafta☹

D/Auta ce👌🏻
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*________________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA🌧*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*__________________________________________*

*COMMENT'S DINKU SHIKE KARA MANI KUZARIN YIN TYPING PLSS KU DAURE KO BA YAWA AYI YAFI AYI GUM DUK DA BA LAIFI WASU SUNAYI AMMAN DAI A KARA😔😒🙄*

*YAWAN COMMENTS YAWAN TYPING🙁*

*PAGE TWELVE*

********************

Malam, da inna hure, da Garzali, sun shiga damuwa sosai akan wannan ciyo na Dada, saboda akullum magani akeyi amma kamar ba'ayi, mai unguwa da kanshi ya turo aka Kai Dada

asibitin birni, tayi jinya ta tsawon sati d'aya acen, sannan taji sauk'i sosai aka dawo da ita agida, kowa yanata farin cikin da samun sauk'inta, har iya kulu taji dad'in ganin ta samu sauki'.

Kwatsam sai ga ciyo ya dawo sabo, anso amaidata asibiti tace dasu, a'a su daina wahalarda kansu akanta, ta kallesu d'aya bayan d'aya zata fara magana tari ya sark'e ta, su malam suka rud'e sai sannu suke yimata, sai da tarin ya lafa, tayi jarumtar had'a kalamomi ta fara magana kamar haka:

"Kuyi hak'uri kuyi hak'uri, inason kuyi man alk'awali koda k'asa ta shafe idona, zakuyi rik'o da zumuncinku, ayuba kaine namiji kuma kaine jagora atsakaninsu, ka zamo mai adalci atsakanin matanka da 'ya'yanka da k'anwarka hure da yaranta"

Malam yace: "Insha Allahu"

Hawaye suna kwaranya akan fuskokin su duka, saboda sunji ajikinsu,Dada wasiyyar bankwana ce takeyi.

Dada ta juyo da kallonta akan izzatu dake kwance agefenta, tamkar wata mara lafiya, duk kiriniya irinta izzatu, amma aranar sukuku ta wayi safiya, sai kuka takeyi anyi lallashi anyi lallashinta har angaji amma abanza, itada kanta tazo gefen Dada ta kwanta.

Dak'yar Dada ta d'aga hannu ta shafo kan izzatu tayi murmushi sannan tace:

Ga amanar marainiyar Allah anan zan bar maku wato izzatu, idan har Allah ya bayyana iyayenta, to kar kuyi wata jayayya kubasu 'yarsu, amma idan basu bayyana ba, duk tsawon zaman da zatayi agidannan, kada ku koreta ku barta taci gaba da zama atare daku, ku rik'eta tsakani d'a Allah, kamar yanda kuke rik'on 'ya'yan da kuka haifa, na yafewa kowa mima ku yafe man Allah yayi maku albarka gaba d'ayanku."

Ta jawo hannun Garzali ta dad'e tana kallon shi, sannan acikin sautin muryar da tasha ciyo ta disashe, ahankali tace dashi :

"Na baka amanar I.. z.. za.. t. u. na"

Dak'yar ta had'a kalmomin, saboda bakinta ya karye, daga nan ta fara kalmar shahada, su malam sunayi tana amsawa, ta hanyar motsa bakinta da lab'b'anta har mala'ikan mutuwa, ya zare ranta acikin salama.

Malam ya share hawayen fuskarshi, sannan ya saka hannu ya shafe fuskarta, idanunta suka rufe, ya saka zane ya lullub'e fuskarta da jikinta gaba d'aya , inna hure ta kwantsama kuka gwanin ban tausayi.

Garzali ko duk da yake da, k'ananun shekaru alokacin, amma yasan mutuwa, ba shiri ya kalli

Malam yace:

"Malam ka bud'e ta Dadar mu fa bata mutu ba"

Ba shiri ya fad'a ajikinta yana kuka yana kiran sunan ta, da ta tashi bata mutu ba, izzatu dake kwance agefenta, ganin Garzali ya fad'a kan Dada yana kuka, itama taje ta aza kanta ajikin Dadar tana ta kuka, Malam yaja Garzali suka fita, inna hure ta janyo izzatu,  ta rungume ta tana ta kuka, saboda tsananin tausayin yarinyar ya kamata, shikenan ta rasa gatanta.

Iya kulu tana rakub'e tunda Dada ta fara wasiyya, jikinta yayi sanyi k'alau, hankalinta bai kwanta ba har saida taji Dada tace ta yafewa kowa, acikin zuciyarta tace:

"Nagodewa Allah da kika yafe man Dada,nima na yafe maki wallahi"

Ta k'ara rud'ewa lokacin da taji Dada tana kalmar shahada, sannan ne wasu hawayen suka gangaro mata.

Abu kamar wasa yau Dada ta bar duniya, tabar izzatunta acikin maraici 😭

Ba akafta😭

D/Auta ce👌🏻

بسم الله الرحمن الر حيم

*_________________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA🌧*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp

*___________________________________________*

*KAR KU MANTA COMMENTS DINKU SHIKE KARA MANI KARFI GWIWA YA ZABURADDANI AKAN INYI MAKU TYPING SABODA HAKA RUWAN SAMAN COMMENTS DINKU KAWAI NIKE BUKATA*

*DUKAN KU I LOVE YOU MAZGA MAZGA😜*

*PAGE THIRTEEN*

*********************

Kwana uku da rasuwar Dada, taron masu amsar gaisuwa suka watse, sai su inna hure da suke zuwa su yini anan su koma gidajensu in yamma tayi.

Iya kulu idan ka ganta alokacin, zaka d'auka cewa wata ustaziya ce, don carbi ne a hannun ta, tana ta lazimi ko magana ma bata son yi saboda mutuwar Dada ta dake ta ba kad'an ba, kasancewar bata san wata uwa ba sai ita Dadar, koda ta bud'a ido itace tasani amatsayin mahaifiyarta, sai daga baya ta gano ashe ba Dada ce ta haifeta ba.

Aranar bakwai Malam ya tara su gaba d'aya yayi masu nasiha mai ratsa jiki, tareda da jadda da masu, amanar da Dada ta bar masu ta izzatu, inna hure ta nemi alfarmar abata izzatu taje da ita, ta had'a da 'ya'yanta ta rik'e, iya kulu har ta fara murna, sai gashi taji malam yana yiwa inna hure tuni, akan wasiyyar da Dada ta bari na abar izzatu ta rayu acikin gidan, har lokacin da iyayen ta suka bayyana.

Inna hure dai dole ta hak'ura ba don taso ba, ta tattara yaranta ta koma gidan mijinta, tareda alhinin rabuwa da izzatu, iya kulu kam taji haushin da ba'a baiwa hure izzatun ba, don ta tsani ta wayi safiya tayi ido biyu da izzatu, tana shawagi acikin gidan.

Koda dare yayi, malam da hannun shi ya d'auki izzatu ya shinfid'e ta akan gadon iya kulu, don sanin da yayi mata bata fitsarin kwance,duk da iya taji haushi amma bata nuna a fuska ba, don itama sheda ce akan cewa izzatu bata fitsarin kwance, sai gashi akayi rashin sa'a koda safiya ta waye ta malka fitsarin ta akan gadon.

Iya kulu tana k'yalla ido taga fitsarin, aiko ba wata wata ta fara dukan izzatu, gashi malam yayi sammakon fita zuwa wata gaisuwa, Garzali ne yazo da zafin naman shi ya d'auketa, daga dukan da iya kulu take yimata, hawaye yana zuba akan fuskar shi yace:

"Haba iya don tayi fitsari, zaki daketa tunda sassafen nan?"

Iya kulu mamaki kwance akan fuskarta tace:

"To tabbatacce ko zaka rama mata dukan ne?"

Garzali yana share mata hawaye yace:

"A'a kidai kawo in wanke fitsarin ba sai kin daketa ba"

Iya kulu ta galla masa harara, sannan tace:

"To ba'ayi yanda kakeso ba ya kenan?, wallahi Garzali ka kiyayeni, don naga kanka yana rawa sosai, akan wannan ruwa da k'ank'arar, in banda rashin hankali irin naka, d'iyar shegun kake damuwa akan an daketa, ai gara ni dukanta nayi iyayent fa da suka d'auketa kacokam, suka jefar a daji fa?, kura da zaki suyi kalaci".

Karaf sai akunnen malam yana shigowa, aiko bakin shi har rawa yakeyi, wajen ya maida mata da martanin cewa:

"Alhmdllh, Allah ba azzalumin kowa bane, tunda har kikaga, bai bari ko k'uda ya sauka a kanta ba, to kinsan akwai wata manufa da ubangiji ya b'oye akan hakan, sannan ina son kisani shi zakaran da Allah ya nufa da cara, ko ana muzuru ana shaho sai yayi, saboda haka kije da bak'in halin ki, dake d'awainiya da rayuwar ki, indai izzatu ce ki kwantar da hankalin ki, zan kawo wadda zata kula man da ita, tsakani da Allah, wadda bata k'yamar ko ta wace hanya ce aka sameta, sabida haka kije kiji da kanki"

Iya kulu ta zabura tana huci tace:

"Malam me kake nufi ne?, ka fito fili kayi mani bayani yanda zan gane, ai dai inajin wannan 'ya ba kaine ka haifeta ba, don haka banga abunda har zaisa ka dinga fifita ta akaina ba, tunda ta shigo a cikin gidan nan, na rasa natsuwa ta da walwala, haka kawai akan wannan tsintacciyar magen za'a dinga yiman cin kashi kala kala, mai kula da ita kuma idan an tashi anemo ta a birnin sin ma idan za'a iya ni ba damuwa ta bace"

Malam dai ci kanki bai k'ara cewa ba, ita ko sai da tayi fad'an har ta gaji don kanta, sannan ta sauke akan Garzali dake baiwa izzatu d'imamen tuwo,ba zato yaji saukar dundu a bayan shi, har saida ya gantsara, da sauri ya sosa wajen tareda b'ata fuska yace :

"Me nayi kuma ni yanzu da zaki dake ni?"

Iya kulu a masifan ce tace :

"Meye ne baka yi ba munafuki?, yanzu wannan uban tuwon da ka lafto, cikin gara ne da ita da zata iya cinye shi?"

Malam ya fito yana saka talkamin shi, yace :

"In duka malmalayen tuwon zata cinye, a barta taci, don ba wani yake nemo man abincin ba, in kuma akwai wanda yake taimako na, to daga yau ya daina bana buk'ata"

Iya kulu ta bishi da kallon mamaki sannan tace:

"Au abun har ya kai cen?".

Malam yayi banza da ita, ya saka hannu a aljihu ya ciro kud'i ya baiwa Garzali yace:

"Gashi idan tana buk'atar wani abu, sai ka saya mata, ni zan fita"

Abu k'anen Garzali ya fara kumbure kumbure yace da malam:

"Ni ina nawa kud'in?"

Malam kam,  a cikin ko inkula ya fara tafiya  sannan yace:

"Kaje uwarka ta baka"

Akafta😜

D/Auta ce👌🏻

[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈*

*NA HADIZA D/AUTA*

*INA JIN DADIN COMMENT'S DINKU NAGODE SOSAI MASOYANA DA MASOYA BUK DIN RUWA DA KANKARA👍🏻👍🏻👍🏻ACI GABA DA RUWAN COMMENT'S NI KUMA INCI GABA DA MURZO MAKU TYPING💃💃*

*PAGE FOURTEEN*

*********************

Malam yana fita,  Abu ya maido da kallon shi akan izzatu ya galla mata harara sannan yace:

"Don ubanki sai kinbar gidannan munafuka, tunda kika zo gidannan kika sa malam ya daina sona"

Yana k'are maganar ya k'wace kud'in ahannun Garzali yana muzurai yace:

"Ko k'wandala bazan bada asiyo maki wani abu ba, sai na gani in da mai k'watar su a hannu na"

Acikin fushi Garzali yayi ciki da shi, suka fara dambacewa, da yake k'arfi ba d'aya ba,  Garzali ya kada shi yanata duka, bayan ya karb'e kud'in.

Iya kulu tana d'aki ta jiyo kokuwar su, da sauri ta fito tana ta masifa dak'yar ta raba fad'an, ta kalli Garzali tace:

"Uban mi ya had'aka fad'a da d'an uwanka har da su dambe?"

Garzali yana sauke numfashi,  saboda  damben da suka sha yace:

"Wai kud'in da malam ya bada, yace asaiwa izzatu biscuits sune ya k'wace gaba d'aya, wai ko k'wandala bazai bada ba"

Iya kulu ta makawa Garzali harara tace:

"Yanzu akan wannan munafukar ne,  ka saki k'wanji ka jibgi d'an uwanka?, saboda kana soko zaka zab'i d'iyar shegu ka bar d'an uwanka ko?to ahir d'inka wallahi bazan lamunta ba, nikam ruwa da kankara tayi kad'an,  da ta shiga a tsakanin yarana, in banda nika tuno wasiyyar Dada, da ayau d'innan sai na korata ta bar gidannan wallahi, inyaso idan malam ya dawo sai ya maida gaba na a gabas ya yanka"

Abu yaje da gudunsa ya kwad'awa izzatu mari, yana huci yace:

"Shegiya sai kinbar gidannan, tunda ba.. "

Kafin ya k'arasa fad'ar abunda zai fad'a ne Garzali ya sauke masa nasa marin shima, Abu ya dafe gefen da yasha marin tareda k'walla k'arar kiran sunan iya kulu, daman itama a zuciye take, ba shiri ta nufi wasu karan dawa dake jingine ajikin katangar gidan, ta zaro wani k'aton kare mai kauri, ta dingi laftawa Garzali yana ta tsalle, bata daina dukansa ba har sai da karen ya kakkarye ajikinsa.

Sannan ta dawo da guntun wanda ya rage ta laftawa izzatu, aiko ba shiri ta k'walla k'ara, zata k'ara kai mata wani dukan ne, Garzali yayi wani tsalle ya tare dukan, ya sauka a bayanshi, da sauri ya d'auketa, yayi waje da gudunsa, ya sami gindin bishiyar dake k'ofar gidansu, ya zauna yana ta lallashin izzatu dake ta faman kuka.

Shima baisan lokacin da ya fashe da kukan ba, saboda tausayin izzatun shi, musamman da yaga dukan da iya tayi mata har wajen ya fashe, karen ya yankata, har jini ya fito, daga nan inda yake azaune yana jiyo sautin iya kulu dake ta masifa, abun bai mata ba har saida ta lek'o ko mayafi babu tana huci tace:

"Yau dani daku ne acikin gidan, tunda ka nuna k'iri k'iri kafi son bare akan d'an uwanka, yo niko bazan tab'a d'aga maku k'afa ba, sai naga wanda zaici riba ni da ku"

Tana k'are zancen ta juya zata shige a cikin gidan, langa langar dake jikin k'ofar gidan ya rik'e mata gefen zane, a cikin fushi ta fisgi zanen aiko sai ji kake b'arrrrrr zanen ya yage, ba tareda ta bi ta kan zanen ba ta shige gidan.

Garzali ya share hawayen shi, da suketa kwarara ya maido da kallon shi akan izzatu dake rungume ajikin shi, da take ta sauke ajiyar zuciyar kukan da tasha, da sauri ya tashi tana sab'e a kafad'ar shi, yaje shagon d'anliti dake a kusa da gidansu, ya siyo mata minti da biscuit, da ledar ruwa pure water d'aya, sannan ya dawo gindin bishiyar ya zauna, ya bata biscuit d'in tana ci yana yimata wasa har ta ware ta saki jikinta tana dariya, ta cinye biscuit d'in tasha mintin, sannan ya bata ruwa tasha ya wanke mata fuska da sauran ruwa, aiko sai gata tana ta jera hamma ya rungumeta ajikinshi yana girgizata, kafin kace me tayi bacci, sai sauke numfashi take a hankali, tana ajiyar zuciya.

Garzali hankalin shi ya kwanta, nutsuwa ta dawo masa, ba shiri ya sauke ajiyar zuciya, ya maida kallon shi, akan wani mahaukaci dake yawan shigowa a cikin k'auyen nasu, wanda a duk lokacin da ya shigo k'auyen, a nanne wajen zamanshi a jikin bishiyar, abun mamaki sai yaga hawaye kwance akan fuskar mahaukacin, sai kwaranya sukeyi sun kasa tsayawa a kwarmin idanuwan shi.

Saboda iya sanin su dashi, baya um baya um um, baya kula kowa da sabgoginsu, baya duka baya zagi, amman da kaga shigar shi zaka gano mahaukaci ne, saboda farkon shigowarshi a k'auyen, sai da mai unguwa yasa aka kawo masa shi, ya k'are masa kallo zuciyarshi ta natsu

dashi akan cewa ba mugu bane, sannan aka fita iskan shi yana ta shawaginsa acikin garin, amma an saka ido akanshi, tsawon shekara har izuwa lokacin, ba'aga wata alama ta cuta atattare dashi ba, shiyasa mutane suka d'auke idanuwansu a kanshi, ba ruwan kowa dashi.

Garzali ya k'ara bud'a idanuwa sosai, saboda yana so ya gasgata shin da gaske kukan ne yakeyi ko kuwa?.

Mahaukacin kam da ya fahimci Garzali yana ta kallon sa, jiki ba kuzari ya tashi tsam ya fara tafiya,  ko waige bai k'ara yi ba har ya bar k'auyen.

Tofa shin wanene wannan mahaukacin?
Jama'a akwai lauje acikin nad'i fa🙀🤔

Akafta😭

D/Auta ce👌🏻
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈*

*NA HADIZA D/AUTA*

*INA JIN DADIN COMMENT'S DINKU YANA SANI FARIN CIKI BA KADAN BA ALLAH YA BAR ZUMUNCI BA🤝🏻*

*KUYI HAKURI BAN SAMU DAMAR BAKU REPLY AKAN COMMENTS DINKU BA AMMA KU SANI NAGA NA KOWA KUMA NAGODE INA JIN DADIN ADDU'O'IN KU AKAINA DUKAN KU I LOVE YOU WUJIGA WUJIGA💃💃💃❤️❤️💋💋*

*PAGE FIFTEEN*

*********************

Garzali bai daina kallon shi ba, har saida idanuwanshi suka daina hangoshi, sannan ya dawo da kallon shi akan izzatu, dake ta sharar baccinta hankali a kwance.

Sannan a cikin zuciyar shi yace:

"Bazan koma gida a yanzu ba, har sai zuwa lokacin da malam zai dawo"

Yana k'are wannan tunanin, ya kinkimi izzatu ya goye ta, ita ko ta lafe a bayansa luf saboda taji dad'in goyon, sannan ya fara tafiya a hankali sai gidan inna hure.

A gajiye ya isa gidan, inna hure tana ganinsa, tayi saurin karb'ar izzatun taje ta shinfid'e ta, sannan ta dawo ta kalleshi kallo mai cike da tausayi tace;

"Daga ina haka?"

Garzali ya waske yace:

"Daga gida, izzatu ce take fitina, nayita lallashi tak'i daina kukan, shine nace bara na goyata nazo gidannan nasan kafin mu k'araso tayi bacci"

Inna hure ta kalleshi da kyau ba don ta amince da zancen nashi ba, yanayin shi kawai da ta gani tasan akwai abunda ya faru a tsakaninsa da iya kulu,  baya dai son fad'a ne, shiyasa bata takurashi ba akan sai ya fad'a,  ta share zancen sannan tace:

"To zo ka zauna in zubo maka abinci, kafin izzatun ta tashi daga baccin itama sai taci"

Aiko ba musu ya zauna,  ta lafto masa tuwo yaci ya k'oshi yayi hani'an, sannan ya shige a cikin matasan yaranta maza sukayita sabgogin su, atak'aice dai basu bar gidan ba har saida Garzali ya tabbatar a lokacin malam ya dawo, sannan ya d'auki izzatu suka koma gida.

Kanshi a tsaye ya shiga gidan da guntuwar sallamar shi a baki, iya kulu tana ganinsu ta fara fad'an cewa:

"Gidan ubanwa ka fito ne?,  ace tunda safe da ka fita sai yanzu kaga  damar dawowa  gidan"

Garzali yana k'ok'arin kare kanshi ne, malam ya fito shima ya dasa tashi tambayar da cewa:

"Me aka yimaku ne a gidan?, da kukaji bakwa iya zama kuka fita tunda safe?"

Garzali zai fara magana, iya kulu tayi saurin fad'in:

"B'aceman da gani tun kafin in sauya maka kamannu, haka kawai zaka tsirowa kanka yawo a banza, abunda ba halinka ba, ka ara ka yafa, wallahi gobe ka koma fita yawo sai na karya maka k'afafu, daga kai har wannan farar kurar"

Garzali ya wuce abinshi yana dariya, malam ta bashi dariya, amma ya dake yace:

"Ai da kin barshi ya fad'i abunda yasa shi fitan, tunda ke da kanki kinsan yawo ba halinsa bane"

Iya kulu tayi gum, don tasan da maganar tayi tsawo, dole ne sai an samu matsala rayuka sun b'ace, don ta fahimci malam tunda Dada ta rasu, abu k'iris tayi sai ya taso mata da fad'a, sab'anin lokacin da Dada tana raye baya biyeta suyi ta musayar baki.

**

Kwana biyu a tsakani malam ya fara gyaran gida, iya kulu bata tantance ba, sai gashi malam yana ta fiddo da kayan su Garzali dake wani d'ayan d'aki, inda suke kwana, yana kaiwa d'akin Dada, bata sha mamaki ba har sai da taga anfara shigo da bulo bulo ana ginar wani d'akin acen bayan d'akunansu, don daman cen d'aki uku ne ajere da juna, na iya kulu a gefe sai na malam atsakiya sai nasu Garzali a kusa da na malam d'in.

Tambayar duniya tayiwa malam, akan me yake nufi da wannan gyare gyaren, amman yayi banza da ita, tun tana d'aukar abun wasa har ta tub'ure, asanadiyyar ganin da tayi anhad'e wannan sabon d'akin da akayi da tsohon d'akinsu Garzalin, ya zama ciki da falo, sannan yabi d'akin ya shafe da fenti, itama yace ta kimtsa komatsanta ayi mata fentin.

A lokacin ne tunanin ta ya bata cewa aure malam zaiyi, aiko ta fara zazzaga ruwan masifa tana Allah wadai da rashin halacci irin na malam, bakinta yana kumfa saboda masifa tace:

"Ashe dama jiran kakeyi k'asa ta shafe idon Dada kaci zarafina?, to wallahi baka isa ba, in ma banda k'addarar aure ni me zanyi da talaka ma irinka, Allah ya jik'anki Dada, gwara da baki ga zuwan wannan ranar , ta cin amanar marainiya 'yarkuluwa ba"

Ta k'are maganar tareda fashewa da wani bajimin kuka, kande dake lab'e a jikin katanga, ba shiri ta k'yalk'yale da dariya har turmin da take hawa tana tsegumi, ya b'angwale ta fad'i kasa tana dariyar mugunta.

Malam dai Ci kanki baice da ita ba, su Garzali ma sukayi cirko cirko suna kallonta,izzatu kam ganin tana kuka itama sai ta fara kukan, ba shiri iya kulu ta maka mata dundu a baya tace:

"Rufa min baki munafuka, ai duk wani bala'in dake b'ub'b'ugowa a cikin gidan, kece kika tono shi, shegiya dangin gayyar na'ayya, nikam ko wa yayi cikinki Allah ya'isa tsakanina dashi, don kuwa nice aka k'unsowa masifa"

Garzali ya d'auketa yana lallashinta, malam ya fito, ya baiwa Garzali kud'i ya siyo mata kayan k'walam, sannan yaja hannunta suka shige d'akinshi, aiko ya k'ara turawa iya kulu haushi, k'iyayyar izzatu ta k'ara linkuwa a cikin zuciyarta, ta dinga jifanta da miyagun kalamai, yinin ranar zir haka ya k'are tanata zuba masifa ruwa ruwa, har sai da ta gaji don kanta tayi shiru.

**
Da safiya ta waye akazo za'a yimata fentin tace bata so, dole aka k'yaleta akaje d'akin Dada aka fente, inda su Garzali suka koma, duk da kasancewar d'akin ginin k'asa ne aka yiwa yab'en siminti, shima ya fito fes su Garzali sai murna sukeyi.

**

Bayan sati d'aya malam yaci kwalliya da babbar riga da takalminshi sabbi k'al,  yaje har d'akin iya kulu sai zuba kamshi yakeyi, ya zauna a kan gadonta yana murmushi yace:

"Uwargida ki shirya tarbon bak'i, saboda  yau  ne za'a d'aura man aure da amaryata ta birnin sin da kikace in kawo, wadda zata rik'a man izzatu idan tazo,  kuma a yau zata tare a gidannan insha Allahu, kiyi hak'uri uwargida abun ne yazo a k'urarren lokaci"

Ya zaro kud'i a aljihunshi ya k'ara cewa :

"Ga kud'i nan ki baiwa Garzali yayo cefane, domin adafawa bak'in da zasu zo abinci, saboda yanzu 'yan jere zasu zo suyi jeren, d'akin abud'e yake idan sun zo"

Iya kulu kam,  ba shiri tayi suman wuccin gadi, dak'yar ta samu kanta, har ta tattaro kuzarin maka masa wata gagarumar  harara, da jajayen idanunta,  da suka daina samun bacci isashe a cikin 'yan kwanakin,  saboda tashin hankalin da take  ciki ma har sun koma 'yan k'ananu, kafin ta shirya abunda zata fad'a har malam yakai bakin k'ofa, yana murmushi yace:

 "Ni na fita sai na dawo, hure zata zo ku had'a k'arfi ku tarbi bak'in"

Yana fita ya kira Garzali da Abu yace suje su k'ara share d'akin, a gabanshi suka fara aikin sannan ya bar gidan.

Shoki💃kuzo mu kwaso shoki😹

Akafta😝

D/Auta ce🤝
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*______________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp

*______________________________________*

*SABODA JIN DADIN COMMENTS DINKU YASA NI KARO MAKU WANI TYPING 💃💃💃💃💃💃*

*MY FAN'S KUZO MUSHA RUWA DA KANKARA 💦⛈😝🏃‍♀️*

*PAGE SIXTEEN*

*********************

Garzali da Abu suna cikin d'akin suna shara ne, inna hure tayi sallama ta shigo gidan, tareda zugar yaranta da suka zo ayi bikin dasu.

Inna hure tayita rafka sallama iya kulu tayi banza da ita, sai su Garzali ne suka amsa mata, jiki ba kuzari ta ajiye kayan da tazo dasu, ta nufi d'akin iya kulu tareda maimaita sallamarta.

Iya kulu zaune ta shiga duniyar tunanin shin miye mafita, a tsakiyar kai taji sallamar inna hure, ba shiri ta zabura tareda cewa:

"Wannan k'ulafuci har ina, zaki zo ki cikawa mutane kunne da makararriyar sallamarki"

Inna hure ta shanye b'acin ranta, a cikin kulawa tace:

"Ki fito ki bada asiyo kayan abincin, domin muyi sauri mu k'arasa kafin mutanen suzo"

Ba shiri iya kulu ta maka mata wata shahararriyar harara, mai cike da sak'on kashedi, sannan tace da ita:

"To ashshibi, yabon da kikeso ayi maki ni bani buk'atar shi, kuje cen kuji da munafuccin ku, kud'i ne dai wallahi ficika bazan bada ba,na danne abuna a matsayin cin amanar da aka yiman, Allah

ne ya tsaga da rabona, don haka sawunki a likkafa ki fita ki bar man d'akina, tun kafin infito maki da sifar ta 'yar kuluwa ta gaske.

Inna hure kam gaskiyar da tayi mata yawa k'anzil bata ce ba, ta fito ta fara k'ok'arin gyara kayan miyan da tazo dasu, kamar tasan za'ayi haka, tazo da shirinta, domin duk wani abu da ake buk'ata sai da ta tanada tazo da abunta.

Iya kulu taji haushin da inna hure bata biyeta ba, sukayi tashin hankalin da zai wargaza farin cikin kowa ba, shiyasa ta fito ta fara zazzaga ruwan rashin mutuncinta da ta saba tana cewa:

"Ku bak'in suka dama idan ta nice ma, motar da zata kwaso su gayyar tsiyar, ta fad'a gada dukansu su margaya zuwa lahira, wallahi ni ko ajikina ballantana in tarbesu da wani abinci cen, don nikam ai kije ma kiyita istigfari, saboda zunubin naki gawurtacce ne"

Inna hure tayi kamar ba da ita take ba, ta tattaro yaranta dasu Garzali, kowa ta raba masa aikin da zaiyi, kafin kace me har sun dafe jalof d'in shinkafa, sai kamshi gidan yakeyi, ta d'auko babbar fanteka ta zuba abincin 'yan jeren, sannan ta zubawa yaran sukaci suka k'oshi, sunata jin dad'i.

Rabon kaddara, izzatu rik'e da kwanon abincinta, tana ci ta nufi d'akin iya kulu, dukansu hankula sun d'auku ba wanda ya kula da shigarta a d'akin, aiko sai jin k'ararta aka yi, sai gasu da rige rigen zuwa d'akin domin suji me take yiwa kuka, suna zuwa suka isketa kwance magashiyya babu alamar numfashi a tattare da ita, Garzali yana k'yalla idanu ya hangota kwance a k'asa kamar matacciya, ya kurma kuwwar kiran sunanta, inna hure tayi saurin d'aukota ta fito da ita waje da gudu ta kinkimo ruwan tukunya masu sanyi ta watsa mata, aiko sai ga izzatu da sauke wata k'atuwar ajiyar zuciya tana kuka, inna hure tasa zane ta goyeta, duk da a lokacin ta fara wuce goyo, sannan ta fara jijjigata tayi bacci.

Yaran duka sai kuka suke tayi, musamman Garzali da ya aza hannu akai, yana ta zabga kuka na tashin hankali, don shi a tsammaninsa, izzatun shi mutuwa tayi.

Iya kulu ta fito tana borin kunyar cewa :

"Gobe don ubanki in kina da shi, ki k'ara zuwa d'akina kiyiman b'anna, wallahi sai nayi maki dukan da yafi wannan"

Inna hure tayi mata wani kallon, ke gudu mahaukaciya, sannan tace:

"Duk cutar da kike yimata, ta fili da b'oye kisani Allah yana kallon ki, kuma da sannu sai ya sakamata akanki wallahi"

Iya kulu tayi shewa mai k'arfi, sannan tayi gud'a, har sai da kande dake jikin katanga ta k'ara kwalalo idanuwa, bakin iya kulu har rawa yakeyi, wajen fad'in:

"Ko zaki rama mata ne kafin zuwan lokacin?"

Inna hure zatayi magana sai ga sallamar, masu jeren sunzo, nan ta bar iya kulu, taje ta tarbosu da fara'arta, sai lale da marhaban takeyi dasu.

Iya kulu kam tana hango shigowarsu, kamar walk'iya ta fad'a d'akinta, kirjinta yana dakan luguden uku uku.

Kuzo a danni k'irjin uwargida sarautar mata🤪

Akafta💃

D/Auta ce🏃🏻‍♀️
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*_____________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*_______________________________________*

*RAWA DA GIRGIZA ZANYI GABANKU IN JUJJUYA💃💃💃💃COMMENT'S DIN DA KUKE INA JIN DADI💃💃💃💃💃💃💃😝*

*PAGE EIGHTEEN*

*********************

Aiko sai naga ashe har mutane sun fara watsewa a cikin gidan,sai tsararun mutane da aka bari, cen na hango inna hure tana had'in kayanta, tareda had'a kan yaranta tana cewa suzo su tafi gida.

Aiko ina tsaye a gabana, suka kimtsa kayansu, inna hure ta nufi d'akin amarya tayi mata addu'ar zama lafiya, sannan sukayi sallama da juna ta fito, ta nufi d'akin iya kulu badon ranta yaso ba, saboda gudun abunda zaije ya dawo, don tasan izuwa lokacin a wuya take da kowa, musamman ita dai k'iris take jira tayi AYI uwar watsiya.

Taje bakin k'ofar ta iya kulun ta d'aga murya daga wajen tace:

"To 'yar kuluwa mu mun wuce sai wani jik'on"

Iya kulu daga cen d'akin itama, ta d'aga muryar tace:

"Umma ta gaida Aysha munafukai, bazaki jira ayi zaman auren dake ba?"

Inna hure tayi murmushi, ta fara tafiya sannan tace:

"Wani garin ai yafi gaban kunu, babban goro ai sai magogin k'arfe, kedai ki zauna ayi tayi dake, a sannu zaki gane cewa ashe shayi ruwa ne sai an saka masa madara yake sauyawa"

Iya hure tana k'are maganarta ta saka yaranta a gaba suka bar gidan, don gudun haukar iya kulu ta motsa su rabawa kansu abun fad'a acikin tsirarun mutanen da suka rage a d'akin amarya.

A hankali mutane suka sulale aka bar iya kulu da amarya, sai su Garzali da suka shige d'akin amaryar yayin da amarya hassatu ke rungume da izzatu a jikinta, tana basu labarai sunata dariya, sab'anin abu dake kallonsu yana jin haushin SU gaba d'aya, da ya gaji da kawaicin ya buga masu tsaki ya bar d'akin.

Amaryar malam ta bishi da kallo a cikin mamakin ganin rashin kirkin da ya aikata, Garzali yaji haushin abunda Abu yayi, shine ya fara baiwa amarya hak'uri a cikin ko in kula tana murmushi tace dashi :

"Ba komi"

A tare sukayi sallah da Amarya, har bacci ya sace izzatu a jikin amaryar, tace da Garzali yaje ya

d'auko kayan shinfid'ar izzatu na bacci ya kawo mata, aiko sai gashi ba jimawa ya dawo dasu ya mik'a mata kasancewar a kullum sai ya wanke kayan tass,  ko tayi fitsari ko batayi ba, don izuwa lokacinma ta daina yin fitsarin kwancen.

Amarya ta shinfid'awa izzatu shinfid'ar akan makeken gadonta mai kyau, sanna ta d'auketa ta kwantar a kai, aiko izzatu taji laushin katifa ta baje tana ta baccinta har da su minshari.

 Garzali yaji dad'in abund amaryar malam tayi, wanda farin ciki ya kasa b'oyuwa akan fuskarshi, har saida ya kalli amaryar yace:

"Mun gode iya"

Amarya tayi murmushi tace:

"Daga yau sunana MAMA ba iya ba"

Garzali yayi dariya, tareda gyd'a kai yace:

"To Mamarmu"

Amarya tace dashi yaje ya kwanta yayi bacci don yayi saurin tashi yayi sallahr asuba, aiko ba musu yayi mata sai da safe ya fita yana ta jin dad'i.

Misalin k'arfe tara da rabi, malam ya shigo gidan, bakinshi d'auke da sallama, kai tsaye d'akin amaryar shi ya shige, yana mai jin kansa a cikin wani tsatsar farin ciki, bayan ya zauna akan gadon gefen da izzatu take akwance, bai kula da itaba yazo zai baje shima ya d'and'ani dad'in gadon amaryar tashi ne, Mama Hassatu tayi saurin fad'in:

"Allah yasa dai idanunka su bud'e ka hango 'yata dake bayanka kar ka tada man ita tana baccinta"

Ba shiri malam yakai dubansa akan izzatu, ya zaro ido awaje yace:

"Allah ya soni, wallahi ban kula da tana a gun ba, sai yanzu"

Mama hassatu, ta feshe da wani tsadadden murmushi, sannan tace:

"Taya zaka sani tunda idanunka arufe suke da ganin sabuwar amarya dal akwali"

Malam ya dafe bakinshi yana dariya, sannan yace:

"Sherin da zakiyi man kenan, a cikin dare?"

Hassatu tana dariya tace:

"Sha kuruminka, gobe ma zanyi maka a cikin rana"

Gaba d'ayansu suka tuntsure da dariya, aiko sai jin sautin iya kulu sukaji tana cewa:

"Cin amanar ta fara aiki tun a daren farko?, to wallahi bazan tab'a lamunta ba,  ace inaji ina gani amaidan borar k'arfi da yaji,  a cikin gidan aure na ba"

Malam yayi tsam ya tashi, sannan yace da hassatu ta sameshi a d'akinshi, don shi bazai kwana anan ba, haka ko akayi yana fita ta k'ara kimtsawa, sannan ta fito tana canki in cankar ina ne d'akin malam d'in?,ta gane d'akin ne ta sanadiyyar talkaminshi da tagani ajiye a k'ofar d'akin.

Da sallama a bakinta ta shiga, idonta suka sauka akan k'wayar idanun iya kulu dake zaune ta zurawa k'ofar idanu, tana jiran taga shigowar amaryar, domin taga wace mai ganganci ce,  da zata had'a kishi da ita!, aiko sai gashi taga  hassatu ce da ta sani, waton tsohuwar masoyiyar malam da yaso aure Allah bai nufa ba, aiko ganinta yasa gaban iya kulun ya k'ire ya fad'i,a nan take jib'i ya dinga  kwaranya a duk wata k'ofa dake jikinta, jikinta ya d'auki rawa tamkar ana kid'a mata gsngunma.

Hassatu ta wayance ta fara gaidata, amma ina iya kullu an lula kogin tunanin makomarta, saboda ita kanta tasan kishi da hassatu ba riba bane a wurinta.

Sau biyu hassatu tana gaidata, amma batasan tana yi ba, har sai da malam ya kira sunanta da k'arfi, sannan ta zabura a cikin d'imaucewa tace:

"Itace ko, wallahi itace!"

Malam da hassatu suka bita da kallo, a cikin mamaki, kallon da taga suna biyart da shine yasa hankalinta da ya b'ace na wuccin gadi,  ya dawo ya shigeta,  ta gyara zama ta natsu da kyau fara kumbure kumbure tana shan k'amshi.

Malam yace:

"Bakiji amarya tana gaidaki ba?"

Iya kulu b'acin ranta da tsantsar kishinta,ya  k'ara hauhawa acikin fushi tace:

"Banji ba, daman akan in saurari gaisuwarta ne, kace inzo zamuyi magana, to bani buk'ata ta adana gaisuwarta wa mai so"

Malam ya gyara zaman shi da kyau,acikin jarumta irinta mazajen k'warai yace:

"A jiye wannan zance naki, muyi maganar da ta taramu a nan, daman ba komi bane yasa na had'a ku, saboda ina son ku had'a kanku kuyi zamanku lafiya, ku tsara yanda zamanku zai kasance, insha Allahu zan kasance mai adalci a tsakaninku"

Iya kulu tayi wani mere sannan ta mik'e a tsaye ta rik'e kunkuru, sanna ta k'are masu kallon uku saura kwata tace:

"Kwaji da munafuccinku dai daga kai har ita,  kuje ku fad'awa 'yan kaji, wad'anga 'yan zabbi ne, a dalci wane kala kake kira?, kana adalci kayi mata d'aki biyu ka had'e mata ni ka barni da d'aki d'aya k'wallin k'wal, sannan ka dawo ka dinga karanta man karatun bayan littafi"

Malam kam wata damuwa ta ziyarceshi, saboda yaji zafin kiranshi da iya kulu tayi munafuki, amman ya share don kar ta b'ata masa daren farin cikinsa, yace:

"Ita ta bada kud'inta aka gina mata wani d'akin, kema idan kinaso ko yanzu bata b'aci ba, sai ki kawo naki kud'in gobe a fara yimaki aikin"

Iya kulu ta d'age d'ankwali ta juya baya tace:

"Fad'awa k'eya"

Ran malam yayi k'ololuwar b'aci, hassatu tana ganin yanayin da ya shiga, a cikin wayancewa taje ta fad'a a jikinshi ta fara yimasa tafiyar tsutsa da hannunta, ba shiri ya dawo da hankalinshi akanta,ta sunbace shi, sannan ta kirashi da wata murya, mai d'auke da aika sak'on abunda akeso a wurin wanda ake yiwa ita, sannan tace dashi:

"Nifa Alhajina bacci nikeji"

Aiko malam ya rud'e gaba d'aya, ya d'imauce suka fara musayar kalamai tareda aikawa juna sak'onni, sun manta shaf da iya kulu tana d'akin, sukam sai b'arje gumin soyayyarsu sukeyi.

Iya kulu tajira taji bala'in da malam zaiyi, don tasan ta kunno shi da yawa, amman taji shiru, juyawar da zatayi idanunta sukayi mata mugun gani, domin kuwa sun fita hayyacinsu, sai neman hanyar da zasu gamsar da juna sukeyi, da sauri iya kulu ta dafe kunnuwa ta kurma kuwwa, ba shiri suka dawo hayyacinsu, aiko iya kulu ta kasa juyawa a million ta fara gudu  zata fito a d'akin, malam ya d'aga murya yace:

"Idan kin fita ki rufo muna d'akin"

Wayyo Allah iya kulu nidai kar ki fad'i kiji ciyo garin gudun🙀

Akafta🙈

D/Auta ce😹
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*________________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*__________________________________________*

*COMMENT'S DINKU YANA SANI FARIN CIKI BA KADAN BA💃💃💃💃💃💃💃KUCI GABA DA RUWAN COMMENT'S MUTANE NA ONE LOVE❤💋🤝*

*PAGE SAVENTEEN*

*********************

Ba shiri takai zaune, zuciyarta sai bugawa takeyi da sauri da sauri, amman duk da hakanan tana jin sallamarsu a k'ofar d'akinta, sai da tayi k'arfin halin d'age kai sama tana hurar hanci, ta amsa sallamar da cewa:

"Ku shigo d'akin ne ai kun kawo, lafiya?, me kukazo nema?"

Aiko suna jin lafazin bakinta, ba shiri suka ja birki a k'ofar d'akin, d'aya daga cikinsu tace:

"Barmu kawai muyi  abunda ya kawo mu, ba sai mun shigo ba makullin d'akinmu zaki bamu"

Iya kulu ta taso tazo bakin k'ofar d'akin, tana k'are masu kallo sama da k'asa,  sannan tace:

"Ku da d'akinku kuma ace ku kasa makullin shi, to kuje gida ku d'auko tunda har kun manta shi acen"

Tana k'are maganar ta saki labulenta,  ta komawarta d'aki, ta barsu anan tsaye, kowace mamaki fal ranta, sai ga inna hure tazo tana fad'a masu cewa d'akin fa abud'e yake, suzo suje  har sauran 'yan uwansu, sun fara aikin, sannan sukaja k'afafunsu suka isa d'akin, amma zukatansu kowace da abunda take saka masu.

Suna ta hada hadar jerensu har marece,  sai firarsu da dariya sukeyi, inna hure kam bayan ta kawo masu abincin, ta shige a cikinsu anata aikin, sai shewa sukeyi suna gud'a idan firar tayi dad'i.

Bayan ank'are jeren ne, wasu suka tafi wasu suka tsaya anan har sai ankawo amarya, inna hure ta k'ara aza masu wata sabuwar sanwa, wasu 'yan unguwa da abokan arzik'in inna huren suka taimaka aka dafe abincin bikin ras, sannan suka fara kaiwa dangin amaryar, sannan aka baiwa 'yan biki masu shigowa, don kuwa abun kamar had'in baki, duk da iya kulu  bata gayyaci kowa ba, amma mutane sai tud'ud'uwar shigowa sukeyi, suna sanyawa auren albarka, inna hure ta baje abunta sai karb'ar bak'in takeyi tareda sakin fuska, don a d'akin Dada wanda ya zama nasu Garzali a yanzu, acen ta koma abinta tana hada hada da bak'i masu shigowa.

Iya kulu tana d'aki bak'in cikinta yana cinta, don kuwa duk wadda tsautsayi ya sakata shiga d'akinta, wai yimata Allah sanya alkhairi, to cin mutunci ne ke rabasu, saboda ta tub'ure sai zabga hauka take yiwa,  'yan unguwa da dangin babanta masu shiga d'akinta.

Ana yin magriba sai ga 'yan kawo amarya sunzo, gida ya runtume sai murna ake tayi da zuwan amarya, Amarya ta danno kai sai wani k'amshi ne na jiyo yana tashi ajikinta.

Abun mamaki koda aka shigo da amaryar,  ko kallon d'akin iya kulu ba'ayi ba aka shige da amarya a cikin d'akinta, sai shewa danginta  sukeyi suna ta rafka gud'a.

Nidai nayi k'ok'arin kutsawa na fad'a d'akin,  ina shiga na  k'yalla idanuna na hango, wata hamshak'iya k'irar matan masu kud'i, mace ce mai jiki, fara,mai kyau, wayayya taci ado irin na 'yan birni, sai shan k'amshi takeyi, na k'ara gwalalo idanuna domin in tabbatar shin itace amaryar malam, koko matar wani hamshak'i ce a birni,don kuwa naga da tayi murmushi harda k'yallin hauren makka na hango a bakinta,  don wannan kam batayi kama da mutanen k'auyen ba,  sam ma babu mahad'i, to shin nikam taya aka haihu a ragaya??????.

Na kasa samun wanda zai bani wannan amsar☹.

Mutane sai turuwar shiga d'akin sukeyi domin suga wacece amaryar malam, nidai na samu na fito dak'yar, domin kawai inyi nad'iyar rahoton, abunda ke gudaana a wajen.

Cen naga wasu mata su biyu sun fito daga d'akin amaryar,  fuskokinsu d'auke da mamaki fal, d'aya ta jawo hannun d'ayar da sauri suka fito gidan, suka yada zango a kofar gidan, ni kuma ina ganin haka, nasan lalle da magana abakin wannan mata mai suffar tsegumi, ba shiri na biyo bayansu, na samu na mak'ale ajikin k'ofar gidan nasha jinin jikina domin in d'auko maku rahoton abunda zasu fad'a.

Aiko sai naji mai siffar tsegumin tana cewa:

"Ke wai kinko gane wacece malam ya aura?"

D'ayar tace :  "A'a nikam taya zansan wannan zuk'ek'iyar 'yar birnin "

Mai tambayar tace:

"Yanzu kina nufin baki gane hassatun gidan idi mai icce ba?"

Wadda ake ba labarin ta zaro ido bakinta yana rawa tace:

"Ki bari don manzo yanzu kina nufin itace wannan mai siffar hajiyoyin?"

Mai bada labarin tayi wata shewa sannan tace:

"Ai ni inbaki labari daman cen,  abunda ya kawoni kenan, don in ganar wa idona da gaske hassatu ce malam ya auro?, lalle soyayya gaskiya ce, tunda har hassatu ta bar 'yan birnin dake sonta, ta dawo k'auye ta zauna, saboda son  Ayuba da takeyi, kinsan fa ita yaso ya aura tun farko, sai gashi Dada ta lik'a masa 'yar kuluwa, saboda yawon ta zubar d'in da ta tab'a zuwa yi a birni"

Wadda ake baiwa labarin a cikin jimami tace:

"Yanzu kina nufin 'yan birni sunyi sonta, shine ta yankawa kanta kazar wahala  ta dawo a nan garin ta zauna saboda soyayya?"

Mai bada labarin tace:

"Tabbas ko, don abokan Alhajin da ta aura, sunyi ta zuwa a garinnan da zunduma zunduman motocinsu, suna neman aurenta, amma tak'i kowa saboda son malam Ayuba da takeyi, to yanzu dai k'urunk'us kan b'era ta auri Ayuban, gata ga 'yar kuluwa nan sai suyita fafatawa"

Wadda ake ba labarin ta rik'e baki a cikin jin haushin amaryar malam tace:

"Ita yanzu ita ko makkar da akace Alhajin,  ya kaita kafin ya rasu bata dubawa, taje taci gaba da auren alhazawa taci arzik'inta, tafiso ta dawo a nan tashin hankalin 'yar kuluwa ma bazai barta tayi wani kumari ba, 'yar k'ibar da tayo a birnin ma sai ta zube ta ai, ta koma zubin muciya, saboda dambacewar da zasu dinga yi a kullum, oni ige arzik'i yana biyarka kana gudu"

Abokiyar firar tayi wani mere tace:

"Zo muje abunmu, tunda tace zata iya had'iye gatari, ai sai arik'e mata b'ota, mu meye namu aciki?"

Ina lab'e abayan k'ofar gidan, ba shiri wata dariya tazo man nace:

"Nace naku a ciki shine tsegumi"

Bayan tafiyarsu ina k'ok'arin fitowa mab'oyata ne, langa langar dake k'ofar gidan, ya kartoni da sauri nace wash, na samu na fito zan wuce ya rik'e mani gefen hijabi,ba shiri nace wayyo ni dije, saboda naji tsoron ya b'arka man shi,  jin tsegumi ya jaza man shiga uku, saboda hijabina ne na sallah da ogana ya saiman ko wankinshi ban tab'a yi ba saboda sonshi da nikeyi, da dubara na cire hijabin,  nayi hamdala da naga baiyi komi ba, sannan na koma cikin gidan domin inji,  shi kuma me zan samu, inga wace wainar ce ake toyawa.

Ashe Malam  fashi yayyi😹

Akafta🤣

D/Auta ce👍🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*________________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA🌧*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp

*____________________________________*

*ALHMDLLH RUWA DA KANKARA YAYI  MASOYA YAKAI HAR INDA KO NI BAN TABA TUNANIN ZAN KAI WAJEN BA SAI GASHI A SANADIYYAR BUK DIN SUNANA YAJE ALHMDLLH ALLAH ABUN GODIYA NAGODE SOSAI MASOYANA ALLAH YA BAR KAUNA DUKANKU I LOVE YOU ALL💋💋💋*

*PAGE NINETEEN*

*********************

A sukwane iya kulu ta fad'a d'akinta, idanunta a rufe taci tuntub'e da kwanon k'anzon da ta karkare a jikin tukunyar abincin da su inna hure suka dafa, tana ganin mutane sun watse ta fito da sand'a ta karkare k'anzon tayi saurin shigewa d'aki don kar wani ya ganta, amma tana shiga d'akin loma d'aya da tayi dak'yar ta samu ta had'iye, ta tasa abincin a gaba tana kallo, saboda halin da take a ciki ma yasa taji bata iya cin abinci,  yunwar ma ta tafiyarta ta dangware abincin nan a tsakiyar d'aki saboda haushin kowa da takeji.

Aiko shigowarta a d'akin ido a rufe, at mance shaf da kwanon abincin dake tsakiyar d'akin, ta shura shi da k'arfi kwanon har sai da yayi sama,sannan ya dawo,  bai tashi fad'awa a ko'ina ba sai a saman goshinta, yace: "k'wall!!".

Ba shiri ta dafe goshin tace:

"Wayyo ni 'yarkuluwa karuwa zata sa in halaka"

Ta samu gefen gadonta ta zauna, tana murza goshin, zafi biyu da biyu ga na zuciya gana fili, kafin kace me goshi ya haye, har ya kumbure, aiko bak'in ciki ya k'ara shigarta, musamman da ta tuno abunda idanunta suka gano, wanda majigin photonsu sai yawo yake a idanunta, ba shiri ta k'walla kuwwar kiran sunan Dada tace:

"Wayyo Dada, ki dawo kiga cin kashin da Ayuba yake yimani, daman ashe ganin idanunki ne yake mutumin kirki, Wayyo Dada zan ari bakinki in tsine masu gaba d'ai shida tsohuwar karuwar shi, subi dare su b'ace b'at a shafe labarinsu, na tsane su na tsani kowa na duniya tunda babu mai sona sai ke, gashi ke kuma k'asa ta shafe idanunki, wayyo ni kaina zuciyata zata buga idan ban d'auki matakin gaggawa ba, wallahi duk hanyar da zanbi sai na bita, ko don insami salama a zuciyata, idan ba haka ba wallahi ina gaf da haukacewa inbi duniya"

Aiko 'yar kuluwa ta fara kuka kashirb'in, har da su gurje gurje,  ita kad'ai a cikin d'aki ba wanda yasan abunda takeyi, har sai da ta gaji don kanta sannan tayi shiru.

Zuciyarta ta kitsa mata ta d'auki matakin kashe izzatu kawai, ko don ta rama cin zarafin da malam yayi mata, na auro tsohuwar kilaki ya kawo a cikin gidan aurenta.

Aiko a cikin zafin nama ta zabura,  taje ta lalabo sharb'eb'iyar wuk'a ta nufi d'akin Dada,  inda dasu Garzali suke kwana akayi dace basu rufe d'akin ba.

 Tana zuwa ta baza idanuwa ko'ina bata ga izzatu ba, a cikin jin haushi ta kaiwa Garzali wani shuri da k'afa, a zabure ya falka, ya fara waige waige, bai tantance ba yaji saukar wani bahagon mari a kan fuskarshi, da sauri ya mik'e tsaye yana kallonta a cikin mamaki,  kafin yace wani abu ta rigashi,  ta hanyar tambayarsa ina izzatu, a cikin tsoro da fargaba, yana in ina yace:

"Tana d'akin Mama"

Iya kulu saboda son ta aiwatar da nufinta, bata bi ta kan Garzali ba, da ya kira hassatu mama ba, ta fita fuu kamar wata bajimar zakanya, jikinta har rawa yakeyi ta kai d'akin.

Garzali yana ganin fitarta, yazo da sauri ya rufe k'ofar d'akinsu, dafe da k'irjin shi, don idan har ba idanunshi bane ba,  ya hango kamar wuk'a a bayanta ta b'oye.

🙀🙀🙀🙀Ku kawo agaji iya kulu zatayi kisan kai😢

Kuyi manage wlh banida caji wanga ma dakyar na kukuta nayi  maku typing🤦🏻‍♀️

Akafta☹

D/Auta ce😉

[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*MY FANS BANDA BAKIN DA ZAN GODE MAKU AMMA KUSANI COMMENT'S DINKU YANA SANI FARIN CIKI BA KADAN BA INA JIN DADIN ADDU'O'INKU A GARENI NAGODE SOSAI ALLAH YA BAR ZUMUNCI👍🏻🤝🏻*

*PAGE TWENTY*

**********************

Koda iya takai k'ofar d'akin hassatu, ba shiri taja burki, ganin k'ofar rufe ruf, abun mamaki harda su guzurin saka kwad'd'o, dole taja baya tana huci.

Garzali dake jikin k'ofar d'akinsu, ya fad'a tunanin ya fita ko ya k'ara mak'alewa, wata ziciyar tace dashi:

"wuka ғa ce a нannunтa кuмa тana тaмвayar ιna ιzzaтu wayyo allaн вa d'aι кasнeтa zaтa yι вa мu sнιga uкu"

Aiko ba shiri  ya bud'e k'ofar da k'arfi, har sai da Abu dake bacci ya zabura, saboda tsoron da yaji, aiko ganin Garzali ya fita shima ya biyo sa a baya, domin yaga me Garzali zaiyi a waje a cikin wannan dare, saboda sun saba idan zasu fito fitsari, a tare suke fitowa, d'aya ya rako d'aya, aranshi yace kodai kashi ne ya kora shi, shiyasa ya biyo bayanshi.

Iya kulu dake a tsaye bakin k'ofar hassatu tana huci, sai kace wata kububuwa, tana jin motsi a bayanta ta juya da k'arfi takai suka da wuk'ar.

Garzali dake bayanta yayi sauri yayi tsalle, har ya ture Abu dake bayanshi shima suka fad'i

k'asa a tare, amman a cikin rashin sa'a sai da wuk'ar ta yanki gefen cikin Abu, aiko ba shiri ya k'walla k'ara, don yaji zafin yankan har a cikin k'wak'walwarshi, da sauri ya dafe inda iya kulu ta yankesa, aiko saiga jini yana ta b'ub'b'ugowa, kamar an kunna famfo.

Garzali ko k'arar da yaji Abu yayi, ta kid'imesa ya tashi ya zuba da gudu sai k'ofar gida, yana kuwwa a kawo masu d'auki iya ta kashe Abu.

Iya kulu kam tana k'yall ido taga aika aikar da tayi, ba shiri ta jefar da wuk'ar ta aza hannu a kai ta fara kuwwar kiran sunan Abu, a d'ari ta nufi wajen shi, ta rungume tana wani marayan kuka, da taga jinin yaki tsayawa, jikinta yana rawa ta fisge d'ankwalinta, ta d'aure gefen cikin, Abu ya k'ara kurma kuka, ganin haka itama  iya kulu ta k'ara sautin kukanta tana sambatun kiran sunan Abu, wai yayi hak'uri bata zaci shi bane.

 Malam da hassatu kam suna tsaka da farantawa juna rai, suka jiyo kuwwa da kuka yana tashi a tsakar gidan, ba shiri malam ya zura rigarshi ya bud'e d'aki ya fito, Hassatu ma ta kimtsa ta biyo bayanshi.

Malam yana fitowa, yayi arba da iya kulu rungume da Abu tana kuka, a cikin mamaki ya k'arasa wajen da suke,  kafin yayi magana sai ga zugar mutanen k'auyen sun shigo gidan, Garzali yana gaba suna bayanshi,  kowa da abun bugunshi a hannu, mamaki ya k'ara kama malam, idon shi akan Garzali yace:

"Wai meke faruwa ne?"

Garzali ya kalli Abu dake murd'e murd'en zafi, ya kalli iya kulu dake kuka na tashin hankali, ba shiri wani kuka yazo masa bakinshi yana rawa yace:

"Aljannun iya ne suka tashi, suka d'auko wuk'a sukace sai sun kasheta, to shine Abu ya fito fitsari yaga zata sokawa kanta wuk'a yazo hanawa suka yankeshi a gefen cikinsa, gashinan jini yana ta zuba amm...."

Kafin Garzali yakai k'arshen maganarshi ne, wani ya cira kulki ya makawa iya kulu and baya, aiko kamar had'in baki, wasu daga cikin zugar 'yan k'auyen suka yita laftar iya kulu da sandunansu, iya kulu da taji zafin duka a d'imauce ta fara kiran:

"Yanzu nice ba su bane, Wallahi nice ba su bane, su sun wuce ni kad'ai ce suka bari, sune suka aikata suka tsere, wayyo ni kuyiman rai, na tuba bazan sake ba, in har na sake ku cemani ba 'yar kuluwa ba"

Da k'yar malam ya dakatar dasu, don wasu har sun fara kiran akashe shegiya kawai a huta, aljanun k'arya ne, bak'in kishi ne, malam yana jin lafuzzansu ya fara yimasu bayanin cewa da gaske tana da aljanu sune suka sakata wannan aika aikar, don in sun tashi a kullum lafazinsu kenan sai sun kasheta.

Kande dake tsaye tana kallo,  ba shiri ta dafe bakin tana dariyar k'eta.

Jikin 'yan garin yayi sanyi, domin sun yarda da maganar malam d'ari bisa d'ari, sanin da suka yimasa mutum ne mai gaskiya, sannan gashi mijinta ne, dole ne yafisu sanin wacece ita, aiko suka fara bada hak'uri, acikinsu akwai mai bada maganin miki, aka rakashi yaje gida ya d'auko kayan aikinshi irin na gargajiya, ya fara duba Abu.

A cikin k'warewa ya tsaida jinin dake zuba, sannan ya saka magani a wurin yankan, sai aka jik'a masa wani yasha, sannan ya fara rage jin zafin rad'ad'in yankan ya daina kuka.

Sannan sukayi sallama da malam suka fara ficewa, Malam yayi hamdala tareda godiya a wurin mai maganin, shima sukayi sai da safe ya fice, Garzali yaje ya rufo gidan ya dawo.

Malam da Garzali suka rik'a Abu a hankali suka kaishi d'akinsu, Malam ya tofesu da addu'o'i sannan yace da Garzali ya rufe d'akin, a gabansh ya rufe sannan ya juyo zai shige d'akinshi batareda ya kalli ko gefen da iya kulu take ba, ya shige abunshi, hassatu dake tsaye cike da mamakin wannan abu da ya faru, ta sauke ajiyar zuciya, ta saka ma bud'i ta bud'e d'akinta, ta shige ta k'ara saka makullin ta dantse.

Iya kulu kam tana nan a tsaye ko motsawa ta kasa yi, saboda jikinta gaba d'aya ciyo yake yi mata, saboda mazgar da tasha bilhak'k'i da gaskiya, ga goshinta ya k'ara suntumewa, ga hannunta da take tsammanin ma ya goce,saboda wani dukan da aka kawo mata, ta saka hannun ta tare, ba shiri taji hannun yace k'ut!.

Tun a nan taji ta jimu, ba shiri wani marayan kuka yazo mata, sai Allah ya isa takeyi a cikin zuciyarta, da taga tsayin ba zai fisheta ba, dole taja jikinta tana d'ingishi ta shige d'akinta, sai k'ara tsinewa hassatu da izzatu takeyi a cikin ranta, ta k'ara cin alwashin sai taga bayasu dukansu, tunda suka sakata ta aikatawa d'anta mafi soyuwa a zuciyarta, sannan ga dukan da tasha ba zato ba tsammani.

A zuciyarta tace:

"Ai duk munafukin cen ne ya jaza man, da yaje ya kwaso zugar mutane don suzo su kassarani, su kaini barzahu ba tareda na shirya ba".

A haka dai dukansu suka kwana zuciyoyi ba dad'i, koda safiya ta waye, iya kulu jiki yayi tsami, ko sallah ma dak'yar ta samu tayi, tana nan a kwance tana jinyar jiki, hassatu tayi sallama tana rik'e da hannun izzatu sunci kwalliya irinta 'yan birni  gwanin sha'awa, iya kulu tana k'yalla ido ta hango su, wani mak'ok'on bakin ciki ya tokareta a mak'oshi, dak'yar ta had'iye miyau ta b'ata fuska, hassatu ta k'araso ta zauna akan gadon da iya kulu take kwance, ta jawo izzatu ta aza akan cinyarta, ta feshe iya kulu da wani munafukin murmushi tace:

"Sannu uwargida ya jikin Allah ya k'ara tsare gaba"

Tana k'are zancenta, bata jira taji me iya kulun zata ce ba,  ta mik'e tsam ta jawo izzatu suka fita, Iya kulu ta bisu da wata gawutacciyar harara, tayi tsaki ta juya kwanci, a cikin muryar mara lafiya tace:

"Shegu biyu sai nayi maganinku, muga k'arshen dwandi"

Kuzo muje dubo iya kulu🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️a aza mata ruwan zafi ta gasa jikinta🤪

Akafta🤭

D/Auta ce🥴
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*INA GODIYA MY FAN'S 👍🏻👍🏻👍🏻*

*PAGE TWENTY ONE*

**********************

Shikam Garzali yana cen yana ta faman lallab'a Abu dake borin wai iya kulu tak'i zuwa ta dubashi, bayan itace tayi silar shigar sa a cikin matsalar,ana cikin haka ne Malam ya shigo tareda hassatu, suka dubashi, hassatu ta tausaya masa sosai ganin yanda yake ta fama.

Ba shiri ta fita sai gata ta dawo hannunta rik'e da flack's tareda izzatu da ta d'auko biredi, hassatu tace da Garzali ya had'a masu shayin su sha su k'oshi, aiko ba b'ata lokaci Garzali ya

samo kofuka ya tsiyaya masu shayin, saboda an riga an had'a shi kafin a kawo masu, aiko suka saki jiki suka sha abunsu suka k'oshi, sannan Abu ya daina borin rashin zuwan iya, ashe daman yunwa ce take cinsa, malam ya samu wuri ya zauna, yana k'ara tambayarshi ya jiki?, hassaru ma tayi masa ya jiki ta jawo izzatu suka fito, to a lokacin ne taje d'akin iya kulun.

Bayan fitar hassatu malam ya gyara zama ya kalli Garzali yace:

"garin yaya mahaukaciyar uwarku, tayi wannan karen aikin?don nasan ba wani aljannu da take dasu"

Garzali kam jiki a sanyaye, ya fara baiwa malam labarin duk abunda ya sani, har ya kai k'arshen zanceshi, malam bai katse sa ba, saboda wani firgicin da ya shiga, tareda tunanin ta ina zai shawo kan wannan rashin hankali na 'yar kuluwa?.

Gashi aurensu, aure ne kamar na zobe ba'a rabuwa, saboda yana son ya cika wasiyyar da Dada ta bar masa, akan duk tsanani kada ya rabu da ita, to shin ta wace hanya ce zai horata har ta gano Annabi ya faku?,

Shi ba abun ya turata gidansu ba, ace saboda ganin yayi amarya ne, yasa zai fara cin amanarta ya yi mata wulak'anci, amman duk da haka zai tauna takuwa ko don aya taji tsoro, don bazai zura ido ba har watarana taje ta jawo masu abunda dukansu zasu shiga uku ba.

Yana k'are wannan tunani, ya tashi tsam ya nufi d'akin iya kulu, fuskarsa shimfid'e da b'acin rai, yayi sallama har sau biyu yaji shiru, iya kulu tana ta sharar baccinta, a ta uku ne ya fad'a ya d'aga murya da k'arfi, aiko ba shiri ta zabura tana fad'in :

"Sai na kashe ku, duk ku biyu d'in, ba wanda zan bari a cikinku"

Malam yana jin lafazinta ya gano inda zancenta ya dosa, aiko a cikin zafin nama yayi tattaki ya zabga mata wani jarumin mari har sai da taga wasu tauraru, aiko ba shiri iya kulu baccin dake idanunta ya wartsake, ta dafe kumci, tana kallonshi da mamaki akan fuskarta tace:

"Yanzu malam baka ji kunyar d'aga yatsunka biyar da Allah ya halitta maka ba ka saukesu akan fuskar amanar da Dada ta bar maka ba?"

A cikin fushi yace :

"Ank'i a ji kunyar, ke kinsan kunyar kika aikata abunda kikayi a jiya, iya rashin kunya ta sauka a kanki, tunda har kikaso ki kashe d'an da kika haifa da cikinki saboda kishi, kishi hauka ne?, da hankalinki zai b'ace har ki tabka rashin imanin da zakizo kina da kinsani?, haka kawai ki saka mutane shiga a bakin duniya?, to wallahi kinyi na farko kinyi na k'arshe kika k'ara bari makamancin haka ya k'ara faruwa, wallahi sai na shayar dake gubar mamaki, don bazanji kunyar tsinke duka igiyoyina dake kanki ba"

Ba shiri iya kulu ta fashe da kuka tace:

"Ba shi nayi niyya ba, tsautsayi ne kawai ya hau kanshi, amman wallahi nayi danasani da wuk'ar ta yanki  Abu, don ba shi nayi niyyar yankawa ba, azal ce ta fad'a kanshi "
Malam ya bita da kallon takaici yace:

"Me yasa ke k'wak'walwarki take ta kifi ne?, ke a ganinki Allah zai barki ki, kiyita cutar yarinyar mutane?, kin mance maganar da na fad'a maki ko a ranar kenan?, to Alhmdllh da reshe ya juye da mujiya, ko don ya zama iznah a gareki akan idan kin tashi gina ramenki na mugunta, to sai KI ginashi a gajere, don idan kikayi wasa kece zaki rufta a ciki, don yanzu ma ga zahiri kin gani, kin yanka d'anki kinsha duka, ga hannunki nan a kumbure, duk akan haukar ki k'waya d'aya tak, in kunne yaji jiki ya tsira, amman kisani  daga yau bazan sake d'aga maki k'afa ba, da kinyi abu kad'an zanyita jibgarki, tunda naga har jikinki yana shanye dukan k'attin maza, to balle nawa k'waya d'aya tak!, saboda haka ki kiyayi lokacin da zan sauke k'wanji na a kanki"

Yana k'are maganar ya fita, ba tareda ya jira yaji abunda zata fad'a ba, aikam iya kulu ta fara kururuwar kiran sunan Dada tana sambatun fadin:

"Nikam dai 'yar kuluwa,  mutuwa tayiman yankan k'auna, da ta d'auke mani Dada ta barni a duniyar ina ta ganin tasku iri iri, wayyo ni Allah na duniya meyasa kika yimani d'aurin huhun goro?"

Haka tayita sambatun ta har saida malam ya dawo tareda mai gyara, ya gyara mata gocewar tana ta ihu tana b'arin hauka, bayan ank'are yimata gyaran ne, ta lallab'a ta dubo Abu da jikinshi, sannan ta koma d'aki ta dunk'ule akan gado tana ta kukan zuci.

**

Bayan sati d'aya iya ta murmure garas, Abu ma yaji sauk'i sosai, malam kam da shi da 'yarshi izzatu har k'iba naga sun k'ara, kwanciyar hankali ya samu a gidan, don iya kulu ta rage wannan duk wasu miyagun halaye nata, ta zama wata saliha ko magana bata sonyi, amma fa kar ku zaci ta shiryu a'a, tunda kande tazo dubata ne, da suka k'ule d'aki sukayi ta k'us k'us, tun daga ranar ta zama haka, bata kula duk wata rawar kai da hassatu da Malam sukeyi a gidan, illah ta bisu da wata gwarzuwar harara tayi kyafci, izzatu kam da ta kuskura ta matsa a kusa da ita ba wani d'aga k'afa, take saka hannu ta make ta tayi saurin barin wajen sai dai aji kukan izzatu, a tambayeta me akayi tace IYA ce.

**

Sati biyu da zuwan hassatu, ta fara cukucukun maida Garzali da Abu makarantar boko, wadda shi garzali har ya k'are primaryn dake  nan a cikin k'auyen nasu, don daman cen d'iyan k'auyen iyakacinsu primary sun k'are karatun, ko ita d'in tsiraru ne suke jurar har su gama, wasu daga aji

biyu ko uku sai a watsar, Alhmdllh shi Garzali ya k'are, Abu ne kawai bai k'are ba, aiko tasaka malam ya maida Abu and makarantar domin ya k'arasa, sannan aka saka izzatu itama.

Duk da ita kanta hassatun iyakarta prmary d'in, amma yanda taje birni taga ana fad'i tashi d'a karatu, sai abun ya dinga burgeta, tayita sha'awar Allah ya bata haihuwa, ko don yaran su samu ilimin da ita bata samu ba, sai gashi har mijinta ya rasu bata sami haihuwa dashi ba.

To shine yanzu tayi sha'awar su Garzali su sami ilimin suma koda zasu tallafi 'yan k'auyen nasu, watarana ayi alfakhari da samun irinsu a k'auyen, musamman da taga Garzali yana son karatun sosai, sab'anin Abu da komi bai sani ba a bokon,   tunda ba kullum yake zuwa ba, sai yayi wata baije ba, kuma malam ba zama gidan yakeyi ba, yana cen yawon cin kasuwanshi, k'auyukan dake mak'otaka dasu, ita kuma iya kulu bata matsa masa akan sai yaje, Dada ma ba sanin ta kan bokon tayi ba,  balle ta saka baki akan sai yaje.
Garzali dake zuwan ma,ra'ayinsa ne ba mai cewa tafi makaranta.

Aiko hassatu ta baiwa malam shawarar a saka Garzali makarantar gaba da primary a cen birni, ba musu malam ya amince, sai dai ya nuna mata aljihunshi fa ba nauyin da zai iya d'aukar karatun Garzali zuwa birni, tace bakomi ita ya barta zata in da matsalar karatun, kawai dai yaji da abunda zai ciyar da su.

Kasancewar hassatu ta sami gadon kud'i da kadarori a wurin mijinta na farko, bata sha wuya ba wajen saka Garzali a wata makarantar kud'i dake birni ba, inda ta kasance ta kwana ce,ta hanyar wata mak'ociyar su a cen birnin  da ta kasance malama a makarantar.

Ansha gawurtaccen daru a wurin  iya kulu akan cewa,  ba wanda zai kai mata d'a a birni a saida shi, haka kawai a yanka kanshi batada labari, har saida malam ya nuna k'arfin ikonsa akan Garzali, sannan ta amince yaje, amma da kuka wiwi suka rabu.

Sai yazo zai fita, taje da gudu ta rik'eshi tana kuka, wai ya jira tayi masa ganin bankwana, sai da malam yaga abun nata yayi yawa, sannan yaja Garzali suka fita,  wanda shima kukan yakeyi kashirb'an,  ganin yanda za'a rabashi da izzatunsa ya daina ganinta, itama kukan takeyi, saboda taga yana kuka shiyasa itama sai ta fara kukan,  saboda shak'uwar dake a tsakaninsu.

Bayan fitar malam da Garzali ne, iya kulu ta fara yiwa hassatu tujara tana cewa:

"Duk bak'in cikin tanda sai munci waina, wato gurinki ki salwantar man da yaro, tunda kinga ke ba haihuwar zakiyi ba, to ko ni yanzu kasuwa ta watse ai d'ankoli yaci riba, don na haihu uku, ke ko fa nawa kikayi?, sai dai kije masai ki dinga tula k'aton kashi, amma haihuwa sai dai kiga mata sunayi, a hayye nanaye sama tayiwa yaro nisa sai dai ya d'aga kai yayi kallo, kuma wallahi ki sani duk abunda ya sami yarona banyafe maki ba, kuma wallahi in zan tafi zindir, saboda rashin zanen d'aurawa sai nayi shari'a dake"

Anya iya kulu🤔

Akafta😅 amma fa kusani har yanzu muna akan shinfid'ar labarin akwai sauran rina a kaba muje zuwa my gay's 🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️

D/Auta ce😘
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*______________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*________________________________________*

*MY FAN'S GA TAKU 👍🏻👍🏻I LOVE YOU ALL IRIN TRILLION DINNAN❤️❤️❤️❤️❤️❤️❤️❤️❤️❤️❤️❤️💋💋💃*

*TWENTY TWO*

*********************

Hassatu kam ko kallo iya kulu,  bata ishet ba ma balle at kulata, a cikin ranta tace:

"Sakarya bazaki gane taimakon ki akayi ba sai a gaba"

A haka aka ci gaba da zaman k'ek'e da k'ek'e a tsakanin malam da iya kulu, k'iris tayi sai ya nuna mata kuskurenta, tayita masifa akan cewa baya sonta ya tsaneta, idan har ya gaji da ita ya sauwak'e mata, amma malam kam ya biyeta suyi tayi, har ya nuna mata darajar cewa, ai darajar wasiyyar Dada taci da yanzu tuni yayi maganinta, tanajin haka zatayi muk'us ba shiri.

Amma fa kam kande shawarar da ta bata,  akan ta bi bokaye ta k'wato mijinta, sannan ta kora hassatu da izzatu su bar gidan, aiko shawarar tayi tasiri a kanta, domin kuwa a sace sukaje wajen wani boka itada kanden, suka karb'o kayan surkullensu suka yo gida.

 Iya kulu ta bada himma akan aiwatar da abunda akace mata, amma duk ta k'ulla mugun abunta, sai malam ko mama hassatu sun wargaza mata tsari, duk da basuda masaniya da abunda take k'ulla masu, wani zubin itama ce da kanta take lalace abun, saboda mantuwar da takeyi, akan ta yaya zatayi amfani da surkullen, har sai ta aikata shirmenta, sannan ta tuno ba haka aka ce ba, tayi ra jin haushin me yasa tayi kaza.

Hassatu kam dariya shirmen iya kulu yake sakata, ta maidata mahaukaciya,  tayi amfani da damar da ta samu ta mallake malam tass ba boka ba malam, izzatu ma malam ya sakata a makarantar primary dake k'auyen, da kanshi yake kaita har aji, idan zaije cin kasuwarsa sai yaga ta zauna a cikin ajin sannan ya tafi wurin sabgoginsa.

Garzali kam ana cen an duk'afa karatu ba kama hannun yaro,duk ranar visiting malam sai yaje masa, tareda duk abunda duk abunda Allah ya hore, wani zubin Ma har da izzatu da Mama hassatu sai sunje, Abu kam da iya kulu cewa sukeyi basu zuwa kar aje a yanke masu kai a banza.

Shekaru sunja da dad'i ba ba dad'i, har Garzali ya jajirce  ya k'are secondary, yayin da a lokacin ne itama izzatu ta k'are primary zata je secondary a birni, amma malam yace sam baisan da zancen ba, wanda har hatsaniya taso ta shiga a tsakaninshi da mama hassatu, don shi kam tsoron shi d'aya ne, iyayen izzatu su ganta su k'wace 'yarsu, bayan su shak'u da ita.

Rikici yayi tsamari har hassatu tayi fushi ta koma gidansu da zama, malam ya d'au zafi yace idan dai akan izzatu sai taje birni karatu ne,  take fushi,har ta koma gida, to tasha zamanta.

Iya kulu sai murna takeyi tana jin dadi tana tunanin, bokanta ne yayi aiki a kansu.

Aiko rashin hassatu a gidan ya saka shiga izzatu a cikin matsalolin iya kulu, wanda jira kawai takeyi  malam ya bar gidan, aiki kala kala take sakata, daga wannan sai wannan,  kasanceawar a lokacin girma ya fara bayyana a jikinta, mak'erin 'yanmata ya fara bayyana irin tsantsar halittar da ubangiji yayi mata.

Izzatu fara ce tass mai surki jaja jaja, gata da hanci santam kamar biro, ga idanuwa darara masu d'auke hankalin wanda ta kalla, gata da d'an k'aramin bakinta gwanin sha'awa, ga gashi har gadon bayanta bak'i sid'ik, gata dirarrar mace son kowa, wadda a kallo d'aya idan kika mata, zaki gano idan ta k'ara shekaru ta zama cikakkiyar 'yanmata, za'ayi mace mai suna mace a wurin,.

Amman duk da wannan tsantsar kyaun da Allah ya wadaceta dashi, iya kulu bata ko son ganinta, saboda k'iyayyar da take mata, shiyasa a yini zungur a bautar iya kulu take k'are shi, idan dare yayi ta kwanta tayita juye juye, jiki yayi tsami, da abun yayi mata dad'i ma har da talla ta tsira d'orawa izzatu.

Idan ta fita yaran k'auyen suyi ta kiranta da sunan ruwa da k'ank'ara, saboda sunan da iya da Abu suke kiranta dashi kenan, abun yayi ta bata mamaki,saboda ita dai tasan sunanta izzatu, to miye ma'anar sunan da wasu suke kiranta dashi wai RUWA DA KANKARA, saboda ita a iya saninta Mama hassatu ce ta haifeta, malam ne babanta.

Saboda tun kawo hassatu a gidan yaja hankalin iya kulu da kowa na gidan,  akan koda wasa bai lamunta a nunawa izzatu ba shine ya haifeta ba, shiyasa duk izgilin iya kulu bata yarda ta furta cewa ba hassatu ce ta haifi izzatu ba, shiyasa hankalinta ya natsu da cewa su malam ne suka haifeta.

A duk lokacin da ta d'auki tallar, bata zuwa ko'ina sai wata daba ta matasan k'auyen, inda wajen ya zama kamar wata 'yar k'aramar  kasuwa, da taje da tallar maza suyi mata rumfa su saye, masu jawo mata hijabi daban, masu yimata kalaman banza ma daban, a haka zata baro kasuwar tana kuka, tazo gida ta fad'awa iya kulu, amma bai hana ta k'ara loda mata wata tallar, haka zata d'auki tallar tana kuka har taje ta saida ta dawo.

Duk wainar da ake toyawa malam baida labari, shiyasa take ta cin karenta babu babbaka, saboda a d'an tsukin lokacin malam idan ta fita sai dare yake dawowa, saboda takaicin hassatu da take fushi dashi, kuma ya kasa zuwa yayi bikonta ta dawo, 'yan k'auyen har sun fara yimata Allah ya k'ara, suna ta yimata habaici kala kala, amma duk ta saka auduga ta toshe kunnuwanta, saboda son tsakani da Allah take yiwa Malam, duk wani kushe da mutane sukeyi, bata bi takai.

Izzatu tana a cikin wannan halin ne, ta d'auko talla zataje kasuwar, akan hanyarta tane wasu samari su biyu suka b'oye a cikin duhun gero da yayi tsayi  a wata gona, tana tafe tana 'yar wak'arta sai kawai taji motsi a bayanta, da sauri ta juya, aiko tana hango su Dahiru roja, ta dafe tallarta ta balbala da gudu, aiko suka bita suma, kafin kace me har sun cimmata sun cafko ta, ba shiri ta fara kuwwar neman ceto, Roja yana dariya yace:

"Yau sai munga me kike b'oyewa a cikin zane, da bazaki bari mu tab'a ko gyalenki ne muji sanyi ba, to yau dai yasin ko ina sai mun lagude a jikinki, wannan jiki haka luguf bazamu bari muyita

had'iyar miyau a banza ba"

Yana k'are maganar ya kai hannu da nufin ya  cire mata hijabi ne, yaci saukar wani bahagon duka a fuskarshi, ba shiri ya rafka k'ara.

Da sauri izzatu ta waiga, saiga wani bawan Allah mai siffar majiya k'arfi, da sauri tayi bayansa ta b'oye jikinta yana ta rawa, tana kiran sunan Mama hassatu.

A cikin fushi wannan mutumin ya saki k'wanji yayita jibgar su roja, saida yayi masu ligya ligya sannan yasaka su rankaya and na kare, bayan yayi masu kashedi da idan suka kuskura suja maimaita, to ba su ba har iyayensu sai sunyi zaman kaso a birni.

Ya dawo akan izzatu ya tambayeta me yahad'ata dasu tayi masa bayanin duk abunda suke yimata idan taje tallar, a cikin jimami yace da ita, kayan tallar na nawa ne  ake azo mata, ta fad'a masa ya saye kayan kaf ya bata kud'in har da rarar canjin sama, yace da ita a kullum ta dauko tallar ta tsaya a dai dai nan inda suke zaizo ya dinga sayewa tana komawa gida ba sai taje kasuwar ba, aiko izzatu taji dad'i tana ta murna tana godiya, don dama ba son tallar takeyi ba, don ba yanda zatayi ne shiyasa, idan ta sulale taje wurin mamarta hassatu tana kuka ta fad'a mata komi harda abunda 'yan iskan samarin suke yimata, sai tace tayi hak'uri na d'an lokaci ne ta kusa dawowa, amma fa baza masu samata idanuwa a tarbiyyar izzatu,a cen kasuwar don wani zubin har dambacewa akeyi a tsakanin wad'anda  da hassatu take biya kud'i akan kula mata da izzatu, shiyasa suka daina takurata a cen wurin tallar sai ga abunda ya faru a yanzu har wannan bawan Allahn ya taimaketa ya garfad'eta sosai akan kar ta fad'awa kowa tayi shiru taimakon rayuwarta zaiyi a tsakani da Allah bazai cutar da ita ba.

Suka rabu da wannan bawan Allah, shi a cikin matsananciyar damuwa wadda sai da ta saka shi zubda hawaye, ita kuma ta tafi tana ta murnar jin za'a dinga saye mata sana'arta a kullum ta d'auko.

Haka ko aka dinga yi a kullum ta d'auko, shine zai saye ya bata kud'inta cas, ta koma gida, iya kulu sai murna akeyi ganin kud'in dake shigota, amman duk da hakanan bata tab'a tambayar ta a ina yimata juyen tallar ba, saboda ita kud'in ne kawai a gabanta ba tarbiyyar izzatu ba, don inta itace ma anhad'e ba'a farkata biyu ba k'arewar fyad'e.

Izzatu tabi ta rame haskenta ya fara dusashewa saboda azabar da iya take bata, tallah kuma a kullum idan batayi biyu ba zatayi uku, kuma duk wannan bawan Allahn yake sayarwa, har saida masu kula da izzatu suka je suka sanar da hassatun izzatu ta daina zuwa tallah, taji dad'in dainawar da tayi, amma tace su dinga lura da shige da ficenta a k'auyen, aiko a kwana biyu sukaje suka sanar da ita wannan bawan Allah dake yima juyen, hankalin hassatu ya tashi da kanta taje taga mutumin, duba da yanayinshi da tayi ta gano baya kama da mutumin banza, ainahi ma har wani kwarjini yayi mata, amman duk da haka taja kunnenshi sosai tareda gargad'i akan basu buk'atar abunda yakeyi ya daina, a cikin magana mai dad'i hassatu ta fahimtar dashi, yaji dad'i kuma ya amince da hujjojinta, suka rabu a cikin mutunci, yana mai jinsa kansa da wani

farinciki da jin dad'i.

Oni dije shi kuma wannan mutumin wanene???

Shin malam zaije bikon hassatu ta dawo ko ya abun yake????.

Zai amince da zuwan izzatu karatu a birni ko yaya???.

Akwai gumurzu a k'asa fa domin kuwa idan har ya sake ta taje birnin to daga lokacin ne wasar zai fara ku biyoni domin kuji labarin RUWA DA KANKARA💃🏃‍♀️🏃‍♀️.

Wanda duk yaji dadin wannan page tayiwa mummyta addu'a Allah ya maidata gida lfy.

akafta💃

D/Auta ce😉
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*_______________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsap
p
*________________________________________*

*NAGODE DA COMMENT'S DIN KU TAREDA ADDU'O'IN KU GA MUMMY ALLAH YA BAR ZUMUNCI🤝🤝🤝*

Hassatu suna kan hanya itada izzatu, sai faman fad'a take ta yimata, saboda k'arancin wayonta a lokacin, ya kasa hango mata illar, abunda mama hassatu take son ta fahimtar da ita, duk da ita kanta hassatu bata ga alamun rashin gaskiya a tattare dashi ba, duk da karin maganar da bahaushe yake fad'a ta cewa; MUGU BAIDA KAMA.

Izzatu kam ba wayo, sai zubawa hassatu labarin mutuncin da yake yimata takeyi, tana tafiya tana ta tsalle tace:

"Wallahi mama yanada mutunci, nidai bazai yiman komi ba"

Hassatu tace:

To naji, amma ki kiyaye, ko ma wanene kar ki bari ya k'ara tareki a hanya yana yimaki juyen, tallar ma insha Allahu kin kusa dainata, gaba d'aya a huta.

Saida hassatu ta rakata har kwanar gidansu, sannan ta juya tayi gidan mai unguwa, ba b'ata lokaci ta samu ganinshi, bayan sun gaisa ne, tayi masa bayanin abunda ya kawota a cikin mutuncin da suke ganin juna dashi, kasancewar shi shugaba a garin, ita kuma matar aure, a ladafce tayi masa bayanin tallar da iya kulu take d'orwa izzatu, wadda shi malam bai ma san tana yi ba, saboda rashin zaman gidan da baya yi, ta nuna masa tana so akira malam, domin a sanar dashi abunda yake faruwa, saboda ya hana a k'ara d'orawa izzatu tallar, amma ta nemi alfarmar a sakaya sunanta a yayin da za'a yimasa bayani.

Mai unguwa yaji dad'in abunda Mama hassatu tayi, saboda shima yaji labarin tallar da izzatun ke yi, kuma yanada niyyar tsawatarwa akan hakan, amma yana jin nauyin idanun malam, kasancewar rik'on da yayiwa izzatu tsakani da Allah, tareda mahaifiyarshi wato marigayiya Dada, amma yaci alwashin zai kirashi, a cikin magana mai dad'i ya fahimtar dashi, sannan sukayi sallama da juna ta koma gidansu .

Sab'anin da aka samu a ranar, wanda ya hana malam dawowa gida shine, yayi dare a garin da sukaje saboda ruwan da aka tafka, kamar da bakin k'warya, gashi ba abun hawan da zai kawosu k'auyensu, saboda ruwan ya hana duk wani motsin kirki a inda suka ci kasuwar, kayansu ma suna jibge basu saida ba, shine abokan tafiyar suka yanke hukuncin su kwana acen kawai, sai gobe sai suje suci wata kasuwar, dake a kusa da inda suka je d'in, idan sun k'arasa siyar da kayansu, sai su dawo gida a cikin lokaci, dukansu suka aminta da wannan shawara, saboda wani zubin suna kwana acen idan buk'atar hakan ya taso.

Aiko sukayi kwanciyarsu acen, da safe suna k'arewa suka juyo gida, shigar malam keda wuya a cikin k'uyen da zumud'in yaga iyalinshi, sai kawai aka sanar dashi mai unguwa yana nemansa, bai kawo komi a ransa ba ya nufi fada, saboda yasan dai ba abunda ya aikata, sai da izzatu ta fad'o masa a rai ne yaji gabanshi ya fad'i rass, jikinshi yayi sanyi k'alau,  d'an kuzarin dake tare dashi,  na son yaje gida yaga halin da suke a ciki ma, ya nemesa ya rasa, saboda yana jin tsoron ace iyayen izzatu ne suka bayyana.

A haka dai yaja k'afunshi ya nufi fada,  bayan sun gaisa ne a cikin tattausar magana,  mai unguwa yayi masa bayanin abunda ke faruwa a gidanshi, ba tareda yasan anayi ba, malam hankalinshi ya tashi, jikinshi ya d'auki rawa,  sai ga wani jib'i da ya tartsatso masa tun daga kaai har tafin k'afafunshi, acikin b'acin rai yabada hak'uri sannan yace insha Allah zai d'auki mataki akan hakan.

Sannan ya fito ya nufi gida, acikin fushi wanda ke shimfid'e a kan fuskarshi, tun a k'ofar gidan ya jiyo sautin kukan izzatu, tana ta baiwa iya kulu hak'uri,a kan bazata sake ba, a d'ari ya shuri k'ofar gidansu mai lanlanga ba shiri saiga k'ofa a k'asa ta fad'i, don dama katakon yaji jiki canji yake nema, iya kulu kam bata maji k'arar fad'uwar k'ofar ba, saboda hankalinta ya d'auku wajen dukan izzatu da takeyi tana masifa tana cewa:

"Shegiya nice ajalinki, tunda kike so ki k'ulla man salalan tsiya, saboda kin k'ware da munafucci, shine zaki fad'awa mutane kisa abarni da tuwo tsibi guda, ki dawo dashi don kiyiman asarar dukiya,  kinsan ko nawa na kashe da zakije ki jaza man asara to wallahi duk inda zakije ki nemo man kud'ina kije, ni ba abunda ya dameni kud'in kawai na sani ungo ki koma in zaki kwana acen kar ki dawo sai kin sai..."

Maganar ta mak'ale ne a sakamakon, juyowar da tayi tayi ido biyu da malam dake a bayanta, ya rungume hannuwa yana kallon ikon Allah, tareda nanata innalillahi wa'inna ilaihurraji'un a zuciyarshi, don baya son ya sauke duka fushinsa akan iya kulun.

Iya kulu tana ganinsa ta fara rawar jikin yimasa sannu da zuwa, da taga kallon da yake yimata batareda ya tankata ba, sai ta fara borin kunyar cewa :

"Wai fa tuwon dawa na aza mata talla da miya, shine da taje wajen tallar duk wanda yace mata yarinya tuwon mine?, sai tace tuwon dawa, ace miyar miye wai don tana ja'ira sai tace, miyar guro da kuka ce aka had'e, waifa don kawai nazo kad'a miyar guron bai isaba na had'a da kuka, ashe ta gani shine taje ta fallasa don tana asararriya tasa aka k'i siyen tuwon ta dawo dashi, saboda tana son inyi asar.... "

Malam bai bari ta k'arasa zancenta ba,  ya saka k'afa yayi ball da kwanonin tallar tuwon, gaba d'aya miyar da tuwon suka tarwatse a cikin  k'asa, saiga mulmulallen tuwon dawa,  bak'i k'irin da miya a k'asa warwas sun zube, sannan ba b'ata lokaci yayi ciki da iya kulu yana ta kaimata

duka, ta ko ina sauke mata jibga yakeyi, da gudu ta fad'a d'akinta ta rufe, malam yana huci yake fad'in :

"Gara da Allah bai baki haihuwar d'iya mace ba, don kuwa wannan bak'in son kud'in, naki, tsaf zaki maida 'yar jari kina turata tana nemo maki kud'in, haka kawai ki jazawa mutane bala'i, to wannan salon rashin mutuncin naki ba a gidana ba, ki tattaro kayanki ki barman gida, kije cen gidanku har sai na nemeki, zaki fito ko sai na b'alla k'ofar?".

Sumui sumui iya kulu ta bud'e d'aki ta fito, zata fara bashi hak'uri yayi saurin cewa da ita, duk kalmar da zata fito bakinta a lokacin to a bakin aurenta ne.

Aiko jiki ba kuzari taja k'afafu ta fita gidan, tana ta kuka wiwi tabar gidan, kande da ta kasa kunne take saurare tayi shewa ta buga cinya tace:

"K'urunk'us kan d'an b'era"

Izzatu dake rakub'e tana kuka, malam yaje ya tada ita yakaita d'akin hassatu ya tambayeta abunda ya faru, aiko bakinta a sake ta fara yimasa bayanin duk azabar da iya kulu take bata, malam har saida yayi hawaye saboda tausayinta, suna cikin firar ne Garzali ya dawo daga birni, saboda wata jarabawa da yaje yi ta fagen share karatun shiga jami'a direct, da suka zana tsawon sati biyu duk yana cen a birnin, duk wannan badak'alar da akayi, baya gidan yana cen wajen fafutukar zana jarabawar.

Garzali yayi mamaki sosai da yaga baiga, mama hassatu da iya kulu ba, bakinshi yana rawa ya tambayi malam ina sukaje ne?,malam ko saboda damuwowin da suka cunkushe zuciyarsa sunyi masa yawa, ba b'ata lokaci ya fara zayyanawa Garzali abunda ya faru a tsakaninsu duka.

Jin abunda ya faru Garzali hankalinsa yayi k'ololuwar tashi, jiki a mace ya fara baiwa malam hak'uri, akan ya dawo dasu, malam ransa a b'ace yace:

"Koda zanje bikon hassatu ta dawo, to ba zancen zuwan izzatu karatu a birni, 'yar kuluwa kuma sai ta horu, sannan zata dawo a gidannan"

Duk da garzali yaji zafin, abunda iya kulu tayiwa izzatu, amma yaji haushin hukuncin da malam ya yanke mata, amman ya b'oye damuwarsa, ya fara nunawa malam amfanin karatun izzatun, saboda ko halin da take a ciki idan ta samu ilimin, koda ta gano wacece ita daga baya, to damuwar bazata yimata yawa ba in tana da karatunta, zai amfaneta har wasu su amfana da baiwar da Allah ya bata.

Malam ya shiga zurfin tunani na 'yan lokuta, sannan ya d'ago kai yace:

"Koda zan amince da karatun, to sai dai idan zata dinga zuwa ta dawo a kullum ta kwana a gida"

Garzali yayi murmushin jin dad'i, sannan yace:

"Akwai makarantar jeka ka dawo ta 'yanmata zallah za'a iya sakata a cen, amman fa akwai aiki ja, idan akace kullum taje ta dawo, zirga zirgar zai bata wahala sosai"

Malam fuska a had'e yace:

"Abunda na riga naji zan iya kenan, saboda ku taso muje dukanmu,  mu baiwa mamarku hak'uri ta dawo, tunda dama dalilin fushin da takeyi kenan, to anyi abunda takeso sai a zauna lafiya"

Aiko suna zuwa, suka bata hak'uri, duk da taso ta d'an ja aji, amman dai tausayin izzatu da yanda taga malam duk ya rame yasa ta amince zata dawo d'in, don itama a takure take zaman da takeyi, saboda son zama da malam yafi mata komi a rayuwa, haka suka gangamo suka dawo gida, a cikin farin ciki da kewar juna.

Dawowar mama hassatu da kwana biyu ne,  aka fara yiwa izzatu cuku cukun neman makaranta a birni, aka samu wata makarantar kud'i ta 'yanmata zallah aka sakata, mama hassatu ce ta biya kud'in makarantar, a kullum Garzali ne yake rakata makarantar, yayin da shi kuma yake wucewa wajen wani aikin gini da akeyi, yayi dace aka d'aukesa, a yini dubu d'aya ake badawa idan sun k'are, saboda shi iya aikin nasa dai dai lokacin tashin su izzatu makaranta ne sai abashi d'ari biyar, sai  yaje ya d'auko ta  su shiga mota su tafi gida.

Haka sukeyi har lokacin da sakamakon jarabawar su Garzalin ta fito, aka yi dace ya canye duka, inna hassatu ta baiwa malam shawara aka sayar da wata k'aramar gonar shi, ya biyawa Garzali kud'in shiga jami'a, akayi komi a wadace ya tafi University, ya fara karatu a sashen lafiya.

Tafiyar Garzali ta saka wasar zata ta fara bugawa, muje zuwa mutanena yanzu wasa zata fara👭🏃‍♀️⛹‍♀️.

Shin ina iya kulu da Abu?????🤣

Akafa🤺

D/Auta ce
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*___________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp

*___________________________________*

*SORRY MY FAN'S NAYI MANTUWA BANSA NUMBER A PAGE DIN DA NAYI BA🤦🏻‍♀️PAGE 23 NE WANCEN KUYI MAN UZURI KUNSAN RAI AJIZI😥*

*PAGE TWENTY FOUR*

**********************

Iya kulu dai ana cen  tsohon kangon gidansu, kasancewar babanta ya dad'e da  rasuwa,  matar babanta ce a gidan zaune da yaranta, aiko wulakancin da take sha a gidan ba d'an kad'an ba ne, domin kuwa k'annenta samari da masu auren ma a gidan, duk sun rena ta, saboda haushinta da sukeji, musamman wulak'ancin da tayi masu, a lokacin da sukaje bikin mama hassatu da malam, tayi masu rashin mutunci mai degree, 'yan uwanta mata da matan k'annenta da sukaje, aiko suka samu dama suma d'aya bayan d'aya suke ta shikka mata rashin mutunci, sun renata matuk'a gaya, matar babanta ma, ba wani bata raga mata, abu kad'an zaisa tayita jifarta da gori da habaici iri iri, tun iya kulu tana dauriya bata tankawa, har ranar da ta gaji da abunda take yimata, aiko ta fara zagewa tana ramawa, ta saki jiki ta wanke matar babanta tass da soso da sabulu, matar baban ko ta aza hannu akai,  tana ta kuka tana kwakwazon cewa, azo a gani iya kulu ta dake ta, aiko yaranta samari da masu auren dake a gidan zaune da matansu,  sukaji haushi ba tunanin komi suka had'u sukayita jibgar iya kulu,  tana ta kururuwar neman mai ceto, amma ba wanda yazo rabo,  rigima ta kacame a tsakaninsu, saboda Abu yazo ganin iyar ne yaga ana wannan hargitsi, shima ya shiga da nufin ya ramawa iyar dukanta a wurin wani tsarar shi a gidan, aiko shima aka had'a dashi
suka yimasu dukan kawo wuk'a,  har saida sukayi tib'is gaba d'ayansu, aiko kusan rabin k'auyen Suka taru a k'ofar gidan,  sunata kallo suna tsegumin abun, wasu suna yiwa iya kulu Allah ya k'ara, yayinda wasu kuma suka tausaya mata, rigima dai da tayi tsamari har sai da suka garzaya, a fadar mai unguwa saboda ayi masu shari'a,.

Kafin kace me labari ya game k'auyen kaf, malam yaji dad'in faruwar hakan, koda Allah zaisa ta gyaru, duk da yasan cewa da wuya iya kulu ta canza halinta, ita kam mama hassatu ta tausayawa iya kulu, saboda cin zarafin da ake yimata yayi yawa, duk dai halinta ne ke jamata, kuma tak'i ta gano inda matsalarta take sai ta daina.

Iya kulu ta fashewa mai unguwa da kuka, akan ya kira malam a bashi hak'uri ta koma gidan mijinta, saboda tace ita da gidansu haihata haihata, har abada bazata sake zuwa gidan bama balle taje ta zauna.

Mai unguwa yasa aka kira malam ya bashi hak'uri, tareda yi mata jan kunne kala kala,  sannan taci darajar mai unguwar malam ya maida ta gidanshi.

Bayan komawarta ne, ta fara karatun ta nutsu, ba laifi ta rage duk wasu miyagun halaye nata, zamansu lafiya da malam, amma bata shiga sabgar mama hassatu, saboda a ganinta ita mama hassatun ba sonta take yiba tunda tasa aka rabata da d'anta, aka kaishi wata uwa duniya, don kawai bata son ta wayi ido ta ganshi a gidan.

Abu ma da akazo kanshi zaa kaishi secondary tayi ruwa tayi tsaki ta hurewa Abu kunne, akan kar ya amince yaje birnin nan, kashe shi akeso aje ayi, daman cen shi ba makarantar yake so ba, shiyasa da akace za'a kaishi karatun yak'i, yafiso ya biye d'iyan kande suje suyita shiga daji suna sato amfanin gonar mutane, yana kawo mata tana b'oyewa, wasa wasa sai gashi ya fara koyon shaye shaye,  a wurin matasan yaran kande dasu daman cen suna sha, su k'ule daji suyita shaye shayensu, sai sunyi tatil sannan su nufo gari suna mashalo, suje gida suna ta hauka.

A ranar da malam ya ga wannan tashin hankali, ba k'aramin bak'in ciki ya shiga ba, ace a cikin gidanshi a samu d'an shaye shaye, wannan abun kunyar dame yayi kama?, mama hassatu kam da taga ya shigo gidan taganshi a buge, shigewarta d'aki takeyi ta rufe, sai dai tayita jiyo artabunshi da iya kulu, yana ta surfa mata zagi  ta uwa ta uba.

Izzatu ma da ta ganshi bata tsayawa, saboda tana gudun tasha dukan banza, duk da ba zama take yiba a kullum tana makaranta, sai ranar asabar da lahadi shima gidan inna hure take zuwa karatun Allo, saboda mijinta malamine sosai a garin har makaranta gareshi yana koyawa yaran garin karatu.

Ana cikin haka ne inna hassatu ta samu ciki, murna a wurin malam sai kace ba'a tab'a yimasa haihuwar ba, itama mama hassatu taji dad'i ba kad'an ba, suka b'oye abunsu a tsakaninsu, don mama hassatun itace ta rok'i malam,  da yayi shiru har zuwa lokacinda zai fito kowa ya ganshi, saboda tana jin tsoron kaidin iya kulu akan d'an tayin cikinta.

***

Izzatu ce a gefen bakin titin dake garinsu, kasancewar shi babban titi,  sai  motoci ne kawai

suke wucewa, daman tunda Garzali ya tafi karatu, anan take fitowa ta tsaya ta samu abun hawa ya shiga da ita birnin.

Tana nan a tsaye tana waige waigen motar da zata tare, sai kawai ga wata mota ta alfarma tazo zata wuce, har tayi gaba saigata tana dawowa a hankali, har ta tsaya dai dai inda izzatu take a tsaye, aka zuge glass d'in motar ganin wanda ke a cikin motar ne ya saka izzatu maye fuskarta da murmushi, sab'anin tsoron da ya cika mata zuciya, a cikin murna irinta k'urciya tace:

"Laaa baba dama kana nan, ka daina zuwa garinmu?"

Mutumin yayi murmushi, ya kawar da tambayar da tayi masa yace:

"Ina 'yar baba zata je ne naganta da shirin zuwa makaranta?"

Izzatu washe da baki tace:

"Abin hawa nike nema zanje makaranta"

Da sauri yace:

"Shigo muje kar kiyi latti a dake ki"

Izzatu tayi shiru tana tunani, mutumin ya kalleta yayi murmushi har saida hak'oranshi suka bayyana sannan yace:

"Ki kwantar da hankalinki 'yata ni a matsayin d'iya na d'auke ki, ko wani bazan bari ya cutar dake ba, balle ni shigo muje in kai ki kar kije ki makara"

Izzatu ta bud'e gaban motar zata shiga, yace ta koma baya ta zauna, sun fara tafiya ne ta ya tambayeta ina yayanta? da sauri ta kalleshi a cikin mamaki tace:

"Yaya Garza na, ya tafi makarantar jami'a ya barni, gashi yanzu in zanje makaranta a kullum sai nasha wahala, sabida na saba shi yake kaini idan antashi ya dawo dani"

Ta k'are maganar tareda zubowar wasu k'walla akan fuskarta, sannan ta kalli mutumin tace:

"Amman Ina kasan yaya Garza na?"

Mutumin kam damuwa kwance a kan fuskarshi, yayi murmushin yak'e sannan yace:,

"Saboda me kika yiman wannan tambayar "

Izzatu tayi murmushi tace:

"Saboda naga lokacin da kake siyen tallata, baya garin ma ai a lokacin"

Mutumin ya shiru na minti biyu sannan yace :

"Ai na tab'a zuwa k'auyenku  naga yana fad'a da wani da yace maki RUWA DA KANKARA, nine ma na raba fad'an ai"

Izzatu tayi dariya tuno lokacin, sannan ta b'ata fuskarta a lokaci d'aya tace:

"Ai yaya Garza baya son yaji an kirani da wannan suna, nima haka kawai idan aka kirani da sunan, nike jin kirjina ya buga sosai, wani b'acin rai ya ziyarci zuciyata"

Ba shiri mutumin ya kallota, shima tashi fuskar a cikin damuwa yace:

"To me ake nufi da sunan ne da bakya so?"

Izzatu ta share hawayenta tace:

"Nima ban san me yake nufi ba gaskiya, amman watak'ila shi yayan nawa yasani shiyasa bayaso a kirani da sunan"

Daga nan firar tasu ta tsaya, har suka shigo garin, sannan ya tambayeta sunan makarantar ta fad'a masa,jin sunan makarantar ba shiri ya kalleta yace:

"Wa ke biya maki kud'in makarantar?"

Izzatu tana dariya tace:

"Mamata da malam suna sona sosai"

Mutumin ya tamata murmushin yace:

"Allah ya biyasu da gidan aljannah"

Izzatu taji dad'in addu'ar da yayiwa iyayenta, sannan tace:

"Tareda kai, saboda kana da kirki kaima, kana taimakona a duk lokacin da nike buk'atar taimako"

Mutumin yayi murmushi, bai ce da ita komi ba, har suka je k'ofar makarantar ya ajiyeta, ya d'auko kud'i ya bata tak'i karb'a tayi godiya ta shige makarantarsu da gudunta.

Yabita da kallo har ya daina ganinta, sannan ya share hawayen da yake ta mak'alewa a idanunsa, yaja motar jikinshi a sanyaye, tareda d'inbin damuwar da ta cunkushe zuciyarshi.

Koda aka tashi makaranta, izzatu tana fitowa a bakin get d'in makarantar, tayi tozali da motar da ta kawota d'azu, amman zuciyarta ta kasa yarda da cewa shi d'inne, don tayi tunanin to me zai dawo dashi in har shi d'in ne, koko akwai yaranshi a makarantar yazo d'aukarsu.

Har ta fara tafiya zata wuce motar, yayi mata  oda tayi saurin juyowa, aiko taga yayi mata alama da hannu da tazo, a cikin farinciki ta dawo ta gaidashi a ladafce, ya amsa a tak'aice sannan ya fito ya bud'e mata bayan motar yace:

"Zo muje k'auyenku zanje yanzu, sai in ajiyeki"

A cikin jin dad'i izzatu ta shige mota, suka kama hanya sannu a hankali har suka kai bakin titin dake garinsu, inda ya d'auke ta anan ya ajiyeta, zata fita ya waigo da fuskarshi akanta yace:

"Akwai wani aiki da nike zuwa yi garinku a kullum, idan kina so sai ki dinga fitowa anan tunda safe sai in jiraki anan mu wuce in rage maki hanya, amman fa idan kin dad'e bazaki sameni ba"

Izzatu  tana jin dad'i tace:

"Ai baba har sai ma na rigaka zuwa saboda sammakon da zan dinga yi"

Tana k'are maganar ta b'alle murfin ta fito, tayi masa godiya, har ta fara tafiya, sannan ya kirata ta juyo yace da ita:

"Idan kika gayawa mamarki zata yimaki fad'a don haka kiyi shiru ba sai kin fad'a a gida ba ni don Allah zanyi Allah ya bani lada"

Izzatu ta amince da zancenshi, tayi masa alk'awalin bazata fad'a ba, sannan suka rabu.

Tun daga ranar shi yake kaita makaranta, ya dawo da ita, hankalin su malam bai tashi ba sai ranar da sukaje biya mata kud'in 2rd term, principal d'in makarantar tayiwa malam bayanin, an biya mata kud'in shekara, kud'in su ma da suka bayar a farkon shigarta makarantar,  dana komi da komi ta basu tace ga abunsu nan.

Tofa🙀🙀🙀🙀🙀 jama'a wani lauje ne yayi wannan nad'in🤔🤔ko zaku fassaraman me hakan yake nufi???🤣

Akafta🏃‍♀️

D/Auta🥴
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*_______________________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*__________________________________________________*

*MUCH LOVE MY FANS 💋💋💋*

*PAGE TWENTY FIVE*

**********************

Malam kam, yana jin wannan hargitsatstsen bayani, wanda ya saka shi shiga, tashin hankalin da ba zato bale tsammani, jikinshi yana rawa bakinshi yana b'ari yace:

"Wane ne da wannan aikin?"

Principal ta nuna masa itama batasan shi ba, aiko malam ba shiri yace a kira masa izzatun, minti biyar a tsakani sai gata anzo da ita, ba tareda wani jinkiri ba, yace tazo su tafi, acikin mamaki izzatu ta kallesa, amman ba musu tabi bayanshi, har sun fara tafiya zasu bar office d'in ne, principal taga da gaske Malam ya firgita, kuma da alamu d'auke 'yarsa yakeso yayi, a cikin d'aga sautin muryarta tace :

"Malam lafiya?, me ke faruwa ne wai? Wanda hukumar makaranta batasan da zaman shi ba?"

Malam ya juyo jikinshi ya kyarma yace:

Mu muka kawo 'yarmu makaranta, to ta yaya wani zaizo ya biya mata kud'in makaranta har na shekara ba tareda mun sani ba?, don haka daga yanzu na fiddata a makarantar, saboda nagano akwai rashin tsaro sosai a cikinta, don haka na barku lafiya"

Yana k'are wannan zance, yaja izzatu kamar zasu tashi sama, suka bar makarantar, a cikin jin haushin malam da abunda yayi, principal da wasu tsirarun malamai, da abun ya faru a gabansu sai maida zancen sukeyi a tsakaninsu, saboda sunyi mamakin dalilin da yasa malam yayi wannan haukar daga taimako?.

Kai tsaye suka zarce a kauyen su, izzatu sai faman kuka takeyi, tana tambayar malam meke faruwa?, ita fa tana son makarantar ta, amma malam kanzil baice da itaba, har suka je gida.

Mama hassutu ko tun daga yanayin da taga shigowar malam, tasan akwai wata a k'asa, musamman ganinshi da izzatu, tasan akwai abunda ya faru tunda lokacin tashinsu a makarantar bai yi ba.

Mama hassatu rik'e da taguminta, izzatu ta zo ta gabanta ta wuce ranta a had'e, ta shige d'akinsu ta b'are baki sai kuka takeyi, saboda jin haushin an rabata da makarantarta , gashi ko littafanta a cen ta barosu.

Mama hassatu bata bi takanta ba tayi wurin malam domin taji meke faruwa?, aiko ba b'ata lokaci malam yayi mata bayanin komi, itama kanta taji tsoron abunda taji, saboda har ga Allah tana son izzatu, bata fatar abunda zai rabata da ita, jikinta a mace tace:

"To idan har haka ne, ai sai a canza mata wata makaranta kawai"

Malam b'acin rai kwance a kan fuskarshi yace:

"Ba wata makaranta da zata koma zuwa yi a cen, domin jikina yana bani ko wanene da wannan aikin, to yanada alak'a da izzatu, ni kuma a yanzu duk abunda zaisa ta gano ba mune muka haifeta ba to bana fatar zuwan shi, shiyasa kikaga duk wani rawar kai na Garzali akanta na dakatar dashi, don bana son abunda zai d'aga mata hankali, nafi son muyita zamanmu asirinta a rufe ruf, batareda tonuwar wannan sirrin da muke b'oyewa ba, shekara da shekaru ace ya bayyana a gareta ta jishi ba, mafita kawai ta hak'ura da karatun, daman cen ni bai wani kwanta man a rai ba"

Mama ta fad'a zurfin tunani na d'an lokaci, sannan ta d'ago fuskarta da damuwa shinfid'e akanta tace;

Kayi hak'uri sai a canza mata matakarantar, sannan aja hankalin ita uzzatun da ta iya bakinta,

duka daman cen batada surutu, sannan itama shugabar makarantar, a fahimtar da ita kada hakan ta koma faruwasu, yafi da atsayar da karatun, saboda nidai bana son karatunta ya tsaya gaskiya, saboda shine kawai abunda zamu bata wanda zatayi alfakhari dashi a gaba, don haka don Allah malam ka janye komi,  ka bari taci gaba da karatunta insha Allahu ba abunda zai k'ara faruwa"

Malam kam ba'a son ranshi zai k'ara barin izzatu ta koma zuwa birni karatu ba, amma tuno wasiyyar Dada inda take cewa;

IDAN HAR IYAYENTA SUNZO KAR AYI JAYAYYA A BASU 'YAR SU.

Malam wata zufa ta karyo masa, ya saka hannu ya share, sannan yace da Mama;

"To yanzu meye abinyi?, don ke kikasan makarantun, yanzu kuma wace za'a sakata?"

Mama tayi murmushin jin dad'i tace;

"Akwai wadda za'a sakata a yanzu, hakan bazata koma faruwa ba insha Allah,  saboda tana da tsaro sosai fiye da wadda tayi;

Malam kam jinta kawai yakeyi, amman badon zuciyarshi ta amince da wannan karatu na izzatu ba.

Iya kulu dake lab'e tana saurarensu, ba shiri tabar wajen, tana farinciki, ta shige d'akinta tana ta shek'a dariya tace;

"Gayyar ta kusa watsewa kowa ma ya huta, ni dama ace nasan inda zanje in sami iyayen nata, da wallahi da kaina zan  kirasu suzo su kwashi kayan tsiyarsu, muga ta k'arshen iyayin masifa da ake damun mutane dashi, ba'a aje komi ba,  sai k'aton kashi ana ta cikawa mutane masai"

**

Anyi k'ok'arin canzawa izzatu makaranta, ta hanyar wata abokiyar Mama dake birnin, inda yaranta suke yi, saboda ta tabbatar wa da Mama akwai tsaro sosai a makarantar.

A rana ta biyu ce, da zata je sabuwar makarantar da aka maidata ne, tana fitowa a bakin titin da take taron abun hawa, sai kawai ga wata mota ta tsaya a gefenta, da sauri tasha jinin jikinta, saboda jan kunnen da Mama tayi mata,  akan kowa kada ta amince dashi, don har yaran abokiyar tata da tayi ja gaba wajen sakata a makarantar, tace kada ta saki jiki dasu, kada tayi sakacin da wasu zasu san sirrinta, balle ta fad'i inda take a zaune, aiko nasihar ta shiga jikinta sosai kuma tana jin tsoron abunda zaisa asake cireta daga makarantar ta shiyasa da taga wannan motar gabanta ya fad'i .

Sannu a hankali, mai motar ya sauke glass d'in mazaunin direba, ya fesheta da murmushi, itama ba shiri ta mayar masa da murmushin ganin ko wanene, mutumin yana murmushin yace:

"'yata zo muje sauri nikeyi"

Izzatu ta fara waige waige, sannan tace;

"Kaje kawai Baba yanzu zan sami abun hawa insha Allah"

Mutumin ba shiri ya bud'e murfin motar ya fito, a ladafce yace da ita;

"Kiyi hak'uri ranki shi dad'e, ki shigo muje in ajiyeki sauri nikeyi, akwai sabgogin dake gabana, a yanzu haka ma jirana akeyi"

Izzatu a cikin mamakin wannan ladabi da yayi mata, ba musu ta shiga motar suka fara tafiya, hannunta ne izzatu takai hannunta akan tulin wasu takardu, dake ajiye a bayan sit d'in, dake kusa da ita masu d'auke da photo, kamar ance ta duba, aiko ta zura hannu ta janyo d'aya ta fara kallon photon, ba shiri taji k'irjinta ya buga dam! dam!.

Da sauri ta dafe zuciyarta, a cikin magana mai sauti ta kira sunan da taga an rubuta a k'asan jikin photon:

ALHAJI YAHAYA BADAWI.

For Governor.

Insha Allah.

Da sauri mutumin ya juyo ya kalleta, shima nashi k'irjin ya buga dam!, gaba d'aya ya rikice, bakinshi yana rawa yace;

"Daman kinsan shi ne?, ko kin tab'a ganinsa?".

Izzatu a cikin rashin kula da yanayin da ya shiga, idonta akan photon tace;

"A'a bansanshi ba gaskiya, kuma ban tab'a ganinsa ba, sai a yau, amman dai a tashi guda naji mutumin ya burgeni sosai, ina mashi fatar nasara"

Ba shiri mutumin ya sauke ajiyar zuciya, sannan bakinshi a washe yace;

"Alhmdllh"

Daga lokacin yaja bakinshi yayi gum saboda, yana tsoron fad'in abunda zaisa izzatu ta ranfo

tashin hankalin da ya shiga, bai sake magana ba har sai da izzatu ta cillo masa tambaya da cewa;

"Yanzu shi wannan takarar gwamna yakeyi kenan?, "

Yace mata: " Eh ki taya mu da addu'a"

Izzatu ta k'ara kallon photon, a cikin wani shauk'i tace;

"ALLAH ya baku sa'a yasa shine alkhairi "

A cikin jin dad'i yace : "Ameen "

Yana kai bakin get d'in makarantarsu, ya ajiyeta sannan ya ciro wani k'aramin kwando, mai d'auke da wata kula mai masifar kyau, tareda wasu tarkace da batasan meye a ciki ba, ba musu ta karb'a tace;

"A jiye maka zanyi ne?"

Yace: "A'a naki ne idan kinji yunwa sai kici"

Yana k'are fad'in maganar ya fad'a motarshi ya bata wuta ya bar wurin da sauri,sannan ya sauke ajiyar zuciya.

Izzatu kam sororo tayi da kwando a hannunta, sai da ta daina hango motar sannan ta juya ta shige makarantar amma zuciyarta cike take, da tunanin abu biyu, na farko fuskar mutumin da takasa b'oyuwa akan gilashin idanunta, na biyu mamakin wannan kayan dake rik'e da hannunta, wanda ta kasa gano a wane dalili ne zai bata su_ne? tunda dai ita ba cemasa tayi tana jin yunwa ba.

Koda aka tashi breakfast, ta janyo kular ta bud'e, saiga lafiyayyiyar indomi wadda taji kayan had'i,tareda zuk'a zuk'an namu a cikinta, asamanta kuma an shimfid'e wata masar k'wai lafiyayya, a gefe d'aya kuma ga tea nan mai kauri, , acikin wani k'aramin Flak's, da ruwan faro har gora biyu, tareda wasu sweet masu shegen kyau, ko ledarsu abun burgewa ce.

Jiki a mace izzatu ta fara cin abincin, dad'in da ya ziyarci bakinta ne, ya saka kunnenta kad'awa, kamar walk'iya ta cenye abincin tass, ba tareda ta tantance ba, ta had'a da tea din ta kwankwad'e, sai gata da aza wata k'atuwar gyatsa, tareda sauke nishi sama sama alamun k'oshi, ta ciro sweet d'in ta saka a jaka, sannan ta rufe komi ta ajiye kwandon a gefe, ta fad'a tunanin wannan d'an takarar Governor d'in a cikin zuciyarta tace:

"YAHAYA BADAWI"

Haka tayi ta nanata sunan a cikin zuciyarta, har aka tashi makaranta bata daina tunanin ba.

Koda ta fito a bakin get d'in makarantar yana zaune zaman jiranta, tana zuwa yayi saurin karb'ar kwandon, bakinta a sake tayi masa godiya, yana murmushi yace:

"Ba komi, ai yiwa kai ne "

Har zata wuce, yayi saurin cewa:

"Zo muje in ajiyeki nima a cen garin naku zanje yanzu"

Ba musu ta shige suka fara tafiya, tambayar dake cin ranta ta furzo masa wadda har saida ya taka burki ba shiri, motar dake bayanshi ta daki murfin motar dasu izzatu suke a ciki, mutanen da suka lura da abunda ya faru suka fara salati, da sauri ya saita natsuwarshi, yaja motar da k'arfi ya fita a cikin dandazon motocin dake roundabout din, sannan ya mik'i hanyar k'auyen su izzatu, sun kusa zuwa k'auyen ne izzatu ta kalleshi ta maimaita tambayarta tace:

"Baba wai aikin me kake zuwa yi garinmu a kullum? "

Mutumin yayi saurin fad'in:

" wata kwangilar shinfid'a titi ce aka bada, a nan kusa da garinku me ma sunan garin?, shiyasa nike zuwa duba ma'aikatan a kullum"

Izzatu tace :

"Allah sarki, aini ko a garinmu ba fita ake barina inyi ba, don ni ba ko ina ne na nasani ba"

Mutumin yayi murmushi yace:

"Ai kwanan nan ma zamu zo campaign a garin naku insha Allahu zaku zab'e mu dai ko?"

Izzatu tace :

"Insha Allah"

Akafta⛹️‍♀️

D/Auta ce🥰
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*___________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*_____________________________________*

*MUCH LUV MY FANS 💃💃💃💃💃💃💃*

*PAGE TWENTY SIX*

*********************

Koda a kazo dai dai inda yake ajiyeta a kullum, a nan ya tsaya izzatu ta muskuta ta fito, rik'e da jakarta ta makaranta, ta dubi mutumin tana murmushi tace;

"Nagode baba, da wannan taimako da kake yimani, amman don Allah idan ba damuwa, ina son ka bani poster d'aya nima naje na lik'a a gidanmu"

Mutumin yayi murmushi mai sauti, sannan yace;

"Wannan ba damuwa ba ce 'yarbaba, idan ma kina buk'ata zan baki su da yawa kije ki rabawa 'yan garinku"

Izzatu ta zaro ido a waje tace:

"Rufaman asiri, wallahi mama da malam sai sun tuhumeni, akan ina na samo su?"

Mutumin yayi gajeruwar dariya yace:

"Asirinki a rufe yake ruf 'yar baba, ga d'ayar da kika nema nan,  kiyi sauri ki k'arasa gida kar aga kin dad'e"

Izzatu tasaka hannu ta karb'a, sannan ta k'ara yimasa godiya,  ta tafi tana ta jin dad'in da ta rasa na minene?, tana tafe tana ta tsallenta  har ta kusa kaiwa gida ta had'u da Abu da zugar abokanshi, masu zauna gari banza, sun lab'e a wani kangon gida suna ta bushe bushen kayan mayensu.

Yaron kande mai suna idi,  ya tab'o Abu yace:

"Wai ita wannan jan k'osan, karatun uban miye take zuwa yi a birni ne?,a kullum ta wuce da shaggun k'afufuwanta, tana yiwa mutane kuri, nifa wlh ta fara bani haushi, ubanta zanci 'yar iska mai siffar aljanu, mu za'a nunawa boko"

Abu yayi wani arnen zagi, sannan yana huci yace:

"Kai haushi kawai take baka, to ni na tsaneta wallahi, tun tana k'arama, saboda nagano malam yafi sonta akan mu, to bank'i in saka wuk'a in farka cikin shegiya ba, kawai ina k'yaleta ne don bata shiga sabgata, da daga ita har munafukar marik'iyarta, sai na  shikka masu rashin mutunci wallahi, ai bata kulani da sai naci uwarta shegiya"

Izzatu tana kawowa a dai dai inda suke, ta d'auke kanta kamar bata gansu ba, idi ya d'aga murya yace da ita:

"Ke 'yar cika, don ubanki baki ganmu bane?, da bazaki gaida iyayen gidanki ba?"

Izzatu ta waigo kamar bata damu da zagin da suka yimata ba, a cikin sakin fuska tace dasu;

"Sorry idi, i didn't see you"

Gaba d'ayansu suka zaro idanuwa, bakin Abu yana rawa yace;

"Mu kika zaga?"

"How should I abuse you"

Gaba d'ayansu suka zaro ido a waje, idi yace ;

Yanzu ke don kina shegiya, shine kika sake zagin namu?,  ashe ko yau sai munci namanki d'anye a garin nan, baabaa mu k'addamar mata kawai sai muga wanda ya d'aure mata gindi"

Aiko kafin yakai k'arshen maganarshi, duk suka yo cira tareda fiddo makamansu dake mak'ale a jikinsu, aiko izzatu tana ganin yanayinsu, ta cire sandal d'in dake sanye a k'afarta,  ta balbala da gudu kamar wadda zata tashi sama,   suka biyota aguje suna fad'in a tare a tare, izzatu bata zame ko'ina ba sai a gidan mai unguwa.

Kai tsaye ta fad'a fada, a sukwane ta yi bayan mai unguwa ta lab'e,  ana lafiya?,  lafiya?,  amma sabida gudun da tasha, yasa ta sauke numfashin a wahalce, shiyasa ta kasa yin magana, sai ajiyar zuciya takeyi, kafin ta samu damar yin magana,  sai ga k'ungiyar su Abu sun fad'o fadar, kowane rik'e da makaminshi a hannu.

Mai unguwa,  tareda sauran mutanen dake zaune a fadar, suka tashi a tsaye ba shiri suna zaro idanuwa, wani bafade ya fara yimasu banbamin fad'a akan su fita ko ya koya masu hankali, suka fara yimasa rashin kunya, akan bazasu fita ba har sai an fiddo masu da izzatu sun lallasata, mai unguwa yana jin haka ba shiri ya d'aga waya ya kira 'yansanda a birni, saboda ganin yanayinsu yasan baza'a kwashe dasu ta lalama ba, sannan yayi gyaran murya yace da bafaden, abar su Abu su shigo yaji meke tafe dasu?.

Suna jin zancen mai unguwa suka ture bafaden suka shigo, sunata muzurai, mai unguwa yace dasu su zazzauna, amma saboda suna jin kansu dai dai da kowa, saboda tik'ewar da sukayi da kayan maye, shiyasa sukayi tsaye cirko cirko suka kasa rusunawa, sai furzo miyagun kalamai sukeyi akan izzatu, gaba d'aya fadar tayi shiru su kawai ake saurare.

Shigowar 'yansanda a cikin k'auyen ya tada hankulan mutane da yawa, saboda jin k'arar jiniyar zuwan 'yansandan, yasa mutane da dama suka rud'e sai gudun ceton rai sukeyi, 'yan gani kashe ne suka biyo motar har k'ofar gidan mai unguwa.

Su Abu ko suna jin zuwan motar 'yansanda,  cikinsu ya fara d'urar ruwa, sai zarar idanuwa sukeyi, suka fara neman hanyar ficewa, wannan bafaden yayi cira ya rigasu fita ya rufo k'ofar, yaje yayiwa  'yansandan iso suka shigo fadar, su Abu suna ganin shigowarsu sai gasu a k'asa dab'as suna kai gaisuwa a wurin maigari.

Mai unguwa yayi murmushi, sannan ya tambayesu me izzatu tayi masu mai zafi ne, da har suka biyota a  nan wurin?.

Abu zai fara magana, idi yayi caraf yace ;

"A tambayeta, saboda itace tasan kalar zagin da tayi masu"

Mai unguwa yace da izzatu ta fito mab'oyar ta tsaya a tsakiya tayi bayanin miya had'ata da su, izzatu ta fito tana muzurai jikinta yana rawa, tayi bayanin duk abunda ya faru a tsakaninsu tsaf, 'yansandan suka fara dariya suna turanci a tsakaninsu.

Mai unguwa yace da izzatu ta fassara ma su idi abunda tace da turanci, aiko izzatu ta fad'a masu ita ba zaginsu tayi ba ga abund take nufi da hausa, sannan su Abu suka fara mazuran rashin gaskiya, mai unguwa yayi masu fad'a sosai tareda barazanar 'yansanda su tafi dasu, aiko suka rud'e suka fara rok'on a yafe masu bazasu koma ba, sannan 'yan sandan suka ja masu kunne, a kan idan suka sake tada hankali a garin sai sunzo sun tafi dasu sun rufesu a gidan yarin birni.

Aiko jikinsu ya d'auki rawa, suka yita bada hak'uri, akan bazasu koma ba, mai gari yaja kunnensu sosai akan idan suka k'ara shiga sabgar izzatu, duk abunda aka yimasu su suka ja, sannan aka sallamesu suka tafi, itama izzatu akace ta tafi gida, amma kar ta sake kulasu daga yau.

Kafin izzatu ta kai gida har labari yaje kunnen su iya kulu da Mama hassatu, mama taji dad'in da izzatu bata zo gidan ba, tayi wurin mai unguwa saboda rashin mutuncin Abu, komi zai iya yimata idan ya shigo gidan.

Iya kulu kam sai murna takeyi akan su Abu zasu ci mata uban izzatun, sai gashi tana jin ance ga 'yansanda nan sun shigo gari, cikinta ya d'uri ruwa da sauri taja buta tayi bayi, saboda ziyarar da wani gawurtaccen zawo, ya kawo mata ba shiri ba shiryawa, mama hassatu tabita da kallo tana dariya, hankalinta a kwance ta shigewarta d'aki.

Koda izzatu ta shigo da fara'a kwance a fuskarta ta tarbi 'yarta, izzatun ma dariya ta fashe da ita, har saida tayi mai isarta, sannan ta fara baiwa mamar labarin abunda ya faru, ita kanta mamar abun ya bata dariya, aiko sukayita dariyarsu suna ci gaba da zanta abunda akayi.

Iya kulu tana fitowa a bayin taji sautin daiyarsu, jikinta har tsuma yakeyi ta fara zazzaga ruwan masifa, mama hassatu dai k'anzil bata ce da ita ba, sai cewa da tayi da izzatu taje ta tub'e uniform tayi sallah, taci abinci,tayi wanka taje makarantar allo, aiko izzatu kafin tayi komi sai da ta zuge zip d'in jakarta ta makaranta, ta ciro poster d'in da ta rok'a ta samo kunu, sannan taje ta lik'ata ajikin k'ofar d'akinsu, mama ta kalleta tace:

"Ina kika samo wannan poster?"

Izzatu tayi murmushi tace:

"Ina kan hanyar dawowata gida ne, naga ana rabonta na karb'o"

Mama ta rik'e baki tace;

"To ke izzatu miye had'inki da siyasa nikam?, da har zaki lik'a muna ita a k'ofa"

Izzatu tana dariya tace;

"Wallahi mama nidai haka kawai naji ina son mutumin, don naga alamun shi kamar zaiyi adalci"

Mama hassatu tayi mata wani kallo tace;

Raba kanki da 'yan siyasar nan izzatu, kirkinsu iyakacin in suna neman a zab'esu, amma da sunci shikenan sai su manta da kowa.

Izzatu ta b'ata fuska tace;

"To dai mama shi wannan daga ganinsa zaiyi jink'an irinmu talakawa"

Mama ta zaro ido a waje tace;

"Izzatu miye had'inki da shine, da har kike b'ata ranki a banza kanshi"

To nima dai shi nagani mama, daga ganin sarkin fawa sai miya tayi zak'i🤣🤣🤣🤣

Akafta🏃‍♀️

D/Auta ce⛹️‍♀️
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*_________________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*________________________________________*

*I love you too my fans💃💃*

*PAGE TWENTY SEVEN*

**********************

Izzatu ta zunb'uro baki tace;

"Nifa mama bakisan yanda nike sonshi bane shiyasa"

Mama tayi shiru, tareda k'urawa photon idanu, sannan ta dawo da kallonta akan izzatu, ta fad'a zurfin tunanin anya ba wata alak'a ta jini a tsakanin izzatu da wannan bawan Allah?, Sai dai abu d'aya da yasaka mama cire wannan tunanin a zuciyarta shine, ganin halittar izzatu tamkar ta fararen buzaye, shi kuma wannan mutumin dake jikin photon,hausa fulani ne, ma'ana bahaushe ne sid'ik haifuwar nigeria, to amma fa idan ba idanunta ne suke gaya mata k'arya ba, sai taga kamar akwai yar kama da taga izzatu takeyi dashi, sai dai ita don tana fara baza'a yi saurin gano kamar ba.

Mama hassatu tabar abun a zuciyarta, don bata son ta jawowa kansu abunda zai d'aga masu hankali suna zaman zamansu.

Taja k'afafunta ta koma d'aki, koda malam ya dawo, tayi masa bayanin hasashen da takeyi, malam ma yaji jikinshi yayi sanyi, yace koda wasa kada ta d'aga wannan magana, don gudun abunda zaije ya dawo, su rufawa kansu asiri suji da abunda ke gabansu.

Izzutu taci gaba da zuwa makarantar ta, har lokacin da term ya k'are, za'a biya wasu kud'in makarantar, koda malam yaje biya yaji zancen iri d'aya ne dai har yanzu, anbiyawa izzatu kud'in makaranta har na shekara, aka mayarwa da malam kud'insu da suka bada, sai dai inda hankalinshi yad'an kwanta, da yaji ance wani mai neman kujerar gwamna ne ya biyawa d'alibai ashinrin kud'in makarantar, harda izzatu tayi sa'ar shiga a cikin jerin d'aliban da aka biyawa

kud'in, saboda hazak'arta akan karatu, domin tazo a sahu na farkon wad'anda suka cenye jarabawar wannan term a ajin nasu.

Malam yaji dad'in wannan labarin, amma fa zuciyarshi tana kokwanto sosai akan lamarin, saboda kwatankwacin abunda ya faru ne a waccen makarantar da ya fiddata.

**

A ranar wata assabar izzatu tana kan hanya zata dawo gida, antaso daga makaranrar safe,tana rik'e da allonta tana tafiya, sai wasa takeyi da wani dogon karen dake hannunta, sai jin sautin kukan motoci tayi suna dosota, tayi saurin juyawa aiko sai ga motoci, a jere reras sunfi guda goma, wata a bayan wata sai wak'ar siyasa ke tashi.

Tana cen wajen kallon motocin ne bakinta a sake, bata ankara ba sai ko taji d'aya daga cikin motocin tayo kanta aguje, da sauri taja baya duk da k'ok'arinta na son ta kaucewa motar, sai da motar ta shiga wani rame da k'arfi, inda ruwan kwatami suka kwanta, ba shiri taji saukar ruwan kwatar akan fuskarta, da jikinta gaba d'aya, allonta ma dake rungume a jikinta bai tsira ba, duk kwatar ta wanke rubutun dake jikin allon.

Kafin tayi wani yunk'uri, sai kawai taji saukar mari akan fuskarta, da sauri ta dafe fuskarta, tareda d'ago kai ido cikin ido ta kalli wanda take zaton shine yayi marin, duba da yanayin fuskarshi da ta kalla, tayi masa wani kallon me nayi maka, hawaye cike fam da k'wayar idanunta.

Wanda yayi marin ranshi a b'ace yace da ita;

"Ke wace kalar dabba ce a cikin dabbobin k'auyen naku?, da zaki tsaya kina ganin mota a tafe ki kasa janyewa, salon a buge ku, kuce da gangan aka y..... "

Kafin yakai k'arshen zancenshi,izzatu ta d'aga allonta tareda yin tsalle ta rafka masa allon a baki, a zabure ya dafe bakin saboda dukan ya shige shi sosai, mamaki kwance akan fuskarshi, a zuciye yayi ball da ita, ya d'aga hannu zai kai mata naushi ne yaji anrik'e masa hannun ta baya.

Da k'arfi ya juyo ya kalli wanda ya rik'e masa hannun yace;

Haba Baba kallah ka bar ni inci uban matsiyaciyar yarinyar nan, d'iyar talakawa dangin tsiya,daman ai ire irenku sunfi kowa bakin ciki da mu masu arziki, sai naci uban ubanki, inga waye shi a duk fad'in garinnan, shegiya matsiyaciya a haka zaku k'are da tsiyarku, sai dai bak'in cikin mai kud'i ya kasheku, yar iska dangin matsiyata"

Wanda aka kira baba kallah, yayi saurin dafe goshi yace;

"Kash!, shu'aib banji dad'in wannan magana taka ba,
 ka dinga tauna lafuzzanka idan har zaka furzar,  gudun kaje kaji kunya watarana, saboda ita magana zarar bunu ce, da ta fito bata maiduwa"

A zuciye wanda aka kira shu'aib yace;

"Haba haba ka daina yawa mana baba kallah, akan wannan tushen tsiyar zan ji kunyar, wallahi kinci arzik'in shi da sai na b'allaki gunduwa gunduwa a nan wurin, shegiya mai idanun mayu,"

Yana k'are maganar ya fad'a motarshi ya fisgeta da k'arfi, sai k'ofar gidan mai unguwa, inda a cen ne zasuyi rabon kayan.

Baba kallah ranshi a b'ace yaje ya tada izzatu tsaye, wadda  ke rakub'e tunda shu'aib yayi ball da ita takasa tashi, tana had'a ido da baba kallah tace;

"Laa ashe baba kaine da gaske?"

Baba kallah yana murmushi yace da ita;

"Nine 'yar baba, ina ne gidanku halan?"

Izzatu ta nuna masa wata hanya tace;,

 "Da anbi hanyar aka sha kwana, aka k'ara mik'ewa sai a k'ofar gidanmu"

Baba kallah yayi murmushi yace ;

"Yanzu sauri nikeyi 'yar baba,  amma insha Allahu idan na sake shigowa a garin, zan zo har gidanku  mu gaisa da babanki, idan kinje ki gaidasu"

Tana ta jin dad'i tace ;

"To baba nagode"

Baba kallah ya bud'e motar shi, ya d'ebo kayan da suka zo rabo na siyasa ya ajiye mata a k'asa, ya kira wasu yara dake kallonsu yace dasu su kaiwa izzatu kayan gida, ya saka hannu ya ciro d'ari biyar ya basu, suka karb'a suna ta murna,  suka kwashi kayan suna ta gudu  suka kaimata gida.

Kuyi hkr🙏🏻 banida caji, amma insha Allahu zakujini anjima🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️.

Akafta😜

D/Auta ce🤝
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*________________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*__________________________________________*

***MUCH LUV MY FANS💋💋💋💋****

*PAGE TWENTY EIGHT*

*********************

Koda izzatu taje gida,  ta iske mama hassatu rungume da kayan,  tanata kallo d'aya bayan d'aya, mamaki cike da fuskarta, tana mamakin taya ankayi izzatu ta samu wad'annan kayan?, kuma duk d'auke da photon mutuminta, wanda a kullum batada aiki shafa kunu a gefen da taga

poster'r ta d'an taso domin ta k'ara mannewa a jikin k'ofar d'akin, saboda kawai tsananin k'aunarta da mai photon.

Izzatu tana shigowa gidan ta jingine allonta, sannan ta cika bokiti da ruwa fam ta fad'a bayi, sai da ta sille jikinta tass da soso da sabulu, warin kwatar da ke jikinta ya fita kaf,  sannan ta fito ta shige d'aki tana shiryawa, mama hassatu tana tambayarta lafiya taga allonta da kwata, tace da ita ta bari tazo zataji komi.

Aiko tana kammalawa ta fito ta zauna, ta fara duba kayan da Baba kallah ya bata, mama tace da ita:

"wai ke a'ina kika samo wad'annan tulin kayan ne?, izzatu yaushe kika fara shiga shirgin da ba naki ba?, ki kiyayeni tun kafin musa k'afar wando d'aya nida ke"

Izzatu ta b'ata fuska, sannan tace:

"Mama fa ba rok'arsu nayi ba,  ina tafiyata bankula ba, sai kawai naji anwatsoman kwata a jikina gaba d'aya, har da allona duk ya b'ace, kafin in tantance sai kawai naji mari akan fuskata, mai motar ne ya mareni wai natare masa hanya, to shine wani bawan Allah daga cikinsu ya tausayaman, yabani wad'annan kayan, yamace zaizo watarana ya gaisa da malam"

Mama ta zaro ido a waje tace;

"Na shigesu izzatu, yazo gidannan yayi mi ni hassatu"

Izzatu ta fara dariya tace;

"Mama tsoron me kikeji ne?, keda za'azo a gaida har gida, mutuminfa yana da kirki wallahi"

"Izzatu izzatu, sau nawa na kira sunanki?"

Izzatu ta gimtse dariyarta tace;

"Sau biyu mamata"

Mama tace; "to bari ink'ara wani su cike uku, izzatu idan baki fita a cikin shirgin 'yan siyasar nan ba, wallahi saina sassab'a maki a cikin gidannan, yau tazamo rana ta k'arshe da zaki k'ara shigo da wani abu da ya danganci siyasa kinji ko bakiji ba?"

Izzatu idanunta a cike taf da hawaye tace;

Naji mama, don Allah kiyi hak'uri wallahi NI haka kawai naji ina k'aunar wannan mutumin, amman insha Allahu kodon gudun b'acin ranki zan kiyaye, hakan bazata sake faruwa ba"

Tana k'are maganar wasu hawaye suka zubo mata, wad'anda ita kanta batasan ko na miye ba, da gudu ta tashi ta shige d'akinsu tana ta kuka.

Mama ta bita da kallo, tareda rik'e baki tana mamakin, abunda ke damun izzatunta, wai kidai da gaske YAHAYA BADAWI jininta ne?, indai har da gaske hakan ne, to tayaya sukayi had'in?shin miye matsayinshi a wajenta?, me yayi silar rabata da iyayenta tun tana jaririyarta?.

Mama hassatu ta sauke wata doguwar ajiyar zuciya tace;

"Allah ka yaye muna wannan duhu da ka lullub'ewa idanuwanmu ganinshi, a cikin salama ba tareda mun afka ramen da zamu kasa fitowa ba"

(Ameen).

Mama tana nan a zaune kayan suna watse a kan tabarma, iya kulu ta shigo gidan, ta dawo daga k'ofar gidan mai unguwa,  sai mai numfashin wahala takeyi, saboda tasha matsar k'uli k'ulin da tasha,  kafin ta samo sabulun wanki mai d'auke da photon YAHAYA BADAWI a jikin ledar da aka saka sabulun.

Saboda tana zaunenta, kande ta shigo jikinta yana rawa tace da ita, tazo suje gidan mai unguwa, anacen ana rabon kayan siyasa, jikinta yana rawa taja hijabi a saka ta fita, ko talkami a k'ofar gida ta k'arasa sakawa, saboda tsabar saurin da takeyi, don kar a rabe kayan batareda ta samu ba.

Sai gashi ta dawo gida, da sabulu k'waya d'aya a hannu tana murna,  kwatsam sai  ta iske abunda ya shalle tunaninta, ba shiri tayi turus tana kallon kayan dake gaban hassatu, don ma ta k'ara tabbatarwa, har sai  da taje gaban kayan tana baiwa idanunta abinci, bakinta yana b'ari tace;

"Hassatu ya akayi ban ganki a gidan mai unguwar ba?, watak'ila dai akwai wanda kika sani a birni, cikin masu rabon kayan ko?, wai ni kande ta kaini ta baro, danasani da najiraki mun tafi tare inci albarkacinki"

Mama hassatu tayi murmushin takaici tace;

"Nikam 'yar kuluwa mezaisa infita har zuwa k'ofar gidan mai unguwa, batareda na fad'awa malam ya bani izini ba?, ai rabonka duk inda yake bazai wuceka ba, har sai yazo ka sameshi, kingansu nan ko ina banje ba, har gidannan akayi sallama akace in ajiyewa izzatu"

Iya kulu ta zaro ido a waje tace;

"Izzatu fa kikace?"

Ta gyad'a mata kai alamar tabbatarwa, iya kulu ta dafe k'irji tace;

"To ita izzatun wane kalar shishigi da maula tayo har ta samo su?, don dai nasan ko kusa dasu bata isa taje ba balle su d'auko wad'annan uwayen kaya su bata don an maidasu mahaukata, indai sato su tayi gara tun da wuri kiyi bayani, in rufa maku asiri araba biyu a bani rabi"

Mama hassatu ta bita da wani kallon tashi bani waje sakarya, sannan tace;

"Allah ya raba izzatuna da sata, fiddunya wal'ahkhirah, masuyi ma suna kawowa uwa ana b'oyewa Allah ya shiryesu, shishigi da maula kuma ai iyawa ne, don rawar da wani yayi ya samo kud'i wani idan ya kuskura yayita sai yasha bala'in duka, hanya a bud'e take kowa yaje yabi mai fiddashi"

Iya kulu ta cika fam da gugar zanar da mama hassatu tayi mata, jikinta har rawa yakeyi wajen cire d'ankwalinta tasha d'amara, sannan tace;

"Lalle hassatu wuyanki yayi kauri a gidan malam, da har zaki iya kallon tsabar idanuna kina soka mani habaici kala kala, to indai akan waccen munafukar yarinyar ne, sai kunyi kuka da idanunku,tunda har kukaji  kuma kuka saya da kud'inku, waiku wayayyu kun d'auki 'ya kun jefa a makarantar birni, to muna zaune sai ta janyo maku abun kunyar da sai kun rasa ina zaku jefa kanku saboda bak'in cikinta, a dai juri zuwa rafi watarana tulun zai fashe yayi kwatsa kwatsa don uban da yayi silar zuwanshi duniya, haka kawai an kawo muna bala'i an aje muna acikin gida, salon a b'ata muna suna"

Mama hassatu dai bata kulata ba, don sanin halin da take a ciki, amman taji zafin maganganun da ta jefi izzatu dasu, sai da ta tattara kayan tsaf ta kalleta dakyau tace;

"D'an hakin da ka rena dai watarana shine zai tsone ma idanuwa, har yayi sanadin makantar ka, saboda haka ni bazan biyeki ba, amma sannu a hankali zaki gano izzatu tafi k'arfin ahalinki kaf gaba d'aya tun daga samanku har zuwa k'asa, ki adana wannan magana, saboda sai kin tunota ranar da kanki ranar duk kikaga gaskiya ta bayyana a idanunki"

Tana k'are maganar ta kwashi kayan ta shige d'aki, iya kulu ta fara tsalle tana ta zuba ruwan bala'i, akan mama hassatu in tacika ta fito a cire reni, mama hassatu dai cikanki bata koma cewa da ita ba, takoma lallashin izzatu, daketa gurzar kuka, saboda duk abunda suke fad'a akan kunnuwanta, tarasa abunda tayiwa iya kulu da har bata sonta, taketa jifarta da miyagun jafa'i kala kala.

**

Ranshi a b'ace ya shiga da motarshi, a wani katafaren gida kantameme na alfarma, wanda a kallo d'aya zaka hango miliyoyi kud'in da aka lak'ume wajen k'awata gidan.

A zuciye ya tsaida motar tafito, ba tareda yayi parking d'in motar inda ake ajiye motocin gidan ba, da sauri ya fito motar ya cillawa wani tsoho dake biye da shi key d'in motar, ya shigewarshi a cikin wata k'ofa dake a tsakiyar tangamemen gidan, ko waiwayen tsohon baiyi ba, balle yayi masa bayanin abunda zaiyi masa, tsohon dai yabishi da kallo har ya shige sannan ya girgiza kanshi, ya shiga motar ya kaita wajen da ake ajiye motocin, acikin wata k'atuwar rumfa doguwar wadda ta kunshi motoci a k'alla da zasu kai goma sha biyar a jere reras sai shek'i da k'yallin sabunta sukeyi suna d'aukar ido.

Ina biye dashi naga ya shiga wani bajimin zakin palo, wanda idan banyi k'arya zai lak'ume saitin kujerun da suka kai takwas saboda tsabar fad'in palon, ina biye dashi naga ya haye up sai taka step step da sauri da sauri yakeyi, ina biye dashi abaya naga wani k'aton falo shima mai d'auke da saitin kujeru uku DUK kala d'aya, anan naga ya fad'a a d'aya daga cikin kujerun yace:

" wash"

Tareda shafa bakinshi,wanda da alama wajen yimasa zafi yakeyi, duba da yanda yaketa b'ata fuska, ya kai dubanshi da wata k'ofa, ya d'aga k'afarshi sama akan wani malatsi, naga ya danna da k'arfi saiga wata 'yar k'ara mai d'aukeda wani sauti mai dad'i yana fitowa, minti biyar a tsakani saigashi naga anbud'e wata k'ofa k'iiiii tayi k'ara, saiga wata hamshak'iyar hajiya shafaffa da mai ta fito, sai takun k'amshi takeyi, idanuwanta suna sauka akan wannan matashin saurayin, sai naga ta fad'ad'a fuskarta da fara'a a hankali tace;

"Shu'aib har kundawo?, ina ka baro kallah?"

Rigiji gabji🙀🙀🙀🙀🙀🙀🙀a yanzu aka tsunduma gundarin labarin🏃‍♀️

Shin wanene shu'aib?????

Miye alak'arshi da baba kallah?????

Wannan kantamemen gida na waye?????

Akafta🏃‍♀️

D/Auta ce🤝
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*___________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*_____________________________________*

*YAWAN COMMENT'S YAWAN TYPING 😒*

*PAGE TWENTY NINE*

*********************

Shu'aib ya b'ata fuska, sosai,  tamkar wanda bayason yin magana, a hankali yace;

"Suna cen na baro su a kan hanya, amma sun kusa k'arasowa a yanzu, saboda ni wata shegiyar yarinya ce ta dagula man lissafi a k'auyen da mukaje, ita bak'ar bak'auyiyah harda

wani d'aga allo ta makaman akan baki, gashi tajiman ciyo, bakina sai zafi yake yiman, ai wallahi naso inci ubanta, baba kallah ya hana ni, da na nuna mata k'aryar rashin kunya"

Ya k'are maganar tareda b'ata fuska, ya shafo gefen bakinshi da yake jin ciyon, sai muzurai yakeyi tamkar yakai naushi, kai kace  izzatun ce a gabanshi.

Hamshakiyar hajiyar kuwa shu'aib yana ambatar wata yarinya a k'auye, taji gabanta ya k'ire ya fad'i, jikinta ya d'auki mazarin rawa, hankalinta ya tashi, nutsuwar da ke tattare da ita ta gushe, ta tashi jikinta yana kyarma zata shige d'akin da naga ta fito, shu'aib ya kalleta a cikin mamakin shigar ta a wannan yanayi a cikin k'ank'anin lokaci, damuwa kwance a kan fuskarshi yace da ita;

Don Allah hajiya kidaina d'aga hankalinki, akan k'ananan abubuwa, kinsan fa ba isashiyar lafiya ce dake ba, kar kije ki janyo muna abunda zaisa mu koma asibiti a cikin wannan lokaci da muke ta zirga zirgar zuwa campaign"

Yana k'are maganar ne ya mik'e yaje ya rik'o kafad'arta ya dawo da ita falon, sannan ya zaunar da ita a  d'aya daga cikin kujerun dake falon, hajiyar sai maida numfashi takeyi sama sama, shu'aib ya kalleta yace;

"Ki kwantar da hankalinki hajiyata, kidaina saka damuwa a ranki kinsan likita yace ki rage tunani fa"

Hajiyar ta kalleshi dakyau tace;

"Shu'aib bazaka gane irin tarin damuwowin dake cunkushe a cikin zuciyata bane, kawai dai kaci gaba da tamani da addu'ar da kake yi, Allah ya fiddani a cikin wannan tashin hankalin da nike ciki, mik'o man magunguna na insha gasu cen"

Jikinshi yana rawa ya d'auko maganin,  tareda bud'a wata doguwar frizer dake ajiye a wata kusurwa ta falon, ya d'auko ruwa a wata gora mai kyau ya mik'a mata, ta amsa jiki ba kuzari ta b'alli magungunan tasha, sannan tafara maida numfashi d'aya bayan d'aya, ta mik'e tsaye a hankali zata shige d'akin da ta fito, saida takai k'ofar d'akin, sannan ta juyo ta kalli shu'aib tace;

"Ni zanje in d'an kwanta, idan kallah ya dawo kace dashi ya zo falon k'asa ina nemanshi"

Tana k'are maganar fuskarta a cunkushe ta shige d'akin ta turo k'ofar, shu'aib ya kasa d'auke kallonshi akan k'ofar a cikin zuciyarshi yace;

"Hajiya meke damunki ne nikam?, tsawon shekara da shekaru, wanda har ya hanaki sukuni da walwala?, gashi lafiyarki ma tana so ta kub'uce maki a dalilin wannan damuwa da kika saka a zuciyarki?"

Yana k'are tunanin ya furzar da wani iska mai zafi a bakinshi, saiga photon fuskar izzatu yana yawo akan gilashin idanunshi, a zabure ya gyara zamanshi, sannan ya fad'a dogon tunanin, wannan fuskar yarinyar da ya gani a yanzu, yaga kama tamkar kwabo da kwabo, a tsakaninta da Aunty hadizatou, don da ace a Niger ne yaga wannan yarinya ba tantama zaice k'anwa ce ga Aunty hadizatou, to amma ita wannnan bak'ar bak'auya me yahad'ata da Niger ma balle Aunty Hadizatou, kai kama ce kawai gaskiya don wannan bagidajiyar ko hanyar birni bazata sani ba balle wata k'asar Niger cen.

Ya ajiye wannan tunanin nashi marar tushe, ya sauko k'asa kai tsaye ya shige sashen shi domin ya watsa ruwa yaga in zai iya cin abinci da wannan baki nashi.

**

Koda malam ya dawo, mama hassatu takai masa kayan, tareda sanar dashi duk abunda sukayi da izzatu, amma ta b'oye masa abunda iya kulu tayi, don gudun abunda zai janyo tashin hankali a tsakanin iya kulun da malam d'in.

Malam kam ganin kayan, sun saka jikinshi yayi sanyi k'alau, ya tsurawa kayan kallo ko k'iftawa bayayi, saboda ya fad'awar da yayi a cikin dogon nazari, akan wannan rikici da yake so ya tunkaro su.

Ya sauke ajiyar zuciya yace da mama hassatu, suci gaba b'oye wannan sirri a tsakaninsu, har zuwa lokacin da gaskiya zata bayyana, don bayason izzatu ta gano ba sune suka haifeta ba a yanzu, har sai zuwa lokacin da ta k'ara mallakar hankalinta, mama hassatu tayi masa alk'awalin insha Allahu bazata bada wata k'ofar da izzatu zata gano wacece ita a wannan lokaci ba, saboda gudun abunda zai tab'a zuciyarta, har ya kawo cikas a karatunta, daga nan suka ci gaba da tattaunawa akan matsalar.

Mama ta d'ibi kayan siyasar kowane d'aya d'aya, taje har bakin k'ofar d'akin iya kulu tayi sallama, iya kulu dake ciki ta amsa ciki ciki, saboda har izuwa lokacin tana jin zafin kalaman da, mama hassatu tayi mata idan ta tunosu, mama ta shiga d'akin rungume da kayan, ta ajiye mata su akan gado ta fito ba tareda tace da ita k'anzil ba, saboda itama lafuzzan da iya kulun ta jefi izzatu dasu, sun mata ciyo ba kad'an ba, amma saboda hak'k'in zamantakewa yasa ta d'ibi kayan ta kaimata, ko ba komi zataci albarkacin izzatun,tunda ita duk da matsar k'ulin da tasha ta kasa samowa kanta irin su.

Iya kulu tabi mama hassatu da wani kallo tana mere, a cikin mamakin ganin kayan da ta zube mata a kan gado, shin bata kayan akayi?, ko ko gani akeso tayi?, a cikin zuciyarta tace;

"Koma dai miye ne, ni tunda har suka shigo hannu na, wallahi in kaf garinnan zai taru, to ba wanda zai sa in bada wad'annan kayan, tunda akazo har d'akina ana yiman kuri da gadara"

Ta shiga bud'a kayan tana jin dad'in samun su da tayi a b'agas.
Tun daga ranar da mama hassatu da iya kulu, sukayi wannan sa'insar, ba mai kula wani a

tsakanin su, sai zamansu ya koma irin na doya da manja, daman cen ba wani sakin jiki sukeyi da juna ba.

Mama ta kama kanta sosai da iya kulu, sannan taja kunne izzatu akan kada ta kuskura tayi wani abu da zai janyo iya kulu ta k'ara jifarta da wasu miyagun kalamai, don gudun ta fallasa sirrin da suke ta jin tsoron iya kulu ta fallasa.

Aiko iya kulu ganin mama ta daina shiga shirginta ne,  ta fara takale takalen abun da zaisa mamar,  ta biyeta suyita cacar bakin da takeso, don tunda taji malam bai yimata magana akan jafa'in da tayiwa izzatu ba, tasan mama hassatu bata fad'a masa fad'an da sukayi ba.  domin kuwa da yaji tabbas da bazaiyi shiru ya k'yaleta ba.

Cikin mama hassatu yana da wata biyar, alamomi irin na mace mai juna biyu,  suka fara bayyana ajikinta, ta k'ara haske fau, ta k'ara jiki, cikin ma ya d'an fito amman sai ka kula dakyau kake hangoshi, saboda cikin ya baje sosai a jikinta.

Kande da iya kulu suna zaune a tsakar gida, suna gulmace gulmacen da suka saba, mama hassatu ta fito tana ta aikace aikacenta, saboda izzatu bata nan tana makaranta.

Kande tabi mama da kallo, tareda yimata k'uri da idanun ta na munafucci, ta gyad'a kai sai faman kiran;
"Tabbas tabbas"ta keyi, iya ta kai kallonta gareta, sannan ta kai dubanta a wurin mama domin ta ganarwa kanta, abunda kande take kallo tana kiran tabbas.

Da bata hango komi ba, ta kaiwa kande duka a cinya tace;

"Waike kande meye abun kallo a wurin hassatu, da har kike ta kallonta, salon kisa ta rena mu"

Da sauri kande tace;

"Reni?,   na nawa kuma?, aike ta dad'e da gamawa dake gaba d'aya ma,  bama reni kawai ba, tunda har kikayi saken da kika barta tayi ciki a gidannan, aike taki ta riga ta k'are kuma, sai dai ki barwa hassatu gida ya zama nata, don d'iya ne zata yita b'ulb'ulowa a gidan, shikenan ke kinzama 'yar kallo tunda ke taki haihuwar an rufe maki magudanar ruwan ta tsaya cak! dole ne kiyi hak'uri  kiyi kallon masu d'uwawun haihuwa"

Ita dai mama hassatu ko kallo basu isheta ba, aikinta kawai takeyi tareda neman tsari da sharrin su a cikin zuciyarta, iya kulu kam tunda taji lafazin kande hankalinta ya gushe na wuccin gadi, har saida kande ta zungurota,  sannan ta dawo cikin hankalinta, ba shiri ta zabura tace;

"Ci  me?

Kande tace ;

"Ciki kuwa,  nan da watanni k'alilan,  Garzali da Abu za'a haifo masu  d'an uba ko 'yar uba, saboda haka sai ki fara tariyar kayan jarirai, kishiyarki zata haifo maki d'a, ashe rabon haihuwar a gidan malam  yake"

Iya kulu ta cika fam, sai huci takeyi, ba shiri ta shak'o wuyan kande, ta mak'ure saiga kande idanu sunyi ja sun turo waje,  sai k'ok'arin  k'watar kanta takeyi, amma ta kasa, aiko tana samun sa'a ta kaiwa iya kulu wani naushi a fuska, dole ta saketa don azabar da ta ziyarceta, kande taja takalminta a hannu tana cewa;

"Bani na kar zomon ba, ni ko rataya ma ba'ani ba kije cen kiyi haukarki akan wad'anda suka yimaki laifin bani ba, daga fad'in gaskiya?, shikenan  kizo kice zaki sauke fushinki a kaina?, to ni kinga tafiyata, na baki fili  kiji da yak'in dake a gabanki"

Tana shiga gidanta ta haye katanga ta lab'e tana sauraren iya kulu
da  tayi ta zuba ruwan  bala'i iya bala'i, tayi ta masifa har bakinta yana kunfa, don kawai mama ta biye ta suyi  dambe ayi sanadin cikin, amma mama tak'i biyeta, iya kulu ko da taga wankin hula zai kaita dare ne, ta fad'a har d'akin mamar ta kamata da kokawa, aiko mama hak'urinta ya k'are ta rarumo wani k'aton flak's dake cike da ruwan zafi, ta bugawa iya kulu, aiko marfin ya cire  ruwan zafin suka zube kaf ajikin iya kulu.

Ruwan suna sauka a jikinta, taji zafin ruwan ya ratsa ta, aiko ta fara  kururuwa tana neman hanyar fita d'akin,  tazo zata fito ne, ta saka hannu biyu ta ture Mama, ba shiri ta fad'i akan cikin ta k'wallah k'ara, kafin kace me saiga jini yana gudana a k'afafunta.

 Kande dake lab'e  tana ganin iya kulu ta shiga d'akin mama, aiko saigata ta zagayo ko takalmi babu, ta lab'e a k'ofar d'akin tana kallon abunda yake faruwa,  ganin jinin da ke fita a jikin mama yasa taji tsoro ta kwantsama kuwwa.

 Izzatu dake k'ok'arin shigowa gidan ta dawo daga makaranta, aguje ta fad'o saboda jin kuwwar kande, gabanta ya k'ire ya fad'i lokacin da tayi arba da mamarta a kwance,  jini yana malala a cikin d'akin, da sauri ta aza hannu akai taje ta rungumo mamar, tareda k'walla k'arar kiran sunanta, mama ta d'ago dak'yar tace da izzatu taje gidan mai unguwa ta fad'o masa azo akaita asibiti, aiko aguje ta fito, kande ta rik'eta tana kukan munafucci  tace da ita ;

"Ki rufa muna asiri don Allah,  kar ki fad'o wa mai unguwa"

Izzatu ta fisge daga rik'on da tayi mata,a cikin tashin hankali ta tureta,  aguje ta nufi gidan mai unguwa ta sanar dashi abunda yake faruwa, a gurguje yasa aka zo da mota aka kwashi mama sai asibitin birni.

A gurguje aka shiga da ita emergency room, izzatu da direban da mai unguwa ya turo, suna

zaune akan wasu kujeru, sautin  kukanta izzatu ne ya karad'e wurin, tana tanata wani irin kuka na tashin hankali gwanin ban tausayi, direban da sauran mutanen dake wajen gaba d'aya ta basu tausayi  sai hak'uri ake ta bata.

Nima dai kam na tausaya mata 😥

Akafta 😒

D/Auta ce🤝🏻
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: بسم الله الرحمن الر حيم
*______________________________________*

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*________________________________________*

*I love you too my fans💃💃*

*PAGE THIRTY*

*********************

An d'auki lokaci mai tsawo kafin a fito da mama hassatu, a kaita wani d'aki da majinyata suke jinya  a ciki, aka kwantar da ita, izzatu tazo da sauri ta rik'e hannunta tana kuka.

Dr, dake biye da su ne yace ina mutanen mama hassatu?,  direban mai unguwa, ya nuna kanshi da izzatu yace;

"Gamu"

Dr ya kalleshi ya kalli izzatu dake ta kuka, ya mik'awa direban wata farar takarda yace dashi ya biyoshi office, bayan sunje ne yake yimasa bayani kamar haka;

 "Munyi nasarar tsaida cikin da yayi barazanar zubewa,  Alhmdllh mun shawo kan matsalar, saboda haka a sanadiyyar fad'uwar da tayi,  jini ya zuba sosai a jikinta, wanda a yanzu haka ake buk'atar a saka mata wani jinin a cikin gaggawa, tareda wasu magunguna da ake buk'atar aje a siyo su yanzu yanzun nan, don tseratar da lafiyarta da ta abunda ke cikin"

Direban ya saka hannu a aljihu ya ciro kud'in da mai unguwa ya bada ya mik'awa Dr, a cikin damuwa yace;

"Gasu sai ka rik'e a hannunka, ka taimaka a siyo magungunan da abunda ake buk'ata, yanzu zanje k'auyen mu,  in fad'awa mai unguwa abunda yake faruwa sai a nemo mijinta, domin asan yanda za'a asamo jinin da ake buk'ata"

Dr ya karb'i kud'in jikinshi a sanyaye, yace dashi yayi sauri ya dawo, saboda ana buk'atar jinin asaka a gaggauce, in ba haka ba rayuwarta tana cikin k'ila wa k'ala.

Da sauri direba ya tafi kamar ya kifa, saboda tausayin mama hassatu da ya mamaye zuciyarshi, Dr d'in ya fito yaje yabada aka siyo abunda ake buk'ata, shiru shiru direba bai dawo ba, sai kawai ya nufi d'akin da aka kwantar da mama, don yasan izuwa lokacin zata shiga yanayin da ba'a fata.

Aiko yana zuwa ya iske izzatu rungume da ita tana ta wani marayan kuka,gwanin ban tausayi, saboda shak'uwar da mama take tayi jere a jere, izzatu dafe da gadon hannunta cikin na mama gwiwowiinta a k'asa tana kiran:

"Mama ki tashi kar ki mutu, don Allah kar ki mutu mamata, idan kika barni bansan ya zanyi da rayuwata ba"

Tausayi ya mamaye zuciyar likitan, ganin yarinya kamar izzatu kyakkyawa ajin farko, ace ta shiga gararin rayuwa, asanadiyyar ciyon mahaifiyarta, jikinshi yana b'ari yaje aka auna jininshi,

Alhmdllh  zaiyi dai dai da nata idan an saka, aiko batareda wani jinkiri ba ya  kwanta aka d'ibi gora d'aya, ya bada umurnin aje asaka mata kafin mijinta yazo, aiko ba b'ata lokaci, aka mak'alawa mama hassatu jinin, izzatu tana gefe sai kuka takeyi, idanunta da fuskarta sunyi ja sosai,  saboda tsananin kukan da tasha.

Bayan an k'are lak'awa mama jinin ne, izzatu ta tambaya ina direban da sukazo tare dashi, wata nurse ta fad'a mata cewa yaje k'auyensu bai dawo ba har lokacin, shiyasa  Dr ya bada jininshi a sakawa mama, yanzu haka yana cen kwance kafin ya murmure ya fito, aiko ba shiri ta dubesu tace ;

"Idan kunje ina gaida shi sosai don Allah kuyi masa godiya kafin yazo"

Suka ce "to" sannan suka fita, izzatu a cikin zuciyarta tana ta jinjina irin mutuncin Dr'n.

Bayan kamar minti talatin, sai ga Dr ya shigo, a lokaci d'aya ya rame ba kamar ganinshi da izzatu tayi a farko ba, haka kawai taji ya burgeta, tana yimasa wani kallo irin na girmamawa, saboda tsananin mutuncin da yayi masu, tareda tausayin da yakeyi na bayin Allah masu buk'atar taimako.

A ladafce ta sunkuya ta gaidashi, tareda yi masa godiya akan abun alkhairin da yayi masu, a cikin rashin damuwa yace:

"Ba komi ai yiwa kai ne"

Daga nan ya dudduba mama yace;

Idan jinin ya k'are ba wanda yazo daga cen k'auyen, za'a siyo mata wani jinin sai a k'ara mata, izzatu ta k'ara yimasa godiya sannan ya fita, zuciyar shi fess take da farinciki, sabida ya hango wa kanshi yabanyar da ta dace dashi, domin tunda ya k'yalla ido akan kyakkyawar fuskar izzatu,  yaji a duniya kaf ba macen da yakeso sai ita, daman shi cen ba gwanin soyayya bane, amma gashi caraf izzatu ta tafi da tunanin shi.

Izzatu tana nan zaune har jinin ya k'are direban bai dawo ba, Dr ya shigo da wani jini da ya siyo, ya sake mak'ala mata, yana cikin aikin ne, saiga Garzali ya shigo d'akin hankalin shi a tashe, izzatu tana k'yalla idanuwa ta hango shi, da gudu taje ta fad'a jikinshi, tareda fashewa da wani kuka  mai tada hankalin mai sauraro.

Shima a buk'ace yake da ganin 'yar k'anwar tasa, ya saka hannu ya rungumeta sosai a jikinshi, ya bubbuga bayanta alamar tayi shiru, saboda ya kasa furta wata kalma a bakinshi saboda cunkoson damuwowi da suka yimasa yawa a zuciya.

A cikin dubara ya b'anb'areta daga jikinshi,  saboda kallon da yaga ana ta yimasu, sannan ya rik'o hannunta suka k'araso a jikin gadon mama, wasu hawaye masu zafi suka kwaranyo akan fuskarshi, duk da kasancewarshi jarumin namiji, wanda ba komai ne yake saurin sakashi kuka ba, amman yaji tausayin halin da yaga mama a ciki, sannan ga iya kulu cen itama ya baro sai kuka takeyi, saboda jikinta kaf k'unar ruwan zafi ne, ya rasa ina zai jefa kanshi yaji sanyi, gashi anyita kiran number malam ba'a sameshi ba, k'arin takaicin kuma kukan da izzatu ta taresa dashi.

Da sanyi jiki ya mik'awa Dr hannu suka gaisa, yayin da shi Dr haushin Garzali ya cika masa ciki, ganin irin rungumar da yayiwa izzatu a gabanshi, wanda a ranshi yaketa sak'e sak'en Garzali ba ciki d'aya suka fito da izzatu ba, shiyasa yana k'are abunda yakeyi ya fita yabar masu d'akin, saboda takaicin narkewar da yaga izzatu tayiwa Garzali a jiki,  yana ta faman lallashinta.

**

Hamshak'iyar hajiyar nan ce,  a katafaren d'akinta da ya k'awatu, kamar baza'a bar duniya ba, sai faman safa da marwa takeyi a tsakiyar d'akinta, fuskarta d'auke da d'inbin damuwar da ta kasa b'oyuwa a gareta, sai faman tunanin mafita takeyi, sai sak'awa da kwancewa kawai takeyi, a bayyane ta furta cewa;

"Ni Fatima ya zanyi da rayuwa ta ne?, nayi abu ya dawo ya dameni, fushin zuciya da sharrin shed'an sun sakani aikata abunda idan ban tona asiri  na warwareshi ba, har abada bazan tab'a yafewa kaina ba, wanda nasan Allah ma bazai yafeman ba, na saka rayuka da yawa a damuwa, don kawai in rama abunda aka yiman, sai gashi nice nafi kowa shiga damuwa akan hakan, hak'k'in da na d'auka sai bibiyata yakeyi"

Ba shiri ta fashe da kuka, sai istigfari takeyi a fili da zuciyarta, tana datasani akan abunda ta aikata.

Yafi tsawon minti biyar a tsaye yana kallonta, ganin ta saka kanta a damuwar da likitoci da yawa suka ce ta daina shifa, tun yana d'aukar abun ba komi ba, to yanzu shi kanshi a sanadiyyar halin da take a ciki baya da sukuni, duk da ruguntsumin siyasar da suke a ciki, amman yafi jin damuwarta akan wannan.

A hankali ya tako har inda take, durk'ushe a jikin gado tana ta kuka, cikin murya mai cike da tausayi ya kira sunanta yace;

"Hajiya fatima! Wai menene kike b'oye mani ne?,  wanda har bakya son insani, wanda ya saka ki a cikin damuwa shekara da shekaru, idan laifin da nayi maki ne na baki hak'uri, kuma kince kin yafeman, koko dai matsalar da kike ta samu ne a wajen haihuwa shine yake saki wannan damuwa?".

Hajiya fatima ta girgiza kai, a cikin damuwa yace;

"To me yayi zafi bintu?, ki fa yi imani  da duk abunda kika ga ya sameki, ke mai ilimi ce, yakamata ace kinyi tawakkali kin rungumi k'addararki"

Oh ni dije Shin meke faruwa da wannan ahalin?😥🤔

Akafta🧑‍🦯

D/Auta ce😘

[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*FIRST CLASS WRTTERS ASSOCIATION*

*Albishirinku masoya littafan  hadiza d/Auta akwai wani sabon buk dina zai fito kwanan nan mai suna BAKAN GIZO... littafine mai kunshe da ban TAUSAYI, cin AMANAR KAUNA,Rashin TAWAKKALI,  tareda DAUKAR FANSA, dama sauran abubuwan da ba'a lissafo ba kar ku bari abaku labari🏃‍♀️*

*PAGE THIRTY ONE*

*********************

Hajiya fatima ta k'ara fashewa,  da wani gigitaccen kuka tareda cewa ;

"Bansan ya zanyi da rayuwata ba ABBAAH, tunda yarinyar nan ta b'ata natsuwata ta gushe,

farincikina yayi k'aura, komi na duniya ya daina bani sha'awa, shin taya zanyi in dawo da farincikin da na rasa Abbah?, ka bani shawara don Allah nima nagaji da ganin kaina a cikin wannan hali"

Anan take Abbaah'n ya had'e fuska, annurin dake kwance a fuskarshi ya gushe, a cikin jin haushin kalamanta yace; ,

"Haba bintu wai meyasa kika kasa yarda da k'addara ne?, Hadizatou ma da ta haifo yarinyar nan, izuwa yanzu ta hak'ura ta daina shiga damuwa akan b'atanta, amma ke kin kasa hak'uri ki cire abun a ranki, haka kawai kin d'aukarwa kanki fitina kin d'orawa kanki, kin hana kanki zama lafiya, kin hanawa mutane, lafiyarki tayi k'aranci duk a kan haka, shin wannan tashin hankali har ina?, to bari kiji daga yau idan har baki daina irin wannan shirmen ba, to zan d'auki mummunan mataki akanki"

Yana k'are maganar ya fita fuuu, ya bar mata d'akin, Hajiya fatima ta k'ara sautin kukanta, tareda kiran sunan Allah akan ya kawo mata agaji, ya warware wannan matsala a cikin ruwan sanyi, batareda mutuncinta ya zube a idanun duniya ba.

**

Dr ya kasa zaune ya kasa tsaye, sai zarya yakeyi acikin office d'inshi, har ga Allah son izzatu yayi masa shigar sauri, batareda zato ko tsammanin hakan ba, yana cikin farinciki, sai gashi kwatsam zuwan Garzali ya rusa masa komi, a ranshi sai tambayar kansa yake, Shin meye dangantakar Garzali da izzatu, don a zahirin gaskiya a son izzatu ba gudu ba ja da baya, har sai yaga abunda ya turewa buzu nad'i.

Jikinshi har rawa yakeyi akan ya koma d'akin majinyatan, domin ya k'ara gasgata abunda yake zargi.

Koda ya shiga ya iske d'akin a cike yake da mutane, shigowarshi ya katsae masu firar da sukeyi, izzatu fuskarta a washe ta feshe shi da wani sihirtaccen murmushi, wanda ya ratsa tun daga kanshi har zuwa tafin k'afarshi.

A ladafce izzatu ta nuna Dr ga malam dasu inna hure da wasu 'yan uwan mama hassatu da sukayo angaya suka zo ganinta, tareda cewa;

"Kunga likitan nan ma ya shigo, shine ya bada jininsa aka sakawa mamata"

Gaba d'aya har had'a baki sukeyi wajen yimasa godiya, a kunyace yace;

"Ba komi yiwa kai ne"

Mama hassatu ma da a lokacin ta farfad'o, daga kwancen tayi masa godiya, acikin muryarta ta

da ta dusashe,  sai kace wadda taja lokaci tana jinya, saboda ciyon ya bugeta sosai, a fakaice Dr yakai kallonshi akan izzatu, yayinda ita kuma a lokacin suna magana k'asa k'asa itada Garzali, inna hure da hankalinta yakai kansu tana dariya tace;

"Yaya da kanwa gulmar wa akeyi ne a cikin asibiti?, ku a ko'ina ma sai kun nuna halinku?, to tashi dai ka koma makaranta, mun gode da ziyarar hakanan"

Izzatu tayi saurin yin magana tace;

"Haba inna hure, don Allah ki bar man yayana, nidai bangaji da ganinsa ba gaskiya"

Ta k'are maganar tareda b'ata fuska, wasu sababbin hawaye suka zubo mata.
Inna hure tana dariya tace;

"Ah lalle akwai aiki ja a gabanku"

Mama daga kwancen ta rik'o hannun izzatu, tareda yimata alama da ido, akan tayi shiru, izzatu kam daman cen kukan a kusa yake, shiyas hawayen suka dinga sirnano mata akan fuska, Garzali ya rik'o hannunta yace;

"Taso muje waje kiji k'anwata"

Aiko tayi tsam tabi bayanshi, inna hure sai tsarguwa take yimasu, malam duk da zuciyarshi a cunkushe take da damuwa, sai da ya dara, yace da inna hure;

"Mudai iyakacin mu kallo, amman ke hure yaushe suka zamo jikokin ki?"

Inna hure tana dariya tace;

"Na ari bakin Dada yau"

Daga nan suka k'ara yiwa Dr godiya, yayinda Dr ya fito malam ya biyo bayanshi, Dr tafiya yakeyi zuwa office d'inshi,  amman idanuwanshi suna kan Garzali da izzatu da suke zaune yana lallashinta.

Bayan sunje office d'inne Dr yayiwa malam bayanin komi akan ciyon mama hassatu, malam yaji dad'i akan taimakon da yayi masu, ya tambayi Dr abunda aka kashe sai ya biya, amman Dr ya nuna yayi komi don Allah badon a biyashi ba, malam yaji dad'in wannan karamci na dr tareda jaddada godiyarshi a gareshi.

Inna hure da wata k'anwar mama hassatu sai izzatu da Garzali, sune sukayi jinyar mama hassatu har taji sauk'i, Dr ma sai fad'i tashi yakeyi dasu, ta b'angaren jikinshi da aljihun shi, su inna hure sai jinjina kirkin Dr sukeyi, duk da zuciyarsu ta basu da biyu a cikin wannan hidima da

yake yimasu, amman saboda bai furta abund ke zuciyarshi ba,  shiyasa suma suka share, sai kwasar ganimar su sukeyi, har saida malam yace dashi d'awainiyar tayi yawa, amman bai fasa ba, saboda shima malam  a kullum nan yake yini,  sai da yamma ya koma k'auyensu.

Mama hassatu taji sauk'i sosai aka sallamesu, tareda gindaya mata dokoki masu yawa, saboda kare lafiyarta data abunda ke cikin, dukansu sunji dad'in ganin mama hassatu ta sami sauk'i, musamman Dr da ya matsu su koma gida ya fara kafa gwamnatinshi a wurin masoyiyarshi izzatu, duk da ganin shekarunta a lokacin basu kai ba, amma ya k'uduri aniyar zaiyi ta rik'o har zuwa lokacinda zata san minene so.

Ranar da aka sallamaesu, Dr da kanshi ya d'auki malam,  da mama  da inna hure,  da sauran dangin mamar ya kaisu k'auyen, yace da Garzali da izzatu da d'iyar inna hure Amina su jira ya kaisu malam ya dawo ya kaisu suma, aiko haka akayi yana ajiye su malam ya dawo ya d'aukesu, har sun fara tafiya  yace dasu, don Allah suyi masa uzuri ya karb'o wani sak'o a wani wuri, sukace;

" Ba duwawa"

Dr kai tsaye ya wuce wani katafaren shago, wanda a saman shi aka rubuta ;

BADAWI SHOPPING COMPLEX.

Izzatu tana d'aga kai tayi arba da sunan, a nan take poster'r YAHAYA BADAWI ta fad'o mata a rai, jiki a sanyaye tace da Dr ;

"Don Allah inzo in raka ka?"

Garzali ya maka mata harara,
Dr yayi murmushi yace;

"Bismillah zo muje"

Izzatu ta kawar da kanta kamar bata ga hararar da yayant yake yimata ba, tabi dr jiki a sanyaye.
A k'ofar shagon ne,  izzatu taji kirjinta ya buga, amma ta daure sai  kalle kallenta takeyi, ba shiri taci karo da wata mata har tana k'ok'arin fad'uwa,matar ta saka hannu zata d'agota, izzatu kuwa idonta akan matar, gabanta sai dakan lugude yakeyi, bakinta yana rawa zata baiwa matar hak'uri ne, aiko  matar tayi saurin juyawa da sauri, saboda kiran da wani yaro dake cikin wata had'ad'd'iyar mota yayi mata yace;

"Ammi kizo Ammar ya yanke hannunsa da clipper"

🙀🙀🙀🙀

Akafta🏃‍♀️

D/Auta ce🤝🏻
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*NAJI DADIN COMMENT'S DINKU MASOYA NA DA MASOYA BUK DIN RUWA DA KANKARA KUNA SANI NISHADI BA KADAN BA KUSANI KUNA CIKIN ZUCIYAR D/AUTA DUKANKU I LUV YOU ALL MY GAY'S 💋*

*KUZO MUSHA RUWA DA KANKARA⛹️‍♀️💃*

*PAGE THIRTY TWO*

**********************

Har ta shige motar,  taja ta da k'arfi ta bar harabar shopping complex d'in,  izzatu bata daina kallonta ba,baki a sake tana mamakin wannan fuska da ke yimata gizo, idan ba k'arya tayi ba tabbas ko tantama babu, fuskarta ce sak ajikin fuskar wannan mata, banbancinta da ita shine shekaru,  amma tabbas ba makawa wannan mata da aka kira da suna AMMI suna kamanceceniya da juna, to tayaya?, shin miye had'inta da ita da suke kama?, izzatu ta kasa baiwa kanta wannan amsar, wata zuciyar tace da ita ;

"Kama ce kawai, amma taya zaki had'a kanki da wannan mata irin hutu, wadda a duba d'aya zaki gano hutun da ya ratsa fatar jikinta, kina 'yar k'auyenki, ya zaki had'a kanki da ita?, kin manta ance a duniya akwai mutanen da Allah ya halitta iri d'aya, ba tareda sun had'a jini ba, wani ma ba'a k'asa d'aya dashi ake ba, to kema hakan ce ta faru dake ko yanzu"

Tana nan a tsaye jiki ba kuzari, har Dr ya fito hannuwansa rik'e da ledodi, ba tareda ya kula da yanayinta ba, yana murmushi yace da ita;

Sorry my izzah! na b'ata maki lokaci ko?, to kiyi hak'uri muje gani na fito, amman meyasa baki shiga daga ciki ba,  sai kikayi tsayenki a nan?.

Izzatu tayi saurin saita natsuwarta, sannan tayi murmushi tace;

"Ba komi"

Dr ya kalleta tareda wanke fuskarshi da wani murmushi mai tsada, suna tafe suna 'yar firarsu a hankali, har suka k'araso a jikin motar, izuwa lokacin Garzali ya cika fam, sai Harbin iska yakeyi da hannu, don jinsa yakeyi tamkar ya kama Dr yayita jibgarsa, a zuciye ya b'alle murfin motar ya fito, ya nufi titi ya tare wani d'an acab'a ya haye, izzatu ta kira sunan shi a cikin d'aga murya tace;

"Yayana ina zakaje ne?, gashi muna ta sauri zamu wuce gida"

Garzali ya maka mata wata bajimar harara, yace da d'an acab'an su wuce, a cikin d'aga murya, aiko d'an acab'a ya fisgi mashin d'in kamar walk'iya suka bar wajen, izzatu ganin hararar da Garzali ya maka mata, ta saka jin kanta a cikin damuwa,a nan take wasu hawaye  suka zubo mata, Dr ya kalleta yayi murmushi saboda yagano kishi ne yake d'awainiya da Garzali, a cikin sakin fuska yace da ita;

"Muje ko?"

Ta kalleshi da kyau tace;

"Mu jira ya dawo, don kar yazo ya tarar da bama nan, kasan bazai ji dad'i ba"

Dr yana murmushi yace da ita;

"Muje kawai nasan bazai dawo ba, idan munje,  zamu tarar dashi a gidan kada ki damu zo muje"

Izzatu ta k'ara b'ata fuska tace;

"Kuje kawai,  NI zan jirashi a nan d'in,  har sai ya dawo"

Dr yaji zafin maganar amma ya dake, yana murmushi yace;

"Kizo muje, don bafa zai dawo ba, ko bakiga  fushi yayi bane?,"

Sannan izzatu ta tuno da hararar da maka mata, bayan ya haye mashin, jikinta a sanyaye ta shiga, tana ta nuk'u nuk'un kukanta har sukaje gida, Amina sai hkr take bata, amma kamar k'ara zugata takeyi, saboda zuciyarta ko kad'an bata yimata dad'i.

A bakin bishiyar dake k'ofar gidan Dr ya tsaya, yaran k'auyen, har sun fara taruwa wajen kallon su, jiki a sanyaye izzatu ta fito,itada Amina har suna had'a baki a wajen yimasa godiya, Amina ta shige gidan, izzatu ma ta juya zata shiga ne dr ya kira sunanta, da wata murya dashi kanshi baisan yana da irinta ba sai a lokacin, duk da k'arancin shekarun izzatu, amman taji kiran ya ratsa jikinta, a cikin ladabi ta juyo, tareda takowa har inda yake, idonta a kanshi tace;

"Allah yasa ba laifi nayi ba?"

Dr ya gyara tsayuwar shi yana murmushi yace;

"Kinyi laifi kam, tunda kika k'i tsayawa muyi sallama"

Izzatu tayi murmushin k'arfin hali tace;

"Sorry, nayi laifi ayiman afuwa, mungode sosai da d'awainiyar da kayi muna, Allah ya biyaka yasaka maka da gidan aljannah, ya baka abunda kake nema duniya da lahira"

Dr sai Ameen yake fad'i, saboda yaji dad'in addu'o'in izzatu, tarbiyyar izzatu da shagwab'arta, sune suke k'ara fisgar shi a soyayyarta, a cikin wani farinciki da ya tsinci kansa a ciki ya bud'a motar ya ciro ledodin dake ajiye ya mik'a mata, bakin shi a washe yace ;

"Gashi idan kinje gida ki bud'a ki gani, naki ne tukuicin addu'ar da kika yiman"

Izzatu tayi jim tana tunani, sannan tace dashi;

"Kayi hak'uri idan naje dasu nasan malam zaiyi fad'a, tunda ko a asibiti yayi fad'a akan ka daina wannan d'awainiya tayi yawa, abunda kayi ma mungode wallahi, don bazamu iya biyanka ba, sai dai muyi maka fatar gamawa lafiya"

Dr ya b'ata fuska yace;

"Idan har da gaske kike fad'ar maganganunki, to ki karb'a kawai, idan kuma renawa kikayi shikenan ba damuwa sai in hak'ura"

Izzatu ta saka hannu biyu ta karb'a tayi masa godiya ta shige gida, Dr ya bita da kallo har ta shige sannan yaja motarshi yabar k'auyen, tareda jin kansa a cikin wani shauk'in so da k'aunar izzatu.

Kuyi manage  kwanan ina da matsala sosai akan rashin caji😥

Akafta😅

D/Auta ce🥰
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*Na zaune baiga gari ba, ba sauri nike ba, sai inbar gudun fama,in waigo in k'i sufuri dole a d'auki  tabarma, nai nazari akan samu dole yafi zuwar wa mai nema💃💃💃💃*

*Da damana kwari sukeyin sansani, mara gaskiya a cikin idonsa zaka gani,ki gudu sai mu kira masa sa gudu ya gani,raba gardama zaki cikin dawa yake sa natsuwa, da damana ni nasan sama ke zubda ruwa💃💃💃*

*PAGE THIRTY THREE*

**********************

Jiki ba kuzari izzatu ta shiga gida, ganin takalma da yawa a k'ofar d'akinsu ne,hakan ya tabbatar mata d'akin acike yake da 'yan dubiya, tayi d'akin Garzali, saboda malam yasa an raba  d'akin Dada biyu, Garzali rabi Abu rabi, ganin rayuwar da Abu ya jefa kansa a ciki, saboda idan garzali ya ajiye kayanshi, kafin yaje ya dawo Abu ya salwantar, da ya dawo ayita rigima, shiyasa malam ya raba masu d'akin hankalin kowa ya kwanta.

A bakin k'ofar taja ta tsaya, har sai da ya bata umurnin shiga,  sannan ta d'aga labule ta shiga da sallama, ta ajiye kayan a gefe sannan ta zauna, ta tsurawa Garzali ido,ganin ko inkular da yayi da ita ne, wasu hawaye suka gangaro mata akan fuska, da taga yak'i kulata ne ta fara kuka a hankali tareda shesheka.

Ba shiri ya d'ago fuskarshi ya kalleta, ranshi gabaki d'aya a dagule yake, shiyasa tun shigowarta a d'akin yak'i kulata, amman jin sautin sheshekar kukanta ne, yasa jikinshi yayi sanyi, a hankali

yace da ita;

"Me aka yimaki ne   kike kuka?"

Izzatu ta d'ago fuskarta ta kalleshi ido cikin ido, sannan tace;

"Bansan laifin me nayi maka ba, da har zaka tsaneni"

Garzali ya tsura mata ido, zuciyar shi sai hasko masa izzatu da Dr takeyi, lokacin da suka fito shopping complex suna murmushi, ya k'are had'e fuskarshi alamun ba sauk'i yace;

"Miye alak'ar ki da wannan Dr?"

Izzatu ta zaro ido a waje tace;

"Wani abu yace maka nayi masa halan?"

Garzali ya harareta yace;

"Ko kin masa laifin ai ba gani zaiyi ba,bale ya kawo k'ararki tunda yana sonki"

Izzatu ta k'ara zaro ido, tareda dafe k'irjinta dake bugawa tace;

"So fa kace yayana?, nikam ya zanyi da wannan k'atoton mutumin?, inyi yaya dashi?, kalleni fa 'yar k'aramata dani zai ce yana so?, wallahi  mutunci ne kawai da yake dashi, amman ba wani so a tsakaninmu yayana, ka yarda dani"

Ta k'are maganar tareda mayar da fuskarta kalar tausayi, Garzali kam yaso yayi dariya amma ya dake, a fili yace ;

"Wannan tada hankali na miye?, bakya son shi ne?"

Izzatu ta rufe fuska tana dariya tace;

"Ni kam ba wanda nikeso kaf, duniyar nan"

Da sauri garzali ya zaro ido, tareda dafe k'ijinshi da ya buga dam! dam! Yace;

"Yanzu kina nufin harda ni bakyaso?"

Izzatu ta rufe bakinta tana dariya tace;

"To ai kai d'an uwana ne, taya zan auri yayana?"

Garzali kam a lokaci d'aya ya b'ata fuska, yaji wasu hawaye masu zafi sun zubo masa, a cikin dubara ya share hawayen, sannan a cikin muryar kuka yace;

"Yanzu shikenan ashe ni ba  sona kike ba"

Izzatu ta b'ata fuska ganin, hawayen da yake k'ok'arin b'oye mata, a cikin sanyin murya tace;

"Yaya Garza na!, kaf duniya idan aka cire malam da mama, babu wani wanda nike so sama da kai, don bakasan yanda nike jin k'aunarka a zuciyata bane yayana, ko mama da tace dani, idan nayi sallah na dinga rok'ar Allah ya bani miji nagari, to aduk na tashi rok'on da siffarka nike rok'o,  akan Allah ya bani miji na gari irinka, fuskarka, tsawonka, hasken ka,  yanda kake d'an gayen nan, to ka gani idan bana sonka taya zanyi wannan addu'ar"

Ba shiri wani farin ciki ya mamaye zuciyar Garzali, a cikin zumud'i ya ri'ko hannuwanta duka biyu ya saka a cikin nashi, wasu hawaye suka kwaranyo akan fuskarshi, bakin shi yana rawa yace da ita;

"Ina son kiyi man wani alk'awali k'anwata"

Izzatu Ma ganin hawaye a fuskar shi,  hawayen takeyi, a cikin k'arfin hali tace;

"Nayi maka alk'awali matuk'ar ba sab'awa mahaliccinmu bane, to zan amince da duk abunda kazo dashi yayana"

Garzali zai bud'a baki yayi magana, iya kulu ta d'aga labulen d'akin, ganin Garzali rik'e da hannun izzatu ne yasa  ta rafka salati, ba shiri suka saki hannun juna, iya kulu ta d'aga hannu ta kwad'awa izzatu wani bahagon mari, tana kururuwar azo agani izzatu zata yiwa Garzali fyad'e.

Aiko duk mutanen dake gidan, masu zuwa ganin jikin mama hassatu sukayo d'akin Garzalin, duk wanda ya lek'a yaga izzatu zaunenta har da hijabinta sanye, Garzali ma haka suturar shi, sai ayi turus, saboda kowa ya kasa ganin illar abunda,  iya kulu take so ta sanarwa mutane.

A hankali,  mama hassatu ta tako, ta shigo d'akin tareda yimasu kallon tsaf, jiki ba k'arfi ta rik'o hannun izzatu tace;

"Tashi muje d'aki, kai kuma ka shirya ka koma makaranta yanzu, ka gani naji sauk'i ko?,  to aje aci gaba da karatu, Allah ubangiji yayi taimako"

Mama hassatu ta fito d'akin hannunta rik'e da izzatu, bayan ta d'auko ledodin suka fito, kai tsaye suka shige d'akinsu, iya kulu ko tana nan a tsaye k'ofar d'akin Garzali cike da mamakin ganin yana had'a shirginshi yana lodawa a jaka, yana k'are had'a komi nasa ya fito, iya kulu mamaki bai daina kama ta ba, har saida taga Garzali yana rufe d'akinshi da makulli, baki a sake tace;

"Au waton dai ashe da gaske ba donni kazo gidan ba, ii lalle abu ya girmama, an shanye uba an shanye d'a"

Garzali bai kulata ba, fuskar shi a had'e yace da ita ;

"Ni na wuce sai Allah yayi dawowata"

Yana k'are maganar ya nufi d'akin mama yayi mata sallama a tsatstsaye, yaja jikar shi ya fice gidan, izzatu ta fito d'akinsu da gudu ta nufi, bayan d'akunan su Garzalin, ta duk'a ta tone wani abu a leda ta fita a guje, har yayi nisa ta k'walla masa kira, ba shiri ya waigo, ta isa tana haki ta mik'a masa ledar, a cikin mamaki yace da ita;

"Miye a ciki ne?"

Ba tareda tayi magana ba, ta kwance ledar, saiga kud'i dami guda, ta ciro  su ta mik'a masa, yasaka hannu ya karb'a mamaki a fuskarshi ya lissafa kud'in,sannan yace da ita;

"Naga kud'i na minene?"

Izzatu ta b'ata fuska, sannan tace;

"Malam ne yace a baka, shine mama tace inkawo maka"

A nan take wani murmushi ya maye gurbin, b'acin ran dake kwance a fuskarshi, fuska a washe yace;

"Malam ko ya manta ya bani kud'i kafin ya tafi?"

Izzatu tayi saurin fad'in ;

"Eh yana sane ai, yace ne ka k'ara, koda  za'a buk'aci wani abu acen makarantar"

Garzali yayi murmushi yace;

"To kice dashi nagode sosai"

Shima ya ciro dubu d'aya a cikin kud'in ya mik'a mata yace;

"Kema gashi kije ki k'ara a kud'in break"

Izzatu tayi murmushi tace;

"Nagode yayana kaje kawai Allah ya kiyaye"

Da sauri ta fara tafiya da baya baya, tana yimasa bye bye, jikinshi a mace ya gyara goyon jakar da yayi, sannan ya hasketa da wani shaharren murmushi yace;

"Sai na dawo ki kula da kanki"

Wasu hawaye suka zubo mata, da sauri ta juya ta fara tafiya har ta kusa k'ule wata kwana, sannan ta waigo yana nan inda ta barshi, ba shiri wata kunya ta ziyarceta, da sauri ta rufe fuskarta da tafukan hannyenta, ta sha kwanar ta lab'e.

Garzali ya girgiza kai yana dariya, ya juya ya fara tafiya, izzatu ta lek'o kanta, akayi dace shima ya waigo, ba shiri dukansu, suka k'yalk'yale da dariya.

Soyayya ruwan zuma in kasha kaba masoyi💃💃💃💃😹

Akafta 🤺

D/Auta ce😜
[8/23, 1:43 PM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*Na zaune baiga gari ba, ba sauri nike ba, sai inbar gudun fama,in waigo in k'i sufuri dole a d'auki  tabarma, nai nazari akan samu dole yafi zuwar wa mai nema💃💃💃💃*

*Da damana kwari sukeyin sansani, mara gaskiya a cikin idonsa zaka gani,ki gudu sai mu kira masa sa gudu ya gani,raba gardama zaki cikin dawa yake sa natsuwa, da damana ni nasan sama ke zubda ruwa💃💃💃*

*PAGE THIRTY THREE*

*********************

Jiki ba kuzari izzatu ta shiga gida, ganin takalma da yawa a k'ofar d'akinsu ne,hakan ya tabbatar mata d'akin acike yake da 'yan dubiya, tayi d'akin Garzali, saboda malam yasa an raba d'akin Dada biyu, Garzali rabi Abu rabi, ganin rayuwar da Abu ya jefa kansa a ciki, saboda idan garzali ya ajiye kayanshi, kafin yaje ya dawo Abu ya salwantar, da ya dawo ayita rigima, shiyasa malam ya raba masu d'akin hankalin kowa ya kwanta.

A bakin k'ofar taja ta tsaya, har sai da ya bata umurnin shiga, sannan ta d'aga labule ta shiga da sallama, ta ajiye kayan a gefe sannan ta zauna, ta tsurawa Garzali ido,ganin ko inkular da yayi da ita ne, wasu hawaye suka gangaro mata akan fuska, da taga yak'i kulata ne ta fara kuka a hankali tareda shesheka.

Ba shiri ya d'ago fuskarshi ya kalleta, ranshi gabaki d'aya a dagule yake, shiyasa tun shigowarta a d'akin yak'i kulata, amman jin sautin sheshekar kukanta ne, yasa jikinshi yayi sanyi, a hankali yace da ita;

"Me aka yimaki ne kike kuka?"

Izzatu ta d'ago fuskarta ta kalleshi ido cikin ido, sannan tace;

"Bansan laifin me nayi maka ba, da har zaka tsaneni"

Garzali ya tsura mata ido, zuciyar shi sai hasko masa izzatu da Dr takeyi, lokacin da suka fito shopping complex suna murmushi, ya k'are had'e fuskarshi alamun ba sauk'i yace;

"Miye alak'ar ki da wannan Dr?"

Izzatu ta zaro ido a waje tace;

"Wani abu yace maka nayi masa halan?"

Garzali ya harareta yace;

"Ko kin masa laifin ai ba gani zaiyi ba,bale ya kawo k'ararki tunda yana sonki"

Izzatu ta k'ara zaro ido, tareda dafe k'irjinta dake bugawa tace;

"So fa kace yayana?, nikam ya zanyi da wannan k'atoton mutumin?, inyi yaya dashi?, kalleni fa 'yar k'aramata dani zai ce yana so?, wallahi  mutunci ne kawai da yake dashi, amman ba wani so a tsakaninmu yayana, ka yarda dani"

Ta k'are maganar tareda mayar da fuskarta kalar tausayi, Garzali kam yaso yayi dariya amma ya dake, a fili yace ;

"Wannan tada hankali na miye?, bakya son shi ne?"

Izzatu ta rufe fuska tana dariya tace;

"Ni kam ba wanda nikeso kaf, duniyar nan"

Da sauri garzali ya zaro ido, tareda dafe k'ijinshi da ya buga dam! dam! Yace;

"Yanzu kina nufin harda ni bakyaso?"

Izzatu ta rufe bakinta tana dariya tace;

"To ai kai d'an uwana ne, taya zan auri yayana?"

Garzali kam a lokaci d'aya ya b'ata fuska, yaji wasu hawaye masu zafi sun zubo masa, a cikin dubara ya share hawayen, sannan a cikin muryar kuka yace;

"Yanzu shikenan ashe ni ba  sona kike ba"

Izzatu ta b'ata fuska ganin, hawayen da yake k'ok'arin b'oye mata, a cikin sanyin murya tace;

"Yaya Garza na!, kaf duniya idan aka cire malam da mama, babu wani wanda nike so sama da kai, don bakasan yanda nike jin k'aunarka a zuciyata bane yayana, ko mama da tace dani, idan nayi sallah na dinga rok'ar Allah ya bani miji nagari, to aduk na tashi rok'on da siffarka nike rok'o,  akan Allah ya bani miji na gari irinka, fuskarka, tsawonka, hasken ka,  yanda kake d'an gayen nan, to ka gani idan bana sonka taya zanyi wannan addu'ar"

Ba shiri wani farin ciki ya mamaye zuciyar Garzali, a cikin zumud'i ya ri'ko hannuwanta duka biyu ya saka a cikin nashi, wasu hawaye suka kwaranyo akan fuskarshi, bakin shi yana rawa yace da ita;

"Ina son kiyi man wani alk'awali k'anwata"

Izzatu Ma ganin hawaye a fuskar shi,  hawayen takeyi, a cikin k'arfin hali tace;

"Nayi maka alk'awali matuk'ar ba sab'awa mahaliccinmu bane, to zan amince da duk abunda

kazo dashi yayana"

Garzali zai bud'a baki yayi magana, iya kulu ta d'aga labulen d'akin, ganin Garzali rik'e da hannun izzatu ne yasa  ta rafka salati, ba shiri suka saki hannun juna, iya kulu ta d'aga hannu ta kwad'awa izzatu wani bahagon mari, tana kururuwar azo agani izzatu zata yiwa Garzali fyad'e.

Aiko duk mutanen dake gidan, masu zuwa ganin jikin mama hassatu sukayo d'akin Garzalin, duk wanda ya lek'a yaga izzatu zaunenta har da hijabinta sanye, Garzali ma haka suturar shi, sai ayi turus, saboda kowa ya kasa ganin illar abunda,  iya kulu take so ta sanarwa mutane.

A hankali,  mama hassatu ta tako, ta shigo d'akin tareda yimasu kallon tsaf, jiki ba k'arfi ta rik'o hannun izzatu tace;

"Tashi muje d'aki, kai kuma ka shirya ka koma makaranta yanzu, ka gani naji sauk'i ko?,  to aje aci gaba da karatu, Allah ubangiji yayi taimako"

Mama hassatu ta fito d'akin hannunta rik'e da izzatu, bayan ta d'auko ledodin suka fito, kai tsaye suka shige d'akinsu, iya kulu ko tana nan a tsaye k'ofar d'akin Garzali cike da mamakin ganin yana had'a shirginshi yana lodawa a jaka, yana k'are had'a komi nasa ya fito, iya kulu mamaki bai daina kama ta ba, har saida taga Garzali yana rufe d'akinshi da makulli, baki a sake tace;

"Au waton dai ashe da gaske ba donni kazo gidan ba, ii lalle abu ya girmama, an shanye uba an shanye d'a"

Garzali bai kulata ba, fuskar shi a had'e yace da ita ;

"Ni na wuce sai Allah yayi dawowata"

Yana k'are maganar ya nufi d'akin mama yayi mata sallama a tsatstsaye, yaja jikar shi ya fice gidan, izzatu ta fito d'akinsu da gudu ta nufi, bayan d'akunan su Garzalin, ta duk'a ta tone wani abu a leda ta fita a guje, har yayi nisa ta k'walla masa kira, ba shiri ya waigo, ta isa tana haki ta mik'a masa ledar, a cikin mamaki yace da ita;

"Miye a ciki ne?"

Ba tareda tayi magana ba, ta kwance ledar, saiga kud'i dami guda, ta ciro  su ta mik'a masa, yasaka hannu ya karb'a mamaki a fuskarshi ya lissafa kud'in,sannan yace da ita;

"Naga kud'i na minene?"

Izzatu ta b'ata fuska, sannan tace;

"Malam ne yace a baka, shine mama tace inkawo maka"

A nan take wani murmushi ya maye gurbin, b'acin ran dake kwance a fuskarshi, fuska a washe yace;

"Malam ko ya manta ya bani kud'i kafin ya tafi?"

Izzatu tayi saurin fad'in ;

"Eh yana sane ai, yace ne ka k'ara, koda  za'a buk'aci wani abu acen makarantar"

Garzali yayi murmushi yace;

"To kice dashi nagode sosai"

Shima ya ciro dubu d'aya a cikin kud'in ya mik'a mata yace;

"Kema gashi kije ki k'ara a kud'in break"

Izzatu tayi murmushi tace;

"Nagode yayana kaje kawai Allah ya kiyaye"

Da sauri ta fara tafiya da baya baya, tana yimasa bye bye, jikinshi a mace ya gyara goyon jakar da yayi, sannan ya hasketa da wani shaharren murmushi yace;

"Sai na dawo ki kula da kanki"

Wasu hawaye suka zubo mata, da sauri ta juya ta fara tafiya har ta kusa k'ule wata kwana, sannan ta waigo yana nan inda ta barshi, ba shiri wata kunya ta ziyarceta, da sauri ta rufe fuskarta da tafukan hannyenta, ta sha kwanar ta lab'e.

Garzali ya girgiza kai yana dariya, ya juya ya fara tafiya, izzatu ta lek'o kanta, akayi dace shima ya waigo, ba shiri dukansu, suka k'yalk'yale da dariya.

Soyayya ruwan zuma in kasha kaba masoyi💃💃💃💃😹

Akafta 🤺

D/Auta ce😜
[8/23, 1:54 PM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*KUCI GABA DA RUWAN COMMENT'S NI KUMA INCI GABA DA SUBURBUDO MAKU TYPING 🥰*

*MUJE ZUWA⛹️‍♀️ MUTANE NA INA YINKU SOSAI💋*

*PAGE THIRTY FOUR*

**********************

Bayan fitar izzatu,  iya kulu tabita da kallo baki a sake, sannan ta fara bambamin fad'an anshanye mata miji,don bala'i d'an da ta haifa ma da cikinta  anshanye shi, ta fara kuka tana sambatun ina zata saka kanta taji sanyi?.

Ba wanda yace da ita k'anzil, da taga bata samu yanda takeso ba ne, ta fara cewa;

"Tsakanina dake hassatu, sai tsinuwa kwando kwando, itace kawai zata rabani dake, daga ke har malam wallahi kun cuceni kunci amanar marainiyar Allah, itako wannan munafuka da takeson ta lalace man yaro, wallahi sai nayi shari'a dake muddin kika yarda kika yimasa lalata, bak'ar jarababbiya, ai baki yar a k'as ba don anyi gadon halin tsiya a wurin tsofaffin 'yan bariki".

Akayi dace tana cikin banbamin fad'an ne malam ya shigo, tana ganin shi tayi tsit, jiki yana rawa taja buta ta shige bayi, malam ya girgiza kanshi ya shige d'akinshi, don yaji duk abunda take fad'a, amman ganin mutane a gidan sai bai kulata ba, har sai da dare yayi kowa yayi bacci,

sannan yaje ya isketa tana ta sharar bacci, ya saka hannu ya watsa mata wani gawurtaccen mari, a zabure ta falka tareda kurma ihu,  tana sambatun kiran ;

"Ku ke ganinmu, ba mu ke ganinku ba,  innahu min sulaimanu"

Malam ya d'auko ruwan da yagani ajiye a gefen gadonta a kofi, ya d'auko su ya watsa mata a fuska, da sauri ta sauke ajiyar zuciya, tareda shafe fuskarta, ganin malam a tsaye gabanta fuska a had'e, nan take idonta suka rena fata, ta fara bashi hak'uri, baice da ita k'anzil ba ya mik'a mata wata farar takarda yace;

"Karbi ki tashi kibar man gidana sawunki a likkafa, kisan inda dare yayi maki"

Iya kulu ta fara muzurai tareda k'ara ja da baya, tana bashi hak'uri, idonta akan takardar tana girgiza kai jikinta sai rawa yakeyi, malam yana ganin ta tsorata da gaske yace;

"Karb'i nace"

Iya kulu bakinta yana rawa tace;

"Ka tuno da wasiyyar Dada, kar ka mance lokacin da tace ka rik'eni amana,idan ka mance to yanzu na tuna maka, don haka kayi hak'uri kawai,  banison ka sab'a Allah yayi fushi dakai, uwa fa ai ta wuce wasa malam"

Malam ya suk'e dariyarshi, a cikin zaro ido yace;

"Muddin kika koma fad'ar abunda zaisa izzatu ta gano matsayin ta a gunmu to tabbas ki sani sai kinbar gidannan, don haka yanzu ruwanki ne,  ki zauna da hassatu lafiya ko akasin haka, don ni yanzu ba wani jira da zanyi zan tsige aurenki in yada k'wallon mangwaro in huta da k'uda"

Malam yana k'are maganar ya futa fuuu, iya kulu tana zarar ido tareda maida numfashi a wahalce tace;

"Haka kawai zan karb'i tikitin wahalata, ai wallahi ba mai sani komawa wancen k'addararren gidan, su kaini lahira ban shirya ba, zama daram nida ku wallahi"

***

Ta cinna kan motar ta a saman titi, sannan ta waigo ta kalli yaron da akace ya yanke mai suna Ammar, ta kalli yanda yaketa b'ata fuska, sai kallon hannun yakeyi yanason yayi kuka, a cikin kulawa tace dashi;

"Kada ka kuskura inga hawaye akan fuskar ka, don ba wani yace ka bud'a ledar ba, bale har ka d'auko clipper ta yanke ka ba, ai kaga sakamakon rashin ji, gobe sai ka k'ara"

Fahat ya kallesa yayi masa gwalo, da sauri Ammar ya kai masa duka, aiko sai gashi ya fama ciyon, ba shiri ya k'wallah k'ara tareda rik'e hannun.

Ammi ta saka hannu ta make kan fahat tace;

"Kai kuma sai na dena fita da kai, tunda baka jin magana"

Daga nan taci gaba da yimasu fad'a, har suka isa katafaren gidannan, dandazon masu hidimtawa gidan sai gaisuwa suke kaiwa, tana  d'aga masu hannu a cikin sakin fuska, sai da taje har rumfar ajiye motoci, sannan tayi parking, kafin ta fito har yaran sun rigata futowa, aguje suka fara rige rigen shiga cikin gidan, suna kiran sunan AMMAH.

Ita ko sai da ta daidaita sannan ta fito, tareda saka makulli  ta rufe motar, ta d'auko ledodin da tayo siyayya, ta fara tafiya sai ga wata 'yar aiki ta fito, daga cikin gidan da saurinta ta karb'i kayan, tana yi mata sannu da zuwa, a cikin fara'ar dake k'ara k'awata kyakkyawar fuskarta tace;

"Yawwa sannu da gida ladidi"

Tana gaba ladidi na biye da ita a baya har suka shige gidan, tana shiga kai tsaye wajen hajiya fatima ta nufa, inda su Ammar suketa kokowa tana rabon fad'an.

Ta sami kujera ta fad'a tace;

"Wash wallahi na gaji da yawa"

Zamanta keda wuya sai ga Alhajin gidan ya sauko da matattakalar gidan sama, fuskarshi d'auke da murmushi ya sami d'aya daga cikin saitin kujerun da suke kai ya zauna, ya kalli hajiya fatima dake ta sabgar su fahat, yayi murmushi yace;

"Yaran Ammah yau ma fad'an ne, ku bakwa gajiya?"

Hajiya fatima, tana dariya tace;

"A barni da yarana, ba ruwan kowa da sabgarsu, a daina sa masu ido,  bance kowa ya raba ba"

Ya dawo da kallonshi akan Ammi, ya jefeta da wani shu'umin murmushi, Ammi ta k'ara narkewa a jikin kujera, don batason hajiya fatima taji ba dad'i, shiyasa tayi kamar bata ganshi ba, da taga zai takurata ma, tayi tsam ta tashi takalli hajiya fatima tace da ita;

"Na gaji da yawa Ammah ni zan je in kwanta"

Hajiya fatima ta mayar mata da murmushinta tace;

"To afito lafiya, tunda yau bazaki tsaya ayi firar dake ba"

Ammin tana murmushi tace;

"Yaranki bazasu bari ba ai, don haka nikam bazasu sakani ciyon kai ba, kunga inda nayi"

Ta nufi part d'inta, ta haye sama tana yimasu dariya, Alhajin ya bita da kallo har ta k'ule, sannan ya kai dubanshi akan hajiya fatima, caraf suka had'a idanuwa, ba shiri ya diririce ya fara sosa k'eya, hajiya fatima tayi murmushin k'arfin hali tace;

"Kunya ta miye Abbah?, kawai ka tashi kabi matarka in don tani, kada kaji komi, yanzu zan shige da yarana mu kira SUDEIS da SADIS musha firar mu"

Aiko tana k'are maganar, taja hannun su Ammar suka haye abunsu, suka barshi anan zaune yana tunanin, karamci irin na bintu, shiyasa a koda yaushe yake jin nauyin, nuna zalamarshi akan Hadizatou, saboda baya son ya maimaita kuskuren da yayi mata abaya.

Jiki ba kuzari yaja k'afafunshi ya haye part d'in hadizatou, wadda a koda yaushe k'aunarta, linkuwa takeyi a cikin zuciyar shi.

Ammi tana shiga katafaren falonta, ta fad'a a kan wata luntsumemiyar kujera ta kwanta, aiko sai tunanin yarinyar da sukayi karo da ita, a shopping complex yaa fad'o mata a zuciya.

Ba shiri ta tashi zaune tareda dafe k'irjinta, dake ta yimata dakan lugude, tsam ta mik'e ta fara zarya a tsakiyar falon, tana so ta tuno fuskar yarinyar amma ta kasa, saboda ba wani kallon fuskarta tayi sosai ba, hankalinta baya kanta kwata kwata, sabod tunanin su Ammar da ta baro a mota, kuma tasan kafin ta shiga ta fito sunyi kokawa tafi kala biyar, shiyasa da ta fito idonta akansu, tana ta sauri taje ta samesu, domin taga wace wainar ce suke toyawa.

Aiko sai gashi d'an tsaikon da tayi fahat ya kirata yana cewa da ita, tazo Ammar ya yanke hannunsa da sabuwar clipper'r da ta siyo musu, Ammar yana ganinta a leda ya saka hannu zai d'auka, fahat ya buge hannunsa ya karb'e, to shine shi Ammar wajen k'ok'arin ya fisga da k'arfi ne, a hannun fahat clipper'r ta yanke sa a hannu, shine dalilin kiran.

Ita Ammin hankalinta kacokam yana kansu,shiyasa bata sami damar yiwa izzatu kallo kona secon biyu ba, amma fa kamar taso taga fuskar, musamman kamar da sukeyi da yarinyar, sai dai tana kwakwanton ko hasashen da takeyi ne, a kullum yake yimata gizo.

Ba shiri ta fad'a a kan kujera dab'as! ta zauna, tareda k'ara tariyo abunda ya faru a lokacin, shigowar Abbah ne yasakata katse wannan tunanin nata, amma fa zuciyarta tana ta so ta gasgata mata cewa lalle tabbas taga fuskar yarinyar.

**

Izzatu ta koma makaranta taci gaba da karatunta, yayinda a kullum baba kallah ne yake kaita ya dawo da ita, izuwa wannan lokaci, ta saki jikinta dashi sosai sun saba wanda idan ba wanda yasanta ba zaice babanta ne, saboda d'awainiyar da yakeyi da ita, yakaita ya dawo da ita, sannan ga abincin mai rai da motsi da yake ta bata,  a kullum safiya da kalar da ake sauya mata, kud'in da ake bata a gida ma, na transport da break tariyar su takeyi, a duk lokacin da yayanta yaje makaranta ganinta, ta bashi tace inji malam ko mama hassatu.

Aiko yau da gobe bata bar komi ba, ance rana dubu ta b'arawo rana d'aya tak! ta mai kaya, sai gashi labari ya fara bazuwa a k'auyen, izzatu biyar Alhazan birni takeyi suna sharholiyarsu, saboda a kullum sai an ganta wani Alhaji ya d'auketa a bakin titi, kuma idan lokacin dawowar makaranta yayi,  sai ya dawo da ita ya ajiye, tana lab'awa da makaranta tana yawon barikinta.

Injisu fa🙀 ba injini ba🤭

Akafta 🏃‍♀️

D/Auta ce😹

[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*ROKON ALLAH NIKEYI HADANI DA MASU SO NA💃💃💃💃💃💃BAKANDAMIYA NIKE YI ALLAH BANI BANI BANI MASU SONA KO GIDA KO DAWA 💃💃💃💃*

*DARE DA YAWA RANA DA YAWA  ZASUYO GUSHEWA GA RUWAN SAMA YAYYAFI

LOKACI NA DAMANA ZAIYO WUCEWA💃💃💃*

*AYYE TAMBARI SAI SARKI SAI SARAUNIYA TAMBARI NA DOKA DAKU NAKE YAKU JARUMAI NA GAGARAGASA💃💃💃*

*PAGE THIRTY FIVE*

*********************

Labari har gidan mai unguwa, malam ma aka tareshi ana yimasa shagub'en,  abunda ake zargin izzatu tana aikatawa,duk da malam yaji zafin abun, amman zuciyarshi ta kasa amince masa izzatu zata yi hakan, shiyasa da yaje gida baija abun da tsauri ba, ya dai kira mama hassatu ya sanar da ita, mama hassatu ranta ya b'ace sosai akan wannan k'azafi da aka yiwa izzatu, amman tace da malam,  su jira izzatun ta dawo sai suji ta bakinta.

Aiko baba kalla yana kawowa a dai dai inda yake ajiyeta ya Parker, izzatu zata bud'e k'ofar ta fito, sai ga fadawan da mai unguwa yasa su lab'e, akan su sakashi a gaba har sai sun kaishi fada, aiko suna zuwa ba b'ata lokaci d'aya ya shiga gaban motar ya zauna, yayinda d'aya ya bud'e baya inda izzatu take a zaune ya zauna.

Baba kallah da izzatu sai rabon ido sukeyi a cikin fargaba, suna mamakin abunda yake shirin faruwa dasu, kafin baba kallah ya samu abin cewa, fuska a had'e sarkin fada yace dashi;

"muje k'ofar gidan mai unguwa, yana son magana dakai"

Izzatu tana jin haka, tayi saurin bud'a k'ofa zata fita, jikinta yana ta rawa, sarkin fada ya daka mata wata arniyar tsawa yace;

"Gidan ubanwa zakije ne?"

Bakinta yana rawa tace;

"Gidanmu zanje"

Don tsawar da sarkin fada yayi mata, ta firgita ta, har  fitsarin da take ta matsewa ya fito sha!, yana biyar k'afafunta, ba shiri ta koma ta zauna, sai had'iyar yawun wahala takeyi.

Baba kallah baice dasu k'anzil ba, har sukaje k'ofar gidan mai unguwa, wanda izuwa lokacin labari ya bazu a garin, akan cewa ankama izzatu da Alhajin da ke d'aukarta a mota, kafin kace me k'ofar gidan ta cika mak'il kowa da abunda yake fad'a, wasu su kare izzatu, yayinda wasu suke ta aibantata, tareda tofin alatsine akan asalinta.

Jiki a sanyaye Baba kallah ya fito motar, saboda ganin cincirindon mutane, 'yan ganin k'wak'waf da suka baza ido suga me za'ayi, domin kada suyi mantuwa idan sunje bada labari, amma ganin yanayin baba kallah da kwarjinin da ke fuskarshi, yasa mutane da dama suka sha jininsu, musamman yanda sukaga izzatu ta fito tana ta wani marayan kuka, saboda ita ba komi yake sakata kuka ba, sai tuno abin kunyar da ta jawa su malam a k'auyen.

Baba kallah da mai unguwa, tareda sauran masu fad'a aji a k'auyen, suka saka izzatu a tsakiya suna tambayarta miye had'inta da baba kallah, izzatu tana kuka tayi bayanin tun farkon had'uwarsu ranar da ya taimaketa a hannun 'yan iskan da sukaso suyi mata fyad'e, har izuwa ranar, amman ta b'oye abincin da yake bata, don ta rage girman tuhumar da ake yimasu, baba kalla ma yayi masu guntun bayanin taimakon da yake yiwa izzatu, sannan ya k'ara da cewa;

"Izzatu tamkar 'yata na d'auketa, bazan tab'a bari a cutar da ita ba ma, balle har ni in aikata da kaina, ni katanga ne a wurinta,raina fansa ne a wajen kare lafiyar izzatu, saboda ni kaina idan wani abu ya sameta, kwatankwacin wanda kuke zargi a yanzu, to wallahi tabbas bazan tab'a yafewa kaina ba, wanda nasan Allah ma bazai yafe man ba, da kunsan kowanene ni a wurin izzatu nasan da baku zargeni ba, amman ba komi nayi maku uzuri, saboda rashin sani ne ya kawo hakan"

Yana k'are maganar wasu hawaye suka zubo masa, ya ciro kud'i a aljihunsa, dami guda ya ajiye a gaban mai unguwa yace;

"Ga kud'i nan a siye mashin d'in da zai dinga jigilar kaita makaranta na barku lafiya"

Ya tashi ya fita, ya fisgi motarshi da k'arfi, yabar k'auyen, tareda rakiyar 'yan iskan garin suna yimasa a ture.

Gaba d'aya wanda ke fadar jikinshi yayi sanyi, saboda dukansu sunsan matsayin izzatu ga su malam, shiyasa suka shiga tambayar junansu, kodai shine baban izzatun?,idan ma ba shi bane to akwai wani abu da yasani dangane da izzatun, shiyasa sukayi tsit kamar ruwa ya cisu, mai unguwa yayi gyaran murya yace;

"Sarkin fada aje a sanar da mai shela ya shiga lungu da sak'o na garinnan ya fad'awa mutane, Allah ya wanke izzatu daga zargin da ake yimata, wannan Alhajin da yake kaita makaranta d'an uwanta ne a birni"

Aiko kafin kace me gari ya rincab'e da guutsuri tsoma, wasu sun amince, wasu kuma sun d'auka kareta ne kawai akeyi, su malam Ma suna cikin gida sukaji wannan sanarwa, hankalinsu ya d'an kwanta, amman dai sunfison suji a bakin izzatun.

Har gida mai unguwa yasa aka rako izzatu, tareda yiwa su malam bayanin da mai shela yakeyi, sannan aka sanar da malam mai unguwa yana nemansa, iya kulu dai farinciki fal ranta, amman

bata ce uffan ba don tana jin tsoron abunda malam zai kad'ata gidansu, da ta kira k'addararren gida.

Amma tana ganin fitar shi, ta fara k'yalk'yala dariya tareda yin gud'a ta buga cinya tace;

"Yau dai kun fara girbar abunda kuke shuka,watak'ila ma watanni ne a tsakanin uwar da d'iyar, hassatu sai a fara murnar zuwan d'a da jika d'an boko ayyururui nanaye sama tayi ruwa k'asa ta shanye, yarinya gado sai d'an gado"

Mama hassatu da tirtsetsen cikinta ta tashi tsam, taja hannun izzatu suka shige d'aki, suna shiga ta jawo wuk'a tace da ita, ko tayi mata bayanin abunda ke tsakaninta da Alhajin ba, ko tayi mata gunduwa gunduwa.

Aiko izzatu jiki yana kyarma tayiwa mama bayanin komi tass, mama hassatu ta zaro ido awaje tace;

"Waton duk kashedin da nayi masa ashe baiji ba ko?, to wallahi idona idonshi, taimakon dole ne?"

Haka dai mama hassatu tayi ta yiwa izzatu fad'a kamar zata daketa, tace kuwa muddin ta sake kulashi, sai ta tsine mata tunda haka takeso, izzatu sai kuka takeyi tana bada hkr akan bazata sake ba,iya kulu har da saka tab'arya a turmi tana kid'a tana wak'ar, habaici kala kala.

malam ya dawo yana yiwa mama bayanin abunda mai unguwa ya sanar dashi akan baba kallah, wanda shi kanshi malam jikinshi yayi sanyi da yaji, don ya tabbatar kallah yasan wacece izzatu, tunda har ya bada kud'i asiye mashin a dinga kaita makaranta dashi, mama hassatu ma ta zargi lalle kallah, yanada masaniyar asalin izzatu, a nan take yiwa malam bayanin juyen da ya dinga yiwa izzatu, a lokacin da iya kulu take d'ora mata tallah, aiko dukansu suka aza alamar tambaya akan baba kallah, shin miye dangantakar sa da izzatunsu?.

Mai unguwa ya bada an siyo mashin d'in, sabo dal ya kira malam yace dashi idan akwai wanda zai dinga kaita makarantar, sai abashi, malam ya fad'awa mama hassatu, tace dashi a baiwa Abu ya dinga kaita, idan ya ajiyeta sai ya d'an zagaya yayi acab'arshi, har zuwa lokacin da ya daidaici an tashi, sai yaje ya d'aukota su dawo gida, iya kulu tayi tsalle ta dire akan Abu bazai koma baya ba, ya rasa aikin da zaiyi sai jigilar kai izzatu yawon gantali.

Abu ma da yazo akayi masa bayani, saida ya zunduma uwar asharr sannan yace ;

"Wallahi ko na rasa aikinyi, bazan tab'a d'aukar wannan munafuka inkaita yawon ta zubar ba, sai dai tsiya takasheni da in zama bawanki, shegiya wallahi muddin kika yarda na d'auke ki, sai dai adawo da k'asusuwanki, na kakkarya ki acen"

Mama hasatu tace tunda abu yak'i abaiwa, ummaru yaron hure na biyu, aiko inna hure ta dinga godiya, ummaru akwai zafin nema, gashi yasan ciyon kansa, don ko anan k'auyen baya rena sana'a, aiko a kullum yazo har gida ya d'auketa, ya kaita makarantar, idan ya ajiyeta yaje sabgoginsa, a cikin sati d'aya ummaru ya fara gano, ba k'aramar bajinta akayi masa ba, yaji dad'in wannan abun alkhairin da Mama hassatu tayi masa silar samu.

**

Cikin mama hassatu ya shiga watan haihuwa, tana fara jin nak'uda tace da malam akaita asibiti, kamar wasa suna zuwa akace haihuwa ce, cikin ikon Allah mama hassatu ta haifo 'yarta santaleliya, murna a wajen malam da danginta ba kama hannun yaro, bayan angama bincikar lafiyarta da 'yar jaririyar, aka tabbatar ba wata matsala suka garzayo gida, cike da farincikin wannan k'aruwa da ubangiji ya basu.

Izzatu tana dawowa gida, tayi arba da 'yar jaririya, ta fara murna, a kullum tana nanuke da jaririya, mutane sai zaryar zuwa ganin jaririya akeyi, ana taya mama murnar ganin 'yarta a duniya itama kamar kowa.

Iya kulu kam, bak'in cikin kamar ya kasheta, amman duk da haka tayi sha'awar ace itace ta haifi 'yar, sabida yanda take kwad'ayin haifuwar macen Allah bai kawo mata ba, har kuka ta shige d'aki tayi tana rok'on Allah akan ya bud'e mata mahaifa hakanan itama ta haifo macen taji me ake ji, a huta da yimata rawar kai.

Ranar suna yarinya taci sunan Dada, wato MARYAM, izzatu da mama da malam a tsakaninsu sai ka rasa banbance wa yafi son maryam, saboda kulawar da suke bata, tarairayarta sukeyi tamkar k'wai, wanda hakan shi ke b'atawa iya kulu rai, tayita maka masu harara, tana mere.

Garzali yazo yaga maryam kwana d'aya ya koma, saboda suna cikin jarabawar shekara ta biyu a jami'a.
Dr ma yana zuwa jefi jefi, yana kawowa su mama gaisuwa, tareda alkhairin shi ga maryam ko izzatun, har saida malam ya zaunar dashi, yayi masa godiya, sanan ya dakatar dashi da wannan d'awainiya da yakeyi, a cikin dubara ya fayyacewa malam gaskiyar abunda ke kawo shi, malam yayi jim, sannan ya d'ago fuska a cikin damuwa yace dashi;

"Naji dad'in yanda ka nuna k'aunarka ga izzatu, amman wani hanzari ba gudu ba, izzatu ba mu muka haifetab, tsintar ta mukayi, shin kaji ka gani zaka aureta da zuciya d'aya?"

Dr yayi shiru na d'an lokaci sannan yace;

"Tsakani da Allah nike son izzatu, ko ta wace hanya aka sameta, naji na gani zan iya aurenta"

Malam yace;

" Alhmdllh, to kaje kayi shawara da iyayenka, idan sun amince kazo zamuyi mgn dakai"

Tofa malam ko ka mance da Garzi😒

Akafta😅

D/Auta ce🥰
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*MEERAHGEE,  DA K'AWATA BILKISU,  WANNAN PAGE NAKU NE SUKUTUM KUYI YANDA KUKE SO DASHI NAGODE DA KARAMCIN KU A GARENI🤝🏻*

*Ina alfakhari daku mutane na inayin ku over wallahi💃💃💃💃💃💃💃💃💃💃💃💃💃*

*Ruwa da kankara fan's ga jinjinar ban girma, saboda kaunar da nike maku zan iya shanye gorar sob'o🤪*

*PAGE THIRTY SIX*

*********************

Bayan kwana biyu Dr ya dawo, ya sanarwa da malam cewa, iyayenshi sun amince, malam yaji dad'in abun sosai, yace da Dr yaci gaba da nema idan Allah yayi matar shi ce shikenan, zasu taya shi murna.

Farin ciki  ya mamaye zuciyar Dr, saboda jinsa yakeyi tamkar Ma har an bashi  auren izzatun, don yasa a ranshi ruwa da iska bazasu hanashi auren sahibal-k'albinsa gimbiya izzatu ba,amma duk zuwan da yakeyi ya kasa fitowa k'arara ya sanar da izzatu sonta yakeyi, sai dai a duba d'aya idan kayi masa, zaka gano tsantsar k'aunar da yake yimata.

Malam ma bai sanar da kowa wannan magana ba, ko mama hassatu batasan abinda ke faruwa ba, amman dai itama jikinta ya bata Dr son izzatu yakeyi, tun asibiti, sai gashi kuma uwar siyayyar da yayi mata, a ranar da aka sallamota daga asibitin, ya nuna tabbas da zafinsa ya fito nema, amma a yanayin izzatu da ta gani har yanzu bata gano Dr sonta yakeyi ba, ita iya saninta da k'urciyarta, mutunci da ke tsakaninsu ne yake kawo shi gidansu.

Garzali bai cika dawowa k'auyen ba, saboda ya tsani halayen iya kulu da take yi a gidan, idan ma yazo da b'acin rai suke rabuwa, shiyasa yafi gane ma yayi zamanshi a cen, yayi ta buga bugarshi yana samun, abunda zai rik'e kanshi dashi,idan yaso ganin izzatu sai yaje makarantar ya dubota.

Yaji dad'i da yaji ummaru yana kai izzatu makaranta, izzatu tayi masa bayanin mai unguwa ne ya bada mashin a dinga kawota, yayi ta yiwa mai unguwa addu'ar gamawa lafiya.

**

Wasa wasa soyayyar Dr, ta fara shiga zuciyar izzatu, saboda a sannu sannu yake ta koya mata yanda zata soshi, sai gashi akayi dacen hankali ya k'ara shigarta, ita da kanta ta gano, ashe da gaskiyar yayanta Garza da yace Dr sonta yakeyi.

Soyayya mai k'arfi ta k'ullu a tsakanin Dr da izzatu, duk da a gefen zuciyarta a kullum tafi girmama son Garzali akan Dr, ta dai jingina abun ne da cewa soyayya ce irinta 'yan uwan juna.

Mama hassatu har ga Allah ba dr taso ace izzatu ta aura ba, amman dai tabar maganar ne, don ganin malam bayason maganar, shiyasa baiyi shawara da kowa ba ya amince wa Dr, a kan ya kafa soyayyarshi a wurin izzatu, don a k'ara tabbatar mata da cewa sune suka haifeta, mama hassatu tayi ta nunawa malam, Garzali ne ya dace ace ya auri izzatu ba Dr ba, malam yayi tsayinshi akan idan dai ba iyayen izzatun ne suka bayyana ba, to tabbas  ba wanda zai auri izzatu sai Dr, don ya yaba da mutuncinshi, kuma yana da tabbacin izzatu zatayi rayuwar farin ciki a gidan shi.

Duk zuwan da Dr yakeyi, bai amince yazo da kowa a wurin izzatu ba, saboda yana jin tsoron a ganar masa ita, haka  kawai yakejin tsoron bayyanata a wurin abokanshi, don gudun yana jin tsoron wani yayi masa shigar sauri,  amman yakai labarinta gidansu, sai dai ya b'oyewa

iyayenshi wacece izzatu.

Sunyi mamaki da sukaji, a k'auye yake neman aure, duk  matan dake birni ba wadda tayi masa sai 'yar k'auye, yayi ta  kwatanta masu irin had'uwar da izzatu tayi, amman dai su har lokacin, zuciyoyinsu basu natsu da auren 'yar k'auyen da yake so ya yi ba.

Shiyasa ya yanke shawarar, kawai ya kawo masu izzatun su ganta da idanunsu,koda zasu gasgata cewa ita daban take da 'yar k'auyen da suke fad'a.

 Aiko watarana da yaje fira yayi mata zancen zuwa gidansu, ta nuna masa sai abunda malam yace, aiko baki a sake ya rok'i malam alfarmar, a bar izzatu taje ta gaida iyayenshi,.

Mama hassatu bataso izzatu taje ba, don ita duk da mutuncin da Dr yake dashi, tafi sowa Garzali ita da shi.

Amman malam  saboda jin nauyin Dr da yake yi, yasa ya amince da zuwanta, amma da sharad'in bazata je ita kad'ai ba, sai dai suje ita da d'iyar mama hure Amina, Dr yaji dad'in wannan karamci da malam yayi masa, yace gobe zaizo ya tafi yana murna akan gobe zai zo su tafi.

Koda safiya ta waye da shirin zuwa gidansu Dr izzatu ta tashi, tana zaune mama tana shace mata tsibin gashinta da baya kitsuwa, a kullum sai dai mama tayi mata kitso k'wara  biyu ko uku da gashin, amma baya kwana uku yake kwancewa,  saboda sulb'in gashin.

Mama da izzatu  sai firar su sukeyi a tsakaninsu, maryam 'yar shekara biyu tana kukan ala dole sai an bata abun shartar kan  itama ta shatawa izzatu, mama ta hana saboda bata son Dr yazo yayita jira.

Izzatu ta janyo ta, ta d'ora ta akan cinyarta, tace;

 "Zo nan ki zauna my ilham, k'yale mama kina zuwa muje dake ko?"

Ilham ta d'aga kai, izzatu ta lakuce mata kumatu tace ;

"Zaki shiga mota ko?"

Aiko carab sai a kunnen iya kulu, aiko ta k'yalk'yale da dariya ta fara banbamin ta da ta saba, mai had'e da habaici tana cewa;

"A hayye su mota manya, inda ba'asan asalin kaza ba, da tace daga makkah ta fito, oni 'yar kuluwa  kwad'ayi dai mabud'in wahala ne, anga mai kud'i an lik'e, to adaiyi a hankali, don idan ba'a iya kama b'arawo ba, sai shi b'arawon ya kama mutum, sai amfani akeyi da farin komo ana tatse bawan Allah, wannan yaro yana bani tausayi a gidan duniya, an yi masa rufa rufa za'a lik'a

masa kaska rab'i kisha jini, Allah dai ya ceci wannan yaro shikam don an riga anyi masa kamun fatsa"

Mama hassatu jin iya kulu tana k'ok'arin b'aro zance, tace da izzatu ta tashi taje ta shirya, ranta a dagule ta kalli mama tace;

"Wai mama ni me nayiwa iya ne da bata sona ne?, sai inji tana ta wasu maganganu da ni nike rasa gano abunda takeso ta sanar dani"

Mama ta had'e fuska sosai tace da ita;

"Kul! Kada na sake jin kin k'ara magana irin wannan , yau kika fara sanin halinta ne?, da zaki damar da kanki akan zantukanta?".

Hawayen  da suka cika idanunta, suka gangaro a kan fuskarta, tasa hannu ta share sannan ta d'auki ilham,  suka shige k'uryar d'aki domin ta shirya.

Mama hassatu ta bita da kallon tausayi, a zuciyarta tace;

"Allah ya bayyana maki iyayenki, kodon mu fita a cikin wannan fargaba da muke ciki  kullum"

Amina ta shigo da shirinta, tayi kyau gwanin sha'awa, ta gaida iya kulu, tayi mata wani kallon banza tace;

"Gayyar sod'i an zo?, to adai bi a hankali kar ayi k'auyanci"

Amina tayi dariya tace;

"Ko zaki rakamu ne sai muje dake?"

Mama tayiwa Amina dak'uwa don tasan Aminar  kar,  bakin tsiwa ne da ita, bata shayin yiwa iya kulu bak'ar magana, Amina ta shige d'akin mamar tana dariya, aiko iya kulu inda take shiga ba anan take fita ba, har Dr yazo bata daina banbamin fad'an ba.

Izzatu ta fito a cikin shigar ta mai kamala,  wata doguwar rigar jallabiya ce bak'a da Dr ya siyo mata ta saka, sannan tayi Rolling d'in d'ankwalin rigar a kanta, farinta ya k'ara fitowa tamkar wata balarabiya a k'asar sudan, izzatu daman cen kwalliya ba damunta tayi ba, iyakacinta powder da lip a baki, ko jan baki bata cika shafawa ba, amma ranar ta d'an shafa kad'an, aiko dress d'in yayi mata kyau sosai matuk'a.

Saboda tunda mama tazo gidan, ta dinga koyar da ita komi irin na 'yan birni, bata barinta yin d'ige d'igen kwalliyar da 'yan garin sukeyi, shiyasa Amina itama ta dinga koyar kwalliyar izzatu, duk da ita ko a had'i batayi wayewar izzatu ba, don ko a makaranta primary kawai tayi, saboda

mijin mama hure babban malamin zaure ne, bai yarda da yabar 'yarshi karatun gaba da primary ba, yafiso yayi mata aure idan ta sami mijin da ya kwanta mata suka daidaita, yanzu haka zaman jiran miji takeyi ayi mata aure.

Mama ta biyo su goye da ilham, da aka sakata baccin dole, don kawai kar tayi kuka idan su izzatu zasufita, don izzatun taso taje da ita mama ta hana.

Mama tayi masu addu'a tareda nanacin abunda ta tsara masu suyi, da wanda tace kar suyi idan sunje cen.

Dr idonshi a k'ofar gidan k'yam, yana son yayi tozali da gimbiyarshi, aiko suna fitowa da ka kallo ya bita har suka k'araso a jikin motar, da kanshi ya bud'e masu suka shiga.

Kande da yaranta 'yanmata da suka rasa mijin aure, sai turereniyar juna sukeyi, wajen kallon Dr da su izzatu, don tunda ya ajiye motar shi suke lab'e soron gidansu suna kallonshi, suna inama ace a cikinsu ne yakeso da sun cab'a.

A gaban idonsu Dr ya ja motar tareda bad'a masu k'ura suka bar k'auyen, suna tafe Dr yana jan izzatu da fira har suka kai gidan.

Gida ne madaidaici, shiba na manyan masu kud'i ba, shi ba na talakawa tilis ba, tsaka tsaki dai, ba laifi akwai rufin asiri sosai a gidan, anyi masu tarba ba yabo ba fallasa, don a yanda sukayi tsammanin ganin izzatun ba haka suka ganta ba, don dai ya fada masu a k'auyen da take, da sun k'aryata shi, tun k'arfe sha d'aya suke a gidan har k'arfe biyu, bayan sunyi sallah sukace wucewa zasuyi, mamar Dr tayi masu kyautar turare guda biyu, dr ya kwashe su sai wata plaza ta mallakin BADAWI FAMILY.

Izzatu duk da farincikin da ta tsinci kanta a ciki, na ganin sunan BADAWI tayi, bai hana ta tambayar Dr ba, akan lafiya ya kawo su wurin?.

Dr yayi murmushi yace ;

"Saida ku nazo inyi"

Amina tayi caraf da maganar tace;

"Aiko da ka baiwa mai sayenmu aiki babba, don ni kaina wuk'a bata iya yanka shi, sai dai in izzatu"

Gaba d'ayansu suka YI dariya, sannan yayi parkin yace dasu su fito suje, a hankali suke takunsu kamar wasu wayayyu, har suka he wurin wasu kujeru da Dr ya nuna masu suka zauna, yasa akayi masu odar abinci da abin mak'ulashe har saida aka cika table d'in dake tsakiyarsu,

ya kalli izzatu da wani duba mai k'unshe da sak'onni da yawa, yace da ita;

"Bisimillah hajjaty"suka nuna masa sufa a k'oshe suke, anan take ya b'ata fuska yace;

"In cen gidanmu kunya ta hana kuci abincin, to a nan wa kuje jiwa kunya?, kuyi sauri kuci muje inkai ku gida, zanje ciki in ga manager,  kafin in dawo kun k'arasa"

Dr yana murmushi ya shige cikin wani office inda da alama cen ne na manager'n wurin, su izzatu suna ganin ya shige suka fara loda abunda duk sukeso, sunaci suna yanga kamar wasu wad'anda suka saba zuwa ire iren wad'annan wuraren.

Sunja lokaci suna kwasar gara kafin Dr ya fito hannun shi sark'e da na wani abokinsa, wanda da alama akwai sanayya sosai a tsakanin su, duba da yanda suketa cisgar dariya.

Su izzatu suna ganin sun nufo wurin suka shiga taitayinsu, abokin Dr yana k'arasowa wai sai naga ashe ma shu'aib ne, kan izzatu a duk'e dr yake yiwa shu'aib bayanin ta a matsayin wadda zai aura.

A cikin farin ciki shu'aib yace;

"Sannu Amaryar mu, ashe mun kusa zuwa ashafa fatiha da...... "

Izzatu a cikin jin kunyar maganarshi ta d'ago fuskarta da nufin ta jawo gefen d'an kwalin ta rufe fuskarta, karaf shu'aib ya hango fuskarta, da sauri ya matso yana tabbatar da itace, ya fara salati, a cikin wani fushi da ya ziyarceshi ba shiri, yace;

"Kanbala'i Dr wa nike gani kamar wata shegiyar yarinyar dana tsana a wani k'auye da muka je campaign, cab ke ubanwa ya kawoki a garinnan?, yanzu kai don shafewar basira me zaka yi da wannan abar, wannan matsiyaciya ni wallahi ko a k'afa a d'aura man ita sai na since, cab amma wallahi Allah ya isarwa maza sabida ka gama cutar su iya cuta"

Daga izzatu har shi Dr d'in kallon shu'aib sukeyi cike da mamakin shi, ba shiri izzatu ta fashe da kuka ta tashi ta fice wajen ta nufi bakin titi tana kuka, sai ga AMMI ta doso motar ta acikin plazar, Fahat da ammar suna bayan motar da ladidi.

Caraf idanunta suka sauka akan izzatu dake bakin titi ta madubin motar ta, sai sharar hawaye takeyi.

Rigiji gabji🙀

D/Auta ce⛹️‍♀️

 yanzu dai baa
[8/23, 1:54 PM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*PAGE THIRTY SEVEN*

**********************

Ba shiri gaban Ammi ya k'ire ya fad'i da sauri ta tsayar da motar, jikinta yana rawa ta b'alle murfin motar tafito kafin taje inda izzatun take a tsaye,  har ta tari d'an acab'a ta haye sun lula titi sai balbala gudu yakeyi, a cikin tashin hankali Ammi ta koma motar ta fisgeta da karfi tabi bayansu, d'an acab'a sai zuba gudunshi yakeyi a sanadiyyar umurnin da  izzatu ta bashi, don bata son ace Dr ya cimma su tafi son sai dai ya sameta a gidansu, don miyagun lafuzzan shu'aib sun cusa mata k'iyayyar Dr,  a cikin lokaci k'ank'ani taji auren Dr ya fice mata akai gara ta tsaya a k'auyensu tayi aurenta ba wanda zai mata gori.

Ammi dake biye dasu bata hange komi sai d'an acab'ar da take kallo, sai over taking take yiwa mutane duk don k'ok'arin ta samu ta cimmasu idanunta a rufe, saura k'iris ta sha gabansu sai kawai taji ta bugi wata mota dake a gabanta,  aiko mutane sai lalati sukeyi ba shiri hankalinta ya dawo a jikinta, da sauri ta samu ta saki titin tayi gefe tayi parking, yayin da mai motar da ta daka shima ya samu yaci birki da sauri, aiko gaba d'aya mutanen dake tafiya akan titin suka tsaida abubuwan hawansu,  suka yo kan mai motar da Ammi ta daka ana duba lafiyar shi.

Allah ya tsare baiji wani rauni sosai ba nan mutane suka yo kan Ammi da zagi, kowa da kalar

zagin da yake yimata duk da sun ganta  mace amma basu d'aga mata k'afa ba, Ammi da ladidi suka fito jikinsu yana rawa musamman Ammi,  saboda taji tsoro sosai shiyasa bakinta har rawa yakeyi wajen bada hak'uri,  har wajen mai motar sukaje suka bashi hak'uri yace ba komi su tafi kawai k'addara ce, sannan ta ja motar jikinta a mace suka koma gida ko plazar da tayi niyyar zuwa bata je ba.

Dr kuwa tun daga lokacin da yaji miyagun lafuzzan dake fita a bakin shu'aib, wani b'acin rai ya ziyarci zuciyarshi sai mamakin yakeyi mi Izzatu tayiwa shu'aib ne har yayi mata wannan mummunar tsana, wadda baya shayin tozarta ta a ko'ina kuma ko a gaban waye, kafin ya tantance abunyi sai ganin yayi izzatu takai titi ya so ya bita amma yafison sai yayi wa shu'aib wankin babban bargo don kada ya bar bak'in cikin da yake ji ya tafi a banza, aiko jikin shi har b'ari yakeyi wajen kaiwa shu'aib wani mummunan duka a baki, kafin kace me sai ga dambe ya kacame a tsakanin su, aiki hankalin mutane ya dawo a kansu kafin a raba shu'aib ya lallasu a hannun Dr, sabida k'arfi ba d'aya ba akwai banbanci a tsakanin mai cin tuwon dawa da mai cin na shinkafa, dak'yar a ka raba wannan kokuwa sai suka koma fad'a da baki, a cikin fushi Dr yace    "Kaci sa'a akwai mutane wallahi da sai na yimaka dukan kawo wuk'a a wurinnan,  gobe ko ba matata ba sai kayi shayin tozarta wata mace a gaba na, useless kawai, dabba mai k'wak'walwar kifi, ka rasa da wacce zaka tsaya kayi rigima sai mace macen ma k'aramar yarinya,  wallahi anji kunya girma yayi k'asa indai akan izzatu ne to nafison ni da kai daga yau komi ya k'are a tsakaninmu."

Yana k'are maganganun yace da Amina ta shiga mota suje, aiko shu'aib sai so yakeyi ya k'wace daga rik'on da aka yimasa yaje su ci gaba da caskaluwa, a zafafe ya d'aga murya yace       "Sai kasan ka cira dakeni wawan banza wai akan mace kake hauka."

Dr ya tada motar shi ya lek'o kanshi yace      "OK ina jiran duk wani tanadin ka"

Yana k'are maganar ya fusgi motar shi ya mik'a titi, koda yazo dai dai inda su Ammi suke yaga taro anata maganganu, amma bai bi kan ba'asin komi ba ya wuce sabida zuciyar shi a k'age take da ya cimma izzatu, don yasan izuwa lokacin ta kusa kaiwa a garinsu.

Aiko ya take motar sai wuta yake bata sai gasu ya tarar dasu a wurin wani mai fetur a kan hanya,  ana sakawa d'an acab'an man fetur a mashin d'inshi, da sauri yayi parking a dai dai gefen titin, izzatu tana ganinshi ta b'ata fuska sai kace ba izzatun shi ba, jikinshi a sanyaye ya fito yana bata hak'uri akan tazo suje ya kaisu gida, a cikin b'ata fuska alamar ba wasa tace dashi,

"Kaje kawai zan isko ku a gida."

Tana k'are maganar tazo zata haye mashin d'in, da sauri ya sallami d'an acab'an yace dashi ya tafi kawai, aiko yaja mashin d'inshi ya tafi yana murnar kud'in da Dr ya bashi linkin kud'in da sukayi jinga da ita.

Izzatu ta koma gefe tayi kicin kicin da fuska, Amina ta fito tana bata baki akan tazo su tafi, Dr ma ya marairece fuska a cikin damuwa kamar yayi kuka yace, "Haba my izzah!, kinsan fa ba laifina bane kiyi hak'uri kizo mu tafi, sai mu k'arasa maganar acen kinga a nan mutane sai kallonmu sukeyi"

Aiko ta waiga sai ko taga idanuwa da yawa akansu, dole ba don taso ba ta shiga motar suka tafi.

Sai da ya biya dasu BADAWI SHOPPING COMPLEX, yayi masu siyayya sannan suka kama hanyar zuwa k'auyensu izzatu, Amina sai hak'uri take bata tana ta bata labarin abunda akayi bayan tafowarta, jikin izzatu yayi sanyi k'alau saboda taji akanta Dr yayi fad'a da abokinshi, a nan take ta saki jikinta kamar ba'ayi komi ba suka ci gaba da firar su, amman fa taji haushin abunda shu'aib yake yayi mata, taci alwashin a karon su na uku ba zaiji dad'inta ba, don sai ta shayar dashi gubar mamaki, sai ta banbance masa a tsakanin 'yar k'auye da 'yar birni.

Koda suka je gida izzatu ba wani tsayawa tayi fira da Dr ba, ta dai yimasa sallama tareda godiya suka shige gida ita da Amina, wadda hannuwanta suke d'auke da ledodin siyayyar da Dr yayi masu.

Shigar su gidan keda wuya suka ci karo da iya kulu, aiko tana ganinsu da ledodi nik'i nik'i ta fara habaice habaice, dukansu ba wanda ya kulata suka je k'ofar mama inda take zaune akan tabarma tana baiwa ilham abinci suka zazzauna, mama ta kallesu fuskar ta a washe tana farin cikin ganin sun dawo lafiya, sai dai a kallo d'aya da tayiwa izzatu ta gano cewa lalle izzatun ta tayi kuka, a nan take taji ranta ya sosu ba shiri ta tashi tsam tace dasu su shigo daga ciki, suka kwashi ledodinsu suka shige d'aki, iya kulu tana ganin haka ranta ya b'aci don taso ace an bud'a ledodin taga abunda ke ciki, aiko ta fara bala'i tana cewa,

"Munafunci dodo ne wallahi maishi yake biya, ni za'a nunawa bak'in hali?, to ni banda rabo na a nesa yake ai da yanzu ina gidan wani hamshak'in attajiri a birni, wallahi da yarinya kallon tsiya ma bata isa inyi mata ba, ku huta da k'unbiya k'unbiya duk abunda kukaci na yaron nan wallahi Allah ya isa ce kuke ci, don nasan iyayenshi bazasu tab'a barinshi yayi wannan aure na yaudara ba, don ranar da duk asirin ku ya tonu to ina tabbatar maku a gidan yari zaku k'are rayuwar ku."

Tana k'are maganar ta juya aiko idonta sukayi karaf da malam, jikinta ya d'auki rawa ta dafe baki tace "Don Allah kayi hak'uri sub'utar baki ne."

Malam ya maka mata harara yace "Ko ki b'ace man da gani ko nima hannu na ya sub'uce inyi ta jibgar ki wallahi anan wurin."

Iya kulu jiki yana rawa ta fad'a d'aki tareda dafe k'irji tace,

"Oni 'yar kuluwa nikam da sa'a ta 'yar dubu ta haife ni."

Mama hassatu ko ta saka su izzatu a gaba da tambayoyi, har sai da taji komi sannan hankalinta ya kwanta, tayita baiwa izzatu hak'uri amma tace muddin ya koma tarar gabanta da cin zarafin, kar ta koma kuka tayi jarumta wajen nuna masa cewa ita fa daban ce,  a cikin duk wasu k'auyawan da ya tab'a gani a duniya.

Mama ta d'auki kayan da Dr ya siyo ta kaiwa malam, daga nan aka baiwa Amina nata kaso tayi gida, iya kulu ma anbata ta karb'e amma ko gidiya  babu bale sa albarka.

***

Shekaru sun mik'a abubuwa da dama sun faru, a ciki hadda cin zab'en da YAHAYA BADAWI yay na d'ale kujerar gwamna, mutane sai sanbarka sukeyi, yayin da d'aya b'angaren suke bak'in cikin rashin nasarar da sukayi.

Sannan Garzali ya k'are karatunshi har ya tafi service, wanda izuwa lokacin soyayyar izzatu tayi masa nauyin da ya kasa b'oyewa, a fakaice sai k'ara cusa mata soyayyarshi ta gaskiya yakeyi a zuciya, don ko lokacin da yaji labarin Dr ba k'aramin tashin hankali ya shiga ba, har sai da malam yayi masa katanga mai k'arfi a tsakaninshi da ita, sannan ya rage damuwar da ya sanyawa kanshi, don kafin ya bar garin k'aura yayi daga gidan ya koma a d'akunan su samarin d'iyan inna hure, don bayason malam yaga bai bi umurninsa ba, don muddin in yana ganin izzatu to bazai iya jure b'oyon soyayyar ta ba, aiko lokacin service d'inshi yana zuwa ya lula k'asar inyamurai yabar izzatu da kewar rashin shi, da d'inbin soyayyar shi da ta dank'are zuciyarta tana hak'uri ne kawai da Dr don taga yanda malam yakeso ta aure shi.

Malam yana ganin Garzali ya tafi yace da Dr ya turo iyayen shi ayi maganar auren izzatu, don a nufin shi ayi komi a gaggauce tun kafin Garzali ya tone asirin da suke ta rufewa, a sanadiyyar soyayyar izzatu da hango ta rufe masa idanuwa, komi zai iya aikatawa akan ya sameta.

A lokacin Izzatu tana Ss3 a makaranta suna gaf da k'arewa, aiko Dr yaji dad'i a cikin zumud'i ya sanar da iyayenshi, iyayenshi suka turo a b'oye ayi masu binciken wacece izzatu da halin iyayenta.?

A binciken farko suka gano izzatu d'iyar tsintuwa ce, suka buga kansu akan cewa Dr bazai auri izzatu ba, shi ko ya kafe akan cewa sam baisan zancen ba, dole ne sai ya auri izzatu.

Takanas mahaifiyar shi da mak'arrabanta sukayi tattaki suka je har k'auyen, koda suka je gidan suka iske iya kulu a tsakar gida, ba tareda b'ata lokaci ba mahaifiyar tace,

"Kece mahaifiyar izzatu?."

Iya kulu ta zabura tace

"Rufani ki saya kin dai ga d'akin marik'iyarta, amma nikam Allah ya tsari gatari da saran shuka."

Iya kulu ta k'wallawa Mama kira tace,

"To hassatu a fito ga ranar girbar abunda kuka shuka tazo."

Mama hassatu jin muryar iya kulu a sama yasa ta zare jikinta daga kwanan da takeyi tareda ilham, ta d'aga labule ta fito,karaf idanunta sukaci karo da wad'annan gogaggin yan gayu, da sauri  ta fito idanunta a kansu tana yimasu sannu da zuwa.

A cikin hayagaga mahaifiyar Dr tace,

Nazo ne inyi maku gargad'i akan 'yat tsintuwa da kuke so ku lik'awa d'ana, idan ba mugunta ba yarinyar da ba'asan asalinta ba, zaku cusawa wani ya aura?, muna fa da labarin izzatu shegiya ce, wadda aka haifa ta hanyar banza aka jefar a daji kuka tsinto, ina kuka tab'a ganin aure a tsakanin mai asali d'an babban gida da d'iyar shegu d'iyar tsintuwa a cikin kwali a tsakiyar dokar daji"

Izzatu dake tsaye a bayansu rataye da jakar makarantar ta ba shiri ta k'walla k'ara tareda zubewa a k'asa sumammiya.

Kuyo agaji lik'i ya b'alle😳😳😳😳😳😳😳wayyo Allah🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️

Akafta😭

D/Auta ce😇

[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*I LOVE YOU ALL MU FAN'S 💋💋💋💋💋*

*PAGE THIRTY EIGHT*

**********************

A million Mama tayo kan izzatu ta rungumeta,  tarea kiran sunan ta amma ina izzatu ko gezau bata yi ba, da sauri ta tashi ta ciko wani jug da ruwan tukunya mai sanyi ta watsa mata, ba shiri izzatu ta falko a firgice tareda kurma wata irin k'ara iya k'arfinta, Mama ta rungumota a jiki itama tana kuka, izzatu ta ture hannun mama ta tashi da gudu zata bar gidan mama ta cafko ta, aiko sai tayi tsalle ta fad'i a k'asa tana ta tumurmusa a cikin k'asa tana wani kuka na tashin hankali.

Kande dake a saman katanga itada yaranta suna lek'e, jikinta har b'ari yakeyi akan taga ya wannan rigimar zata k'are, don bata son rigimar ta tsaya iya nan,  shiyasa tace da wani d'anta ya tafi gidan mai unguwa da sauri ya sanar da shi abunda ke faruwa, aiko yaro ya balbala agujensa duk wanda ya had'u dashi sai ya fad'a masa cewa

"Gidan malam Ayuba 'yan birni suna cen sunzo zasu kashe izzatu"

Kafin kace me  sai ga  dandazon mutanen sun cika k'ofar gidan kowa da abun bugun shi, sai muzurai sukeyi wasu suka ce a shiga a fito dasu, yayin da wasu suka ce a jira sai sun fito, amma fa daga nan cikin gidan suna jin duk hayagagar da akeyi.

Mahaifiyar Dr da muk'arrabanta dake a tsaye,  suna yiwa izzatu da mama wani kallon hadarin kaji, suna jin sautin ruwan bala'in da  mutane suke yi  a waje,  ga wasu 'yan ganin k'wak'waf har sun fara shigowa, aiko cikin su ya d'uri ruwa tsoro ya shige su sai kallon juna sukeyi, suna tambayar juna miye mafita?, wata daga cikin su ta kalli katangar dake zagaye da gidan, tana neman ta wani gefe zata dira, sai gashi  ta hango katangar gefen bayin su ta ruguzo tsawonta ya rage, a d'ari ta nufi katangar kamar wata mai gasar tsallake katangu ta kama ta dire, sauran suna ganin wannan hanyar itace  mafi sauk'i da zasu tsira, aiko suma suka kama suka diddire, kande da d'iyanta da sai kururuwa sukeyi suna fad'in,

"Gasu cen sun dire, ga su nan zasu tsere, abisu kar su sha banza."

Aiko mutanen dake k'ofar gida suna jin ana kuwwar sun dire, suma suka raka su a guje suka bisu suna kururuwar a tare a tare.

Suko suna ganin sunci nasarar fita daga gidan,suka fara gudun fanfalak'i, Allah yaso su duk ba wani jiki ne dasu ba dak'yar suka kai bakin titi suna haki, sai ga wata mota zata wuce ta kwaso yashi, a d'ari suka tareta suka fad'a cikin yashi suna ta hakin wahala, koda 'yan k'auyen suka k'araso sai dai suka hango su sun shige mota, suka bita aguje har saida suka ga bazasu cimmata ba sannan suka hak'ura da biyar su.

A cen gidan malam ko izzatu ta haukacewa mama akan sai ta fad'a mata asalinta, zuwan mai unguwa da kanshi a cikin gidan,  shi ya ladaftar da izzatu daga tashin hankalin da take yi, da kanshi ya saka ta a gaba  ya tafi da ita gidanshi, bayan ya bada sallahun aje a d'auko masa malam kasuwa.

Malam tunda yaji sak'on neman da mai unguwa yake yimasa, jikinshi yayi sanyi k'alau don yasan ba lafiya ba, a cikin tashin hankali ya isa gidan mai unguwa.
Bayan malam yazo ne mai unguwa da wasu mutum biyu da sukayi saura, wad'anda a gabansu Dada da malam suka zo da izzatu tana jaririya, aka saka izzatu da ke ta sharb'ar kuka kashirb'in a tsakiya, mai unguwa yayi gyaran murya yace,

"Nasan tabbas dole ne ki shiga tashin hankalin da yafi wannan, saboda kunnuwanki sunji abunda ya rikita tunanin ki, izzatu kiyi hak'uri da duk abunda kikaji, saboda ita k'arya fure take bata 'ya'ya, tunda gashi yau sirrin da ake ta rufe maki shekara da shekaru ya bayyana, to dole ne muyi maki bayanin komi,  amma ki tsaya da kyau ki yiwa maganganun mu kyakkyawar fahimta, don mu dukanmu farin ciki muke nema ba abunda zai sak ki a matsala ba, tabbas ke d'iyar tsintuwa ce da gaske malam ayuba shi ya tsinto ki, don haka yanzu zakiji yanda akayi ya tsinto ki har kika tashi a hannun shi, yayi maki rik'o irin na amana tareda mahaifiyar shi Dada 'yar tsohuwa Allah ya jikanta"

Gaba d'aya fadar akace     "Ameen"

Malam a cikin d'inbin damuwa ya fayyacewa izzatu komi, tun daga ranar da ya tsinceta, har izuwa gata da tattalin da Dada tayi mata, da wasiyyar da ta bari akan a rik'e mata izzatun Amana da rasuwar ta, har zuwa auren Hassatu da yayi itama ta rik'eta tamkar itace ta haifeta.

Daga nan d'aya bayan d'aya kowa yana yimata bayanin abunda ya sani akanta, jikin izzatu yayi sanyi hankalinta ya kwanta, musamman da taji ance ita ba shegiya bace, sannan da zargin da sukeyi akan  Baba kallah ko shine mahaifinta.

Daga nan sukayi ta kwantar mata da hankali, akan tayi hak'uri iyayenta sun kusa bayyana tunda har kallah yasan inda take, ko ba shine mahaifinta ba to tabbas yasan wacece ita, daga nan itama ta tuno d'awainiyar da yakeyi da ita, wadda a tsakani da Allah yake yimata hidima ba gajiyawa, sannan ta tuno lokacin da tayi masa tambayar me yake zuwa yi a garinsu kullum, irin yanayin da ya shiga har yaso ya jawo masu accident a titi, lokacin da ya d'auko ta daga makaranta, haka kawai taji hankalinta ya kwanta, amman zuciyarta sai tunanin takeyi su waye ne iyayen nata?, a wani gari suke?, me yasa suka zab'i rabuwa da ita fiye da su barta ta rayu da su?, tana fatar taji wad'annan amsoshin a bakunan su ko bakunan wad'anda suka san asalinta.

A cikin sanyin murya izzatu ta fara yimasu godiyar irin d'awainiyar da sukayi da ita, musamman malam da ya rik'eta  tamkar d'iyar cikinshi, ya nuna mata so fiye da d'iyan da ya haifa, ta k'are maganar tana kuka tuno irin soyayyar da akace Dada tayi mata, gashi bata raye balle tayi mata godiya, amman tayi alk'awalin duk ta kai goshinta a k'asa tayi sallah sai ta rok'arwa Dada rahmar ubangiji ta k'ara ninkuwa a cikin k'abarinta.

Daga nan malam da izzatu suka rankayo gida, duk inda ta wuce izzatu kallonta akeyi ana nunin ta,  ashe daman cen mai unguwa ne yayi jan kunne akan duk wanda yayi sanadin izzatu ta gano wacece ita,  to tabbas hukuncin shi d'aurin rai da rai a gidan yari, shiyasa kowa yake ta taka tsantsan don jin tsoron wannan hukunci, amma in banda haka da izzatu ko k'ofar gida bata isa ta fito ba, aikuwa nan take taji ta tsargu tana sunne sunne har suka kai gida ita da malam.

Koda suka shiga sun iske mama sai kuka takeyi,  idanunta sunyi jawur saboda irin masifar kukan da tasha, na tausayin 'yarta izzatu ganin tashin hankalin da ta tsinci kanta a ciki wanda ba zato bale tsammani, duk tasan komi daren dad'ewa wannan ranar zata ZO, amma ba a haka taso zuwan ranar ba.

Ganin yanayin da izzatun ta shigo ne ya d'an kwantar mata da hankali, izzatu tana zuwa ta fad'a, a jikin mama ta fashe da wani marayan kuka tace,

"Mama nagode da irin k'aunar da kika nuna man, alhali kinsan ba kece kika haifeni ba, amman da rana d'aya baki tab'a barina nayi kukan rashin uwa ba, nagode nagode mama, yanzu na gano dalilin da yasa kike hana ni bin ba'asin gugar zanar da iya take man, ashe kina hana ni zurfin tunanin da zan gano inda maganganunta suka dosa ne, Allah sarki mamata kin toshe kowace k'ofar da kikasan idan naji asalina zan shiga damuwa, Allah ya saka maki da alkhairi,

kin bani kulawarki da aljihunki da kuma gangar jikinki sannu mamata,  wallahi ko a  aljanna ke taki  ta k'ololuwa ce, malam da ke mamata da masoyiyata Dada da yaya Garza na, ina sanar maku  da duk abunda na zama a fad'in duniya bazan tab'a manta ku ba a tarihin rayuwa ta, saboda kune k'ashin bayana a doron k'asa, wanda idan ba d'aya daga cikin ku bazan tab'a jin kaina dai dai ba, ya ALLAH ka barni tareda wad'annan bayi, ka bani abunda zan kyautata maku koda rabin rabin abunda kuka yiman ne."

Izzatu ta tashi da gudu ta rik'e k'afafun malam tace,

"A gaida baya goya marayu sannu jarumi a cikin JARUMAI, kaine babana na har abada wanda idan na rasa shi rayuwata ta tawaya, Allah ya yi maka fiye da yanda kayiwa rayuwata gata, nagode nagode babana!."
Mama da malam da ita kanta izzatu sai kuka sukeyi gwanin ban tausayi.

Har ga Allah nima na tausayawa wannan ahali 😥😥😥.

Akafta 😊

D/Auta ce👍🏻
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*PAGE THIRTY NINE*

**********************

Iya kulu dake tsaye tana kallon su jiki a sanyaye ta shige d'aki, amma a cikin zuciyarta taji dad'in wannan asiri da ya tonu, ko don abarta yanzu ta sakata ta wala yanda takeso.

Washe garin ranar Dr yazo k'auyen, saboda ya sami labarin fitar kutsun da mahaifiyar shi suka yi a garin, tun a jiyan yaso yazo amman jin abunda ya faru ya sage masa gwiwowi, don jikinshi yana bashi ba abun alkhairi suka zo suka shuko a garin ba, shiyasa aka ymasu wannan bajimin wulak'ancin, domin kuwa mahaifiyar shi duk ta gurje jikinta asanadiyyar tsallakar katangar da suka yi, sannan k'afafuwanta duk k'ayoyi sun shige mata aciki, don ko kafin ya fito sai da yayi mata dressing d'in ciwukan yayi mata allurori, saboda tana komawa gida zazzab'in mai zafi ya rufeta, jiki asanyaye yayi parking d'in motar shi ya fito, a k'ofar gidan ya tsaya ya tura wani yaro yace ya kira masa izzatu, aiko madadin izzatu ta fito sai ga malam shi ya fito, saboda abunda ya faru ya hanashi jin walwalar da zai fita kasuwar da ya saba.

A cikin ladabi Dr ya gaida malam, amma malam fuskar shi tamau yake amsa gaisuwar, ba alamun zai iya yiwa Dr sassauci a wannan karon, bayan sun gaisa kafin Dr yace wani abu malam ya riga shi da fad'ar cewa,

"Naga sak'on da ka turo iyayenka akan su ZO su kawo, to sun zo kam sunyi abunda suke so kuma sun janyo abunda muke b'oyewa tsawon shekaru ya tonu, to Alhmdllh da ban riga na aura maka izzatu ba, don haka ina son ka sani daga yau kada in sake ganin k'afar ka anan k'ofar gidan, na raba alak'ar ka da izzatu har abada, koda ko ku biyu ne kawai kuka rage a cikin duniya izzatu bazata aureka ba, abunda kayi muna na alkhairi mun gode bamu rena ba Allah ya saka da alkhairi."

Malam yana k'are fad'ar maganar ya fara taku zai shige gida, da sauri Dr yasha gabanshi ya dyurk'usa gwiwa bibbiyu yana cewa,

"Don Allah kayi hak'uri ka yafeman malam, wallahi ban ma san sunzo ba bale in aiko su da sak'on cin zarafi a gare ku, kai kasani bazan tab'a yin abunda zai cutar da izzatu ba, naji na amince zan daina zuwa insha Allahu amma bazan daina son izzatu ba, don Allah kayiman alfarma ta k'arshe ka amince mani da inga izzatu a yanzu, domin in rok'eta yafiyar abunda aka yi mata don Allah malam"

Ba tareda malam yace k'anzil ba ya shige cikin gidan, minti biyu a tsakani sai ga izzatu ta fito fuskarta da busashen hawaye, saboda tun jiya hawayen dake idanuwanta sun kasa tsayuwa.

A hankali ta tako har inda Dr ya ke a durk'ushe, don k'afafuwan shi sunyi sanyi k'alau, jin yakeyi bazasu iya d'aukar nauyin shi ba, ya d'aga kai yakai dubanshi a kan fuskar izzatu, da ta kunburo saboda tsananin kukan da tasha, a cikin raunanniyar murya ya fara magana yace,

"Izzatu duk wata kalma da zanyi amfani da ita wajen baki hak'uri, ganin nikeyi tayi k'aranci, amman duk da haka ina baki hak'urin don Allah kiyi hak'uri ki yafe man, wallahi bada sanina suka zo ba har sai bayan sun dawo ne na sami labari"

Izzatu da idanunta k'yar akanshi tana yimasa wani kallon da ita kad'ai tasan ma'anar shi, a cikin dusashiyar murya tace,

"Ai ni taimako na ma sukayi, don sun fitar dani a cikin duhun da a kullum ya kamata ace na fito acikin shi izuwa haske, Alhmdllh duk ta hanyar da aka sameni nayi imani da Allah akan cewa shine k'addarata, kuma na rungumeta da hannu bibbiyu, abu d'aya ya hana in nuna maka kalar 'ya'yan tsintuwa saboda naji an fad'a ma asalina kuma kaji ka gani a hakan kake sona baka k'yamace ni ba, asanadiyyar hakan kaje na yafe maka itama mahaifiyarka na yafe mata tashin hankalin da ta sakani,  ALLAH ubangiji ya had'a fuskokin mu a aljannah nida kai,na gode da d'awainiyar da kayi tayi dani, ina maka fatar ALLAH ubangiji  ya baka mace ta gari yar asali wadda zakayi alfakhari da samunta,  na barka lafiya sai watarana"

Tana k'are maganar ta zo da gudu zata  shige gida, a sanadiyyar wani kuka da yazo mata, ya d'aga murya ya kira sunanta, ta tsaya cak ba tareda ta waigo ba,  a cikin wata murya at ban tausayi mai had'e da kuka tace,

Zuciyar Dr hashim ki sani har abada bazata iya daina k'aunar ki ba, son ki a cikin jinina yake bazan iya cire shi ba har sai ranar mutuwa ta, I love you too my izzah! i love you up to end of my life, never mine izzatu, ina yi maki fatar alkhairi a rayuwarki."

Wani kuka yazo mata ba shiri da gudu ta fad'a gidan sai gunjin kuka takeyi, jin kukan da takeyi ya k'ara dagula wa su malam zukata, gaba d'aya ta k'ara famo masu damuwar dake damunsu.

A cen k'ofar gida kuwa,  izzatu tana shiga gida Dr yaji kamar an zare masa duk wata laka dake a jikinshi, ba shiri yakai jikin motar shi ya jingina, tareda dafe zuciyar shi dake barazanar fitowa, saboda bugun da takeyi da sauri da sauri, yana nan a tsaye sai kawai ga d'aya daga cikin 'yanmatan kande, tana wani kwarkwasa tana fari da ido, mamaki ya kama Dr na ganin wannan rashin hankali da takeyi, ba shiri ya maida idanuwanshi ya runtse saboda tsabar takaicin da ta bashi, mariya d'iyar kande ganin hakan yasa ta zaci tarkon da ta d'ana masa yayi kamu, aiko ta fara zuba tamkar kanya tana cewa,

"Sunana mariya amma anan garin anfi sanina da mari, a duk garinnan idan ka zagaya kaf babu wata mace da ta kamo k'afata, tunda ita wannan 'yar tsintuwar bata da rabo, to me zai hana ni ka dawo a kaina?, nayi alk'awali zan baka farin ciki fiye da wanda kayi kwad'ayin samu a wurinta, ka soni ka turo iyayenka ni kaga gidanmu a nan, uwa da uba na duk 'yan garinnan ne kowa yasan asalinmu, don haka idan ka amince ni a shirye niko ko a gobe ne kazo a d'aura muna aure ni da kai"

Dr ba shiri ya bud'e idanuwanshi ya kalleta tun daga sama har  k'asanta, ita ko ganin haka sai wani juye juye takeyi tana murmushin nasara, bai san lokacin da wata dariya ta sub'uce masa ba, sannan ya had'e fuska kamar ba shi ba yace,

Ke wai a zatonki ke mace?, cab to bari in fad'a maki gaskiya a baki d'aya yanayin ki kaf ba na mata, don farkon ganin da nayi maki nama zaci namiji ce, har sai da naji muryarki na gano ashe mace ce ke, to nikam taya zan kwashi mai siffar maza in kai gidana?, idan anzo a kasa gano waye mijin wacece matar.?

Kafin ta tantance ya shige motar shi ya bata wuta, aiko ganin da gaske tafiya zaiyi tayi saurin zuwa ta tsaya a gabanshi, ya zuro kanshi yace,

"Kauce daga nan ko in nuna maki k'arshen rashin kunya."

Mari tayi tsaye tana yimasa gwatsine gwatsinen ido da hanci, aiko Dr da k'arfi yayo cikinta ba shiri ta kauce tana yimasa Allah ya isa.

Kwanaki sun ja a kullum malam da mama sai k'ara kwantar mata da hankali sukeyi akan tayi hak'uri insha Allahu saura k'iris ya rage iyayenta su bayyana a gareta, a nan ne ma take yiwa mama bayanin matar da ta had'u da ita a BADAWI SHOPPING, mama taji dad'in jin wannan labari, domin hakan ya nuna tana gaf da sanin iyayen izzatu.

Takanas Garzali ya aiko ma izzatu da waya ta hanyar wani akokin karatun shi da aka turasu service d'in a garin inyamurai, aiko izzatu taji dad'in wannan waya domin kuwa ta rage mata rabin damuwar da take a ciki, saboda a kullum tana lik'e da wayar suna fira da yaya Garzan ta, malam ma ya karb'i wayar yayi masa bayanin duk abunda ya faru, ba k'aramin dad'i Garzali yaji ba, saboda hakan ya nuna cewa izzatun sa zata zamo mallakin shi, a kullum sai k'ara dulmiya sukeyi a kogin k'aunar junan su wanda a gefen iya kulu ko kad'an bata son wannan bak'ar lik'ewar da izzatu takewa Garzali, don tasa a ranta in dai itace ta haifi Garzali to tabbas za'ayi yak'in badar na biyu,don kuwa ko bazata bari Garzali ya auri izzatu ba.

Lokacin k'are makarantar izzatu yayi malamai suka shirya masu k'wark'waryar bikin k'are makaranta, an gayyato manyan mutane kasanceawar makaranrar ta d'iyan shafaffu da mai ce, shiyasa da aka tashi ba'ayi k'asa a gwiwa ba wajen gayyato mai girma his Excellency Alhaji YAHAYA BADAWI, tareda wasu jigajigan 'yan siyayasa tareda manyan sarakuna, da manyan malamai zasu halarci taron bikin k'are makarantar tasu.

Izzatu sai d'oki takeyi akan zatayi ido hud'u da wannan hamshak'in gwamnan, wanda tun a ganin  farko da tayi masa taji ya kwanta mata a rai, tun a daren ranar bikin take ta jin yawan fad'uwar gaba, ta rasa meke damunta, jin kanta takeyi kamar bata son zuwa taron bikin, amma

kuma a wani b'angaren tana farin cikin zuwan ta ko don saboda abu biyu, yaya Garzanta yace zai zo shima ayi dashi, sai kuma d'okin ganin wannan Gwamnan da takeyi.

A ranar bikin tun da safe mai gari ya bada mota suka cikata fam, Mai unguwa da malam, sai mama hassatu da iya kulu da ita izzatun, ansha uwar barafasa da iya kulu kafin malam ya shawo kanta tazo,  bikin, don a cewar ta ita bazata zo ba a had'a baki aje a saida mata kai tana sake da baki ba, malam ya tilasta mata sai taje ne saboda wani malamin su izzatu ya sanar dashi duk rabin kyautukan izzatu ce ta cenye, to yana so taje taga irin bauwar da Allah yayiwa izzatun, koda Allah  zai sa ta rage tsanar izzatu a zuciyarta.

Aiko taro yayi taro wuri ne na sai wane da wance,iya kulu sai rabon ido takeyi tana kallon manya manyan hajiyoyi tareda zunduma zunduman motoci, a wani k'aton fili ne akeyin taron yayinda  aka k'awata wurin da rumfunoni na alfarma, kasancewar makarantar shafe take kaf da b'urji shiyasa kowa ka hango tsaf tsaf yana takun gwadin ina tsaarata?.

Bayan an zazzauna manyan bak'i sun hallara sai kawai akayi sanarwar ga gwamna nan zuwa, aiko gaba d'aya wuri ya rincab'e da sowa saboda ana son shi sosai, saboda yana mulkinshi a cikin adalci da sanin makamar aiki, kafin kace me wuri ya hautsine da kuwwar ganin gwamna, a cikin tsanaki yake takunshi fuskar shi d'auke da wani mayalwacin murmushi, sai hannu yake d'agawa mutane yana mik'a gaisuwa,   security's a gaba da bayanshi, har suka kaishi wani k'awataccen muhallin da aka tanadar masa ya zauna, mutane sai lik'e suke yau gasu ga Gwamnan jahar su.

Cen na hango iya kulu ta zula kai tana so ta yimasa ganin k'wak'waf don taji dad'in bada labari, sai d'aga masa hannu takeyi daga nesa tana kiran,

"Taka lafiya baya goya marayu,mijin  hawainiya mai tafiyar k'asaita, sukari bakayi farin banza ba"

Abun mamaki sai gashi na hango Hajiya fatima da Ammi Hadizatou tareda baba kallah a bayansu, yayi fari ya k'ara jiki alamun kwanciyar hankali ya bayyana a jikinshi, sai ga wasu security's gaba da bayansu suma sai tafiyar k'asaita sukeyi, aikuwa sai mc ya fara kururuwar zuwan matan Gwamna, wuri ya k'ara hargitewa sai mamaki akeyi ga Gwamna har da matanshi biyu a taro d'aya, lalle wannan biki ya amsa sunan shi, aka bubud'a masu hanya, aka yimasu masauki a kusa da maigidansu, d'aya a gefen dama yayin da d'aya take a gefen hagu, daga nan aka natsar da jama'a sannan aka gayyato wani shahararren malami a jahar yazo ya bud'a taro da addu'a, sannan aka kira sunan IZZATU AYUBA da tazo ta bud'a taron da karatun alk'ur'ani.

K'irjin izzatu ya buga dam!! ba shiri ta janyo lik'abin da mama sako, tun a cikin mota da zasu zo

ne ilham ta cire shi a saman kan mama, shine izzatu ta rik'e mata a hannunta, aiko tana jin an kirata ta saka shi ta rufe fuskarta ruf, ta fito a tsakiyar filin ta fara rero karatun alk'ur'ani tamkar wata balarabiyar makkah saboda a makaranrar akwai sashen karatun arabic to ko ina da ita ake karatun, a nan ta koyi karatun k'ira'ar Hafs, aiko jikin mutane yayi sanyi saboda muryarta dake fito da k'ira'a mai kashe duk wata zuciyar mai imani.

Malam da mama har kukan farin ciki sukayi saboda jin dad'in ilimin da izzatu ta samu.
Bayan taje ta zauna ne aka fara gudanar da shirye shirye, daga nan aka tsunduma rabon kyaututtuka,a dai dai lokacin ne Garzali ya k'araso filin taron, yana jin ankira sunan izzatun shi ya kutsa taro ya shiga ya tsaya a bayan ta, kyauta ta farko da aka bata, tana k'ok'arin barin wajen ne yasha gabanta da sauri ta d'aga lik'abin kad'an ta kai kallonta akan fuskar shi, aiko tana ganinshi wani farinciki ya mamaye zuciyarta, ya zura hannu ta mik'a masa kyautar, daga nan aka sake kiran sunanta ta saki lik'abin ta dawo, ta karb'i kyautuka sun fi goma kuma duk wadda ta karb'a shi take baiwa.

Bayan ank'are kiran sunan ta ne akace taje ta zauna, yaya Garzanta ya rik'o hannunta a cike da farin ciki, sun je kan wasu kujeru sun zauna kenan aka sake kiran sunan IZZATU AYUBA, akan ta fito mai girma gwamna zai bata tashi kyauta ta musamman.

A nan take wurin aka d'auki tab'i izzatu ta tako a hankali tazo tsakiyar filin, mai girma Gwamna ya taso tareda ss nashi masu take masa baya ya tsaya idon shi akan izzatu, dake a tsaye sanye da lik'abinta shif shif baka ganin komi nata sai k'wayoyin idanuwanta, sannan aka baiwa mai girma Gwamna damar ya fara magana ta hanyar mik'a masa microphone yayi magana, ya kalli izzatu tun daga saman tafinta har kanta yaji dad'in shigar da yaga tayi na cikakkiyar 'ya tagari mai tarbiyy, ya fara jinjina mata akan shigar kamalarta da k'wazonta, sannan ya fara jero albishir d'in da yayi niyya a gareta, bakin shi a washe ya fara magana kamar haka,

"A bisa yanda naga jajircewar ki da k'wazon ki, nayi maki alk'awalin kujerar makkah, sannan nayi alk'awalin d'aukar nauyin karatun ki izuwa k'asar london,idan har iyayenki sun amince domin k'ara farfad'o da karatun ki, saboda samun irinki 'yan baiwa abu ne wanda ya kamata ace an tallafa maku, ko don al'ummah ta amfana da irin baiwar da Allah yayi maku, sai kyauta ta ta uku kuma ta k'arshe, amma ita kam bazan bada ta ba har sai naga hafizar mu ta bud'e fuskarta sannan ta karb'a, don bana farin ciki idan aka watse wannan taro ace banga fuskar 'yata 'yar baiwa ba"

Izzatu ta saka hannu ta bayan kanta a hankali ta kwance k'ullin da tayiwa lik'abin, ta janye shi daga fuskarta ba shiri zuciyoyin mutum biyar a wurin suka buga a lokaci d'aya.

Daram dam dam tashin bomb nima tawa zuciyaresai dakan lugude takeyi😂😂😂😂😂.

Akafta🏃‍♀️

D/Auta ce💃
[8/22, 6:52 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*MY SPECIAL GIFT TO YOU MY MUM &MY SUNSHINE DAUGHTER💃💃*

*mum luba yakamata(mum of 3ful H)*

*My lovely daughter Roophaeda Auwal idris💋*

*PAGE FORTY*

*********************

*Shin wad'anni  zuciyoyin ne suka  buga???*

Da sauri mai Girma Gwamna ya yarda microphone d'in dake hannun shi, saboda bugawar da zuciyar shi tayi ba shiri, tareda k'are k'ule hasken fitullun gilashin idanun shi akan kyakkyawar fuskar izzatu.

Hadizatou AMMI itama da hankalinta yake a kan mai gidanta da wannan d'aliba, wadda a lokaci d'aya taji tana muugun k'aunar yarinyar tana ta ina ma ace itace ta haife ta, saboda yarinyar ta tafi da tunaninta wanda har yasa ta tuno yarinyar da ta gani a bakin titin BADAWI PLAZAR, saboda izzatu ta burgeta sosai, anan take tsohon mikin dake a cikin zuciyarta ya taso, abun mamaki  anyi mata bazata cin karo da fuskar yarinyar,  da taso tayi accident domin neman ganinta ido a rufe, sai gashi yau gata a gabanta tana kallo tamkar wata majigi.

Hajiya fatima AMMAH, itama k'irjinta yafi na kowa bugawa, duk da tana da masaniyar izzatu ko wacece,  amman dai bata tab'a ganin ta ido da ido ba sai a yanzu, saboda duk ganin da take yimata a cikin photo ne, amma yanzu ganin zahiri da tayi mata ya tabbatar mata da cewa, da gaskiyar Kallah da yace mata yarinyar tana tsananin kama da Hadizatou tamkar kwabo da kwabo, sannan k'arin tashin hankalinta a yau duk wata k'unbiya k'unbiyar da take yi ta k'are.

KALLAH shima tashi zuciyar ba k'aramar bugawa tayi ba, saboda yau ne ranar tonon asirin da suke rufewa a tsawon shekarru, wanda tabbas fasuwar wannan k'wai  dai dai yake shigar rayuwar shi a cikin garari, don koda anyi masa uzuri kunyar idanuwan mutum uku bazasu tab'a barin shi yaji dad'in zama a kusa dasu.

Mai gayya mai aiki izzatu bud'e fuskarta da tayi a cikin d'inbin dubban mutane, ga y'an jaridu 'yan gidan radio da masu d'auka a gidan television sai aikin su sukeyi, shi ya fara saka zuciyarta bugawa, d'ago fuskarta da tayi ta jefa kallonta akan fuskar mai Girma Gwamna,  ya k'ara saka ta a cikin wani fad'uwar gaba wanda ta kasa tantance shin wai na miye, tayi k'ok'arin wanke fuskarta da wani tattausan murmushi.

Mai girma Gwamna a cikin d'imaucewa ya d'auko microphone yace da ita,    "'yata miye sunan ki na gaskiya.?"

Izzatu tayi wani murmushi tace,    "sunana IZZATU AYUBA."

Mai girma Gwamna jikinshi yana kyarma yace,    "A wani Gari kike.?"

Izzatu tace,    "A k'auyen D'anlasau"

Mai girma Gwamna ya k'ara da cewa, "shekarar ki nawa.?"

Izzatu tace, "Shekarata goma sha tara."

Mai girma Gwamna yayi wata kabbara wadda ta baiwa kowa mamaki yace, "ALLAHU AKBAR ALLAHU ASSAMADU ALLAHU ASSAMI'U ALLAHU AL'ALIMU ALLAHU AL'BASIRU WALLAHI TALLAHI ALLAHU WAHIDUL K'AHHAR NE"

Sai mai girma Gwamna ya fashe da kuka, aiko gaba d'aya wurin yayi tsit sai mamakin wannan abun al'ajabi dake faruwa da mai girma Gwamna ake yi.

Hajiya fatima jikinta yayi sanyi k'alau wani imani ya k'ara shigarta, nadama tazo mata taji idan bata bayyana wannan gaskiya ba, to tabbas kamar mutuwa zatayi a wurin, wanda take ta hango idan fa ta mutu a lokacin a wuta za'a jefata, jikinta ya d'auki rawa tamkar wani mazari, ta tashi tsam k'afafunta suna hard'ewa, da wasu hawayen masu zafi da suke kwaranya a kan fuskarta, ta saka hannu janyo hannun hadizatou dake zaune tamkar wata mutum mutumi, har sai da takaita a gaban izzatu ta rik'o hannun izzatu ta had'a da na hadizatou, kamar wani magnet haka hannunsu ya had'e gam sai kallon juna sukeyi ko k'yaftawa babu.

Hajiya fatima ta karb'o microphone ta kalli mai girma Gwamna yanda yake kuka hawaye wasu suna biiyar wasu, itama wani kukan yazo mata da sauri ta share hawayenta, ta aro wata jarumta ta ta yafa, ta kalli Hadizatou ta dawo da kallonta akan izzatu, tayi tattaki tazo tsakiyar fili ta tsaya ta fara magana kamar haka,

"HADIZATOU GA 'YARKI DA TA B'ATA TSAWON SHEKARA GOMA SHA TARA DA SUKA WUCE, IZZATU GAKI GA MAHAIFIYARKI TA CIKIN KI WADDA TAYI SILAR KAWO KI DUNIYA DAGA YAU SUNAN KI IZZATU YAHAYA BADAWI EXECUTIVE GOVERNOR OF...... "

Ba shiri wurin ya d'inke da sowa kowa sai albarkacin bakinshi yake fad'a.
Hajiya fatima ta fashe da wani bajimin kuka a cikin tashin hankali, zata k'ara wani bayani ne mai daraja gwamna ya rungumo ta a jikinshi yana lallashi, aikuwa wuri ya k'ara d'inke da kuwwa.

Hadizatou jikinta yana kyarma ta rungumo izzatu a jikinta tamkar wani zai k'wace mata ita, IZZATU dai a tsaye take sai walainiya da idanuwa takeyi, amma gaba d'aya gangar jikinta ta daina aiki, har sai da ta hango yayanta Garza yana so ya shigo a cikin filin yazo wurinta, wasu security's suka hanashi zuwa, shi kuma ya nace akan dole sai yazo wurinta.

Aiko wani soja ya cira hannu ya kwad'a masa mari, wasu 'yansanda suka rirrik'eshi, wani soja ya d'aga bindiga zai daki kanshi, ba shiri izzatu ta k'walla wata razananniyar k'ara ta k'wace jikinta da ke mak'ale da hadizatou ta nufeshi da gudu tana kiran sunan shi.

Tana zuwa ta fad'a a jikin shi tana wani kuka wanda ita kanta batasan ko na minene ba, shima kamar zaki haka yayimata wata wawar runguma sai kukan yake tamata, gaba d'aya sai kallo ya koma kansu, masu video da d'auka a gidan television live sai haskawa sukeyi, haka 'yan gidan Radio sai bada labarin abunda ke faruwa sukeyi, yayinda a ko'ina a fad'in jahar abunda ake kallo da sauraro kenan.

Rigiji gabji akwai ruguntsumi da cakwakiya a gaba wallahi 🙀🙀🙀🙀🙀🙀🙀

Ku biyoni don jin yanda zata kaya🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️.

Akafta🏃🏻‍♀️

D/Auta🏃🏻‍♀️

[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*Dole inji da k'arfi a jikina💃 dole in maku komi da gumina 💃babu  iya yimaku komi a gaba na💃 naji duk sharhin da kukayi akaina kuma ya shiga raina 💃dole ne in dauro d'amarata a tare musha madara💃💃💃*

*Wai shin gudu nake💃 ko tafiya nike,💃 wai zafi ake 💃ko sanyi ake,idona gani yake kamar budo muke💃 kutsaya ni nagaji ku bani agaji💃akan ku bani ji 💃a zancen post  bazan yima ku hijira ba💃💃💃💃*

*PAGE FORTY ONE*

*********************

Mama hassatu da malam da suke zaune suna kallon abun da ke faruwa, gaba d'aya suma kukan sukeyi sai k'ara jinjina wa hikimar Allah sukeyi, yanzu izzatun su itace d'iyar gwamna?, lalle Allah buwayi gagara misali ne kawai zai iya wannan lamari.

Iya kulu tana gano abunda ake nufi,, magana ta tabbata lalle izzatu d'iyar Gwamnan ce, ai kuwa da gudu tayi wani lungu tareda tsintar wata leda a k'asa,  afujajan ta duk'a sai zawo take zubawa sai da tayi iya cikinta,  sannan ne ta saka ruwan gorar dake hannunta ta wanke ta fito, jin takeyi kamar tayi tsuntsuwa ta ganta a k'auyensu, a k'auyen ma a cikin d'akinta,  a d'akin ma a k'ark'ashin gado tana addu'ar Allah ya d'auki ranta ta huta kafin su malam su dawo su risketa, don kuwa tasan tabbas had'uwar ta da wannan hamshak'in Gwamnan ba abu bane mai kyau, iya kulu tana hango izzatu rungume da matar Gwamna da gudu ta koma lungun ta kara bajewa sai nishin wahala takeyi, kafin kace kwabo iya kulu idonta sunyi zuru zuru saboda tashin hankali, sai hango kan ta takeyi a gidan yari ana ta lafta mata buloli tareda gana mata azaba kala kala.

Mama hassatu hango Garzali da tayi rungume da izzatu jikinta yana rawa ta zagaya, dak'yar ta samu ta kutsa ana turinta amma bata daina yunk'urin  isa wurin su ba, a cikin d'aga murya ta dakawa  Garzali da izzatu tsawa tace,

"Garzali da izzatu a kul d'inku da wannan rashin kunya a gaban mutane sai d'aukar ku photo akeyi, da sauri izzatu ta saki garzali a d'ari taje ta rungume Mama hassatu tana ci gaba da

kukanta mai tsuma zuciyar mai sauraro,  izuwa lokacin idanunta har sun kunburo fuskarta tayi ja saboda tsakanin kukan da tasha.

Mai Girma Gwamna da kanshi ya tako har inda su mama da izzatu suke a tsaye, ya saka hannunsa ya rik'o hannunta ya feshe ta da wani murmushin farin ciki, itama ba shiri ta fad'a jikinshi ya saka hannu biyu ya rungumeta, tareda bubbuga bayanta akan tayi hak'uri kukan ya isa a hakan, daga nan izzatu ta d'ago ta kamo hannun mama  tace dashi,     "Wannan itace mamata wadda ta nuna man so fiye da yanda uwa take nunawa d'anta, bansan zafin  rashin uwa ba saboda ni tawa uwar mai adalci ce, bata barina a cikin damuwa balle inyi kuka"

Tana cikin maganar ta hango malam da mai unguwa daga cen baya a tsaye da kanta tayi tattaki taje har wurin su malam ta rik'o hannun shi tace,

"Taho baya goya marainiyar Allah izzatu, kaine ka hanani inyi kukan maraici, bansan zafin rashin uba ba saboda ka tare dama ka tare hagu na ta kowane b'angare,  yanda bazan gano ba kaine ka haifeni ba nagode babana."

Ta koma ta rik'o hannun Garzali tace,

"YAYA GARZANA!, kaine abokina kaine yayana wanda rayuwata bazata kammala ba matuk'ar idan ba da kai ba."

Ta saki Garza ta nufi wurin mai unguwa har k'asa ta durk'usa tace,

"Madallah da samun shugaba irinka mai adalci wanda yasan miye shugabanci, Allah ya saka maka da gidan aljannah."

Mai girma Gwamna ganin izzatu kamar ta zauce yace dasu Malam su shiga mota gaba d'ayansu su isa gidan Gwamnati,  domin akwai buk'atar keb'antuwar su sannan gashi  wannan wurin ba wurin tattauna magana bane, aiko wani sanyin dad'i ya kwaranyo a cikin zukatansu, koda akazo neman iya kulu ta ko ina ba'a ganta ba lungu da sak'o an duba,  sai gashi koda Garzali yaje wani aji sai kawai ya hangota a makure sai rawar sanyi takeyi, yaso yayi dariya amma ya dake yace da ita,        "Lafiya iya na ganki a nan?,gamu cen mun had'u gaba d'ayanmu zamuje gidan Gwamna, akayi ta nemanki ba'a ganki ba  kin tada muna hankali sosai sai bid'arki mukeyi."

Iya ta gwalalo ido a waje tace,  "ka bari don manzo Wake nema don Allah?."

Garzali ya dake yace,   "nidai taso muje ke, kawai ake jira, kada mu b'ata masu lokaci."

Iya kulu ta fara turje turjen ita ba inda zata har sai da ta hango zuwan malam tareda wani d'an sanda, sannan ta tashi a zabure tana neman hanyar tsira, ga wani sabon zawo da yake ta barazanar fito mata ba shiri, isowar malam da d'an sandan ya k'ara mata ninkin tashin hankalin

da take a ciki, Garzali ya rik'o hannunta yace,     "zo muje iyata ba abunda za'a yimaki."

Sannan Garzali ya sami sa'ar fito da ita a cikin class d'in, yana rik'e da ita har sukaje wurin motar da suka zo da ita,  yayin da izzatu hajiya fatima ta manne akan dole a cikin motarsu zata je, dole ba don taso ba tabi ta suka shiga wata luntsumemiyar mota, wadda baka tantance shin gudu akeyi ko yaya?, Hadizatou dai sai kallon IZZATU take yi sai jinjina hikimar ALLAH takeyi, wanda ya k'agi halittarta dai dai da ta izzatu sak d'an banbancin kad'an ne, wanda shima har sai anyi dak'yar ake tantancewa, motar su malam wata motar 'yansanda ne take bayansu, iya kulu da ta juya baya ta hango su sai ta fara salatin da bata iyarwa take kamo wani, sabida ta tsure iya tsurewa don ganin takeyi tamkar izzatu ta fad'awa iyayenta abunda take yimata.

A guje jerin motocin suke tafiya tareda tashin jiniyoyi ta ko ina, da angansu tafe mutanen dake kan titin sai darewa sukeyi suna sauka a k'asa da abun hawansu suna kai  gaisuwa, har  suka kai k'aton katafaren gidan Gwamnati, a hankali motocin suke tsayawa d'aya bayan d'aya har ta su malam ma, sanan kowa ya fiffito suka nufi wani k'aton falo na alfarma, Mai girma Gwamna ya bada umurnin aje dasu malam ayi masu sauka ta bajinta,  kafin ya samu natsuwar zama su tattauna, aiko malam da Garza, mai unguwa da direban da suka zo dashi aka kaisu wani keb'antaccen wuri sai hidima dasu akeyi, malam da mai unguwa sai fira sukeyi suna k'ara jinjinawa wannan hikima ta ubangiji, Garzali kuwa jinshi yakeyi a cikin farin cikin da bai tab'a tsintar kansa a ciki ba, musamman in ya tuno izzatunsa ce keda wannan ni'ima da baiwar sai hamdala yake yi a zuciyar shi.

Su mama hassatu kuwa suma muhalli na daban aka ajiyesu, sannan aka fara jejjera masu kalolin abincin da ko mama hassatu bata san dasu balle iya da IZZATU, don hajiya fatima taso taje da izzatu sashenta amma IZZATU ta lik'ewa mama hassatu tace ba mai rabata da mamarta, amman duk da hakanan hajiya fatima bata hak'ura ba har sai da ta karb'i ilham taje da ita kafin su k'are kimtsawa.

Iya kulu sai faman rabon idanuwa kawai takeyi tamkar ace kyat! ta arce da gudu, amman tana ganin anbar su su kad'ai ta fad'i k'asa ta rik'o k'afar izzatu kamar zata yimata sujada tace,
"Ranki shi dad'e don Allah kiyi man rai ki barni in k'arasa kingin tsufana batareda nayi zaman kurkuku ba, wallahi nayi nadamar abunda nayi maki a baya ranki ya dad'e, na amince zan zamo baiwa a gareki har izuwa k'arshen rayuwa ta, ki kalli tsufana kar ki bari babanki ya kaini gidan yari"

Izzatu tayi murmushi mai d'auke da ma'anoni ta saka hannu ta d'ago iya kulu ta zaunar da ita akan kujera ita ta sauko a k'asa tareda dafa k'afafunta tace,

Har abada ba'a tab'a canzawa tuwo suna shi, nice ya dace in durk'usa maki iya ba ke ba, saboda mamata ta dad'e da koyaman yanda zan girmama na gaba da ni, don haka bana fatar ko wani in rena ballantana ke iya, ki kwantar da hankalinki indai ni izzatu jinin YAHAYA BADAWI ce to tabbas ba wanda ya isa yayi maki kallon reni ma balle takai ga zuwa kurkuku, ai ko a lahira wani  yana cin albarkacin wani, to ke ki d'auka kinci albarkacin mutane hud'u masu

muhimmanci a rayuwa ta, DADA, MALAM, YAYA GARZANAH!, sai albarkacin zaman gida d'aya da kikeyi da MAMATAH!, don haka ki cire tsoron komi a zuciyar ki saboda muddin nace zan d'auki fansa a kanki to tamkar nayi ihu ne na lumawa kaina wuk'a, ai girman halaccin da aka yiman kawai ya isa ya fanshe duk wani laifi da kika yiman, har gobe nice izzatun da kika sani sai dai yanzu mai cikakken asali ce gaba da bayanta, ba shegiya ko 'yar tsintuwa ba"

Iya kulu ta fashe da kuka tace,    "tabbas na gano maganar ki hassatu yau ga gaskiya tayi halinta,  d'an hakin da ka rena watarana shi yake tsole maka ido, ina ma ace Dada kina raye kiga wannan magana da kika tab'a cewa, duk inda izzatu ta fito tafi k'arfin matsayina da na kande, oni 'yar kuluwa ALLAH ya jik'an ki Dada."

Mama hassatu ta yiwa iya kulu wani kallo tace,     "Yau dai gaki a gidan su izzatu kinga tushenta kinga asalinta, kuma kinga karamci irin na babban gida,  ya zama izna a gareki ki gyara munanan halayenki,  ki tuba ki komawa ALLAH ki gyara abunda kika b'ata a baya ko don ki ribaci sauran kwanakin rayuwarki da suka rage."

Iya kulu ta fashe da kukan nadama, daga nan mama da izzatu suka baje sai jan girki sukeyi suna firar su, iya kulu ta kallesu taga yanda suke ta cisgar naman kaji sai had'iyar miyau takeyi, ba shiri ta kurma wani kuka da sauri suka kalleta, izzatu tace da ita,        "Lafiya iya?me aka yimaki kuma a yanzu?."

Iya ta fara murzar idanuwa kamar wata k'aramar yarinya tace,

"NI sai naga kamar baki yafe man ba."

Izzatu tayi murmushi tace,       "Na yafe maki iya amma me yasa kike ganin haka."

Iya tana matsar hawaye tace,      "Naga sai cin namanku kukeyi ni baku ce inzo muci ba."

Izzatu tana dariya tace,    "ALLAH SARKI iya yi hak'uri zo muci kinji,  duk abunda kike son ci kici abunki kawai  ba mai hana ki ko in zubo maki ne.?"

Iya kulu tayi saurin girgiza kai tareda kiran,          "A'a barni in yagi rabona kawai, don nasan idan na koma wancen garin  shi kenan wannan gara zata barni, nikam dama malam zai bari da kun d'auke ni aiki a gidannan koda wankin bayi ne inaso wallahi zan iya."

Mama hassatu dai abincinta kawai take ci,  tayi kamar bata ji shiriritar da iyar take yi ba, bayan sun k'are cin abincin ne suka je sukayi wanka, kayan da aka kawo masu sababbi suka saka, iya kallon kanta takeyi kamar ba ita ba tana dubin kanta a madubi tace,      "ashe wallahi da kingin kurciyata har yanzu, ALLAH sarki izzatu ashe kece alkhairinmu arzik'i yana biyata ina gudu, ashe ashe ni mai k'ashin arzik'i ce."

Hajiya fatima tazo da ilham itama tasha wanka an saka mata y'ar kanti tayi kyau gwanin sha'awa, tace dasu idan sun shirya su zo kowa ya hallara su kawai ake jira, aiko suka fito aka yi masu jagora har babban falon da za'a gudanar da tattaunawar, koda suka je sun tarar da falon a cike fam da mutane maza da mata, cen na hango su malam da mai unguwa ansha manyan riguna sai wani annuri ke fita a fuskokinsu, Garzali kam ni banma gane shi ba har sai da na k'ura idanuwa, saboda yasha wata arniyar shadda da hula kayan sun karb'i jikin shi sosai.

Bayan sun samu wurin zama sun zauna ne aka umurci izzatu akan ta fito a tsakiyar falon, a cikin natsuwa ta fito kanta a sunne tana jin wani farin ciki yana ratsa bargon jikinta, ta d'ago fuskarta tana kallon mutanen dake a cike da falon d'aya bayan d'aya, har idanuwanta sukayi zagayo sukayi caraf da fuskar shu'aib, wanda shima ya kur'e kallonshi a kyakkyawar fuskarta fuskar shi a cike fam da d'inbin mamaki.

Ko ya wannan taro zai gudana?don ga dukkan alamu a cikin shi ne za'a fashe k'wan da ya shekara goma sha tara yana dunge🙀🤔ku biyoni domin mu warware wannan badak'alar a tare daku🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️.

Akafta💃

D/Auta ce🤪
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*PAGE FORTY TWO*

**********************

Izzatu tayi masa wani kallo mai cike da reni sannan ta kawar da idanuwanta akan shi,  acikin ko in kula tamkar bata gane ko wanene shi ba, taci gaba da kallon mutanen dake cike da falon, amma a cikin zuciyarta sai tambayar kanta takeyi shin meye alak'arta da shu'aib,  domin tana jin tsoron ace sun had'a uba d'aya sabida ta riga taci alwashin ko wanene shi sai ta rama wulak'ancin da yayi mata, tunaninta ya katse ne a dai dai lokacin da taji wani dattijo ya kira sunan ta, da sauri takai kallonta a kanshi.

Yayi mata murmushi yace da ita,     "Alhmdllh mungode wa Allah da ya kawo mu wannan rana ya dawo muna dake a hannunmu, bayan tsawon lokacin da muka shafe muna neman ki, sai gashi kwatsam ALLAH ya dawo muna dake a cikin ruwan sanyi batareda munsha wahala ba, Alhmdllh mun godewa Allah dukkan wanda kika gani acikin wannan waje idan kin cire bak'in da suke tare dake sai kallah da ya kasance amintaccenmu, to kafatanin mu duk jini d'aya ne mu kuma kema 'yan uwane a wurinki ta b'angarora mabanbanta, dukan mu mun fito ne daga tsatson ALHAJI YUSUF BADAWI, a madadin wannan family gabaki d'ayan mu muna yi maki barka da dawowa a cikin iyayenki da yayyunki da k'annenki da 'yan uwanki duka."

Izzatu ta fad'ad'a fuskarta da wani murmushi wanda ya k'ara k'awata kyakkyawar fuskarta, a cikin tsantsar farinciki tace,    "Nima na godewa ALLAH da ya dawo dani a cikin ahalina."

Ta k'are maganar tareda kai kallonta akan fuskar shu'aib tareda dalla masa wata gwarzuwar harara, wanda a lokaci d'aya gumi ya karye masa ga dukkan k'ofofin gashin dake jikin shi, ba shiri jikinshi ya d'auki rawa hankalin shi yayi kololuwar tashi, saboda yanzu ne ya tabbatar da zargin da yake yi, waton dai wannan y'ar k'auyen yarinyar itace 'yar da hadizatou ta haifa wadda ake cewa ta b'ata, shin to ta yaya taje k'auyen d'anlasau tayi rayuwa acen?.

Wannann dattijon ya fara magana kamar haka,

"Jama'a wannan yarinya da kuke gani itace 'yar da hadizatou ta haifa wadda aka sace a satin haihuwarta, wadda  hud'ubar suna kawai aka yimata ba tareda anyi taron sunan ba."

Gaba d'aya falon aka d'auki kabbara,sai murna akeyi yara da manya sai farincikin ganin izzatu sukeyi suna jinjina wannan hikima ta ubangiji, bayan surutan sun d'an lafane dattijon ya k'ara cewa,   "A yanzu haka muna tareda bayin Allah'n da suka tsinceta suka yimata rik'o na amana tamkar 'yar da suka haifa tun tana k'arama har izuwa girmanta, bari mu kira d'aya daga cikin wad'anan mutane wanda asali ma shine ya tsinceta domin muji ta bakin shi."

Gaba d'aya falon yayi tsit, malam ya fito a cikin natsuwa ya fara kai gaisuwa a wurin mai girma Gwamna, sannan d'aya bayan d'aya yayi masu tiryan tiryan tun daga ranar da ya tsinceta ya

dawo daga gona har izuwa wannan rana da suke a cikinta.

Jikin kowa yayi sanyi musamman mai girma gwamna,  da hajiya fatima da hadizatou da baba kallah da shu'aib, kowanensu da abunda yake sak'awa a cikin ranshi, ba shiri hadizatou ta fashe da kuka yayin da hajiya fatima tashin hankalinta ya karu itama ta fashe da wani jarumin kuka,  baba kallah ma sai matsar hawaye yakeyi.

Hajiya fatima ta tashi k'yam ta tsaya a gaban taron jikinta yana rawa, tana wani irin kuka mai tsuma zuciyar mai sauraro ta fara yin sallama ga daukacin mutanen dake falon, wani kukan yaci karfinta ta durk'ushe sai gunjin kuka takeyi a cikin tashin hankali.

Mai girma gwamna ya kalleta da kyau wani tunani ya zowa zuciyar shi da sauri ya bada umurnin a watse taron amma yana son ya gana da su malam da wannan dattijon da matanshi, aiko a hankali mutane suka dinga fita bayan sun yiwa su malam godiya.

Falon ya rage daga mai girma Gwamna sai matanshi da wannan dattijon sai shu'aib da kallah sai su malam, mai girma ya kalli su malam  gwana yayi gyaran murya yace,   "Ina wa Allah godiya da ya dawo man da 'yata hannuna, sannan ina mik'a d'inbin godiyata a gareku wadda bata misaltuwa, hak'ik'a ku mutane wad'anda ya kamata a jinjina maku,  saboda samun irunku a wannan marra sai anyi bincike, hak'ik'a wannan yarinya da kuke gani duk da banyi wani dogon zama atare da ita ba, amman bantab'a jin son wani d'a da na haifa ba a sama da ita, saboda haka ni ALHAJI YAHAYA BADAWI na raba dukiyata biyu na baiwa 'yata NANA AISHA wadda kuka first sani da suna IZZATU rabi, domin ta taimaki duk wani wanda takeso musamman ku da kuka zama iyaye a wurinta, don na fison ace itace zata yi maku hidima da hannunta  ba ni ba, don nasan ta fini sanin irin abubuwan alkhairin da kuka yimata, nagode nagode nagode da taimakon da kuka yimuna."

Gaba d'aya falon ya rikice da addu'o'i godiya ga mai girma Gwamna, dukansu babu wanda baiji dad'in wannan kyauta da akayiwa izzatu ba, sai mutum biyu da cikinsu ya kad'a wato wannan dattijo da shu'aib, iya kulu kam zaman 'yan bori tayi tana kallon IZZATU kamar bata tab'a ganinta ba, ta d'aga kai ta kalli rufin falon da shi kanshi yasha kayan k'arau, a cikin zuciyarta tace,    "Annabi mai darajja"

Kuyi hkr kuyi manage banida caji🤦🏻‍♀️.

Akafta😜

D/Auta ce😍

"Na fahimci akwai wata b'oyayyiyar maganar da kike so ki bayyana muna amma kafin nan ina son in fara bayyanawa wad'annan bayin Allah masu "
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*PAGE FORTY THREE*

*********************

Malam yayi gyaran murya yace,    "Ranka shi dad'e muna son musan shin ta yaya izzatu ta b'ata daga hannunku, har muka tsinceta a garinmu?,  shin kuna da wani abokin adawa ne wanda kuke zaton shine yayi wannan aikin ko kuwa?, domin mu abunda ya daure muna kai shine kud'in da aka tarar tareda izzatu a cikin kwali, sannan wasik'ar da aka rubuta akace ba shegiya bace, shin me hakan yake nufi?, muna son a warware muna abunda ya shige muna duhu shekara da shekarr.. ."

Kukan hajiya fatima ne ya katsewa malam iyar da maganar shi, mai girma Gwamna ya kalleta anan take wata damuwa ta mamaye zuciyar shi acikin sanyin jiki ya fara magana kamar haka,

"Kamar yanda kuka sani sunana Alhaji yahaya badawi d'a a wurin Alhaji yusuf badawi, mahaifinmu attajiri ne na gaske ya rasu ya bar muna dukiya dai dai gwargwado, mu 'ya'ya

ashirin da hud'u ne a wurin shi, wanda ni kad'ai ne na kasance uwa daban a cikinsu, amman sauran duk suna da abokan haihuwa a d'akinsu, mahaifiyata bafullatanar daji ce, ta rasu bayan rasuwar mahaifinmu da shekara biyu, kasancewar tayi gadon shanu da gonaki masu yawa a wurin mahaifinta, wanda kafin mahaifin ya rasu kaf dukiyar a hannunshi take yana juuya mata, bayan rasuwar shi ne ragamar komi ta dawo a hannuna sai gashi itama Allah yayi mata rasuwa, shine na gadi wannan d'inbin dukiyar da ta bari gaba d'aya, kasancewar ni kad'ai ne d'an da ta haifa a duniya, kuma a lokacin duk iyayenta sun rasu.

Bansha wata wahala ba a wajen ci gaba da kula da dukiyata, saboda tun kafin mahaifinmu ya rasu ya azani akan hanyar da zan juya kwabo ya koma sisi, to shine bayan rasuwarshi wani abokinshi wanda yake shahararren malamine a garinnan, shi ya rik'e ni d'a ya dinga d'ora ni akan hanyoyin da zan k'ara fad'ad'a kasuwanci na, akwai kyakkyawar alak'a sosai a tsakanimmu da shi, shiyasa da na nuna ina son 'yarshi bintu ba musu ya amince man na aureta."

Munyi auren soyayya a tsakanina da hajiya fatima wadda ni nake kiranta da suna BINTU, bintu mace ce mai natsuwa da hankali tareda zurfin tunani, sannan uwa uba ga ilimin addini da take dashi, wad'anan halaye nata sune suka k'ara jawo mata matsayi da girma a wurina, wanda har gobe bintu ta musamman ce a wurina, kasancewarta mace mai kawaici da hak'uri,

Mun d'auki tsawon lokaci ALLAH bai bamu haihuwa ba, a kullum damuwar bintu bai wuce ALLAH ya bata haihuwa ba, saboda mace ce mai tsananin son yara da kyautata masu, shiyasa aduk inda yaro yake ba zaka raba bintu dashi ba,

A zahirin gaskiya ni a lokacin haihuwar ba wani damuna tayi ba, saboda nafi baiwa neman kud'ina muhimmanci akan rashin haihuwar da bamuyi ba, amman ganin yanda ta damu sosai akan rashin haihuwar, shi yasa na d'auke ta mukayi ta zagaya asibitoci akan agano menene matsalar mu nida ita?,

Duk asibitin da mukaje aka auna sai ace muna lafiya kalau muke, kawai dai lokacin haihuwar ne namu baiyi ba,daga nan har k'asashen k'etare mun zagaya a ko'ina maganar ce d'aya ake fad'a muna, amman hajiya fatima ta d'aga hankalinta sosai akan rashin haihuwar,

A lokacin ne 'yan uwana suka sako ni agaba akan in k'ara aure koda zan ga k'wai na a duniya, na nuna masu ni soyayyar da nike yiwa bintu tafi k'arfin inyi mata kishiya don bata haihuwa, photunan mata kala kala ake aiko man akan in zab'i wadda nike so, amma ba wadda na yiwa kallon secon d'aya ma bale inzab'a, nayi biris da kowa na rik'e matata ina k'ara kwantar mata da hankali, domin a lokacin bani da gurin k'arin aure a zuciyata, ita da kanta ta bani shawara akan in k'ara auren koda za'a gano mai matsala a tsakaninmu, amman na bijire sai dai na kwantar mata da hankali da dabara har in sami kanta,

Kwatsam sai gashi wata hark'allar kasuwanci ta kaini Niger, a cen naga

hadizatou kasacewarta k'anwa a wurin wani abokin kasuwancina, wanda shine  yake rik'onta a gidanshi, tunda na k'yalla idanuwa na akanta naji a duniya kaf ba wata 'ya macen da nike so tamkarta, cikin ikon ALLAH itama nayi mata, atakaice dai ban baro Niger ba har sai da aka d'aura man aure da hadizatou, sannan na dawo gida Nigeria da Amaryata, na kaita wani sabon gidana da aka kammala  ginawa a lokacin da nufin mu dawo a nan nida bintu,

Koda na dawo ban gayawa bintu nayi aure ba, saboda ina jin nauyin yanda zan fuskanceta da wannan magana, ina jin kunyar idanunta sosai akan in fad'a mata wai nayi aure har nazo da matar ta tare a gidanmu sabo da na gina domin mu shinfid'a sabuwar rayuwa nida bintu da yaran da ALLAH zai bamu a nan gaba."

🤔🤔🤔🤔Tofa

Manage plss

Akafta😍

D/Auta ce😒
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*Alhmdllh ina jin dad'in yanda kuke bibiyar book dina masoyana da masoya LITTAFIN RUWA da KANKARA aduk inda kuke Alkhairin ALLAH yakai maku ku sani D/AUTA tana yinku over wallah Allah ya bar kauna a tsakanina daku sai dai ince Alhmdllh sabida kuna sani farin ciki ba kadan ba nagode da zunduma zunduman addu'o'in ku a gareni dukan ku i love you all💋💋💋💋❤️❤️🤝🏻*

*PAGE FORTY FIVE*

*********************

Hajiya fatima ta fashe da kuka mai sauti tace, "Tabbas ina da hannu dumu dumu a bacewar 'yarmu izzatu, saboda a lokacin juyin bayan da kayi man, ka nuna rashin adalci fili a tsakanina da hadizatou, shiyasa zuciya ta d'ebeni nayi wannan aika aikar, da ta dawo ta dameni fiye da yanda ku naso zku shiga damuwa, domin a lokacin nayi tunanin ta wace hanya ce ya dace in k'unsa maku bak'in ciki fiye da abunda kuka yiman, nayi tunani kaf ban hango komi ba sai in raba ku da 'yarku, wadda nasan rashinta a gurinku tabbas zai tab'a zuciyarku sosai, to shiyasa kawai zuciyata ta tsayu akan wannan abun kunyar da na aikata.

A ranar da naji ance hadizatou ta haifu na shiga tashin hankali ba kad'an ba, domin a lokacin hauka ce kawai banyi ba, amman a tsaye nike tamkar wata tab'abba, sabida zuciyata ta amince man akan cewa tabbas hadizatou ta k'ara yi man fintinkau a wurinka, don na tabbata duk abunda zaisa ka juyan baya a lokaci d'aya wannan ba k'aramin abu bane, tabbas ansan so gaskiya ne amman nima tunda auren soyayya mukayi, bai dace kayi man wannan tozarci ba, a ganina koda auren had'i ne aka yimuna don ka auro wadda kake so baza k'i kwatanta adalci a tsakaninmu ba, shiyasa kawai a lokacin zuciyata ta bushe, neman hanyar da d'aukar fansa nikeyi ido a rufe, hankalina bai dawo a jikina ba har sai da na tabbar na raba ku da wannan 'ya da kuke gadara da ita,hakan ta kasancene a ranar da ta cika kwana hud'u a duniya, bayan nayi ta k'ulla k'ulla ta har na sami nasara, na had'a kai da wata 'yar aikin hadizatou mai suna larai, wadda nasa kallah ya hilato mana ita har gidana, kai tsaye na nuna mata ga abunda nikeso tayi man akan farashi mai tsoka, duk da taji tsoro amman ganin mak'udan kud'in da na ajiye mata idanunta suka rufe, jikinta ya d'auki rawa tace abata kwana biyu domin a lokacin kwana biyu da haihuwar, akan zata je ta gano ta wace hanya ce mafi sauk'i da zata saci 'yar ba tareda angane itace tayi wannan aikin ba.

A ranar da zata sace 'yar sai da ta kirani a waya tace in turo kallah ya tsaya a kusa da gidan, da ta sami sa'ar d'auko 'yar zata bashi sai ta bashi ita yayi saurin barin unguwar, haka ko akayi na tura kallah yaje sai gashi ya dawo man da yarinya a cikin towel d'inta sai wutsil wutsil d'in jarinta

takeyi, ganin yarinyar da nayi a nan take naji ina k'aunarta sosai, na rungumeta a jikina ina jin wani shauk'in kaunarta yana fisgata, domin a lokacin da ace hadizatou zata barman ita kyauta, to da tabbas ba abunda zaisa in nesanta ta da mu, amman tunda nasan hakan ba zata samu ba na yanke shawarar in bada wani tallafi ga duk wanda yayi sa'ar tsintar ta, na samo k'aton kwali na jera kud'i masu yawa a k'asan kwalin sannan na yago takarda na rubuta cewa, yar sunnanh ce ba shegiya ba duk wanda ya tsinceta yayi mata hidima da wad'anan kud'in, sannan NA saka a k'asan kud'in na shimfid'a towel d'in na kwantar da ita, sai da nayi mata kiss sannan na mik'awa kallah ita nace yaje nesa da garinnan ya ajiyeta ya dawo,ya karb'a ya fita duk da na hango rashin jin dad'in wannan aiki da na saka shi a fuskar shi, amman sanin wanene kallah a wurina yasa banji ko d'ar ba,  koda yaje ya dawo ne yake sanar dani ya gama aikin, a cikin farin ciki na d'auko kud'in shi shima na bashi, ammam yace dani in barsu shi baya buk'ata a dole na tilasta masa sai da ya karb'a ya fita b'acin rai kwance akan fuskarshi.

Bayan 'yan mintuna da kammaluwar komi sai gashi labari ya fara watsuwa a ko'ina akan an sace jaririya, hankalina akwance nayita yiwa kowa kallon wawaye, domin sanin da nayi nice silar b'acewar 'yar domin a lokacin bana jin rashin kyautawar da nayi, a ganina hakan da nayi ma shine daidai shiyasa nike ta jina a cikin wani tsantsar farinciki.

Damuwa ta fara shigata ne a lokacin da maigidana ya dawo gareni, yana rok'ona akan inyi hak'uri in yafe masa duk abunda yayi mani, ya d'auko ni muka dawo gidan da ya aje hadizatou, a hankali na fahimci yarinyar tana da kirki sosai da girmama na gaba da ita, amman naji haushinta sosai akan kasa fahimtar da maigidanmu da tayi,  a lokacin da ya watsar dani meyasa bata lurar dashi abunda ya dace ba, to sannu a hankali dai na ajiye komi na kwantar da hankali muka ci gaba da zanmu lafiya har ta sami wani cikin.

Tashin hankalina ya fara ne a ranar da aka tabbatar man ina da ciki, naji farinciki ba kad'an ba shima kanshi yaji dad'in ganin nima ashe ina haifuwa, a daren ranar nayi mafalkin wannan jaririyar tana ta kuka, a firgice na falka a cikin jin tsoron abunda na aikata, wasa wasa cikina yana da wata uku nayi wani mafalki, wai ga yarinyar nan ina gudu tana ta biyata har naci tuntub'e na fad'i akan cikin, ina falkawa a firgice na ganni a cikin jini duk iya kokarin likitoci akan kada cikin ya zube bai tsaya ba, nazo na kara samun wani cikin naci gaba da wad'annan mafalkai da yarinyar har ranar da nazo haifuwa shima nayi mafalki da ita wai na haifu ta cakawa yaron wuk'a, aiko ta kasance na haifo yaron ba rai, nashiga tashin hankali matuk'a, domin a duk lokacin da na sami cikin hakan take kasanceawa dani har sau hud'u, to daga lokacin ne haifuwar ta tsaya cak!, nima a lokacin ne na auri damuwa a cikin zuciyata, wadda har tayi sanadin kwanciyata a asibiti, domin a lokacin bana sati da lafiya a kullum muna hanyar asibiti har aka tabbatar man inada hawan jini.

Ganin yanda nike shiga damuwa ne kalla yazo muna fira ne yake sanar dani yasan fa inda yarinyar nan take, gabana ya fad'i duk da naji farincikin jin wannan labari, yayiman bayanin komi daga yarinyar, na saka shi aikin zuwa k'auyen a kullum domin ya ganar man halin da take a ciki, har zuwa lokacin da ta fara zuwa makarantar garinnan, nice nace ya dinga zuwa daukarta ya kaita makaranta, bayan na had'a mata abinci na bashi ya kaimata, kud'in makaranta ma nice

nake baiwa kallah  yana biya mata a b'oye, ko wanann makarantar da take a ciki nice na d'auki nauyin biya mata kud'in ina lab'awa akan cewa Abbaah ne yake biya a matsayinshi na d'an takarar kujerar Gwamna a lokacin, sannan ni na d'auki nauyin bud'a b'angaren karatun islamiya a makarantar domin izzatu kawai,  saboda kallah ya fad'a mani cewa tana zuwa ta allo a cen k'auyen, shiyasa nayi tunanin k'ara fad'ad'a mata ilimin ko don in rage zunubin rabata da iyayenta  da nayi, a ranar da zasu k'are ma ni na tilastawa Abbaah zuwa da kanshi a taron bikin k'arewar, domin yaso ya aika wakili shi ba sai yaje ba, sannan na hilace hadizatou akan muje taron nida ita, saboda kawai ina son suga 'yarsu in sauke wannan nauyi da na azawa kaina, sai gashi anci nasara aikin ya tafi daidai da yanda mukayi fata nida d'an uwana kallah, to kunji abunda yake nukurkusar zuciyata shekara da shekaru."

Gabaki d'aya falon yayi tsiy kowa da abunda yake sak'awa, sai jin sukayi baba kallah yace,, "Assalamu Alaikum nima ina son in k'ara warware maku duk abunda ya shige maku a duhu, da farko dai ni sunana musa wanda mutane da dama suke kirana da sunan KALLAH, hajiya fatima 'yar uwata ce ta jini  asalima a gidansu na taso hannun mahaifiyarta, kasancewar da mahaifiyata da tata uwa d'aya uba d'aya, mahaifiyata ta rasu ta barni a hannun mahaifiyar bintu, mun taso a tare nida ita domin kusan shekarunmu d'aya, akwai shak'uwa sosai a tsakaninmu, shiyasa maigdanta ya jawo ni a jikinshi na zama tamkar yaron shi, ko  lokacin da ya k'ara aure da damuwar da hajiya fatima ta shiga, ni nake kwantar mata da hankali, a lokacin da ma ta gayaman zatayi wannan aika aikar na nusar da ita sosai, amman ta nuna man ba hurumina bane idan naji bana iyawa ta samo wani, nayi tunanin muddin ta yarda wani yasan wannan sirrin,  to tabbas asirinta bazai tab'a rufuwa ba, domin yanzu ba kowa bane yake da amana watak'ila ta wannan sanadi aurenta ya lalace, domin kuwa za'a iya amfani da wannan dama domin a wargaza farincikinmu gaba d'aya, shiyasa na amince nayi wannan aikin amman wallahi bada son zuciyata ba, shiyasa da naje na ajiye yarinyar na lab'e a jikin wata bishiya ina kallo har wannan dattijon yazo da kekenshi ya ganta ya dauketa, na biyo bayanshi har sai da naga gidanshi, Allah yasa ba mutane a lokacin kowa ya shige saboda ruwan saman da ake ta tafkawa a ranar, tun daga lokacin nike shigar mahaukaci in shiga k'auyen domin in ga halin da wannan yarinya take a ciki, Alhmdllh wannan 'yar tsohuwa ALLAH ya saka mata da alkhairi, domin tayiwa izzatu rik'on gaskiya da amana, saboda duk abunda yake faruwa a gidan ina sane kuma ina jin labari duk da ban tab'a shiga gidan ba har sai da ta rasu naje gaisuwa, na daina shigar mahaukata ne aranar da naga wannan yaron Garzali yaso ya gano ni ba mahaukacin gaskiya bane, amman ina shiga da sifa ta ta gaskiya ina rangadi a cikin k'auyen, har izuwa lokacin da izzatun ta girma nabi hanyoyi na  kusanta kaina a gareta, Alhmdllh yanzu tunda har komi ya bayyana fatanmu kawai ALLAH ya yafe muna zunubin da muka d'auka."

Ba shiri baba KALLAH ya fashe da kuka, itama kanta hajiya fatimar kukan takeyi,yayinda cikin iya kullu ya fara k'ugi saboda jin da tayi baba KALLAH yasan duk abunda ke faruwa a gidan, a nan take wani jib'i ya karye mata sai saka gefen zanenta takeyi tana sharcewa, saboda tashin hankalin kada kallah ya bayyana irin cin zalin da tasha yiwa izzatu.

Bayan ya k'are maganar ne ya zauna mai girma Gwamna yayi gtaran murya yace,       "A zahirin gaskiya babu wanda yayi sanadin faruwar  wannan badak'alar sai ni YAHAYA, ALLAH na tuba

Ubangiji ya yafe mu gaba d'aya, daga ni har ke bintu har kallah dukanmu ALLAH ya yafe muna."

Hajiya fatima taje ta kama hannun hadizatou tana rokonta akan ta yafe mata, hadizatou tace, "Ba komi nima ki yafeman a sanadina mijinki ya juya maki baya, duk da ba nice na saka shi ba, amman nima inada laifi tunda ban d'ora shi akan hanyar da ya dace ba."

Daga nan suka rungume juna suna kuka, wannan dattijon yayan Gwamna da tunda aka fara maganganun baice k'anzil ba saboda suman zaunen da yayi tun lokacin da yaji an baiwa izzatu rabin dukiya, ba shiri yayi gyaran murya yace,

"Alhmdllh tunda komi ya bayyana ALLAH ya yafe mu gaba d'aya, a madadina na wakilin izzatu wanda nine zan zama mad'aurin aure a wurin 'yata izzatu, na bada aurenta ga yarona shu'aib, tuwo na maina sai fatar kawai Allah ya had'a kawunansu, izzatu na zab'a maki miji d'an uwanki shu'aib, shu'aib na zab'a maka mata 'yar uwarka izzatu, na baku lokaci kuje ku had'a kawunanku ALLAH ya kaimu lokacin kuma ya k'ara had'a muna kan zumuncinmu."

Yasin Akwai kurah🙀🙀🙀🙀🙀🙀

Akafta🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️

D/Auta ce⛹🏻‍♀️
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*Yawan comment's yawan typing😔*

*PAGE FORTY FOUR*

**********************

Sai da hadizatou tayi wata uku a gidana sannan bintu ta sami labari a bakin mutane, wai nayi aure matar tana gidanmu sabo harda cikinta.

Kwatsam a watarana ina gidana sabo wurin hadizatou sai ga hajiya bintu tazo ta kamani dumu dumu da hadizatou, muna wasar mu ta ma'aurata ba shiri ta fad'i k'asa ta sume, hankalina ya tashi sosai saboda nayi danasanin rashin fad'a mata da banyi ba tun a farko, da duk hakan bata faru ba saboda bintu mai ilimi ce da fahimta zata fahimceni, niko a wurina kunyar yanda zan kalli tsabar idanunta in fad'i wannan magana nikeji,

Hankali na a tashe na kwashe ta sai asibiti, bayan ta farfad'o ne ta fara kuka tana cewa sai na rabu da ita, tunda naci amanarta bazata sake zama dani ba, hankalina ya tashi naje na fad'owa mahaifinta, don ina son matata bana son rabuwa da ita, Baba mallam shine ya dinga yiwa bintu nasihohi tareda kawo mata misalai kala, akan tayi hkr ta zauna dani ta yafe man abunda nayi mata.

Kasancewar bintu mai biyayya ce shiyasa bata yi jayayya ba dana bata hakuri ta amince muka koma zaman lafiyarmu, amman a kullum naje gidan zan isketa a cikin tsananin damuwa,

A kullum idan na tashi tafiye tafiye na, wajen huld'ar kasuwancina da hadizatou nike zuwa duk da yaron cikin da take d'auke dashi, don bana son abunda zai raba ni da ita ko da na kwana d'aya ne, don a lokacin kacokam tarewa nayi a gidanta, sai inyi kwana biyu uku ban lek'a gidan bintu ba balle insan halin da take a ciki, nidai a koda yaushe damuwata hadizatou da abinda yake cikinta.

Da abu yayi tsamari ma in akayi dace naje gidan, to zan fada mata tafiya zanyi sai inyi

kwanciyata a gidan hadizatou muna tattalin cikin da Allah ya bamu, sai na daidaici lokacin da nace zan dawo sai in je gidan bintu a zuwan na dawo daga tafiyar.

Muna cikin wannan hali ne har cikin hadizatou ya isa haihuwa, wanda ni a lokacin banida wani guri da wuce naga abunda hadizatou zata haifar man.

Da lokacin haihuwar yayi a cikin ikon ALLAH,  ta haifo man 'yata masha Allah mai kama da ita sak,bazan iya misalta farin cikin da na shiga ba a daliin samun wannan yarinya da nayi, nayi mata hud'uba da sunan mahaifiyata waton NANA AISHA.

'Yan uwa da abokan arzik'i sai murna suke taya ni, akan wannan haihuwar da hadizatou tayi man, kwana hud'u da haihuwa muka shiga a cikin tashin hankalin da a rayuwa ta kaf inbanda rashin iyaye da nayi, ban tab'a shiga irin shi ba, wannan tashin hankalin ba komi bane illah, b'acewar da jaririyar 'yata tayi, yarinyar da nike jin a lokacin babu wani abun halitta da nike so sama da ita.

Gidan Radio gidan television jaridu babu inda bamu je ba wajen cigiyar wannan yarinya amma shiru kamar an shuka dusa,na saka malammai sunyi ta addu'o'i akan Allah ya bayyana muna kuma ya tsare muna ita aduk inda take,  tun muna sa ran zamu ganta har muka cire, amma a kullum muna tunanin 'yarmu a cikin zuciyoyinmu.

A lokacin ganin damuwar da bintu ta shiga sosai a sanadiyyar b'atan wannan 'ya, yasa na nemo d'aya daga cikin yaran wannan babban yayanmu wato ALHAJI SANI BADAWI  mai suna SHU'AIB akan ya dawo hannun bintu da zama koda zai rage mata wannan damuwa da saka aranta,  a lokacin yana da shekara takwas zuwa tara, sannan na  bata hak'uri akan ta yafe man duk abunda nayi mata, saboda ina zargin hak'k'in ta ne ya bibiyeni yasa na rasa 'yata da na kwallafa rai akanta, daga nan na tattaro ta gaba d'aya na kawota wannan sabon gidan na had'e ta ita da hadizatou, kasanceawar bintu mai sanyin hali hadizatou ma mace ce mai dad'in zama ga biyayya,  sai suka hada kansu a wuri d'aya suka yi zamansu lafiya, a cikin wannan lokacin ne ko shekara ba'a rufa ba hadizatou ta sake samun wani cikin, daga NI har bintu muka dinga tattalin ta da yaron cikinta har  ubangiji yasa ta haifo 'yanbiyu  duk maza, aka saka masu sunan SUDEIS DA SADIS, wannan haifuwar da muka samu itace ta d'an rage muna zafin rad'ad'in rashin 'yarmu ta farko da mukayi.

Wanda a lokacin ne itama bintu ta sami nata cikin amma watan shi uku ya zube, ta k'ara samun wani har ta haifu amman abun baizo da rai ba,daga nan ciki hud'u tana samu yana zubewa, har daga karshe ma haihuwar tazo ta tsaya cak!,
Hadizatou ko bayan haifuwar sudeis da sadis, ta kara haifo fahat daga nan sai Ammar.

Hadizatou haifuwar ce kawai takeyi  amma duk wani hidima da renon yaran bintu ce take yi, da zuciya d'aya take k'aunar wad'annan yara, domin kulawar da take basu ita kanta hadizatoun da ta haifesu bata basu, hidimarsu gabaki daya bintu ce takeyi ba gajiyawa, a yanzu haka sudes da sadis a hannunta suke tun suna kanana har izuwa yanzu da suka girma suna Sudan suna

karatun secondary.

To  kunji tarihin abunda na sani dangane da rayuwar zamantakewa ta nida matana, amman bansan su waye suka sace muna 'ya ba, sai dai ga dukkan alamu bintu tana da wata b'oyayyiyen sirrin da  take boye muna, tawon shekara da shekaru, wannda nike zargin bazai rasa nasaba da b'atan wannan yarinya ba, bintu ki fito fii kiyi muna bayanin abunda ke damun zuciyarki tsawon wanda yake saka ki shiga damuwa, asanadin shi har kinsa lafiyarki tayi karanci, don Allah ki fad'a muna ko don ki saukewa kanki nauyin da kika d'orawa kanki, nayi maki alk'awali ko ma minene a shirye nike da inyafe maki shi,  duk ko iya girman laifin da kike ganin kinyi mani, domin nasan sharri ba halinki bane sai dai in sharrin shed'an da bawa baya iya tsallake shi, matuk'ar ba ubangiji ne ya tseratar dashi ba, domin jikina yana bani kina da hannu a b'atan 'yata NANA AISHA (izzatu)."

Tofa hajiya fatima gareki🙀

Akafta

D/Auta ce
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*PAGE FORTY SIX*

*********************

Ba shiri izzatu ta zaro ido a waje tana k'ok'arin yin magana ne, caraf idanuwanta suka had'u da na Ammi, ta gano gargad'iin da Ammin take yimata da idanuwa ba shiri tayi gum, amman fa gabanta sai dakan lugude yakeyi, sai k'iyasta kalar wulak'ancin da zata yiwa shu'aib takeyi a cikin zuciyarta.

Garzali ma jin wannan furuci na yayan Gwamna ya saka shi shiga tashin hankali ba kad'an ba, a lokaci d'aya yaji wani zazzab'i yana so ya rufe shi, jiki ba kuzari ya tashi tsam ya bar falon, wanda fitar da yayi ya k'ara jefa mama da malam a cikin sabuwar damuwa, bayan ta wannan d'anyan hukuncin da wannan dattijon ya yanke.

Iya kulu kam daman tasa a ranta yanzu izzatu tafi k'arfin Garzali, shiyasa bata ji haushi ba don tasan ko giyar wake Gwamna yasha ba zai aurawa Garzali 'yar shi ba.

Shu'aib kuwa shi kanshi k'irjin shi sai da ya buga, saboda jin wannan hukunci da Abbanshi ya yanke, domin shi yasan dalilin da yasa Abban yayi wannan azarb'ab'in, amman shi da za'a bar wannan had'in da yaji dad'i, saboda shi har a lokacin baya jin yarinyar tana wani burgeshi, saboda kallon 'yar k'auyen da yake YI mata har lokacin.

Mai girma Gwamna a zahiri ya nuna farin cikin shi, amman a zuciyarshi bai so yayan shi ya yanke wannan hukuncin ba, musamman fuskokin su malam da ya gani jamar suma basu in dad'i ba, yaso ace har sai izzatun ta zauna dasu na d'an lokaci koda ALLAH zai sa su fahimci junansu da shu'aib din, amman tunda yayan ya riga da ya tanke hukuncin ba yanda zaiyi sai hak'uri kawai, don baya son yayi abunda yayan zai ga kamar don shine ya haifeta.

Daga nan dukansu suka k'ara yiwa su malam godiya akan d'awainiyar da suka yi da izzatu, bayan sun k'are godiyar ne izzatu ta kira sunan da taji, hajiya fatima ta kira mai girma Gwamna dashi wato Abbaah tace, "Don ALLAH ina neman wata alfarma."

A cikin sakin fuska Abbaah'n yace, "Ina jinki 'yata fad'i koma menene matuk'ar bai first karfina ba insha Allah NI mai biya maki da duk bukatocin da kika nema a fad'in duniyar nan gaba daya matuk'ar ba sab'on ALLAH bane."

Izzatu taji dad'in wannan furuci na Abbaah, bakinta yana rawa tace, "Alk'awalin makarantar da kayi man, ina son yaya Garza ya maye gurbi na yaje a madadina."

Abbaah yana murmushi yace, "Kinyi tunani mai kyau kuma naji dad'i sosai insha Allahu zuwa k'arshen shekarar nan za'a fara yimasa process d'in zuwa makarantar UNIVERSITY LONDON, fatar mu kawai Allah ya bada abunda za'a je nema."

Izzatu tana jin wani tsantsar farin ciki yana ratsa ta, ganin gata ga mahaifanta tana fira dasu, a cikin murmushi mai sauti tace, "Kujerar makkah'r ma da kace ka biyaman itama na baiwa

malam yaje a madadina."

Abbaah yayi murmushi mai sauti yace, "Ba malam kad'ai ba duk wanda kike so a biyawa, za'a biya masa acikin dukiyarki saboda ki sami ladar kema, don haka ki zab'i duk wanda kike so wannan ba matsala bane, sannan dangane da zamansu a cen k'auyen idan ba damuwa za'a siya masu gida a nan garin, sai suci gaba da zamansu a kusa damu."

Gaba ki d'aya falon ya runtume da kabbarar su malam, iya kulu harda mintsinin kanta domin tana so ta tabbatar, shin mafalkin da ta saba YI ne na tayi kud'i ko kuwa a falke ne da gaske?, tana jin zafi ta yardarwa zuciyarta ba mafalki bane, jikinta yana b'ari ta tashi ta fara dannawa Abbaah kirari, gaba d'aya falon ita ake saurare har sai da mama ta jawo zanenta, da taxi zai sunb'ule ne ba shiri ta zauna amman bakinta bai fasa zubawa Abbaah da su hajiya fatima kirari ba, har sai da Abbaah ya dakatar da ita sannan tayi shiru.

Sabda jin haushin da yayan Abbaah yayi a tsaitsaye yayi sallama dasu ya fito, fuskarshi a cunkushe ya fita yana d'agawa direbansa hannu akan yazo su tafi ne ya hango Garzali a zaune yana latsar waya, a fusace tayi tattaki zuwa wurin shi a cikin sassafta murya tamkar munafuki yace dashi, "D'an samari a fahimtar ka da nayi kaima son auren izzatu kake yi ko?, to bari in sanar dakai izzatu tafi k'arfin d'an k'auye irinka talaka fak'iri me zatayi dakai, idan ba kana son ka yaudari kanka ba sawunka a likkafa ka cire wannan tunani a ranka, in kuma dukiyar da kaji ance an bata ne kake kwad'ayi, to shafawa kanka ruwan sanyi tun kafin inyi sanadin da zaka k'are rayuwarka a gidan yari, dubara ta rage taka ka shafawa kanka lafiya ko ka jefa rayuwarka a cikin had'ari."

Yana k'are maganganunsa masu busar sarewa a kunnuwan Garzali, ya juya fara taku zai bar wajen, Garzali ya d'aga muryarsa a sama yace, "Samu da rashi duk na ALLAH ne, haka rabon kwad'o baya fad'uwa k'asa banza, haka zalika duk nisan dare tabbas gari zai waye, haka ma dogara ga ALLAH jari ce, nayi imani duk abunda ya sameni daman cen an rubuta bazan tsallake ba, son izzatu kuma ko shafin farko ban bud'a ba, kaje duk abunda kaji zaka iya kayi kawai amma kar ka manta cewa, karya fure take bata 'ya'ya, ni murucin kan dutse ne ban fito ba sai da na shirya, don haka sara da sassak'a sam baya hana Gamji toho."

Ba shiri dattijon ya waigo saboda kalaman bazatan da yaji, suna fitowa a bakin d'an k'auyen da ya rena, a cikin kad'uwa da maganganun da Garzali yayi masa yace, "Da ni da kai sai anga wanda zai yin nasara."

Yana k'are fad'ar haka ya juya ya shige mota yana huci, direban shi ya ja motar suka bar gidan, garzali yabi motar da kallo a cikin mamaki, tareda furzar da wani iska mai zafi a bakinshi, sannan ya kaiwa iska naushi yace, "Ni da ku shege kan fasa."

A cen falon kuwa an yanke shawarar mai unguwa ne kawai zai koma k'auyen, saboda nauyin mutanen gari da yake kanshi, su ko su malam zasu kwana anan sai da safe su koma k'auyen

su tattara abunda suke so kafin a tanadar masu da muhallin da zasu zauna, daga nan taron ya watse su mama da iya kulu suka koma masaukinsu, izzatu ma tabi hajiya fatima zuwa sashenta.

Koda malam ya fito yiwa su mai unguwa sallama, yaci karo d'a Garzali fuskarshi a cunkushe, a cikin sakin fuska ya nuna masa yazo su yiwa mai unguwa sallama, mai unguwa ya tafi tareda direbanshi da rakiyar wasu security's har k'auyen, bayan uban alkhairin da mai girma Gwamna yayi masa, suka rabu kowa yana farinciki.

Daga nan malam yaja Garzali suka koma masaukinsu, yana ta bashi hak'uri akan hukuncin da aka yanke, Garzali kam sauraren malam kawai yakeyi amman zuciyar shi a k'ek'yashe take, domin shi yasa a ranshi ruwa da iska ba wanda ya isa ya hanashi auren izzatu, matuk'ar ba itace tace bata yin auren dashi ba, shiyasa yayi shiru bai fad'awa malam komi ba, don baya son ya d'aga mashi hankali, domin yasan muddin malam yaji zai tilasta shi ne akan ya hak'ura da izzatun, a haka ya biye malam suna ta firar su, kamar ba wani abu dake damunshi.

Izzatu kam tana a part d'in hajiya fatima tana kwance akan kujera, hajiya fatima tazo ta zauna tareda d'ora kan izzatu, a saman cinyarta tana k'ara rok'arta da ta yafe mata rabata da iyayenta da tayi, izzatu tace, "Haba Ammah ni wallahi tuni na yafe maki, don ke kanki ba da son ranki kika aikata ba, tunzuraki ne akayi kika rama abund aka YI maki, ni wallahi ko kad'an bana jin komi a zuciyata sai farinciki da Allah ya had'a NI daku a matsayin iyayena na gaskiya,duk da ko da baku ni nasan bazanyi maraicin iyaye ba, don malam da mama sun yimani rik'on gaskiya da amana, haka ma yaya garzanah!."

Ammah tayi saurin zaro idanuwa tana murmushi tace, "Anya 'yar Ammah ko ba wani abu a tsakaninta da yayan nan?."

Izzatu tayi saurin rufe fuska tana murmushi, shigowar shu'aib shine ya hana ta fad'in abunda tayi niyya, ba shiri ta tashi a zaune tareda galla masa wata gwarzuwar harara a fakaice, shi kam yana ganin suna wannan annushuwa da Ammah, yaji wani bak'in ciki ya tokare masa zuciya, ba shiri ya juya zai bar wurin amma ta kirashi ya dawo fuska ba walwala, amma ta kalkeshi a cikin mamakin wannan fushi da yakeyi tace, "Ba zaka tsaya ka karb'i sak'on ba?."

Sannan ya sosa kai yace, "shi nazo karb'a bani na wuce sauri nikeyi inje in dawo akwai inda zanje."

Amma ta tashi ta shige da nufin d'auko masa sak'on, ya gallawa izzatu wata harara, izzatu ta tashi tsaye tayi wani taku biyu zuwa uku ta k'araso a gabanshi a hankali tace, "Ya kaga 'yar k'auye a gidan Gwamna?."

🤣🤣🤣🤣

Akafta 🏃‍♀️

D/Auta ce⛹️‍♀️
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*Yawan comment's yawan typing😠*

*PAGE FORTY EIGHT*

********************

IZZATU tayi kyau abinta  gwanin sha'awa,  kyaunta ya k'ara fitowa komi dake bayyana a jikin cikakkiyar budurwa, to yaji a jikinta masha Allah, gata da faffad'an kunkuru mai d'aukar hankalin duk wani lafiyayyen d'a namiji, ga na shanunta b'ul b'ul cike da k'irjinta, gashinta acike kaf da kanta  bak'i k'irin sai shek'i yakeyi saboda sulb'in shi, tsawonshi kuwa idan ta sake shi har

tsakiyar bayanta, gata fara tas har da surkin jajaja, ga da  hanci tamkar bir tsawonshi, yayi daidai da 'yar faffad'ar fuskarta, ga d'an karami baki daidai kiss, ga manyan idanuwa farare tas tamkar madara, izzatu ta had'u ta inda duk mace ake so takai.

 musanmman yanzu da kyawon ya had'u da hutu da gyara abun sai wanda ya gani, ruwan k'auye sun fara bacewa a jikinta, saboda hajiya fatima tayi tsaye tsayin daka wajen maida ta mace ta kowane FANNI.

 Wanka ma sau hud'u take yinshi a wuni kuma ko wane wankan da kalar dress d'in da ake yi masa, izzatu ta zama 'yar gayu ta bugawa a jarida ayi talla, wadda idan ka ganta a yanzu bazaka tab'a cewa ta tab'a rayuwa a k'auye ba, kasanceawar daman cen ita ba rayuwa irinta 'yan  k'auyen take yi ba, saboda mama hassatu tayi tsayin daka sosai , wajen maida ta daban da sauran 'yanmatan dake cikin k'auyen.

Rayuwa mai cike da jin dad'i malam yake shinfid'awa da matanshi, musamman mama hassatu da ta goge ta zama wata babbar hajiya acikin wata d'ayan da suka dawo a birni, idan ta cab'a kwalliya bazaka ce itace hassatun da ka sani ba, sabida daman cen mama hassatu 'yar gayu ce lokacin da tayi zama a birni, ilham ma gyara take sha sosai tamkar d'iyar wasu hamshak'ai, saboda siyayyar da izzatu tayi mata kaya ne naji da fad'i.

Iya kulu ma anfara murjewa sai wani jiji da kai akeyi, kasancewar itama ba baya ba wajen son taga tayi abunda zata burge mutane, domin kuwa idan tayi wanka dole ne ta shiga motar da izzatu ta siya saboda zirga zirgar  hidimar gidan idan ta kama, aiko da ita take sa ana fita da ita ayitaa zagayen gari tana kalle kalle, wani wajen ma idan ta gani sai an tsaya ta fita  taje ta d'ebe k'eyar idanuwa, iya kulu a yanzu bata da wata damuwa sai ta Abu, da ya riga ya fand'are ta b'angaren shaye shaye da neman mata, musamman yanzu da suka dawo birni abun nashi sai gaba gaba yakeyi, malam yaso ya taka masa burki amma ina Abu kam ya riga yayi nisa, domin kuwa baya jin shayin yiwa malam bak'ar magana, iya kulu kam har kamar ya doke ta yakeyi idan tayi masa fad'a, 'yan kud'inta idan ta ajiye yabi ya sace kuma bata da ikon yin magana.

Izzatu  ta saya wa  malam tashi mota  daban, sannan ta kawo mak'udan kud'i tace dashi yaja jari, kasancewar malam mutum ne mai zafin nema, shiyasa kasuwanci a birni yayi masa dad'i, domin kuwa a kullum kanshi k'ara wayewa yakeyi akan maida kwabo ya koma sisi, ya jawo Abu a harkar  kasuwancin domin  ya shiga su dinga fafatawa a tare, saboda ya rage biye abokan banzan da ya k'ara samu a birnin,  amma ko sati baiyi da fara zuwa ba ya janyo wa malam, rigimar da tasa ya dakatar dashi da zuwa kasuwar, saboda wani shagon dake mak'otaka da shagon malam d'in ne yaje,  ya fakaici  idanuwan mai tsaron shagon ya kwashi kud'i masu yawa, ashe wani ya ganshi aiko rikici ya tashi, da akayi bincike aka gano tsawon kwana uku yana d'aukar kud'in batareda an gano shi ba, aiko da akayi lissafin abunda babu dole malam ne ya biya kud'in, to tun daga ranar yace dashi kada ya koma ganin k'afar shi a cikin kasuwar.

Mama hassatu taje har k'auyensu ta rok'i alfarma a wurin mijin inna hure, akan ya bata Amina tazo da ita birnin koda Allah zaisa mijinta anan yake, saboda har lokacin Aminar bata yi aure ba,

domin duk mijin da ya fito sai tace bata sonshi, har baban yayi zuciya yace zai had'a ta aure da wani almajirinshi, Amina tayi tsalle ta dire akan bata sonshi.

Da k'yar mama hassatu ta ci nasarar zuwa da Amina a birni,  amma da sharad'in da ta sami miji ayi mata aure.

Iya kulu tana ganin mama hassatu ta zo da Amina itama ta garzaya ta d'auko mari d'iyar  kande, tazo da ita  ta maida ta 'yar  aikatau,  komi bata yi sai dai mari tayi, hatta gyaran d'akin Abu itace keyi masa, randa duk Abu ya shawo kayen mayensa yayi ta zuba amai, itace za'a saka ta gyara wurin bayan uwar hantara da take sha a wurin iya kulun da Abun, kasancewar itama marin ba hali ne da ita ba, don d'ai ma tana gudun tayi abunda za'a maidata k'auyen da ta shikka masu rashin mutunci, amma a hakan duk lokacin da ta sami gararar abun d'auka, to kam d'aukewa takeyi taje ta b'oye,  saboda kande tace zata dinga  zuwa duk bayan wata d'aya, zata zo ta dinga  karb'ar kud'in aikatau d'in da mari takeyi, da nufin idan tazo sai ta bata ta wuce da abubuwan da ta sata d'in.

**

Garzali kuwa ya koma k'asar inyamurai wajen bautar k'asar shi, wadda karewar NYSC d'in zatayi daidai da lokacin da zai tafi k'asar waje k'aro karatunshi, yanzu tsakanin shi da izzatu sai a waya, wadda a kullum suna mak'ale da juna musamman ta hanyar chat, ko abinci zata ci sai ta kirashi suna video call yana lallashinta sannan taci tana zuba masa shagwab'a, soyayyar su ta k'ara karfi sosai, pic's kuma a kullum sai ta d'auka duk wani wanka da tayi  sai ya gani, domin kuwa  sai ta d'auka ta tura masa.

Tun hajiya fatima tana tunanin shak'uwa ce kawai, har ta fahimci akwai soyayya mai karfi  a tsakaninsu, tayi farinciki sosai da faruwar hakan, don ta fahimci ba wata jituwa a tsakanin izzatu da shu'aib d'in, shiyasa ta baiwa Abbaah shawara akan a nemowa izzatu admission ta koma makaranta, kafin su k'ara fahimtar juna da shu'aib d'in, duk da ta fad'a ne kawai don bata son a gano batayi na'am da auren izzatun da shi ba.

Garzali kam a  duk lokacin da yaga photunan izzatu, wutar kaunarta  k'ara ruruwa  takeyi a cikin zuciyar shi, da yaji labarin komawar izzatu makaranta ma,  ba k'aramin dad'i yaji ba don yasan jan lokacin da za'ayi, ba'ayi zancen bikinta da shu'aib  ba, to shinee zai bashi damar mallakar izzatun shi a cikin ruwan sanyi.

Alhaji sani kam da yaji zancen komawar izzatu makarantar,  ba k'aramin haushi yaji ba, saboda yaso ace anyi komi a gaggauce ko don su cimma gurinsu a cikin k'ank'anin lokaci, shiyasa lokacin da shu'aib ya nuna masa baya son wannan had'in auren, jikinshi har rawa yakeyi wajen kwad'a masa mari, bakinshi yana kunfa yace,     "Ka kiyayi abund duk kasan zai janyo fushina akanka, don wallahi asanadiyar k'in wannan aure da zakayi,  har tsine maka zan iya yi idan kayi man ganganci,in ba don kana soko ba wazai ga izzatu yace baya sonta?, ko kai har yanzu rashin hankali ne yasa ka kasa gano baiwar dake tattare da yarinyar, don haka duk runtsi ka

tabbatar ka cusa kanka a wurinta don mu samu mu cimma burinmu a cikin ruwan sanyi, ba tareda wani ya ramfo manufar mu ba."

Shu'aib yana kunbure kunburen fuska yace,

"Nifa Alhaji yarinyar kwata kwata bata kwanta man arai ba, domin ni  wallahi  haushi ma take bani,saboda tun had'uwar da nayi da ita ta farko naji na tsaneta, musamman yanzu da take wani jin kanta wata shegiya, haka kawai in bata fuska taga damata?."

Alhaji yana yi masa wani kallo tamkar ya shak'e shi a wurin ya mussure yace dashi,

Tafi sakaran banza mai k'aramar kwakwalwa, wai kai meke cikin kanka ne?,  da har ka kasa gano abunda nike nufi?, yanzu ba ka ga b'arin dukiyar da ake tayi akan wad'ancen matsiyatan 'yan k'auyen ba?, to ahir d'inka wallahi kaje duk hanyar da zaka BI kaje ka bita ka farauto zuciyar yarinyar nan,  in ba haka ba, ni nasan matakin da zan d'auka akanka, wanda ko kashe ka taci inyi zan iya wallahi, da dai ace in rasa samun biyan buk'ata ta, da na dad'e ina farautar hanyar da zan cikata, sai gashi a lokaci d'aya ALLAH ya kawo man hanya mafi sauk'i kazo kayiman bak'in ciki."

To tun daga ranar shu'aib yake ta tunanin ta wace hanya zai bi,  ya samu izzatu ta saurareshi har su k'ulla soyayyar, saboda yaji tsoron ganin yanda take ji da su malam, musamman shi Garzalin, da yaga hankalinta gabaki d'aya yana wurinshi, amman tuno da yayi abund Garzali yayi masa, yaci alwashin sai ya rama fiye da abunda yayi masa.

A wata rana izzatu tana kwance a falon Ammaah tana bacci, ta d'aga k'afa d'aya a saman kan kujera, yayinda kanta yake bud'e gashinta ya baje sai d'aukar ido yakeyi, daga ita sai 'yar k'aramar shirt da wando iya kacinsa a gwiwa.

Koda Shu'aib ya shigo neman Ammaah ba shiri yaja ya tsaya, saboda zuciyarshi da ta buga dam! ganin yanayin da ya riski izzatu a ciki, da sauri ya k'araso cikin  falon yana k'are mata kallo tun daga fuskarta har zuwa kirjinta da ya cika fam da nashanunta b'ul b'ul, ya dawo da kallonshi akan faffad'an kunkurunta, sannan yayi wajen santala santalan cinyoyinta  da k'afafunta da sukayi luwai luwai tamkar bata taka k'asa, ga fatar ta sai k'yalli takeyi, ba shiri ya lalabo kujera idanuwanshi a kanta ya kai zaune, saboda yanayin da yaji ya fad'a kafafuwanshi bazasu iya d'aukar nauyin sa ba, anan take yaji tsikarshi sai tashi takeyi yirr, da sauri ya kawar da kallonshi akan fuskarta, tareda furta, "Me ke shirin faruwa dani ne?."

Wadda wannan magarar da ya fad'a da k'arfi,  itace ta tada izzatu daga bacci a firgice ta falka, ta kai kallonta akan fuskarshi a zabure ta mik'e tsaye, tareda dalla masa wata jarumar harara ta buga tsaki, ta fara taku tana juya mazaunai ta shige d'akinta da ammaah ta ware mata a sashen.

Shu'aib kam bai d'auke idanunshi akanta ba  har sai da ta b'acewa ganinshi,  sannan ya sosa

kanshi yana wani munafukin murmushi.

Ya tashi tsam ya fice yana ta k'issima had'uwar da izzatu tayi a cikin zuciyarshi, yana ta kwatanta irin yanda zai sha lagwadar dad'i,  idan har aka yi aurensu da izzatu, a lokacin ne yake tabbatar da zancen Alhajin shi, ashe daman don yak'i kwantar da hankalin shi ne,  shiyasa bai gano abunda Alhajin yake so ya fahimta ba, a fili ya furta,

" yanzu za'a fara wasar, domin kuwa ruwa da iska bazasu hana ni mallakarki ba, dole ne insha wannan romon, domin kuwa bazan tab'a bari d'an k'auyen k'ayau,  ya shanye dad'in ya barni a sake da baki ba ina cizon yatsa, sam  ai gida bai koshi  ba za'a kai daji ba, ashe shiyasa shegen Dr'n cen yaso yayi kwaruwa?."

Wai ina Dr da mahaifiyarshi ya suka ji a lokacin da suka ji izzatu yar gwamna ce?.

Akafta

D/Auta🙄
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA ⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*PAGE FORTY SEVEN*

*********************

Shu'aib yabi ta da wani kallo tamkar ya shak'eta yake ji, a cikin kufula ya nunata da d'an yatsa, alamar kashedi saboda miyaun bakinshi gabaki d'aya sun k'afe, saboda bak'in ciki ya kasa iya furta wata kalma daga bakinshi.

Izzatu kam ganin  yanayin da ya shiga a lokaci d'aya ta tuntsure da wata gajeruwar dariyar tura haushi tace,    "Ya zakayi da 'yar da kazo cin arzik'i a gidan mahaifinta?, don haka ina baka shawara da kayi biyayya koda ALLAH zaisa inji tausayinka in rage girman lodin buhu buhun rashin mutuncin da na tanadar maka, don wallahi idan kayi wasa ruwa wad'annan baza ka sha su ta dad'i ba, matuk'ar ina cikin gidannan, don kai kanka kasani agola har abada bai tab'a zama daidai da d'an masu gida, saboda haka be careful kada ka yarda in fara d'ora idanuwa na akanka, matuk'ar kayi saken da hakan ta kasance, to sai na tabbatar maka da tashin k'auye daban yake da tashin birni, ni IZZATU sai na zame maka k'arfen k'afa a cikin gidannan."

Tana k'are maganar ta juya masa baya ta fara taku, tareda d'age masa d'an kwali tulin gashinta ya bayyana ta  waigo a cikin wata murya ta tsokana tace,     "D'an hakin da ka rena da sannu zai tsole maka idanuwa har sai ka zama abun tausayi , da idanuwanka k'uru k'uru kana kallo ba yanda zakayi da 'yar masu gida."

A zuciye ya nufi izzatu da nufin kai mata duka, Ammaah ta fito tana fad'in,

"yi hak'uri yaron Ammah sak'on ne nayi ta nema,  na manta inda na ajiye shi sai yanzu, ashe ma yana kusa idanuwa na basu kai a  kai ba, har sai da na gama wahalar nema sannan."

Tana kai kallonta akan fuskar shu'aib d'in ne taga yanda yake huci, mamaki ya kamata a hankali ta mirgina kanta ta kallo izzatu da tayi kamar ba da ita shu'aib d'in yake wannan ciccikar ba, domin kuwa kwancenta tayi akan kujera tana danna wayar Ammah dake  hannunta, Amma ta dawo da kallonta akan shu'aib tace,     "me ya had'a ka da 'yar uwarka ne?"

Kafin yayi magana izzatu ta rigashi wajen fad'in,

"nima bansan me nayi masa ba haka kawai kina shiga d'aki ya fara zagina, wai ALLAH ya kamani daman cen haushi na yakeji."

Ammah ta zaro idanuwa a waje tace ,

"Lelle ko yaron Ammah abunda ka d'auko  bazamu tab'a shiryawa dakai ba, yanzu don Allah

yarinya daga zuwanta zaka fara nuna mata bak'in halin naka?, to ahir d'inka don ni bazan d'auki wannan sakarci a gaba na ba."

Baki a sake shu'aib ya kalli izzatu saboda mamakin k'aryar da tayi masa,  ta dago fuskarta suna had'a idanuwa a fakaice tayi masa gwalo, saboda haushin da ya k'ule shi ba shiri ya fita fuuu ya bar falon, zuciyarshi tamkar tayi tsalle ta fito, saboda bak'in cikin wannan abunda izzatu ta guma masa,sannan ta biyo shi da k'ulla masa sharri a wurin ammaah, lalle wannan shine ga mari ga tsinke jaka, ya rasa ta wace hanya ce zai rama abunda tayi masa ya huce.

Yana fita amma ta dinga baiwa izzatu hak'uri akan abunda shu'aib yayi mata, izzatu sai dariya takeyi tace da Ammah,     "Ai na fahimci yana da saurin fushi sosai irinsu ba'a biye su."

Ammah taji dad'in samun izzatu da tayi da sauk'in hali a zuciyarta tana ta yiwa su malam Addu'ar gamawa lafiya, saboda tarbiyyar da suka baiwa izzatu mai kyau.

Hajiya fatima tace da izzatu ta tashi taje tayi wanka suje su kaiwa su mama hassatu fira, aiko izzatu jikinta har rawa yakeyi ta fad'a toilet din Ammah tayi wanka, koda ta fito ta tarar da wata doguwar riga mai masifar kyau akan gado, bayan ta dan murza mai da yar powder ne ta saka rigar, tana fitowa Ammah ta fara kod'a yanda tayi kyawo, izzatu kam kunya ta kamata don har lokacin bata saki jiki da Ammah ba.

Koda suka je inda aka sauke su mama hassatun, suka iske iya kulu jingine da kujera tana bacci bakinta dagaje dagaje da maik'o, hannunta rik'e da cinyar kaza wadda da alama ta fara ci baccin yayi awon gaba da ita, yanayin yanda suka ganta dukansu sai da sukayi mata dariya, izzatu ta lallab'a ta zare cinyar kazar dake a hannun iya kulun, aiko ba shiri iya kulu ta zabura tace,

"Wayyo k'afar kazata."

Gaba d'ayansu har da mama hassatu sai da suka yi mata dariya,aiko tana gano da ita suke wannan dariya ba shiri ta shiga taitayinta.

izzatu ta gaida su mama sannan ta janyo  hannun ilham tace,    "Zo nan ilham d'ita nayi keyarki."

Ilham tazo tana murna ta narke a jikin izzatu, mama tana murmushi tace,      "Tun d'azu itama take ta nemanki."

Izzatu tana murmushi tace,       " ALLAH sarki my ilham, wai mama yaya Garza na fa?, ina son fa in ganshi."

Ammah tayi murmushi tace,     "Bari insa ayi maki jagora sai kije kiyi masu sai da safe k'i dawo."

Mama ma tace itama zata je taga malam, iya kulu kam k'ara janyo wata kula tayi tana zuba, wani farfesun naman kajin turawa da suka yi luguf sai kamshi ke tashi, tace dasu suje ita kam bazata je ba.

Aiko tareda rakiyar wata amintacciyar mai aikinsu, da wani shima amintaccen mai hidima da gidan, a hankali suka tattaka ilham sab'e a kafad'ar izzatu har suka je masaukin su malam.

Bayan sun shiga suka fara 'yan gaishe gaishe, ya k'ara yiwa izztun godiya akan abun alkhairin da aka yimasu, izzatu tana jin kunyar wannan godiya da malam yake tayi, a cikin farinciki tace dashi, "Ai malam kunfi karfin komi a wurina, ALLAH dai ara muna rai da lafiya kawai."

Izzatu da tunda ta shigo k'wayar idanun Garzali suke akanta,ganin kyaun da ta k'ara a lokaci d'aya ya d'imauta shi, gabaki d'aya duk wata gaba dake a jjkinshi tayi sanyi k'alau, saboda wata irin zazzafar k'aunar da ke ta aringizo a kowace kofar gashi dake jikinshi, jinshi yakeyi tamkar yaje ya rungumeta a jikinshi, koda zai sami sassaucin abunda yake ji, a cikin wata kasala da ta mamaye ilahirin jikinshi yace da ita, "Barka da dare Aunty izzatu."

Da sauri izzatu ta dafe baki tace, "Yaya Garza yau nice Auntyn kuma?."

Yayi k'ok'arin kauda abunda yake fisgarshi yace, "Tunda kin kasa gaidani ai dole nace dake aunty."

Mama hassatu tayi murmushi tace, "yanzu duk wannan tattaki da tayi tazo don ta ganka baka gani ba?."

Garzali yayi murmushi yace, "To nidai tunda bata gaida ni ba mama ai ban ma san tazo ba."

Izzatu ta b'ata fuska tareda turo baki, alamar tayi fushi tace,

"Yo ai ko ni mama bansan yana a d'akin ba, daman wajen malam nazo tunda na ganshi shikenan ni sai da safe."

Tana k'are maganar ta tashi fuu ta fita, Garzali ko baiji kunyar idanuwan su malam ba, ya tashi tsam ya fita ya bita yana murmushi, mama da malam suna yi masu dariya.

Izzatu ko daman fushin bai kai zuci ba, tana fita ta sami wata baranda ta zauna, tana k'ok'arin tura masa text ne sai kawai taji mutum ya zauna agefenta, da sauri ta d'ago kai ta kai kallonta akan fuskarshi, tana ganin shi tayi saurin washe fuskarta da murmushi, me ta tuna kuma sai gashi naga ta k'ara had'e fuska ta wani zunb'uro baki, Garzali ya saka hannunshi ta bayanta ya rungumo ta a jikinshi, ba shiri dukansu suka sauke wata siririyar ajiyar zuciya, da sauri izzatu ta b'anb'are hannunshi daga jikinta tana cewa, "Yayana ba kyau fa, ko so kake yi mama ta

ganmu tayi man fada."

Garzali yana murmushi tareda sauya murya izuwa wata daban yace, "Ai nafi son ma a ganmu koda ALLAH zai sa aji tausayina ayi gaggawar bani kayana."

Izzatu tsikar jikinta ta tashi yarr ba shiri ta d'an matsa kad'an sannan tace, "Yayana in tambayeka.?"

Garzali ya d'aga kai idanuwansh akanta yana lumshe su tamkar wani mai jin bacci, izzatu tayi tagumi tace, "wai me yasa aduk lokacin da jikinmu ya had'u sai inyi ta jina a cikin wani yanayi, wanda ada sam bana jin haka a tattare da ni.?"

Garzali yayi murmushi mai sauti yace, "alamun girma ne yake dawainiya dake k'anwata, kije ki rok'i Alhaji sani kice masa ke aure kike so, ayi sauri a aura maki shu'aib d'in kawai."

Izzatu ta b'ata fuska alokaci d'aya wani kuka yazo mata, ta kalli Garzali ido cikin ido tace dashi, "Yayana muddin kana son kaga farincikina to don ALLAH ka daina yiman wannan magana, sabida zuciyata ta dad'e da fad'awa a son da k'aunar yayana, har kullum da kai ta saba babu wani wanda ya isa ya rabani da soyayyarka face ALLAH , yayana na soka tun kafin insan wacece ni, tun lokacin da nike tunanin soyayyar 'yan uwantaka ce a tsakaninmu , don haka ruwa da iska banga abunda zai sakani canza ra'ayi na akan ka ba, zuciyata gabaki daya kayi shukar da furanninta suka yi kore sharr, ba abunda take buk'ata face banruwa?,ina son kasani duk runtsi ni izzatu bazan canza ka ba, sai dai idan kaine kace baka so na wanda faruwar hakan nasan zan dad'e ina jinyar zuciyata, karshenta ma k'ila wannan jinyar da zanyi itace ajalina."

Garzali ya sauke wata k'atuwar ajiyar zuciya idonshi akanta har izuwa lokacin, jikinshi yana rawa ya matsa ya rik'o hannunta ya runtse da k'arfi har sai da taji zafi tayi 'yar k'ara, yayi murmushi mai sauti yace, "ke a tunaninki akwai wani abunda zai sauya mani ra'ayi akanki,?, never wallahi domin kuwa zuciyar Garzali da son izzatu take rayuwa, tun bansan minene so ba har izuwa wannan lokaci, soyayyarki mahad'in rayuwa tace, duk wani bugun numfashi na da soyayyarki yake tafiya, akanki idanuwana sun rufe ruf na kasa hango wata 'ya mace da zata kamo kafarki ma balle tace zata jera kafad'a dake farincikin zuciyata, saboda haka, ki ma daina wannan zance da baya da tushe balle makama."

Jikinshi har rawa yakeyi ya sauko k'asa yayi obeying a gabanta, idanunshi akanta ya k'ara cewa, "ni Garzali ba'a halicceni don ko wace mace ba sai donki ke kad'ai izzata, don Allah ki soni koda quarter'r son da nike yi maki ne k'anwata, i love you over and ever, my special diamond in my life."

Izzatu shauk'in son Garzali ya k'ara jefata a cikin farfajiyar tafkin kogin kaunarshi, ba shiri ta sauko itama suna facing din juna jikinta yana b'ari tace,

"Ni taka ce yayana don kai kad'ai kawai aka halicceni,zuciyata da gangar jikina duk naka ne, kasani ina maka son da NI kaina bansan iya adadin shi ba."

Garzali ya fito da wani d'an karamin zobe a aljihunshi yana k'ok'arin saka mata yace, "Zaki aure ni.?"

Izzatu ta share hawayen da ke kwarara akan kyakkyawar fuskarta tace, " kayi yanda kake so dani da rayuwata yayana, ka saka a ranka cewa ni taka ce har abada, ruwa da iska bazasu iya rabani da kai ba."

Garzali ya saka mata zoben suna kallon juna suna murmushi, zai k'ara yin wata magana ne aka dallare su da hasken fitila, dukansu suka shiga taitayinsu, jiki ba kuzari suka tashi sukayi tsaye cirko cirko, suna jiran mai haske su da fitilar ya k'araso.

Aiko sai ga shu'aib ya bayyana wanda har a lokacin bai janye fitilar akansu ba, aiko a zafafe izzatu ta buga wani bajimin tsaki, saboda jin haushin katse masu fira mai dad'i da yayi, a zuciye ta saka hannu ta buge fitilar ta fad'i a k'asa, jikinta yana rawa saboda masifa tace,

"A cikin makafin kai wani tsohon lalataccen makaho ne?, da duk wannan haske dake shinfid'e a lungu da sak'on gidannan, ace baka gani har sai ka saka fitila kayi yadiya.?"

Shu'aib bai bi ta kanta ba yakai kallonshi akan fuskar Garzali da yake Jin tamkar ya rufeshi da duka, a cikin had'e fuska shu'aib yace, "Yanzu kai ka rasa wacce zaka saka lungu a lungu kana k'wak'ula, sai matar da aka bani sadaka na aura?, amman lalle wannan d'an k'auyen ka tarowa kanka aradu da k..... "

Kafin yakai k'arshen maganar shi izzatu tayi tsalle ta faska mashi mari a zuciye, ba shiri shu'aib ya dafe gefen da yasha marin yace, "laa la la yanzu don bakida kunya ni kika mara?"

Izzatu ta d'aga murya tace, "an mareka d'in kai wanene banda d'an lasar arzik'i, wallahi ka kiyayi fushina tun kafin in saka ka barin gidannan talkaminka a hannu."

Shu'aib bai jira komi ba yayi ciki da Garzali ya fara kai masa duka na farko, da sauri Garzali ya rik'e hannuwansa duka biyu ya matse da k'arfi har sai da yayi k'ara, a fusace yace dashi, "Ka kiyayi ranar da ta kuskure na gwada k'wanji na anka, don kasani wallahi sai na sumar dakai k'aramin mara kunya."

Aiko shu'aib da yaji azabar matsa sai gashi yana ihun neman taimako, ba shiri su malam suka fito suka tarar da Garzali ya bank'arewa shu'aib hannuwa duka biyun, a cikin fad'uwar gaba malam ya katsawa Garzali tsawa yace, "Me nake shirin gani Garzali sake shi nace."

Aiko koda Garzali ya sakeshi ba k'aramar galabaita yayi ba, ya fad'i a kasa sharaf yana maida

numfashi, a cikin fushi malam yace, "Me yayi maka ne da zaka jiwa yaron mutane, ka ja mana tashin hankali muna zaman zamanmu?."

Garzali dai baice k'anzil ba saboda zuciyarshi ta kawo wuya, sai shigewa da yayi inda aka saukar dasu yana huci, malam yakai dubanshi ga izzatu yace, "me ya had'a su ne halan?"

Izzatu tana kallon shu'aib yana maida numfashin wahala ta k'ume dariya tace, "Ai shi yaja fad'an shiyasa malam, kasan yayana baya jan fad'a sai dai ajashi, kuma duk wanda rabon wahala ya hau kanshi to zai gano kuskurenshi."

Tana k'are maganar ta dallawa shu'aib wata jar harara, malam ya fahimci izzatu sarai gugar zana ce take yiwa shu'aib d'in, shiyasa ya fara bashi hak'uri, a zuciye ya tashi ya nuna su dukansu yace, "wallahi ya jawo maku shiga uku sai kunsan dani kuje zancen."

Izzatu ta had'e fuska ba shiri tace, "kai ko a tara ma zaka saka kanka wallahi muddin kayi gangancin shiga hurumina nida iyayena."

Shu'aib ya duk'a ya d'auki fitilarshi yayi fuuu ya bar wajen, izzatu ta d'aga murya tace, "in kunne yaji yasin jiki ya tsira."

Mama ta dungure mata kai tace, "wai ke ba mijinki bane?"

Izzatu ta zaro ido a waje tace, "Wallahi mama sai dai in mutu banyi aure ba."

Ta k'are maganar tareda b'ata fuska, malam yace da mama su je su kwanta dare yayi, sannan suka yi masu sai da safe suka wuce, izzatu taso mama tabarta ta kwana anan wurinsu, amma mama tace dole sai ta koma wurin hajiya fatima ta kwana acen, aiko ta d'auki ilham har tana bacci ta sab'a ta a kafad'a suka tafi, mama ta girgiza kai tace, "Wannan yarinya kina da abun dariya wallahi, to asauka lafiya sai da safe."

Takai kallonta ga iya kulu dake baje a tsakiyar falon tana ta sharar baccinta har da minshari, a cikin zuciyar ta tace, "Sannu kura"

Saboda ganin kular farfesun da ta ci ko rufeta ta kasa yi, saboda ta canye fiye da rab'i duk girman kular kuwa.

Koda safiya ta waye bayan sun kimtsa ne aka yi masu iso har cikin gidan, inda su hajiya fatima da hadizatou, iya kulu sai rabon idanuwa takeyi tana jinjina irin wannan daular arzik'i da idanuwanta suka yi tozali, a cikin ranta tace, "Ni ko a lahira na sami rabin rababar hakan

ai na more, balle a nan gidan duniya, wai kodai sun d'auka bazasu mutu ba ne?, oni 'yar kuluwa ashe inda ranka kasha kallo."

Mai girma Gwamna yayi masu godiya tareda goma sha tara ta arzik'i da rakiyar motoci tamkar wad'anda za'a kai amarya har k'auyen, aiko mutanen k'auyen suka cika k'ofar gidansu malam kowa sai barka da zuwa yake yimasu, sai zura ido sukeyi suga ta inda izzatun zata fito, domin kaf k'auyen har garuruwan dake kewaye dasu sun san da labarin IZZATU d'iyar Gwamna ce.

Dak'yar su malam suka kutsa suka shiga cikin gidansu, iya kulu sai d'age hanci takeyi sama alamar tana jin warin su, saboda ita in ta ita ake bi ko k'auyen bazata dawo ba, shigarsu gidan keda wuya kande ta shigo gidan a d'ari domin tazo taji labari a wurin 'yar kuluwa, ta mance duk kashe din da malam yayiwa mijinta akan kada ta sake shigar masa gida, jikinta yana b'ari take yiwa su malam sannu da zuwa, iya kulu dai sai wani kallo take yimata kamar bata tab'a sanin ta ba, kande tace, "haba 'yar kuluwa abun ba ko magana?, ko duk ruwan gidan Gwamnan da aka shawo ne ake yimuna gani gani."

Iya kulu tayi mata kallon hadarin kaji ta zuge wata jaka da tazo da ita, ta ciro wata leda ta bud'e aiko sai ga k'amshi ya bugi hancin kande, ba shiri ta cafko ledar tace,

"Bari in bud'e maki ranki shi dad'e"

Iya kulu tasa k'afa ta shure hannun kande a zafafe tace,

"Dad'ina da talaka kenan masifaffen kwad'ayi ne dashi, ai kya jira kiga abunda zan baki ba sai kinyi zalama ba, ni wallahi bani son jarababben kwad'ayi."

Kande ta b'ata fuska tace, "To ke 'yar kuluwa ai k'uda ma ya shafa maki lafiya indai ta bangaren kwad'ayi ne."

Iya kulu tace, "duk yadda na lalace ai na fiki, keda ko marayar baki tab'a zuwa ba balle kiga Gwamna a idanunki, ni ko fa har kwana nayi a gidan Gwamna na dangwali arzik'in Gwamnati nayo gida, ki bini a sannu koda zan d'auki mariya in je da ita birni ta dinga yiman aikatau, kema ki sheda kin had'a makotaka da 'yar kuluwa mai k'ashin arzik'i."

Kande jiki a sanyaye tace, "nayi biyayya nabi ALLAH na bi ma'aiki na bi ki 'yarkuluwa, aike yanzu dole ne ma adinga a lallab'a ki."

Iya kulu taji dad'in furucin kande ta bud'e ledar ta kwaso naman cike da hannunta ta mik'awa kande tace,

"Tafi gida kici keda yaranki ni bacci nikeji"

Aiko kande ta zuba nama a mayafin zanen da ta yafo ta k'ulle jabau tace da iya kulu, "Taka lafiya mai k'ashin arzik'i a fito lafiya nagode."

Iya kulu ta shige d'aki tana tafiyar tak'ama.

*****

Izzatu kuwa tasha kuka sosai saboda rabuwar ta da su malam, hajiya fatima sai lallashinta takeyi, dak'yar ta samu tayi shiru, aiko ta iske Abbaah har k'aton falonshi na alfarma, tace dashi tana so a siye gidan da su malam zasu dawo a cikin lokaci, mai girma Gwamna ko anan take ma ya buga waya ya bada umurnin a nemo masa gida mai kyau, izzatu tace dashi mai part biyu takeso don kowace ta zauna sashenta ba takura, amman a cikin zuciyarta taso hakan ne don bata son iya kulu ta koma saka mamarta a cikin damuwa, aiko kafin tabar wajen sai gashi ankira ance ansami gidan,a take ya bada kwangilar gyaran gidan ta ciki da bayanshi, izzatu tayi masa godiya sosai sannan ta fito zuciyarta fes, domin tana son taga mamarta a kusa da ita, duk da tasan baza'a dinga barinta tana fita sosai ba saboda tsaro.

Takanas hajiya fatima tasa aka kai IZZATU shopping complex ta zab'o duk abunda take buk'ata, ta b'angaren suturu takalma kayan kwalliya da mayukan shafawa masu kyau da sabulansu, harta kayan k'walam da mak'ulashe bata bari ba, aiko ta saki jiki ta jibgo kaya na ji da fad'i itada ilham da mamarta, malam da iya kulu da yayanta Garza kowanensu sai da ta jido masu uwar siyayya, wad'anda ya dace akai d'inki aka je aka bada.

Kafin sati d'aya izzatu fatarta ta fara canzawa i zuwa kalar larabawan asali sak!, ta k'ara kyau hutu ya fara ratsata.

An gyara gidansu malam komi yayi tsaf tamkar daman cen sabo ne aka gina, mai girma Gwamna yasa aka kwaso su daga su sai kayan jikinsu suka tare a sabon gidansu, inda komi yaji tamkar gidan wata sabuwar amarya d'iyar mai hannu da shuni.

Congrats 💃💃💃💃ALKHAIRI danko ne ALLAH ya bamu zuciyar shuka alkhairin 😅

Akafta🤣

D/Auta ce🤝🏻
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*in ba comments yasin zan fara hutun shekara😂*

*PAGE FORTY NINE*

**********************

A ranar da su izzatu suka yi bikin k'are makaranta, Dr yaje har makarantar domin kawai ya taya izzatu murnar wannan rana, ganin su malam a wurin shi yasaka shi barin makarantar ya koma gida, don baya son malam ya ganshi ya zargi wani abu dangane da shi, tunda yasan yayi masa kashedi akan bashi ba izzatu.

Koda ya koma gida ya bud'a TV a falon magaifiyarshi yana kallon duk abunda ke gudana live a gidan Tv'n, ana hasko fuskar izzatu da mai daraja Gwamna yana kabbarar, yayi saurin k'wallawa mahaifiyarshi kira ta fito a firgice, saboda bacci mai nauyin da takeyi ya tada ita, ta sami gefen d'aya daga cikin kujerun falon ta zauna, idonta a kanshi tana mashi kallon tambayar me ye mak'asudin wannan  kiran mafarautan da ya danna mata?, aiko da sauri Dr idonshi akan tv'n yace da ita,

"Matar da naso aure ce kuka hanani saboda rashin asali, to yanzu dai gatanan a gaban kowa gaskiya tana son bayyana ashe d'iyar yahaya badawi ce."

A cikin kwalalo idanuwa mahaifiyar Dr ta k'urawa TV kallo, akayi dace a lokacin hadizatou rungume da izzatu, masu camera sai haska fuskokinsu masu kama da juna sak! sukeyi, a

zabure mamar Dr ta mik'e tsaye tareda dafe k'irjinta dake bugawa da sauri da sauri, hannun ta yana rawa tayi nuni da photon izzatu da hadizatou, da ake ta haskowa a bayyane k'uru kur'u a cikin gilashin tv'n tace,

"Yanzu kana nufin 'yar k'auyen yarinyar cen ce wannan?."

Dr ya d'aga mata kai hannuwanshi duka biyu yayi tagumi dasu, idanunshi akan tv'n ko k'yaftawa baya son yi saboda mamakin wannan al'amari, musamman fuskar izzatu da matar Gwamna da ake nunawa ta saka shi shiga shock sosai, sabida kamar da suke yi da juna tayi yawa matuk'a.

Mamar Dr taje jikinta yana rawa ta kashe tv'n ta fuskance shi tace, "wai bazaka kalleni muyi maganar fahimta ba zaka maidani wata sakarya.?"

Dr ya mik'e tsaye yana kallonta a cikin wata sabuwar damuwar da ta ziyarceshi a lokaci d'aya, saboda jin haushin rabashi da izzatun da suka yi, fuskarshi cike da takaicin abunda aka yimasa yace, "wace maganar fahimta kike so muyi?, bayan lokacin da ni naso ku fahimceni ban samu wannan damar ba, to ai yanzu gashi nan gaskiya tayi halinta ashe ma asalinta har yafi nawa matsayi nesa, domin kuwa ke kanki kinsan wanene yahaya badawi, don kinfi kowa sanin duk wani tink'ahon Abbanmu na Yahaya badawin ne, kinsani in banda taimakon da yayiwa Abba da yanzu ko abunda zamu saka a bakinmu sai yayi muna wahala, domin shine tsanin rufin asirinmu gaba d'aya gidan duka, shiyasa hausawa suke cewa ka dai ga mutum amma bakasan irin baiwar da ALLAH yayi masa ba, to yanzu dai kinji izzatu mai cikakken asali ce d'iyar yahaya badawi ce, wanda kowa ya sanshi a fad'in garinnan har da kewaye, tun kafin ya zama Gwamna cikakken attajiri ne na gaske."

Dr yana k'are fad'ar maganganun yayi fuu zai fita yabar falon, mahaifiyar ta d'aga murya tace, "To yanzu ya zancen auren naku.?"

Dr saboda jin haushin maganar bai san lokacin da yace, "Tsuntsun da yaja ruwa ai shi ruwa kan doka."

Ya fita fuu ya shige d'akin shi tareda rufo k'ofa garam, mahaifiyar shi ta biyo shi da sauri tana fad'in, "Tunda na fara ganin yarinyar, na hango son da take yimaka a k'wayar idanuwanta, kaje na yafe maka ka dawo da matarka ka aura, ai dama don rashin sanin asalinta ne yasa muka ce a'a, amman yanzu tunda har gaskiya ta bayyana, angano iyayenta na ai'nahi sai ayi auren kawai wallahi mun amince."

A cikin d'akin azafafe Dr yace, "To ai sai kuje ku nemo min auren, tunda daman cen kune kuka b'ata shi."

Mahaifiyar ta zaro idanuwa kamar tana ganinshi tace, "Rufani ka saya inba so kake ayi rugurugu da nama na a gidan Gwamna ba, ai ko mahaifinka bai kai matsayin da zai tunkari Alhaji yahaya ba, yace yazo neman auren 'yarsa gareka ballantana ni ni a suwa?, kare da

gudun layya rufani kasaya da dai kai ka jaraba tunda tun farko kai aka sani."

Dr bai sake cewa da ita k'anzil ba saboda haushin da ya kume shi,domin in yakeyi tamkar a lokacin ne aka raba shi da masoyiyarshi izzatu.

Aiko har ta gama zugar surutun ta bar wajen a cikin danasanin abunda suka aikata, musamman ita da har k'auyen tayi tattaki taje sukayo rashin mutunci, donma Allah ya taimakesu sun sha dak'yar don ta dad'e tana jinyar kafafuwanta saboda sukar da k'aya tayi mata a cikinsu, a sanadiyyar  gudun fanfalak'in da suka sha.

*Shin wane taimako ne yahaya badawi yayiwa baban dr????*

A wata rana ne Abbaah yaje shopping d'inshi domin ya ganewa idanunshi  yanda kasuwar take tafiya, ya fito da wasu kud'ad'e a cikin wata leda mai d'auke da tambarin sunan shagon, a bakin shagon ne ya had'u da wasu mutane ya tsaya suna gaisawa, bayan sun k'are wajen k'ok'arin ya shiga mota ya  mance shaf ya saki ledar a wurin, tada motarshi keda wuya sai ga baban Dr d'an acab'a  ya ajiye shi a daidai wajen, yana k'yalla idanuwa ya hango ledar yashe a k'asa sannan ya hango motar da ta tashi a lokacin, zuciyarshi ta tabbatar masa ledar  mai motar ce, da sauri ya d'auki ledar ya bud'a yaga damin kud'i d'auri d'auri, aiko ya hau acab'an suka bi motar har tsohon  gidan Abbaah, koda suka je har ya ajiye motar ya shige gida, dak'yar mai gadin gidan ya barshi ya shiga harabar gidan bayan ya nuna masa kud'in,yace dashi ya jira anan get d'in sai Alhaji yace ya shigo.

Aiko minti biyar a tsakani sai ga maigadin ya dawo tareda Abbaah, yana hango ledar a hannun baban Dr ya tuna lokacin da take a hannunshi bakin shagon, ba shiri yace da baban Dr ya karaso cikin gidan har babban falonshi ya saukeshi, bayan sun gaisa ya mik'a masa kud'insa zai tashi Abbaah ya dakatar dashi, sannan yayi masa godiya ya zaro d'auri biyu na kud'in ya mik'a masa, sannan yace dashi wace sana'a yakeyi?, baban Dr a lokacin buga buga ce kawai yake yi shiyasa da yay masa bayani, Abbaah yace dashi yazo zai bashi aiki a d'aya daga cikin shagunanshi.

Tun daga lokacin ya bashi aiki ya rik'i kanshi da iyalinshi,  Dr ma karatun shi shine ya d'auki nauyi tun secondary har ya zama Dr a yanzu, ta hanyar wannan zumuncin ne har shu'aib yasan Dr suka k'ulla abota.

***

Izzatu a garden ita da su fahat da ammar sai guje gujen wasar 'yar b'uya suke yi, tana sanye da wasu riga da wando yan kanti sun kama ta sosai, ta rufe fuskarta da k'yalle tana neman inda zata lalabo su ammar caraf taci karo da mutum tayi tagataga zata fad'i, shu'aib yayi sauri ya rungumota a jikinshi.

Ammi dake tsaye a window'n sama tana kallon abunda yake faruwa, da sauri ta runtse idanuwa

saboda ganin rungumar da shu'aib yayiwa  izzatu, sabida daman ta dad'e tsaye a tagar tana kallon yanda izzatu ta saki jiki ta biye su Ammar suna ta wasa kala kala, tana jin dad'in wannan k'auna dake tsakanin izzatu da 'yan k'annenta, domin tunda tazo gidan a kullum suna manne da ita tana koya masu karatu, idan sun k'are a koma wasa har da labarai take basu kala kala da tarihin annabawa, shiyasa shak'uwar tayi yawa saboda suna jin dad'in zama da ita, haka itama tana bala'in tsintar kanta a cikin farinciki musamman in ta tuna k'annenta ne fa uwa d'aya uba daya, shiyasa take zage damtse tana koya masu abubuwan da zasu amfana.

 Izzatu tana jinta a jikin mutum da sauri ta cire k'ullin k'yallen da ta rufe fuskarta da shi, caraf idanunta suka sauka akan fuskar shu'aib, da yake ta feshe ta da wani shu'umin murmushi tareda d'age mata gira d'aya, a cikin zafin nama ta saka hannu biyu ta ture shi yayi baya, ta nuna shi da d'an yatsa a cikin fushi tace,    "this is the first and last da zaka saka kazamin hannunka ka tab'a ni, idan ba haka ba wallahi sai na nuna maka kuskurenka don ni ba 'yar iska bace da zaka wani had'a jikina da kai, kana yiman wani kallo da jajayen idanuwa tamkar wani tsohon maye, to bari kaji mayun ma na gaskiya sun ganni sun barni ballantana kai k'aramin k'waro."

Sai ga su Ammar sun gaji da b'oyon da sukeyi a k'ark'ashin kujerun dake wajen, sun ji shiru ga bata zo kamasu ba shine suka fito, fahat ya kalleta ya kalli shu'aib a cikin rad'a yace da ita, "Kema yaya shu'aib yayi maki muguntar da yake yimuna halan aunty?."

Izzatu ta ri'ko hannun fahat tace,      "Ku zo muje don wasar bazatayi dad'i ba tunda jemagu sun sauka a wurin."

Ta k'are maganar tareda dallawa shu'aib wata harara,  ta duk'a ammar ya haye bayanta ta goyashi suka bar wajen,  a cikin takunta na kasaita mai cike da motsa uku suna sittin saba'in.

Shu'aib yana yi mata wani kallo ya sosa gemunshi, tareda lashe lab'b'anshi tamkar wani wanda ya samu alawa, yana murmushi yace,

"Allah ya kai damo ga harawa ko bai ci ba yayi birgima."

Ammi dake kallonsu ta sauke wata k'atuwar ajiyar zuciya, saboda taji dad'in abunda taga izzatu tayiwa shu'aib,  duk da bata jin me suke  fad'a amman hakan ya burgeta, ta k'ara tabbatarw zuciyarta lalle  izzatu ta sami tarbiyya mai kyau a wurin iyayen rik'onta.

Shin Ammi kema baki son shu'aib d'in 🙆🏻‍♀️🙆🏻‍♀️wanga Black blood fa😥😥team shu'aib ku fito muyi zanga zanga🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️

Akafta 🏃‍♀️

D/Auta ce🏃‍♀️
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*PAGE FIFTY ONE*

*********************

IZZATU tayi shirin zuwa k'auyensu domin taje ta gano aikin ginin da ta bada kwangila, waton gidan mai unguwa da gidan malam da yanzu haka ba kowa a ciki da ta k'ara siyen filin da ke a bayan gidan aka k'ara fad'ad'a shi, sai gidan su inna hure da shima tasa aka rushe aka sake gina masu wani sabo dal, ank'are ginin ne take so taje ta gano sannan ta kai gaisuwarta ga d'aukacin mutanen k'auyen gaba d'aya.

Taci kwalliyarta son kowa k'in wanda ya rasa, ammaah sai kod'a ta takeyi saboda tsantsar halittun kyaunta da suka bayyana, Ammi kanta a ranar da izzatu taje yi mata sallama sai da ta cire kawaici tace da ita, "Anya 'yar Ammaah zaki bari azauna lafiya kuwa?, irin wannan kwalliya da kika zuba ai sai ki firgice mutanen k'auyen naku."

Izzatu tana murmushi tace, "Ammi to ni har wani kyau ma nayi nida ba kwalliyar kirki ma na iya ba, ke dai kiyi man addu'a kawai ALLAH ya dawo damu lafiya."

Ammi tana murmushin jin dad'in ganin 'yarta masha ALLAH tace, "Duk wadda Ammaah tayi

bata isa ba ni har sai na k'ara?, to matso inyi maki irin addu'ar da nike yiwa su Ammar idan kina so."

Izzatu tana dariyar jin dad'i tace,    "Ko ta jarirai ce yiman kawai Amminah! ina so."

Ta k'are maganar tareda duk'awa a gaban Ammi tana dariya, Ammi ta saka hannu ta dafa kanta tayi ta zuba mata addu'o'i tana tofa mata, bayan ta k'are  ne tayi murmushi tace da ita,
"ALLAH ya tsare hanya, amman dai zaki biya gidanku mamarki ta ganki kafin ki wuce ko?."

Izzatu ta mik'e tsaye tace da Ammi,     "Eh sai naje cen kafin in wuce, domin tare da  Amina zamu je."

Ammi tayi murmushi tace,  "to a dawo lafiya ki gayar man da su duka."

Izzatu ta fara tafiya zata bar d'akin tareda cewa,     "Zasu ji sai mun dawo."

Ammi ta bita da kallo a cikin farinciki tareda k'ara yiwa ALLAH godiya da ya bayyana mata 'yarta a cikin aminci, shiyasa a kullum su malam suke da girma a wurinta, musanman mama hassatu da a yanzu ta d'auke ta tamkar wata 'yar uwarta, saboda tana amfanuwa da shawarwarin da take bata idan tabi, don itace ma ta bata shawarar tayi kawaici wajen nuna tsantsar soyayyarta a fili ga IZZATU, saboda yanda ammaah take k'aunar izzatu da sauran 'ya'yanta kaf da ta haifa, hakan zaisa damuwar rashin 'ya'yan  da ta rasa ya rage ta d'auka cewa tamkar itace ta haifi izzatun, domin da gaske take son izzatu tamkar itace ta kawota duniya saboda kyakkyawar zuciyar da ALLAH ya azurta da samu.

Koda izzatu ta fito sashen Ammi, Amma dake tsaye tana jiran fitowarta, saboda tana son taga tafiyarta domin ta koma wurin su fahat da tayiwa wayo don kar suce sai sunbi izzatun, shiyasa tana hangota  ba shiri tayi murmushi wanda ya k'ara kawata kamilallar fuskarta.

 A tare suka rankaya har gindin wata arniyar motar da aka tanada musamman saboda wannan tafiyar,  wadda baba kallah ne zai jata saboda shi kad'ai ne Ammaah ta amince da yaja izzatu.

Bayan motocin da zasu take mata baya tareda escort din da zasu je a tare, sai motar sojoji biyu da zata yi masu rakiya saboda tsaro.

Izzatu ta bud'a motar ta shiga tana yiwa Ammaah bye bye, ammaah tace da baba KALLAH, ga amanar 'yarta nan ta bashi yana murmushi yaja motar, sauran motocin da zasuyi masu rakiyar biyo shi,  wasu a gaba wasu a baya aka saka motar baba kallah a tsakiya har gidansu su malam.

Izzatu direct sashen iya kulu ta shiga a gurguje ta gayar da ita ta fito, mari ta biyo bayanta sai kirari take zuba mata har sai da izzatu ta taka mata burki sannan tayi gum,izzatu ta fad'a sashen mama da gudu tana k'wallawa ilham kira, mamar ma jin muryar izzatun a fujajan ta fito

suka had'u a hanya suka rungume juna a cikin farinciki, mama ta kalli izzatu tun daga sama har k'asa tace,     "wai dai nikam ko musayar 'ya aka yiman ne?, tubarakallah masha ALLAH wannan kyau haka 'yata?."

Izzatu tana dariya yace,       "Mama ina ilham?."

Mama tace,      "Bacci take kinsan ta ko kasa bata fita bacci ba, sai dai in bata ji cikinta da nauyi ba."

Kafin izzatu tayi magana sai ga Amina ta fito a cikin shirinta,  itama tayi kyau gwanin burgewa sai kace ba ita ba, tayi kyau ta murje bazaka tab'a cewa iya kacinta primary ba, duk da yake yanzu an jefata secondary ss1 da taimakon lesson d'in da mama tasa aka yi mata a gida.

Izzatu ta kalleta tace,    "dallah malama muje kin wani mak'ale kina so ki b'ata muna lokaci."

Amina ta harareta tace,     "Lalle ma yarinya yanzu duk lokacin da kika b'ata kafin kizo baki gani ba sai nawa."

Izzatu tayi dariya tareda shigewa d'akin mama inda ilham take bacci, ta duk'a tayi mata kiss tace,    "Rimammata."

Sannan ta fito tana yiwa mama sai sun dawo, mama tayi masu addu'ar a dawo lafiya sannan ta rakaso su suka fito, abin mamaki sai ga iya kulu ta zama kalar tausayi a gaban baba kallah.

Ba wanda ya bi takanta suka fice suka shiga mota suka kama hanya, amma zuciyar izzatu sai mamakin ganin fuskar iya kulu da tayi kamar harda guntun hawaye,tana ta sak'e sak'e a ranta har suka fara tafiya zasu bar garin, izzatu tace da baba kallah,     "Don ALLAH baba wani gida nike so muje kafin mu wuce."

Baba kalla ya juya akalar motarshi sauran motocin ma suka biyo su, izzatu ta kalli Amina da ta cika da mamakin ina zasu je tace da ita,    "Gidansu Dr hashim nike so muje zaki iya gane gidan.?"

Amina ta fad'ad'a fuskarta da murmushi tace,     "keda gidanku ace har sai na nuna maki?, to nima bazan iya gane gidan ba gaskiya a yanzu."

Baba kalla yace dasu, "Dr Hashim d'in da na sani abokin shu'aib kuke nufi?"

Izzatu tayi saurin fad'in,     "shi fa baba kasan gidan su ne halan.?"

Baba kallah yana murmushi yace,   "nasan shi sosai kuma nasan gidansu saboda ai mahaifinshi,  a d'aya daga cikin shagunan maigida yake aiki"

Dukansu suka zaro ido, Amina tace,

"To acen gidan zamuje."

Izzatu kam tuno cin zarafin da mamar Dr taje tayi masu a k'auye, ya k'ara fad'o mata a zuciya ba shiri tayi murmushi amma har a lokacin tana jin zafin lafuzzan da ta yab'awa mamarta akan rashin sanin asalinta, ashe ma a karkashin abbaah suke bata da labari, aiko ta k'ara samun kuzarin zuwanta gidan ko don ta nuna mata ita d'iyar sunnah ce ba shegiya ba, haka zalika matsayinta yayi wa nasu fintinkau.

Manage plss🏃🏻‍♀️

Akafta🤣

D/Auta ce👌🏻
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*PAGE FIFTY ONE*

**********************

Baba kallah bai zame a ko'ina ba sai unguwar su Dr, yana  gaba sauran motocin suna  bayan shi har k'ofar gidansu Dr sannan yayi parking, wanda shigowar su ya jawo hankalin mutane da yawa, yayin da wasu suke ji tsoron ganin wad'annan kosassun sojojin suka fara gudu,  'yan gani

kashe kuma suka tsaya kallo zuciyoyinsu a cike da mamakin, me su Dr sukayi suka tsokano fushin masu hannu da shuni ganin rantsatsun motocin sababbi k'al sai d'aukar ido sukeyi.

Ita kanta maman Dr ta lek'o neman yaron da zata aika ne ta hango motocin suna doso k'ofar gidansu, har ta so ta tsaya kallo amma tana hango motar sojojin ba shiri hantar cikinta ta kad'a, musamman da taga sun tsaya a k'ofar gidan suna dirowa daga cikin motocinsu, abun mamaki kuma sai taga wasu security's sun tsaya a gefe da gefen wata rantsatsiyar mota, waton motar da SU izzatu suka shigo, suka tsaya gefe da gefen motar wani ya saka hannu ya bud'e murfin motar, sannan wanda ke gefen guda ma ya bud'e d'ayan murfin idanuwan maman Dr a waje tana so taga wad'anni shafaffu da mai ne?, aiko tana nan k'urin da idanuwa ta hango k'afar izzatu d'aya da ta sauko a k'asa kafin ta fito gaba d'aya, ba shiri maman Dr ta k'ara zaro idanuwa aranta tace,

"Bak'in turawa mukayi a unguwar tamu.?""

Kafin ta baiwa kanta amsa sai ga izzatu ta fito gaba d'ayanta ai kuwa ba shiri maman Dr ta k'ara gwalalo idanuwa baki a bud'e tace, "tsalki ya tabbata ga mak'agin wannan halitta."

Ta gano da gaske gidan zasu shigo ne saboda ganin izzatu da Amina sun doso gidan, sannan ga wasu security's mata sun take masu baya a guje har tana tuntub'e ta shige gidan, bata tsaya a ko'ina ba sai a k'uryar d'akinta tayi likimo tana sauraren shigowarsu, domin zuciyarta ta bata tabbas ba lafiya don ita a rayuwarta KAF bata tab'a ganin wad'annan halittun ba.

Aikuwa tana jin shigowarsu tareda takun takalmansu dake k'wask'wa, a d'ari ta bazama toilet ta zubarda zawon da taji yana barazanar fito mata ko ba shiri, tana jin sallamar su izzatu amma ta kasa amsawa sabida zawon da take fesawa, bayan ta k'are ne ta fito jiki a sake tana amsa sallamar a cikin raunanniyar muryarta, tana fitowa a tsakar gidan ta k'ara yin tozali da fuskokinsu izzatu, ba shiri cikinta ya k'ara kad'awa duba da yanda taga security's d'in matannan suna ta muzurai, a haka ta daure dai ta k'ara tsuke k'ofar zawon don kada yayi mata tonon silili a gaban mutane, a cikin dakiya ta fara yi masu sannu da zuwa kamar haka,

"Sannunku da zuwa hajiya anzo lafiya?ku shigo daga ciki mana."

Tana gaba su izzatu suka bita a baya har cikin falonta, bayan sun zauna suka k'ara gaisawa fuskar izzatu ba yabo ba fallasa tace da ita,

"Dr fa?"

Mamar tayi k'ara tsurewa ido suka rena fata bakinta yana rawa tace, "Yanzu zaki ganshi ya shigo domin fitar shi kenan yaje yiwa wani abokin babansu allura."

Izzatu tayi warai da idanuwa tareda wani munafukin murmushi tace, "Sai naga kamar baki waye mu ba mama."

Mamar Dr tayi saurin zaro idanuwa domin ta k'ara tantance su saboda jin da tayi izzatu ta kira ta da sunan mama, kafin mamar Dr tace wani abu izzatu tayi wa wata security magana da turanci akan ta bata jakarta dake a hannunta, a gaban mamar security tazo ta rusuna ta mik'awa izzatu jakar ta saka hannu ta karb'a tareda yin murmushi tace, "Thanks."

Sannan ta soka hannu a jakar ta ciro check tareda rubutu dubu d'ari biyu a jiki ta b'allo paper'r ta mik'awa mamar, a cikin mamaki mama ta zura hannu ta karb'a tana jiran taji ba'asin check d'in menene, izzatu ta mik'e a tsaye ta feshe ta da wani shu'umin murmushi tace,

"Idan Dr yazo kice masa izzatu d'iyar Gwamna yahaya badawi tazo."

Tana k'are maganar ta fito falon Amina ta take mata baya, mama kuwa tana jin wannan suna ta dafe gaba saboda dakan luguden da kirjinta yayi ba shiri, tareda zaro idanuwanta duka a waje kamar zasu fad'o a guje ta biyo bayan izzatu har taci tuntub'e zata fad'i, izzatu tayi saurin rik'ota tace,

"Subhanallah mama."

Ido cikin ido mama take kallon izzatu a cikin mamakin da yake barazanar kaita lahira bata tantance ba, tareda kallon tuhumar da mamar take biyarta dashi, izzatu ta lumshe idanuwa tareda bud'esu taras akan fuskar mama saboda karantar abinda ke cikin zuciyarta da tayi, a hankali ta d'aga kai tace, "Kada kiyi mamaki mama nid'in dai ce 'yar k'auyen nan da kuka hanawa Dr ya aura, haka zalika nice yarinyar da kikaje har k'auye kika gorantawa asali, kada ki damu nasan rashin sani ne ya jawo hakan, kada kiji komi ni na yafe maki saboda a tsakaninmu da Dr har gobe akwai mutunci domin yayi muna alkhairin da bazamu iya manta shi ba."

Izzatu tana k'are maganar ta feshe mama da wani murmushin mai cike da ma'anoni ta fito gidan security's suna take mata baya, mama baki a bud'e tayi zaman 'yan bori a tsakiyar gida hannunta aka ta kurma wata bajimar kuwwa, me ta tuna kuma tayi saurin dafe baki tareda bazawa a guje kamar wata k'aramar yarinya tayi toilet tana kwararo zawo.

Izzatu kuwa suna fitowa a k'ofar gidan sai ga motar Dr tayi parking kasancewar k'ofar gidan mai fad'i ne, amman fa fuskarsa a cike take fam da mamakin ganin wad'annan motoci a k'ofar gidansu, mamakin shi ya saitu ne a lokacin da ya hango izzatu da Amina suna fitowa daga gidansu, jikinshi yana rawa ya k'araso tareda fad'ad'a fuskarshi da wani yalwataccen murmushi, izzatu da Amina ma suka mayar masa da murmushinsa, Dr hannunshi a baki yake k'are masu kallo a cikin jin dad'in ganinsu musamman ita izzatun, da yake raba dare a kullum saboda tunaninta, domin yayi iya yinshi akan ya kawar da sonta a gefe amma ina yana nan tsayenshi k'yam a tsakiyar zuciyarshi, yana murmushi mai sauti yace, "'yanmata adon gari yau ziyara aka kawo muna.?"

Dukansu sukayi murmushi Amina tayi caraf tace, "Tunda ku ba kwa nemanmu ai mu sai

muzo mu kwashe ladar."

Dr yayi dariya idonshi akan izzatu yace,     "sannu hajjaju kunyi k'ok'arin gane gidanmu."

Izzatu a cikin nauyi tace masa,     "Baba kallah ne ya kawo mu ai."

Da sauri Dr yakai dubanshi inda motar farko dake kallonshi, yana dariyar jin dad'i ya nufi motar baba kallah ya fito sukayi musabaha, sannan suka gaisa su izzatu suka k'araso jikin motar, sanna izzatu ta kalleshi tayi wani tsadadden murmushi tace,       "Mu zamu wuce sai kuma wani jik'on idan ALLAH ya nufa."

Dr yana murmushin yace da ita,  "okay na fa gode sosai da wannan ziyara ALLAH ya biya ku da gidan aljannah, idan kunje ku gayar man da su malam."

Izzatu da Amina Suka had'a baki wajen fad'in,        " zasuji"

Sannan suka shiga motar baba kallah ya tada motar da sauri Dr ya lek'o saiti da mazaunin izzatu yace,

"Ranki ya dad'e ko za'a taimakan da number?, saboda akwai maganar da nike so muyi."

Izzatu tayi dariya har saida fararen hakoranta suka bayyana tace,    "me zai hana ko? tsaf zaka samu."

Daga nan ta dinga fad'o masa number'r yana sakawa a wayarshi, sannan ya janye tareda d'ago masu hannu alamar bye bye suna maida masa, karaf idanuwan  Dr suka sark'e a cikin na Amina ba shiri ta feshe shi da wani murmushin da ita kanta batsan ko na minene ba.

Baba kallah ya mik'a hanya aka saka shi a tsakiya, motar sojojin d'aya a gaban jerin motocin yayinda d'aya take a bayan su, suka kama hanyar zuwa k'auyen a guje izzatu tayi wani murmushi tace da baba kalla,    "Mun gode fa baba."

Yayi murmyshi yace,    "Kinfi k'arfin komi a wurina 'yata."

Izzatu tayi dariyar jin dad'i tace,    "Yawwa baba wai d'azun me ya had'aka da iya kulu ne?, naga kamar tana 'yan guntayen hawaye."

Ta k'are maganar tareda dariya, baba kalla shima dariyar yayi yace da ita,

"Wata dirama ce mukayi da ita bayan kin shige sashen mamarki, shine tana hangoni lokacin da ta rako ki, jikinta yana b'ari tazo wurina tana gaidani na amsa mata ba sakin fuska, to shine tace dani wai da gaske nasan duk matsin lambar da tayi ta yimaki?,  nace mata eh hadda tallar da tayi ta d'ora maki ina yimaki juye duk na sani, aiko shine hankalinta ya tashi ta durk'usa har

kasa tana rok'ona wai don ALLAH in rufa mata asiri,  kada in fad'i irin abubuwan da tayi maki na zalinci a wurin kowa, don tun ranar da akayi wannan taron tayi ta nemana ta rok'eni sai na b'ace mata, nace mata bazan fad'i ba amma da sharad'in ta gyara tarayyarta da unbangiji, sannan ta k'ara rokarki yafiya akan ki yafe mata to shine kika ganta a rud'e."

Izzatu da Amina suka k'yalk'yale da dariyar shirmen iya kulu, baba kalla yana tamasu yace, "ni sai nake ganin kamar wannan mata ba kanta d'aya ba fa, don na fahimci tana da shiririta sosai a cikin lamurranta,  akwai fa ranar da na tab'a ganinta a bakin badawi plazar,  sai lek'e lek'e takeyi bansan me take nema ba a wurin, saboda a bakin k'ofar shiga wurin na ganta tana rabon idanuwa tamkar wata zararriya, ALLAH yasa bata ganni ba."

Su izzatu ko dariya suka yi ta ci har suka kai k'auyen, sai ga mutane sai gudun tsira sukeyi ganin sojoji da bindigoginsu, ganin sun nufi k'ofar gidan mai unguwa ne da yasha gyara tamkar ba shi ba, sai ga  wasu marasa tsoron sun garzayo domin su ganewa idanuwansu abunda zai faruwa.

Aiko ganin izzatu da Amina sun fito tareda baba kallah sai kallo ya koma sama, saboda dukansu ba wanda ya d'auka mutanen da suka tab'a sani ne ganin sun sha ado ba na wasa ba, kai tsaye izzatu da Amina suka shige gidan mai unguwa wajen matanshi suka gaidasu duk da suma basu  wayesu ba, sannan aka yimasu iso suka shiga fadar mai unguwa shikam yana ganin izzatu ya ganota, saboda farin sanin da yayi mata sannan sanin daular da ta shiga a yanzu yasan dole ne ta canza sosai, a cikin farinciki ganin juna suka durk'usa har k'asa suka kai gaisuwa ga mai unguwa.

Wanda shima k'ok'arin gaida izzatun yakeyi ta hana sai ya buge  da yimata godiyar irin abun alkhairin da ita da mai girma Gwamna suka yi masa, sabida yanzu haka gari biyar dake zagaye da garin duk shine sarkinsu duka, wannan karramawa ce da Gwamna yayi masa saboda yabawar da yayi da adalcinshi.

Bayan sun k'are gaisawa ne izzatu  tayi masa bayanin akan a tara mata mutanen k'auyen duka, domin tana so ta raba masu kyautarsu da tasa aka zo ita tun kafin su k'araso, aiko haka akaje akayi ta shela akan kowa yazo k'ofar gidan mai unguwa ana son ganinsu, wanda kafin su had'u duka akayi ta sauke kwali kwalin da aka ciko tireloli  dasu, sai da aka cika k'ofar gidan mai unguwa taf da kwalayen amma har wasu basu sami fili ba dole aka bar wasu kwalayen acen.

Bayan sun had'u ne mai unguwa ya fara koro masu bayanin kamar haka,     "Assalamu Alaikum nasan zakuyi mamakin abunda yasa aka taraku a yanzu, to ba wani abu bane illah 'yarku ce wasu kuma kanwarsu, itace ta kawo maku ziyara saboda karamci irin nata da tayi gadon mutunci gaba da bayanta, kuma 'yar halas wadda bata mance alkhairi komi k'ank'antar shi, wato IZZATU  'yar gidan malam ayuba da hassatu, wadda a yanzu ta rikid'e ta koma 'yar Mai girma gwamna wato ALHAJI YAHAYA BADAWI."

Gabaki d'aya wurin ya d'auki sowa da farin cikin jin wannan labari, yayinda kowa ya matsu yayi

ido biyu da 'yar Gwamna IZZATU,  mai unguwa ya bada umurnin izzatu ta fito aiko sai ga izzatu ta fito d'auke da wani murmushi akan fuskarta, gabaki d'aya wurin ya ruguntsume da kirari kowa da jinjinar da yake yimata, saboda sunji dad'in wannan ziyara da takawo masu.

Daganan aka ce kowa yayi shiru ba shiri wurin yayi tsit saboda suna girmama mai unguwa sosai gani irin adalcinshi a garesu, sannan mai unguwa yace da izzatu tayi magana, aiko a hankali ta fara kai gaisuwarta ga d'aukacin wanda ke wurin daga nan tace,

"Nayi farinciki sosai da ALLAH ya sake had'ani daku, saboda komi na zama a rayuwa to bazan tab'a mantawa da mutanen wannan gari ba, musamman babana MALAM AYUBA da mamata hassatu da baba mai unguwa, sannan da yayana kuma maigidana insha ALLAH wato yaya Gazanah!."

Aiko fili ya d'auki kabbara fuskokinsu a washe sai jinjina irin wannan karamci na izzatu sukeyi, tsofaffi sai saka mata albarka sukeyi matasan garin kuwa sai fito suke suna furta kalmomin girmamawa tareda jinjina a wurinta.

Daga nan mai unguwa ya sanar dasu kyautar da ta zo masu da ita, aka umurcesu da su layi maza daban matan da suka zo suma  daban, har sun fara ruguguwa aka tsawatar dasu,  dole suka natsu saboda  bindigogin da suke hange a hannun sojoji dukansu suka shiga taitayinsu.

Aka fara rabon kwali kwali ga duk wanda ya halarci wurin, mutane sai tud'ud'uwar zuwa sukeyi cen na hango taku kande da 'ya'yanta 'yanmata a layin mata sai rabon idanuwa suke yi, d'aya bayan d'aya duk wanda yazo wurin sai da aka baiwa kowa, sannan sauran da suka rage akayi ta jida ana shiga dasu gidan mai unguwa, sai da komi ya lafa sannan mutane suka watse bayan sun shiga daga ciki izzatu ta ciro check ta rubutawa mai unguwa kud'i masu tsoka ta mik'a masa,  mai unguwa yayita godiya har da 'yar k'wallar shi sannan izzatu tayi masa sallama suka nufi gidansu kande,mutane suka biyo su abaya suna ta saka mata albarka.

Ko da suka shiga gidan kande ta watse kwalaye anyi masu fillah fillah ana kallon abubuwan dake ciki, saboda tun a waje da d'iyan suka hango su izzatu zasu shigowa suka arto da gudu suna sanar da ita ga IZZATU nan zuwa gidan, ba shiri ta janyo mayafi ta yafa ta fara maida kayan dake cikin kwalin da suka firfito dasu suna kallo.

Koda IZZATU ta shigo kande duk ta diririce wai yau 'yar Gwamna a gidansu, a tsaye suka gaisa izzatu ta ciro kud'i rafar d'ari biyar ta mik'a mata sababbi k'al, ba shiri kande ta kai durk'ushe wajen karb'ar kud'in saboda tsananin rud'ewar da tayi, aiko tana jin d'imin kud'in a hannunta ta fara kuka tana cewa,     "Don ALLAH izzatu ki yafe man duk abunda nayi maki."

Izzatu tayi murmushi ba tareda tace da ita k'anzil ba ta fito gidan suka nufi gidan malam.

Kande ta kalli kwalayen dake gabanta guda biyar da ta samo d'aya mijinta d'aya sai yanmatanta biyu da idi d'aya, sannan ta k'ara kallon kud'in dake hannunta ta fashe da wani zakin kuka tace

da 'ya'yanta ,   "tabbas d'an hakin da ka rena ashe da gaskiyar hausawa shine yake tsone maka idanuwa, yanzu ku duba ku gani ko buhun shinkafar nan zaici tiya biyar biyar fa, sannan ga jarkar manja ga na mank'uli ga maggi ga sugar ga sabulai sannan a kowane kwali ga dubu biyar a ciki sannan ga wad'annan mik'ak'k'in kud'in sababbi k'alk'al, oni kande wannan bajinta ai sai d'an gidan girma wanda ya gadi k'ashin arzik'i a gaba da bayanshi, izzatu yau kin nuna muna cewa tabbas ke 'yar halas ce, mun yimaki sharri kinzo har gida kin saka muna da alkhairi."

Ba shiri ta k'ara fashewa da kukan nadamar abunda tayi ta k'ullawa iya kulu akan tak'i izzatu, da jifarta da miyagun kalamai da take tayi ita da yaranta, tana kuka tana ALLAH muntuba ka yafe muna.

🤔🤔🤔🤔Su kande anfara shiriya?????.

Akafta👍🏻

D/Auta ce👌🏻
[8/22, 1:55 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*PAGE FIFTY TWO*

*********************

Ummaru ya bud'e 'yar k'aramar k'ofar wangalelen get d'in gidan, a cike da karsashi sannan su izzatu suka shiga da bisimillarsu saboda gida ne na ji da gani, wanda a kafatanin k'auyen kaf bayada na biyu, wanda ko a birni sai anyi dak'yar kafin a samo wanda ya fishi, masha ALLAH gida ya tsaru part hud'u ne a cikin gidan kowane ka shiga sai ka d'auka cewa sashen ne kawai a gidan saboda haduwarshi, sun shishiga lungu da sak'o na gidan sun gani tareda jagorancin ummaru d'an inna hure, wanda shine izzatu ta wakilta a matsayin idanunta shiyasa ragamar komi na gidan yake a hannunshi, wanda shima izuwa lokacin ya siye k'aton filin shi har ya fara aza gini.

Bayan sun k'are dudduba gidan ne suka fito suka nufi gidansu inna hure, wanda shima d'in aka gyara shi fesfes da gini irin na zamani gwanin burgewa, Amina ganin yanda gidansu ya koma sai wasar bakin jin dad'i takeyi tana k'ara jin k'aunar izzatu har cikin b'argonta, domin ita har gobe ta d'auki izzatu tamkar 'yar uwarta wadda suka fito tsatso d'aya.

Koda izzatu suka shiga gidan inna hure farin cikinta ya kasa boyuwa saboda jin dad'in ganinsu, kafin kace me da shigarsu aka cika gabansu da kalolin abinci wanda wannan duk hidimar ummaru ce saboda yasan da zuwansu.

Bayan sun gaggaisa ne inna ta fara yiwa izzatu godiya, babansu Amina ma ya shigo suka gaisa tareda k'ara jaddada godiyarsu a wurinta, a gaggauce su izzatu suka ci abinci suka YI SALLAH, sannan suka yi masu sallama bayan izzatu ta dunk'ulo kud'i masu tsoka ta baiwa inna taja jari, shi kanshi baban Amina tayi masa kyautar bajinta ummaru ma gefe ta ja shi ta dunk'ulo kyautar da itama batasan ko nawa bace tace dashi ya k'arasa ginin gidanshi, suka fito k'auyen a cike da kewar juna tareda tsarabar k'auyen da aka lafto masu kala kala.

Suna tafe akan hanya Amina ta fashe da kukan farinciki saboda jin dad'in hidimar da izzatu takeyi dasu ba gajiyawa, izzatu tayi saurin kai kallonta ga Amina a cikin mamaki tace,
"Malama me aka yimaki ne? da zaki cika muna kunnuwa da kuka."

Amina ta ri'ko hannunta duka biyu ta runtse idonta a cikin na izzatu tace, "Mun gode sosai da ALLAH ya azurtamu da samunki a cikin ahalinmu, tabbas ke d'iya ce har da rabin d'iya a rayuwata kaf ban tab'a ganin mai halacci irin naki ba, mun gode sosai da hidindiminki agaremu, ALLAH ya saka maki da gidan aljannah ya nuna muna ranar aurenki da yaya Garzanki."

Izzatu tayi murmushin jin dad'in addu'ar da tayi mata musamman da ta ambato sahibil k'albinta, bakinta a washe tace, "Nifa wallahi har yanzu ji nikeyi tamkar ku d'in jinina ne na gaske, shiyasa bana k'yashin yin komi don ganin nikeyi ai kaina na yiwa idan nayi, naso ace DADATAH! Itama ALLAH yayi mata tsawon rai domin kawai in rab'i jikinta inji sanyi, duk da banyi wayon saninta ba amma ina jin sonta ba kad'an ba ALLAH ya jik'anki DADAtah!, ya k'ara haskaka maki k'abarinki halinki na k'warai ya biki."

(ALLAH sarki nima na tuno da rasuwar masoyiyata Asama
Bawa Kaura ALLAH ya jik'anki da rahama ya k'ara haskaka makwancinki ya sawa abunda kika bari albarka 😭).

Ta k'are maganar tareda zubowar k'wallah akan fuskarta, kai tsaye aka wuce gidansu malam aka ajiye Amina, izzatu tasa aka raba tsarabar biyu aka shigarwa da su mama rabi, sannan ta shiga tayi masu sallama ilham ta lik'e ta ala dole sai ta bita aiko ta d'auko ta suka nufi gida.

****
Maman Dr kuwa ta fito bayin tana zaune tana maida numfarfashi sama sama, Dr ya shigo gidan da sallamarshi a cikin wani farinciki da yake ta ratsa zuciyarshi, koda ya shigo falon yaci karo da check d'in da izzatu ta baiwa maman yashe a bakin k'ofa, ya duk'a ya d'auki check d'in yana dubawa ba shiri ya zaro idanuwa a waje tareda karasowa cikin falon inda mamar take a zaune, fuskarshi a washe yace, "Wannan check d'in fa mama.?"

Sai a lokacin mamar ta tuno da shi tana yatsine yatsinen cikinta da yake ta yamutsawa tace,

"Wannan yarinyar kirkin ce ta bani."

Dr ya sami kan kujera ya zauna idonsh akan mamar yace, "Ai shikenan kuma mama kinyi kud'i kin barmu."

Mama ta kalleshi fuskarta d'auke da kallon son Dr yayi mata k'arin bayani, Dr yana dariya yace,

"'yar k'auyen da kuka hana ni aure ce tayi maki kyautar kud'i nera na gugar nera har dubu d'ari biyu."

Ba shiri mama ta k'walalo idanuwa tareda sakin baki tamkar wata sakarya, Dr ya tabbatar mata da abunda yaga an rubuta a jikin check d'in, aiko sai ga mama ta tashi aguje ta koma masai saboda tahowar wani lafiyayyen zawo da ya k'ara kawo mata ziyara, minti biyar a tsakani sai gata ta fito tana dafa bango ta zauna idonta akan Dr tace, "Don ALLAH ka yafe mani cutar da kai da mukayi, don tabbas wannan yarinya ba k'ashin yadawa bace, inda hali don ALLAH kaje ka dawo da soyayyarku wallahi nayi danasanin hanaka aurenta da mukayi, kana gani dai ko shi babanka tun ranar da yaji 'yar wace, yake sukuku tamkar wani mara lafiya saboda takaicin wannan abun kunyar da muka tafka."

Dr yayi murmushi yace, "mama ina son ki gane da da yanzu ba d'aya ba, domin kuwa ke kanki kinsan izzatu tafi karfina wallahi, ko ba komi zan tayata yiwa marik'anta halacci saboda akwai D'ansu da nasan yana sonta sosai kuma itama tana sonshi, kuma shima malam yasan da wannan soyayyar tasu, amman duk da haka yayi biris ya rufe ido yaso ya auraman izzatun ya hanawa d'anshi, sai gashi kwatsam kunzo kun wargaza komi to kinga yanzu nima na gano izzatu bata dace da kowa ba sai Garzali, zanyi farinciki sosai idan naga ta aureshi saboda nima in zama d'an halas in sowa d'an uwana abunda na sowa kaina."

Mama tayi zuru tana kallonshi na d'an lokaci sannan tace,

"K'awarta fa da suka zo?"

Dr ya sosa kai yana dariya yace,   "ita kuma yanzu kike so ki aura man? ina bintar anfasa da ita kenan.?"

Mama tayi masa dak'uwa tace,   "kai kanka kasan wannan tafi binta komi, don haka in har dama tak'iya ai sai a koma hauni."

😝😝😝😝😝Moddiya'i

Akafta😹

D/Auta ce🤝🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*TAURARI WRITER'S ASSOCIATION*

*BAKON YANAYI littafi ne mai cike da ruguntsumi rikici hargitsi tareda nishandarwa sannan ga fadakarwa kada ku bari abaku labari saboda takunshi daban yake da na saura💃🏾💃🏾💃🏾💃🏾💃🏾💃🏾💋*

*PAGE FIFTY THREE*

*********************

Dr ya tashi zai fita yana dariya saboda ganin yanda mama ta rud'e da yawa, har yakai k'ofa ya waigo yace, "A cikin dubu d'ari biyu d'in ni nawa ne kaso na?, koko gidan marayu zaki bada akai domin kema ki bada taki gudunmuwa ki sami lada.?"

Mama ta k'ara damk'e check d'in tace, "Wai yau nice na zama abur tsokana a wurinka hashim?, to wallahi ka kiyayeni da wannan zance tun ban sab'a maka ba, ai ita d'iyar arzik'in da ta bani tasan da gidan marayun tazo ta kawo man har gida, don haka idan ka kawoman wasa ko k'wandala bazan baka a ciki ba."

Dr ya zaro ido a waje yace, "to shi auren da zakiyiman fa wazai siyo kayan lefen?"

Mama ta galla masa wata jar harara sannan ta tashi tsam ta shigewarta d'aki, ta barshi anan yana murmushin jin dad'in ganin mahaifiyarshi ta gano kuskurenta.

**

Izzatu kuwa koda ta koma gida bayan ta huta ta jawo wayarta ta dannawa yayanta kira, bayan sun gaisa ne yake yimata ya hanya sannan suka b'uge da firar su ta masoya mai cike da shauk'in juna, anan ne yake sanar da ita saura wata biyu su k'are service amma kafin nan zai zo yaga gida sai ya koma, ba shiri ta kwalla wata k'atuwar kuwwa daidai da shigowar shu'aib, ilham ma dake gefenta tana bacci ta falka a firgice, sai ga Amma da gudu ta k'araso d'akin nata tana tambayarta lafiya?, izzatu ta ture ilham dake a jikinta rakub'e taje ta ruk'unk'ume ammaah tace, "YAYANAh! ne zai zo kwanan nan Ammaah."

Ammaah ta rik'e baki tana mamakin wannan soyayyar dake tsakanin izzatu da Garzali, kafin tace wani abu sai kawai sukaji an buga tsaki tareda rufo masu k'ofar da k'arfi tace garam, dukansu suka bi shu'aib da kallo ammaah kanta bata ji dad'in abunda yayi ba, amma ita kam izzatu duk da taji haushi tayi kamar abun bai dameta ba, tana ta tsallen murnarta tana jin dad'in zuwan sahibul kalbinta Garzali.

Aiko anan amma ta biye ta suka shirice ana lissafin irin tarbon da za'a yi masa idan yazo, har su fahat da Ammar suka zo suma aka yita cafta dasu suna tsalle.

Suna cikin wannan firar ne wayar izzatu tayi k'ara alamar shigowar text, da sauri ta d'auka ta duba domin a tsammaninta yayanta ne, sai kawai taga an rubuta kamar haka, "ki sameni a garden ina jiranki."

Aiko ba shiri ta buga wani tsaki saboda gane number'r shu'aib da tayi duk da batayi saving d'inta ba amma ta rik'eta saboda yanda yake yawan damunta da kira da turo text's kala kala,

ammaah ta kai dubanta gareta tace,    "Keda waye kike tsaki kuma.?"

Izzatu ta b'ata fuska tace,,  "Ni na rasa ta ina ma wannan mahaukaci ya sami number ta, haka kawai ya bi ya dame ni da kiraye kiraye yanzu gashi ya b'ata man rai ina tsaka da farincikina."

Amma duk da tasan wa take nufi amma hakan bai hanata tambayarta ba tace,

"Wanene shi.?"

Izzatu ta wani zunb'uro baki tareda k'ara tsuke fuska kamar tayi kuka tace,

"Wanene kuwa banda wannan k'aramin yaron."

Amma taso tayi dariya amma ta mazge tace,

"To ai ni kinma k'ara sani a duhu izzatu shi yaron bayada suna ne.?"

Izzatu ta juya fuskarta a gefe tace,    "yaronki shu'aib mana, don ALLAH kice dashi ya daina matsaman nidai wallahi banason wannan takurar da yake yimani."

Ammaah tayi murmushi mai sauti tace,      "Zan ja masa kunne sosai akan hakan amma yanzu me yace ne da har ranki ya b'aci da yawa haka.?"

Izzatu ta fara hawaye tace,    "Wai in zo garden yana jirana."

Amma ta fara share mata hawaye tace,   "Yi shirunki barni dashi zan yi masa fad'a amman yanzu kije kiji kiran me ne yake yimaki."

Izzatu ta zaro ido a waje tace,    "Wallahi amma idan naje cuta ta zaiyi kina gani fa ko jiya ina falonki sai da yaga kin tashi ya take mani k'afa na dad'e ban daina jin zafin takin da yayiman ba."

Amma ta b'ata fuska tace,    "Eh lalle bai kyauta ba naji yanzu tashi kije sai ki kiraman shi kuzo tare."

Izzatu ta tashi tana cin magani taja takalminta ta fita,  koda taje garden d'in ta iske shi yana ta game a wayarshi,taja gefe ta tsaya tana galla masa wata k'atuwar harara, da taga bai masan tazo ba tayi wata zabura tareda watsa hannuwa duka biyu a saman kanshi  kamar zata buge shi  tace,     "wai baka ganni bane da zaka kirani inzo kayi banza dani."

Aiko a razane shu'aib ya zabura kujera tayi baya dashi sai gashi da yin tullu ba tsuntsu har sai da ya wuntsila, saboda ya tsorata sosai da jin wannan murya a saman kanshi, don shi sam baiji zuwanta ba.

A cikin k'ok'arin b'oye dariyar da tazo mata ne tace, "Kai ashe ma lusari ne bani da labari? kuma a hakan kake hurar hancin wai kai namiji ne cab wallahi da sake don nikam banga namiji ba anan ba, don ko wata macen ma ta fika jarumta daga wannan 'yar magana sai a sami tik'ek'en k'ato a k'asa?, wallahi girma dai yayi boris to hajiya ki tashi a haka kina ta kallona ammaah tana nemanki."

Tana k'are fad'ar maganar ta tara wata tafiyar iskanci tana kyalkyalar dariya, koda ta sami ta b'ullewa ganinshi, aiko me izzatu zatayi ba dariya ba har sai da takai k'asa dafe da ciki tana yi musamman idan ta tuno da wuntsilar da yayi wando ya sab'ule, tana cikin dariyar ne taji an rik'o ta da k'arfi ta zabura ganin shine tayi saurin d'aure fuska tareda mik'ewa a tsaye tace, "lafiya malam zaka rik'eni a haka sai kace wadda tayi maka sata.?"

Shu'aib ya k'ara matso ta jikinshi tareda fesheta da wani kallo yana k'ok'arin saka bakinshi a nata, aiko a cikin wani karfi da batasan tana da shi ba, ta d'aga k'afa ta bugi mazantakarshi, aiko sai ga shu'aib a k'asa dafe da wutsiyarshi yana kururuwar ta kashe shi, ALLAH yasa wurin ba mutane izzatu tayi masa wani kallon reni tace, " wallahi idan baka kiyayeni ba sai na kassaraka a gidannan d'an iskan banza kawai mai tarbiyya irin ta mutanen banza, kai waye da zaka had'a bakinka da nawa dakikin banza lusari mai siffar mata."

Sai da ta had'a masa da wani shuri da k'afarta sannan ta fara tafiya zata shige, sai kiran sunanta yakeyi amma ko waigowa bata yi ba ta tafiyarta abunta, ta barshi a nan yana murk'ususun neman taimako.

**

A gidan su malam kuwa Amina ta kwashe duk abunda ya faru a zuwan k'auye komi ta fad'awa mama hassatu, mama sai jin dad'i takeyi ganin irin taimakon da izzatu taje tayi a k'auyen, saboda ita kanta mamar 'yan gidansu sun kirata suna fad'a mata irin kyautar bajintar da tayi masu, bancin gyaran gidan da tasa aka yimasu a tare da su mai unguwa, taji dad'in abun sosai sai gashi kuma amina tana yimata wannan bayanin, bayan sun k'are zancen ne Amina ta ce, "Mama waiko kinsan muntafi gidansu Dr hashim.?"

Mama ta zaro idanuwa tace, "Me kuka je yi a gidan ni hafsatu.?"

Amina tana dariya ta kwashe komi ta sanar da mama, aiko itama tayi dariyar mamar Dr saboda jin yanda ta rud'e, mama tana dariya tace, "kun kyauta sosai da kukaje kuka nuna mata cewa jiya ba yau ba, kodon ta hankalta tabi duniya a sannu, saboda in kaine yau to ba kai bane gobe duk yanda kaga mutum kar ka rena matsayinshi, saboda arzik'i na ALLAH ne shi yake rabawa ya baiwa wanda yaso,saboda ikon shi ne kuma ganin damar shine, ba wai don yafi son wanda yabaiwa arzik'in ba, saboda wani zubin ma ana ajiyeka a wani matsayine saboda a jaraba imaninka, idan ka canye jarabawar ka tsira idan ka butulce masa ka dinga d'agawa kana nunawa wanda bayada alfakhari sai ya karb'e baiwarshi ya barka gaya ka koma a gareshi kana

kaskantacce, ALLAH ubangiji ya k'ara bamu wadatar zuciya ya azurtamu da ayukka kyawawa kuma ya yafe muna kuskurenmu. "

Amina tace,    "Ameen mama."

Daga nan suka shiga firar su wadda duk rabi yabon izzatu da iyayenta ne, suka yita zuba masu ruwan addu'o'i tamkar zubar ruwan sama masu k'ank'arru.

**

Iya kulu kuwa ana nan anata fafatawa da mari da kuma shalelenta Abu,  saboda a yanzu idanuwan mari a bud'e suke tsaf bata wani shayin iyar, sabida tun ranar da Abu ya sakata a d'akinshi ya rabata da budurcinta, to tun aranar haka take jinta daidai da kowa ma a gidan, saboda yanda Abu yake zuwa ya sato kud'i ko na iyar ko a waje idan sunje operation shida abokan sana'ar shi, a haka zai yita yiwa mari b'arin kud'in tana b'oyewa,  amma da sharad'in duk ranar da zai kwanciya da ita idan sun k'are zai bata wata k'wayar hana d'aukar ciki tasha.

Iya kulu ko a duk lokacin da sukeso su soye d'in, sai su zuba mata maganin bacci a lemu ta kwankwad'e tana lasar baki, ba tareda tasani ba aiko anantake take bugewa tayi ta sharar bacci su talallabeta su kaita d'aki su ajiye akan gado, musamman idan sunsan ba anan malam zai kwana ba, aiko sai su rufe gida suyita cin junansu suna kuwwa ba wanda zai jiyo sautinsu, saboda akwai tazara a tsakanin sashen iya kulu da na mama hassatu.

Saboda Abu tun yana biyar k'ananan b'arayi suna sace sacensu a garin, har suka tab'a zuwa a wani gida sukayi sata aka kamasu aka rufe ko su malam basu sani ba, saboda tunda suka dawo birni wani zubin sai yayi sati baya kwana a gida, ko malam ya tambaya ina yake sai iya ta kare shi tace kullum a gidan yake kwana yana dai sammakon fita ne, tun malam yana damuwa har ya zuba mata nagani ita da d'anta.

To acen gidan kason ne ya had'u da gawurtaccin 'yan fashi suka k'ulla alaka, bayan fitowarsu suka jone dashi  yanzu haka har 'yan fashin yake biya suje operations a manyan titunan garuruwa.

To shiyasa yanzu yake sakarwa mari kud'i itako tana k'ullawe ta b'oye in kande tazo ta bata a b'oye tayi ta jin dad'i, ta karb'e ta tafi tana saka mata albarka shiyasa duk bayan sati biyu sai kande  tazo gidan, duk da D'an karen wulakancin da iya kulun take yimata bata gani, saboda tasan abunda yake kawota ta koma gida tana ta murna kwagirinta a cike fam, sannan uwa uba ganin yanda Mari ta canza a lokaci d'aya tayi jiki tayi fari alamun hutu sun bayyana a jikinta.

Ita kanta iya kulu lura da tayi da yanayin marin ya canza ne ta fara tunanin, kodai satar namanta takeyi tana b'oyewa ta canye a d'aki bata sani ba, sannan tayi  tunanin wane mai ne mari   take shafawa wanda ya karb'eta ya maidata haka?, itama ta samoshi ta dinga shafawa ta k'ara yin

kyau.

Hmmmmmm su duniya manya🤔.

Akafta👍🏻

D/Auta ce🤝🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI 🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*
*Bakan Gizo*
Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏻*

*PAGE FIFTY FOUR*

*********************

Dak'yar shu'aib ya samu zafin ya lafa masa ya tashi a hankali ya lallab'a domin yaje yaji kiran da Ammaah take yimasa, amma a zuciyarshi sai tsinewa izzatu yakeyi tareda cin alwashi kala kala akanta, koda ya shiga ya iske izzatun a saman cinyar ammaah tana sharar hawaye, ita ko amma sai lallashinta takeyi tsaye yayi yana kallon abun takaici, ammaah tana d'aga kai ta ganshi a tsaye sai hararar izzatu yakeyi  ranta ya kara b'aci a cikin fushi tace dashi,

"Wai kai yaushe zaka yi hankali ne? Kabi ka takurawa yarinya me ta tare maka dashi ne a gidan?, wallahi ka kiyayeni tun kafin in sab'a maka meye amfanin mugunta yanzu daga na aiketa ta kiran ka shikenan sai kawai kayi ta jibgarta,  akan me? wane laifi tayi maka? Wanda har ka kasa yafe mata duk inda ka ganta sai kaci zalinta."

Shu'aib baki ya sake yana kallon bakin ammaah yanda take ta fad'a, bayan ta kai k'arshen maganarta ne ya kalli izzatu a cikin mamaki yace,   "Me kika ce mata nayi maki.?"

Izzatu ta tashi zaune ta murzar idanuwa hawaye suna zuba kamar gaske tace,

"Yanzu har ka mance irin dukan da kayi mani?, yanzu haka ma marin da kayi man gefen fuskata zafi yakeyi duba ki gani ammaah wurin har ya kunburo fa."

Amma ta k'ara hawa tareda duba gefen fuskar izzatun  tace,     "Yi shirunki ALLAH ya cece shi banga komi ba da yanzunnan sai na rama maki marinki."

Shu'aib ya zaro idanuwa a cikin firgicin maganar ammaah yace,   "yanzu ke Kin yarda na doketa? To wallahi NI itace ma tayi man mugunta, amma ban kawo k'ararta ba sai ni zata k'alawa sharri."

Ya k'are maganar yana yi mata wani kallon zaki sani, izzatu ta murgud'a masa baki tace,
"Idan har da gaske kake to ai ka fad'i abunda nayi maka d'in."

Shu'aib yana jin haka gabanshi ya fad'i saboda yasan akwai wani k'ullin da takeso ta warware shiyasa tayi masa wannan tambayar, aiko ba shiri yayi k'wafa ya juya a cikin fushin dake shimfid'e akan fuskarshi, saboda har ga ALLAH yana jin haushin yanda izzatu  ta rena shi, k'ara kusanta kanshi da yakeyi da ita a kullum renin k'ara k'aruwa yakeyi, ya rasa ta wace hanya zaibi ya shawo kan matsalar saboda rashin jituwarsu yana damunshi sosai, gashi a kulum Abbanshi sai nanaci yake yimasa akan rashin biyan buk'atar shi har ranshi zai iya salwantarwa, shi kanshi yanzu tsoro Abban yake bashi saboda ganin yanda idanuwanshi suka rufe ruf da son cikar wannan guri nashi, musamman da yaji labarin irin b'arin kud'in da izzatu take yiwa wa 'yan k'auyensu da su malam.

***

Ammaah ta shiryawa izzatu bikin murnar zagayor haihuwarta, wato birthday  d'in cika shekara sha tara dam! dam! amma ta hana kowa ya sanar da ita, ko garzali a b'oye tayi waya dashi ta

sanar dashi aiko yaci alwashin a ranar ma zai diro shima domin ayi dashi, amma ta gargadeshi akan kada ya fad'awa izzatu saboda tana so tayi mata surprise, aiko da Ammi da mama hassatu sai shire shiren birthday d'in sukeyi, idan ma tagansu suna k'us da su ammar da fahat ta tambaya sai ace mata ba komi har taji haushi ta fara fushi.

A ranar da za'ayi birthday d'in amma tace da ita taje tayi wanka ta shirya ta rakata wani biki, izzatu tana ta jin dad'i tace, "Bari inyi sauri in shirya kada sarakan yawon cen suce zasu biyomu."

Amma tana dariya tace, " da ita ai su sun ma fita tare da Amminsu kije kiyi sauri ke kawai ake jira ga ma wata mai kwalliya nan tana jiranki zata shiryaki, saboda bikin na musamman ne ina so kifi kowa had'uwa a wurin."

Aiko da jin haka ta fad'a wanka a gurguje tayo ta fito saboda d'okin ayi aje bikin, koda ta fito wankan taga mai kwalliya tana jiranta, ba b'ata lokaci aka shiga tsantsara mata kwalliya kafin kace me izzatu ta fito tamkar wata 'yar indiya, saboda wata 'yar kantin rigar da ta saka har tana ja a k'asa, tareda wani d'aurin d'ankwali da aka nad'a mata tamkar ba hannu yayi shi ba, ga kunne da wuya da tsintsiyar hannunta sun sha gwalagwalai sun k'ara haskata tamkar wata a cikin taurari.

Ita da kanta da ta kalli madubi ba k'aramin kyaun kanta tagani ba tana ta tsallen jin dad'in zata hade a wurin taron bikin, ammaah itama ta fito da shigarta ta alfarma suka rankaya suka shige mota tareda rakiyar security's da motocin sojoji, suna shiga harabar wurin da za'ayi birthday d'in taga motoci fululu gasunan birjiki na alfarma, a cikin zumud'i ta fito tana wani taku a hankali saboda rigar da ta d'an d'age ta da hannun, sannan ga talkamin dake k'afarta masu shegen tsini amma ta rik'a hannunta suka shiga k'aton hall d'in da za'ayi birthday d'in, suna shiga suka tarar da wata 'yar karamar fitila da su kawai take haskewa, izzatu ta ri'ko hannun ammaah a cikin jin tsoron ganin wani dake takowa a hankali izuwa wurinsu, ammaah tayi dubarar janye jikinta ta shige duhun itama, izzatu ta waiga bata ganta ba da sauri ta juya zata fita aka dallaro haske ko ina ya gauraye tareda had'a muryarsu gaba d'aya suka ce, "Happy birthday to you" da sauri ta juya idanuwanta sukayi karaf da yayanta dake a tsaye hannuwanshi a cikin aljihu yana yi mata wani kallon da su kawai suka san ma'anar shi da sauri ta dafe bakinta alamar mamaki sannan ta d'aga murya tace, "wow."

Aiko a million taje ta rungumeshi wuri ya barke da tafi tareda saka wata had'ad'd'iyar wak'ar birthday da akayi dominta kawai, ana ta buga wasu gangunma masu amsa amo mai dad'in saurare a kunnuwa, Garzali ya b'anb'areta a jikinshi ba don yaso hakan ba ya ri'ko hannunta suna tafe sai k'are masa kallo takeyi har suka je wajen da aka tanada na musamman domin yanka wani k'atoton cake mai zanen sunanta, da wani had'ad'd'en candle mai bada wasu kalolin wuta suna tartsatsi a sama, mutane suka zagaye ta sai d'aukar pic's sukeyi masu video suna yi, Garzali yayi mata nuni da ido ta duk'a ta hure wutar da baki aka saka tafi raf! raf!, sannan ya d'auko wata 'yar k'aramar wuk'a da tasha ado ya mik'a mata ta feshe shi da murmushi sannan

ta saka hannu ta karb'a, ta saita wuk'ar zata yaka Garzali ya aza hannunshi akan nata, shu'aib dake a tsaye haushi kamar ya kar shi shima ya zulo ya aza nashi hannun a saman na Garzali, suka yiwa juna kallon ido da ido shu'aib ya galla masa harara yayinda garzali ya feshi shi da murmushin mugunta mai cike da tura haushi.

A tare dasu duka su biyun izzatu ta yanko cake d'in, ta d'auko k'iren cake d'in da ta yankan ta d'an gutsura sannan ta nufi bakin shu'aib dake kusa da ita, saboda shiga tsakaninta yayi da Garzali shu'aib ya bud'e baki a cikin alfakharin shi zata fara ba, amma ta buga masa wata harara takai dubanta ga fuskar Garzali da sai wani annuri ke fita a cikinta, ta feshe shi da wani tsadadden murmushi ta nufi bakinshi da cake d'in aiko ya saka hannu biyu ya k'ara rik'o hannun ta tura masa cake d'in, aiko sai tafi ya karad'e wurin shu'aib ya bisu da wani kallo a cikin wani bak'in ciki da ya mamaye masa zuciya, ya kallesu yayi k'wafa ya bar wurin fuu ya fita hall d'in ma gaba d'aya, izzatu tayi kamar batasan yayi ba daga nan aka ci gaba da 'yan raye raye da pic's kala kala, ana cikin shagalin ne wayar Garzali tayi k'ara alamar ana kiranshi, koda ya d'aga wayar sai baya jin me ake fad'a sabosa ruguntsumin kid'an dake tashi, hannunshi a cikin na izzatu yace da ita ta jirashi yazo ba don taso ba ta sake shi ya fita da sauri wayar shi a manne da kunne yana magana.

Fitowarshi keda wuya ya d'an rab'a wani sak'o yana magana yaji an saka masa wani abu an rufe masa fuska, wayarshi ta fad'i anan mutane kusan biyar suka rufu a kanshi suka daddaure shi suka ja shi a cen bayan hall d'in, suka yar daga nan suka yi ta jibgarshi har sai da suka tabbatar da ya lallasu sannan suka bud'e k'yallen da suka rufe masa fuskar dashi, suka ci gaba da jibgarshi yayi minti biyar idonshi a rufe sannan ya d'ago ya k'are masu kallo d'aya bayan d'aya, a cikin zafin nama yayi ciki da wani ya kada shi ya haye yana so ya kunce d'aurin ya jibgi wanda ya kada d'in 'yan uwan shi suka yi ta kai masa duka yana karewa har ya samu sa'ar ciro hannuwanshi daga d'aurin aiko yayi ta kaiwa wanda ke k'asa duka na hauka har sai da yaga yayi mashi damage ga fuska, sannan ya koma ga sauran suka yi ta d'auki ba dad'i da guda guda yayita raunatasu, domin idan ya lik'ewa d'aya har sai yaga yaci galabar shi sannan ya koma wurin wani, d'aya daga cikinsu ya ciro 'yar k'aramar wuk'a ya zo yankawa Garzali a ciki ya rik'e wuk'ar da hannunshi ta yankeshi har jini yana zuba, sannan ya kai masa duka a hannunshi da k'arfi har sai da hannun yace k'as! alamun ya karye, aiko ya fad'i a wurin yana kuwwa wanda kuwwar ce ta janyo security's dake wajen hall d'in karasowa wurin, Garzali ya fad'i a k'asa ba shiri saboda jigatuwar da yayi hannunshi sai tsiyayar jini yakeyi.

Akafta 🏃🏻‍♀️

D/Auta ce🤝🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI 🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*
*Bakan Gizo*
   Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏻*

*FIFTY FIVE*

**********************

Izzatu kuwa idonta a k'ofa sai kallon ta inda yayanta zai b'ullo takeyi, idan har wani ya rufe mata inda zata hango k'ofar da kyau har wani tsalle takeyi domin kawai taga shigowarshi, da ta gaji da wara idon ne ta ji shirun yayi yawa har lokacin bai dawo ba, ta d'age rigarta ta fara taku a cikin sauri zata fita hall d'in,Ammi da ammaah  idanuwansu da suke a kanta tareda duk wani motsinta a wurin,  saboda akan idanuwansu Garzali ya fita yana waya, kuma sunga yanda ta damu da rashin dawowar tashi shiyasa ammi ta yi saurin biyota tareda d'an d'aga murya ta kira sunanta, da sauri izzatu ta waigo ta kalli Ammi dake k'ok'arin k'arasowa wurinta fuskarta a d'aure tace da ita,    "Ina zaki je ne.?"

Izzatu ta fara 'yan kame kame Ammi tayi mata wani kallo tace,

"Ki rage wannan zumud'in da kikeyi yayi yawa fa, saboda ba'a nunawa namiji tsantsar so a fili ki kiyaye."

Izzatu ta sunkuyar da kanta saboda jin kunyar idanuwan Ammi da ta gano wurin garzali zataje, Ammi kam tana k'are maganar ta shige taron ta barta anan ammaah da ke tsaye a bayansu kad'an, saboda ganin Ammi tana yiwa izzatu fad'a yasa bata k'araso ba don bata so ta shiga hak'k'in su, har sai da taga wucewar Ammi'n sannan ta k'araso wurin izzatu tareda ri'ko hannunta suka fito hall d'in.

Fitowarsu keda wuya izzatu ta fara waige waige bata hango yayanta, ba sai idanuwanta da sukayi caraf da wayar garzali dake yashe a wurin, duk da ba wani tantance wayar tayi ba amma zuciyarta ta bata cewa wayar yayanta ce, jikinta har rawa yakeyi taje ta d'auki wayar tareda duddubata a cikin tashin hankali ta kira ammaah tace,

"Zo kiga wayar yayana wallahi amma jikina yana bani ba lafiya ba, tunda da wayar ya fito yana ta magana amman yanzu gata a k'asa shi baya nan."

Ta k'are maganar tareda zubowar wasu hawaye masu zafi akan fuskarta, amma ta k'araso idanuwanta akan wayar itama zuciyarta a cike da wasi wasi saboda ta hango lokacin da zai fito yana wayar itama, da sauri ta jawo izzatu a jikinta tana lallashi tareda yimata kalamai masu kwantar mata da hankali akan cewa ba abunda ya faru , izzatu kanta a kafad'ar ammaah taji kamar sautin duka a bayan hall d'in, da sauri ta d'ago jikin ammaah tayi bayan da gudunta aiko zuwanta yayi daidai da wani security da ya tallabo garzali a jikinshi saboda raunin da yaji a hannu jini ya zuba sosai har ya fara bugar dashi yana mashalo.

Aiko a d'ari ta kai wurinshi tareda k'walla kiran sunanshi tana jijjigashi tana kuka,idanuwanta suna kai ga hannunshi da har lokacin bai bar d'igar jini ba aiko ta k'ara rud'ewa ta ri'ko hannun tana hura masa iska a baki tana kuka, me ta tuna a zabure ta saki hannun ta jawo leb'en rigarta da yake ja ak'asa ta yago da k'arfi har sai da hannunta ya yanke, kasancewar rigar wani yadin material ne mai arnen kyau ga k'wari, aiko ta saka shi ta fara d'aure masa hannun dashi tana kuka, sannan ta bada umurnin ayi gaggawar kaishi gidansu a nemo masu duba shi jikinta yana kyarma.

Koda ammaah ta k'araso har an fito wajen za'a sanyashi a mota, izzatu a firgice ta shiga motar itama ta zauna tareda aza kanshi a cinyarta tana kiran sunanshi da yayi hak'uri sai sannu take yimasa, a cikin tsawa tace aja motar su tafi, ammaah tana k'arasowa motar tana tashi itama ta fad'a wata motar aka bi bayansu tareda rakiyar wasu sojoji har gida, tun kafin suje aka kira wasu likitoci suna isa gidan suma suna k'arasowa, aka kai Garzali a wani had'ad'd'en d'aki aka shinfid'e akan gado likitoci suka rufu akanshi da kayan aikinsu sai nuna k'warewarsu sukeyi, bayan sun ciyo kan matsalar suka YI masa dressing d'in ciwukan suka yi masa allurar bacci domin jikinshi ya sami hutu.

Izzatu  zaune a tsakiyar gadon sai sannu take zuba masa duk da tasan bacci yakeyi, bayan likitocin sun tafi amma ta k'araso ta zauna a ranta sai jinjina irin wannan  so da izzatu take yiwa Garzali, yanzu ta k'ara tabbatar da maganar da kallah ya fad'a mata akan shak'uwarsu tun suna k'ananu.

Ammaah ta tabbatarwa zuciyarta tabbas soyayyarsu daga ALLAH ce, kuma muddin ana son rayuwar izzatu ta inganta to dole ne a aura mata yayanta Garzali, domin rabata dashi tamkar an jefa rayuwarta ne a cikin had'ari , taci alwashin zata yi iya k'ok'arinta domin ganin tabbatuwar wannan aure nasu.

***

A cen wajen birthday d'in kuwa wad'annan 'yan iskan da suka daki Garzali an watsa su a motar sojojin bayan an lallasasu da kyau, a cikin hall d'in kuwa ba wanda ya lura da izzatu bata nan in ba Ammi ba, aiko sai cashewarsu sukeyi har sai da lokacin tashi yayi aka watse taron, zuciyar Ammi sai tunanin ina Ammaah da izzatu suka je har yanzu da basu dawo ba?, har suka dawo gida tunanin da takeyi kenan ta d'aga waya ta kira ammaah tana tambayarta lafiya?, ammaah tayi mata bayanin duk abunda ya faru da itama taji abakin wani security, tasanar da ita ga inda suke aiko Ammi jikinta yana rawa ta nufo d'akin,  ganin yawan dressing d'in da  aka yiwa Garzali yasa jikin Ammi ya k'ara yin sanyi  k'alau daman ita mace ce mai tausayi, da sassarfa ta k'araso tana k'are masa kallo a cikin tausayawa musamman yanda taga fuskar izzatu tayi ja saboda tsananin kukan da tasha, wanda ita kanta tasan dole ne hakan ta kasance saboda yanda taga shak'uwarsu.

Garzali ko sai sharar baccinshi yakeyi hankali a kwance,ganin hakan yasa Ammaah tace da izzatu ta taso suje su barshi yayi barcinshi a nutse, izzatu ta kafe akan ita dai bazata bar shi shi kad'ai ba, Ammi tayi saurin galla mata harara ba shiri ta sauko gadon ta fita fuu tana kuka, Ammi ta girgiza kai a ranta tace,      "Wannan yarinya a yaushe zatayi hankali ne.? "

Izzatu koda taje d'akinta fad'awa tayi akan gado tana wani irin kuka gwanin ban tausayi, ammaah dake biye da ita a baya ta shigo d'akin tareda k'are mata kallo na tsawon mintuna, sannan ta tako a hankali ta k'araso ta zauna akan gadon,  itama fuskarta a cinkushe ba walwala ta kira sunan izzatun a hankali, izzatu  ta d'ago fuskarta da tayi sharkaf da hawaye tace,
"N'aam ammaah"

Amma ta sauke k'atuwar a jiyar zuciya tace,         "kiyi hak'uri kinji 'yata insha ALLAH zaiji sauk'i, ki kwantar da hankalinki ki tashi ki cire kayanki kiyi wanka ni da kaina zan raka ki wurinshi ki k'ara ganoshi."

Izzatu tayi saurin share hawayenta tace,

"Nagode ammaah tah! Amman yanzu in har ya falka ba kowa fa.?"

Ammaah tayi murmushi har sai da hak'oranta suka bayyana tace,

"Akwai wad'anda zasu kula dashi ko baki nan ke naki kawai kije ki dubo jikinshi ki dawo."

Izzatu tayi saurin fad'awa a jikin ammaaah tana share hawaye tace,      "Yanzu shikenan ni ba sai naje na kwana a cen ba.?"

Ammaah ta zaro idunawa a waje tace,

"Zaki kwana acen amma ba yanzu ba har sai mun d'aura maku aure keda shi."

Izzatu tayi saurin rufe fuska da tafukan hannunta, tareda mik'ewa tsam ta shige toilet tana dariya ammaah ta bita da kallon tana yimata dariya, bayan shigewarta toilet ne ta fito zata shiga d'akinta ne taci karo shu'aib a tsakiyar falonta yana kai da kawo.

Ammaah tayi mamakin ganinshi a wannan lokacin don tasaN baya shiga wurinta da anyi magriba, idonta akanshi ta karaso kafin tayi magana ya rigata da cewa,     "Ammaah wai da gaske ne wannan d'an k'auyen yana  cikin gidannan.?"

Ammaah tayi mashi wani  kallon tuhuma tace dashi,      "Eh ya aka yine?"

Shu'aib ya wayance yace,      "A'a ba komi daman maganar naji nace bari nazo na tabbatar."

A cikin rashin damuwa da maganar ammaah ta fara tafiya zata shige d'aki, sannan wani tunani ya fad'o mata a zuciya ba shiri  tayi saurin waigowa idanunta a kan na shu'aib tace,      "ina fatar dai ba kaine kasa aka yi masa wannan aikin ba?"

Shu'aib yayi wani munafukin murmushi yace,       "Ni miye ruwa na dashi ne?ammaah? Amma fa wallahi na fara gajiya da abunda yarinyar cen take yimani fa, kina kallo fa agaban kowa tayi man wulak'anci bata shayin tozartani ko a ina ne, a hakan zamuyi auren bata ganin girmana.?"

Izzatu dake fitowa a d'akinta jin wannan maganar tayi saurin k'arasowa tareda rik'e kunkuru tace,      "wane aure kake fad'a?ai wallahi da in aureka gara in mutu banyi aure ba, da bakinka ka fad'a kace ko a k'afa aka d'aura maka ni sai ka kunce, wani kalar zagi ne baka yiman ba nida iyayena matsiyata 'yan k'auye?, sai yanzu zaka zo kana wani zancen aure a tsakaninmu.?"

Ta k'are maganar tareda murgud'a masa baki shu'aib ya rud'e saboda ganin yanayin kallon da amma take yimasa, a cikin rawar murya yace,       "Duk abunda kike fad'a ai a ada ne da bansan 'yar uwata bace ke, amma ai  yanzu tunda Abba ya yanke hukuncin zamuyi aure ai kinga duk da bana so na hak'ura zanyi masu biyayya, amman ke a kullum idan baki wulak'antani ba bakya jin dad'i."

Izzatu ta zaro idanuwa tareda kallon ammaah tace, "Kinji ko ammaah da bakinshi yace ba sona yakeyi ba biyayya zaiyi, to bari kaji ni inada wanda nikeso kuma yake sona, saboda haka kai tunda baka so biyayya ce zakayi ka aureni, to kaje an yafe wannan biyayyar akwai hanyoyin samun lada da yawa idan anyi wa iyaye biyayya, don haka ni kam ko kaine autan maza bazan tab'a aurenka ba wallahi, kuma ka sani duk wani k'ulle k'ullenku kai da mahaifinka a tafin hannuna yake k'iris nike jira in fallasa sir.......... "

Karaf Ammi dake tsaye tana saurarensu ta kaiwa izzatu wani bahagon mari, gaba d'ayansu suka juya suna kallonta ammaah ranta a b'ace tace da AMMI, "me 'yata tayi maki ne da zaki daketa?, meye ruwanki a cikin maganar ne? ina fa sane da yanda kike takura mata fa ."

Ammi a cikin damuwa saboda ganin yanda ran ammaaah ya b'aci tace, "Kiyi hak'uri ammaah amma fa kina kallo take ta tsigalewa yayanta, ko ba komi ai ya girmeta ballantana kuma yanzu yana da matsayi biyu a wurinta."

Ammaah ta jawo hannun izzatu suka shige d'aki ba tareda tace da Ammi k'anzil ba, shu'aib kuwa tunda yaji izzatu ta furta tasan sirrinsu shida Abba, wani gumi ya tsattsafo masa tun daga kai har k'afafuwanshi saboda jin tsoron tonuwar asirinsu.

Ammi takai kallonta akanshi duba da yanayinshi da taga ya shiga ne itama ta zargi wani abun aranata, amma ta yi kamar bata gano yanayin da ya shiga ba tace dashi, "Yi hak'uri shu'aib akwai k'urciya har yanzu akan k'anwarka, ka barni da ita ni zanyi maganin abun."

Shu'aib ya fara inda indar fad'in ba komi Ammi nagode, ya YI saurin barin wurin ya fice zuciyarshi sai kai da komo takeyi yana tambayar kanshi me izzatu ta sani dangane da sirrinsu?.

Ammi ta bishi da wani kallo sannan ta shige d'akin ammaah da sallamarta, koda taje ta iske Ammaah sai lallashin izzatu takeyi akan tayi shiru, itama ta sami gefen gado ta zauna sannan ta fara baiwa ammaah hak'uri, ammaah tace, "ba komi amman ki kiyaye takura man yarinya."

Daganan suka fara hira a tsakaninsu Ammi ta kalli izzatu tace, "ke wani sirri kika sani da har kike barazana dashi.?"

Izzatu tayi dariya tace, "Wallahi ni AMMI na fad'a ne kawai amman bansan komi ba nikam."

Ammi tace, "to ki kiyayi irin wad'annan lafuzzan don kar su d'aure ki a watarana."

Izzatu tace, "insha Allahu na daina Ammi."

Daga nan Ammi take sanar dasu abunda ya kawota, saboda su SUDEIS da SADIS da tayi

waya dasu suke sanar da ita saura sati d'aya su dawo gida, saboda sun k'are makarantar gaba d'aya zasu dawo gida kafin lokacin komawarsu su shiga jami'a yayi, saboda har jami'a akwai a cikin makarantar, aiko izzatu tana ji ta fara tsallen murnar ganin 'yan k'annen ta, ammmaah ma taji dad'in jin wannan daddad'an labari aiko anan suka shantake suna ta fira, har sai da izzatu ta duba agogo ta zaro idanuwa tace,

"Ammaah bamuje muka gano yayana ba fa. "
Amma tace da ita tayi sauri taje minti biyar ta bata ta dawo, aikuwa jikinta yana rawa ta fice tana ta sauri akan taje wurin yayanta, kwatsam sai taji an shak'o wuyanta, zata yi kuwa aka dafe mata baki aka jata wani lungu a cikin wata muryar ban tsoro aka ce, "wani sirrine namu kika sani.?"

Izzatu tana jin muryar ta gano muryar shu'aib ce, aiko a cikin zafin nama ta kai masa halbi da k'afa ta baya, ai kuwa sai gashi ya saketa ba shiri ya duk'e yana kururuwa, wasu security's suka k'araso wurin da gudunsu suna tambayar lafiya, ganin izzatu da shi ne yasa suka yi cirko cirko, izzatu ta maka mashi wata k'atuwar harara tace,

"Da nasan kaine wallahi ko tsoro bazanji ba don ni na rena mai siffar mata irinka, wawa kawai lusari sakarai shashasha."

Tana k'are maganar ta buga masa tsaki tayi d'akin da aka ajiye Yayanta,shu'aib kuwa a zuciyarshi sai saka irin kalar fyad'en da zai yimata yake yi, ko don ta gano cewa da gaske shi d'in namijin ne ba yanda ta d'aukeshi ba.

Zaka kirawa kanka ruwa yaro😏.

Akafta🏃🏻‍♀️

D/Auta ce👌🏻

[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*
*Bakan Gizo*
Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏻ga number ta ga mai bukata 09032685442*

*PAGE FIFTY SIX*

*********************

Har ta kai d'akin zuciyarta a cinkushe take amman tana d'ora idanuwanta akan shi farin ciki ya mamaye zuciyarta, saboda ganin yayanta a zaune alamun sauk'i ya bayyana gareshi, saboda Garzali mutum ne shi mai k'arfin halin gaske, duk da ciyukan suna yi masa zafi amman bai bari zuciyarshi ta karb'i zafin ba, saboda zaunen ma da yake yi lokacin zuciyarshi a cike take fam da tunanin su wanene suka yimasa wannan rashin mutuncin?, ya saka wa ranshi ko su wanene sai ya gano wanda ya saka su yi masa wannan renin wayon, duk da zuciyarshi ta bashi cewa Alhaji sani da d'anshi shu'aib ne suka turo aka dake shi, akan wata biyan buk'ata tasu ta daban wadda su kad'ai ne suka santa, amman insha ALLAHU bazai koma ba har sai ya gano abunda suke k'ullawa.

Shigowar izzatu d'akin ya sanya shi jin wani farin ciki, wanda ya kasa b'oyuwa har sai da ya bayyana a kan fuskarshi, wanda yasa shi saurin ajiye k'afafuwanshi k'asa da niyyarshi ta zuwa ya tarbo ta, itama ganin saukowar da yake niyyar yi ne yasa ta k'araso wurinshi da sassarfa, tareda dafe k'afafuwan tana girgiza masa kai idanuwanta cikin nashi, ya k'ura mata kallonshi mai saukar mata da kasala, ido cikin ido yana aika mata da sak'onnin da baki bazai iya misalto su ba, itama shi d'in take kallo ko kyaftawa bata son yi saboda shauk'in son da ke gudana yana cikin jininta, yana k'ok'arin zagaye dukkan wata gaba dake dake aiki cikin jikinta.

Ganin irin kallon da yake yimata ne ta huro iskan daga bakinta ya sauka cikin k'wayar idanuwanshi, ba shiri ya lumshe idanuwan na d'an lokaci, sannan ya bud'e su suka k'ara sauka

tar akan fuskarta, ba shiri izzatu ta kai kallonta akan kulolin abincin dake ajiye reras  wurin,  ga k'aton Flack's din ruwan zafin dake wurin, sannan da kayan tea reras tamkar wani shago, ba shiri ta sauko ta fara zuba masa abinci tana k'arewa ta dawo kan gadon ta zauna suna facing d'in juna, ta d'ebo abincin a spoon ta kai bakinshi ya yamutsa fuskarshi alamar baya son ci, ta b'ata fuska tareda maka masa wata katuwar harara, ba shiri ya bud'e bakin ta tura masa abincin ya fara taunawa a hankali yana kallonta, bata barshi ba haka tayi ta ciko spoon tana juyewa bakinshi har ya kusan cinye abincin plate d'in, sannan ta ajiye ta had'o masa tea mai kaurin gaske ta bashi ya shanye, sannan ta jawo robar ruwa ta tsiyaya masa a wani glass cup ta bashi, yasha sannan ta ajiye cup d'in ta yunk'ura zata tashi ya yi saurin rik'o hannunta, yana k'ok'arin yi mata magana ne sai ga kira ya shigo wayarta, da sauri dukansu suka kai kallonsu akan wayar dake ajiye saman gadon, jiki ba kuzari izzatu ta zura d'ayan  hannunta ta d'auko wayar, ta duba taga ba suna a number duk da ba kowa ne yasan number'r ba , shiyasa tayi mamakin ganin sabuwar number, har wayar ta tsinke bata d'aga ba aka k'ara kira na biyu sai da ta kusa tsinkewa sannan ta d'aga, batareda tace kanzil ba tayi shiru tana sauraren mai maganar, tana gano muryar mai kiran tayi saurin kallon Garzali tareda dafe baki, a cikin rud'ewa tace,   "Akwai abunda nikeyi  zan kira anjima" tana k'are maganar k'itt ta datse kiran, idanuwan Garzali akanta, zuciyarshi cike da tunanin waye ne ya kirata?, suna had'a idanuwa izzatu ta share gumin da ya jik'a mata fuska tace dashi,    "Zan wuce sai da safe yayanah!"

Garzali ya saka hanu biyu ya jawota ta zauna dab'as akan gadon, tareda tsareta da idanuwa yace

"Yanzu k'anwata ni kike yiwa b'oyo? Wanene ya kiraki da bakya so nasani.?"

Izzatu ta marairece fuska tace,    "Plss yayanah!."

Garzali ya b'ata fuska tareda shan mur sosai yace,     "To muga wayar."

Jikinta yana rawa ta mik'a masa wayar kamar wata wawuya, ya karb'a tareda danna kira ga number'r kira d'aya a na biyu akayi caraf aka d'auka, Garzali ya saka hand's free sai ga muryar Dr tartar ta fito cikin wayar, Garzali yakai kallonshi gareta tareda yimata alamu da idanuwa akan ta amsawa Dr sallamarshi, aiko muryarta tana rawa suka gaisa sannnan Dr ya fara magana kamar haka,   "Tun ranar da kuka zo naso in kira ki amman nace dai bari in d'an d'aga k'afa, don kada na dameki duk da abunda yake damuna a zuciya, sai gashi yau naji kinyi birthday ko gayyata babu nace bari na kira na taya murna, to congratulations Allah's khair nown and forever."

Izzatu ta fad'ad'a fuskarta da murmushi tace,    "tank's"

Sannan Dr ya ci gaba da cewa,    "ranki ya dad'e wata alfarma nake nema a wurinki."

Izzatu ta zaro idanuwa tareda jin wani sabon jib'i ya karye mata duk da Ac'n da ya sanyaya d'akin, ta d'ago idanuwa ta kalli yayanta alamar rok'o amma ya kafe ta da idanuwa alamun ba

sauk'i, sannan ta share gumin fuskarta tace, "OK ina saurarenka."

Dr yana murmushi mai sauti yace, "Amina nike son kiyi man hanyar da za ta cike mani gurabun da kika barni da su, don nasan yanzu ke kin mani nisa amman in da hali a taimakeni Amina ta maye mani gurbinki"

Ba shiri izzatu ta sauke ajiyar zuciya cikin farin ciki tace dashi, "In dai wannan ne baka da damuwa akai yanzu zan turo maka number'rta sai ka kirata ina maku fatar ALKHAIRI."

Tana k'are maganar ta kashe wayar gaba d'aya ta tashi fuu zata fita, Garzali yayi saurin shan gabanta tareda kama kunnuwanshi alamar ban hak'uri, izzatu ta tureshi zata bar d'akin yayi saurin ri'ko hannunshi mai ciyo yace, " wash hannuna."

Aiko sai gata ta juyo da sauri ta rik'o hannun tana yimasa sannu jikinta sai rawa yakeyi, Garzali ya k'ura mata idanuwa ko k'iftawa baya yi, ita ko jin yayi shiru ne ta d'ago fuskarta tana kallonshi taga yanayin yanda yake kallonta, da sauri ta kai masa duka a kirji ta fice da gudu, Garzali ya k'yalk'yale da dariya mai sauti tareda girgiza kanshi ya sosa k'eya, tareda fad'awa toilet yana 'yar wak'arshi kamar ba shine d'azu aka kwaso magashiyyan ba.

Izzatu ko tana shiga d'akinta ta fad'a kan gado tana jin wani irin farin ciki marar musaltuwa, saboda a koda yaushe soyayyar yayanta k'ara linkuwa take yi cikin zuciyarta, koda basu tare ballantana yanzu da suke gaf da gaf suna shak'ar numfashin juna.

Shu'aib kuwa abin duniya ya dameshi ya rasa ta wace hanya zai bi ya shawo kan izzatu, ko don biyan buk'atar mahaifinshi duk da a ranshi yana da k'udurin keta haddinta, saboda ya rage takaicin wulakancin da take yi masa kullum safiya, domin jikinshi yana bashi da wuya in har zai yi nasarar aurenta don ganin yanda take k'ulafucin wannan bak'in bak'auyen.

Ya dad'e yana sak'awa da kwancewa shi kad'ai zaune a bayan d'akunan dake katafaren gidan Gwamnatin, inda yake zaune daidai da bayan toilet d'in d'akin da aka saukar da Garzali, saboda bai da masaniyar nan d'akin aka ajiye shi, saboda neman Garzalin yake yi ruwa jallo.

Shiyasa ya yanke shawarar kiran Abbanshi domin ya sanar dashi abunda ke faruwa, Garzali yana toilet yaji muryar shu'aib yana magana da Alhajinshi, a take ya gano muryar shu'aib yayi saurin komawa d'aki ya d'auko wayarshi, ya fara recording d'in firar da yake jiyowa tana tashi a tsakanin shu'aib da Alhaji sani, wadda muryar shu'aib d'in ce kawai yake ji tana fita.

Shu'aib ko ya saki jiki sai zubo zance yakeyi kamar haka, "WALLAHI Alhaji yarinyar nan taurin kan tsiya ne da ita, nayi duk iya yina amman dai har yanzu ba wata jituwa tsakaninmu, har sai k'arin renin wayon da take yimani kala kala, na rasa ya zanyi da ita wallahi yau ma baka ga wulak'ancin da tayi man gaban dubban mutane ba, akan wannan d'an k'auyen wanda ta janyo na had'a shi da su goga suka lallasa shi, amman naji ana zancen wai security's sun kama su sun mik'awa sojojin su yanzu haka suna wurinsu fa, shi kuma shegen ance yana cikin

gidannan nayi ta ta so na gano inda yake amman security's sun k'i bada fuskar hakan, wai Ammi ta basu umurnin kada abar kowa yaje inda yake sai su kawai ."

Shuaib ya sauke numfashi tareda tsayawa yana sauraren abunda Alhajin yake fad'a, sannan ya sauke ajiyar zuciya yace "OK to yayi sai ka zo goben ai gara ayi komi a huta tun kafin wankin hula ya kaimu dare, OK to sai ka zo bye sai da safe OK thanks."

Ya kashe wayar tareda tashi daga wajen yana kakkab'e wando ya koma d'akinshi, zuciyar shi fess saboda tunanin gobe Alhajinshi zaizo akai k'arshen zancen aurenshi da izzatu.

Garzali kuwa murmushi kawai yakeyi bayan ya gama nad'ar firar tasu, sannan ya fito daga toilet d'in ya zauna kan gado yana k'ara sauraren recording d'in.

***

A b'angaren Dr kuwa kwana yayi yana tsumayin ganin izzatu ta turo masa number'r Amina, amman yaji shiru saboda ita gaba d'aya ma ta mance da zancen, saboda ta tafi da yawa tunanin yayanta kuma masoyinta mijinta insha ALLAH Garzalin iya kulu.

Akafta

D/Auta ce
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI 🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*

*Bakan Gizo*
Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏻*

*PAGE FIFTY SEVEN*

*********************

Koda safiya ta waye Garzali da shirinshi yake na zuwan Alhaji sani gidan, domin ya yi alk'awali duk sai ya gano bak'in nufinsu akan izzatu da mahaifinta, aikuwa bayan izzatu tazo sunyi ina kwana ta fita sai ya fito harabar gidan inda k'atuwar rumfar da ake ajiye motoci ya zauna, yana tsumayin zuwanshi aikuwa kamar misalin k'arfe goma na safe sai ga motarshi ta danno kai cikin gidan Gwamnatin, aka yi dace kai tsaye motar ta nufo wurin rumfar, Garzali yana hango motar da sauri ya lab'e bayan wata mota yasha jikinshi, Alhaji sani ya fito sai harare hararen yake yi ya tako ya zo daidai inda Garzali yake a b'oye ya tsaya, tareda jinginawa a jikin motar ya jawo wayarshi ya fara kira, tareda kara ta kunne yace, "Kazo gani rumfar motoci ina jiranka." Sannan ya sauke wayar ya furzar da iska a bakinshi yana girgizar k'afa, minti biyar a tsakani sai ga Shu'aib ya nufo wurin sai sauri yakeyi, Garzali dake lab'e ya kunna wayarshi tareda yi masu video har suka k'are k'usk'us d'in da suke yi, sannan suka bar wajen yayin da shu'aib ya yi cikin gidan shi kuma Alhaji sani ya nufi inda zai gana da mai girma Gwamna, Garzali kuwa yana ganin shigewarsu ya fito yana murmushin mugunta, musamman da yaga videon ya fito rad'au muryoyinsu tartar, sannnan ya koma masaukinshi yana ta nazarin firar da yaji tsakanin Alhajin da Shu'aib, ba shiri ya furzar da iska mai zafi bakinshi sannan ya d'aga hannu ya kaiwa iska naushi, a fili ya furta cewa, "wato dai da gaske Alhaji da Shu'aib ba zaman tsakani da ALLAH suke yi da mai girma Gwamna ba, aiko yaci alwashin bankad'a wannan sirrin har sai kowa ya ganshi.

Alhaji sani da mai girma Gwamna a cikin babban falonshi na cikin gida, bayan sun k'are gaisawa ne Alhajin ya bijiro masa da zancen had'in auren Shu'aib da izzatu, wanda ya riga da ya yanke hukunci tun ranar da izzatu ta bayyana garesu, Abbaah ya yi shiru na d'an lokaci yana nazarin abunda Ammaah da Baba kallah suka sanar dashi, dangane da soyayyar da ke tsakanin Garzali da izzatu, saboda Ammaah ta sanar dashi komi har rashin jituwar da ke tsakanin Shu'aib da izzatun.

A cikin sanyin jiki Abbaah ya fara magana kamar haka, "Alhaji ban k'i ta taka ba amman ina son kasani da da yanzu ba d'aya bane, don haka yana da kyau aji ta bakin su yaran, domin gudun azo ayi abunda za'a yi danasani daga baya, wajen k'ok'arin had'a zumunci sai zumuncin ya zo ya lalace, saboda haka yana da kyau a kirasu a tambaye su idan har sun amince da juna shikenan, sai mu bisu da addu'a tareda yi masu fatar zaman lafiya."

Alhaji saboda jin haushin wannan bak'in tambihi da yake ganin Abbaah yana yimasa, jin yake yi

tamkar ya shak'e shi a wurin koda zai samu matsalar tazo masa da sauk'i, a cikin b'ata rai yace, "Saboda mi zamu tsaya jin ra'ayinsa? Shin su suka haifemu ko ko mu ne muka haifesu?"

Abbaah yayi murmushin kwantarwa da d'an uwanshi hankali yace,

"Kayi hak'uri Alhaji abi komi da tsari yafi bari a kirasu yanzu a gabanmu domin aji ra'ayoyansu."

Yana k'are maganar ya d'aga waya ya kira Shu'aib da izzatu, ai kuwa sai gasu ba b'ata lokaci sun shigo falon, izzatu a firgice take da jin wannan kira musamman da taga Alhaji, ba shiri taji gabanta ya fad'i saboda tuno abunda yake shirin k'ullawa, bayan sun sami wuri sun zauna ne suka fara gaida Alhajin, don shi shuaaib mazgewa ya yi kamar bai san da zancen ba, Abbaah ya yi gyaran murya tareda kiran sunansu, dukansu suka amsa vikin natsuwa domin sauraren abunda zai fad'a, Abbaah ya k'ara kiran sunan su yace, "Kun amince da zancen auren da Alhaji ya had'a a tsakaninku?"

Shu'aib ya d'aga kai yayin da izzatu tayi saurin girgiza kai tareda zubowar wasu hawaye akan fuskarta, dukansu suka maida kallonsu gareta a cikin damuwa Abbaah yace,

"Me kike yiwa kuka bakya son had'in ne ko ya ya?"

Izzatu ta d'aga kai tareda zubowar wasu sababbin hawaye akan fuskarta, Abbaah kanshi ya k'ulle sosai saboda jin kunyar d'an uwanshi, amma ya saka dauriya don baya son ya tauye wa 'yarshi hak'k'i yace, "Magana zakiyi domin musan abunda kike nufi."

Izzatu ta share hawayen fuskarta tace, "A gaskiya ni dai bana son yaya Shu'aib."

Abbaah ya yi saurin fad'in, "Ba kya son shi to wa kike so?"

Izzatu bata ji kunyar kallon idanuwan Abaah ba tace, "Yayana Garzali nike so saboda shine yafi cancanta da ya aureni ko don irin girman halaccin da suka yi mani, don ALLAH Abbaah kada ku aura mani yaya shu'aib saboda samsam ba jituwa a tsakaninmu."

Abbaah yayi shiru na d'an lokaci sannan yakai kallonshi ga Alhajin yace, "To kaji da bakinta abunda tace."

Alhaji da bak'in ciki ya mamaye kafatanin zuciyarshi, a cikin fushi yace, "Eh naji abunda tace amma ai gida bai k'oshi ba ba za'a tab'a kai wa dawa ba, sai dai in har rashin son ba nata ne ita kad'ai ba harda kai."

Daddy ya yi murmushi tareda baiwa su izzatu umurnin su tashi su fita, aiko suna fitowa Shu'aib ya galla mata wata k'atuwar harara yace, "Wallahi bazan tab'a had'iyar yawun banza ba, dole ne sai na nuna maki kuskurenki saboda haka ki kiyayi ranar da zaki zo hannu na."

Izzatu kam gwalo kawai tayi masa ta wuce ta gabanshi tareda juya masa mazauna, shuaib ya bita da kallo a cike da takaici tamkar ya shak'e ta a wurin yayi mata kaca kaca.

Alhaji kam bai jira jin ba'asin komi ba ya tashi ya fita fuu kamar wanda zai tashi sama saboda bak'in cikin da yake ji a zuciyarshi, yana tafe yana cin alwashi kala kala akan wargaza farin cikin Abaah da ahalinshi.

Abba ya bishi da kallo fuskarshi ba wata alamun damuwa, ya latsa wani abu minti biyar a tsakani sai ga Ammaah ta shigo, tana ido biyu da Abbaah taji kirjinta ya buga, saboda tana jin tsoron ace Alhajin yaci galabar Abbaah wajen raba izzatu da Garzali.

Bayan ta zauna Abbaah ya yi mata bayanin abunda yake faruwa, taji dad'in abunda ya faru aiko ta saki jiki ta yi ta kawo wa Abbaah rashin alfanun auren izzatu da Shuaib.

Akafta 🏃🏻‍♀️

D/Auta 👌🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI 🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*
*Bakan Gizo*
Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏻*

*PAGE FIFTY EIGHT*

*********************

Shu'aib kuwa yana d'akinshi sai kai da kawo yakeyi, zuciyarshi a cike fam da bak'in cikin asarar da zai yi ta rashin samun damar, da zai maida k'ulafucinshi akan izzatu, saboda shi ba ma dukiya ce a gabanshi ba shi dai gurinshi kawai ya yi mata kaca kaca, domin ya yi maganin renin wayon da take yimasa, sabida siffantashin da takeyi da mace ba k'aramin k'ona ranshi yake yi ba, aikuwa ya yanke wa zuciyarshi duk abunda zai faru sai dai ya faru amma shi bazai tab'a d'agawa Izzatu k'afa ba da abunda yayi niyya, shiyasa ya fad'a motarshi ya fisgeta a guje ya bar gidan,, da bak'in k'udurinshi a ranshi.

Izzatu ko bayan fitowarta wurin Abbaah haka kawai taji tana sha'awar zuwa garden, saboda fargabar da take ciki na jin tsoron hukuncin da su Abbaah za su yanke akan aurennta da shu'aib, kada su tilastata dole sai ta aure shi ta zo ta bijire suga tayi masu rashin kunya, tasa a ranta muddin aka rabata da yayanta to ita ko bazata tab'a yi masu biyayyar auren Shu'aib ba, tafi so ta tsere ta bar masu gidan gaba d'aya ta shiga duniya matuk'ar ba yayanta za'a aura mata ba, damuwar da take ciki ce tasa tak'i zuwa wurin yayanta don bata son ta d'aga masa hankali, haka ma tak'i zuwa wurin Ammi domin tana jin tsoron ace itama ta goyi da bayan aurenta da Shu'aib, shiyasa ta zab'i keb'ewa ita kad'ai domin ta samu relief.

Tayi zaune akan d'aya daga cikin wasu k'ananun kujerun dake wajen, tareda aza k'afarta duka biyu akan table d'in da ke tsakiyar kujerun, kanta a sama tana nazarin damuwar da ta cinkushe mata zuciya, d'an kwalin dake kanta ya sab'ule ya fad'i k'asa ba tareda ta sani ba, gashin kanta ya zubo sai iska yake k'adashi ta lumshe idanuwa saboda jin dad'in iskan da ke ratsa jikinta, Ummi dake sama tana kallonta haka kawai taji tana tausayin 'yarta ta, saboda tasan duk rikicin da ake saboda izzatu tana sashenta Abbaah yayi kiranta, haka ma a gaban idanuwanta taga dawowar shu'aib har da fitar da yayi duk tana kulaye da shi.

Shiyasa Ammi ta lek'o windown da tasan yanda izzatu idan taso keb'ewa ita kad'ai anan take zuwa tana hutawa, don ko waya take son yi da Garzali wani zubin a nan take zuwa saboda su Ammar don kada su dameta da bari bari.

Shu'aib yana dawowa idanunshi a rufe ya nufi sashen Ammaah bai ga izzatun ba, ya nufi na Ammi nan ma bai ga kowa ba sai su Ammar da suke buga Game suna gardama, ya sauko ya

nufi Garden don zuciyarshi ta bashi izzatun tana cen, duk da yaji tsoron ace tana tare da Garzali yana lek'awa ya hango ta tana waya ita kad'ai, yaji farinciki sosai musamman yanayin da ya ganta ya k'ara zafafa wutar sha'awarta a cikin zuciyarshi, wanda daman cen fitar da yayi maganin k'arfin maza ya nemo sannan ya nufo gidan bayan yasha k'wayun a matse yake da ya yiwa izzatu farkar takarda, wanda har sai takasa moruwa.

Aiko yana zuwa ya tarar ta k'are wayar idanuwanta a rufe zuciyarta cike da farin cikin zuwan da yayanta zai a nan wurin,  sai kawai  taji maganar Shuaib akanta yana cewa,    "Kina nan a kan bakanki na k'in aure na ko kuwa kin canza shawara?"

Izzatu tayi saurin bud'e idanuwanta akanshi, ba shiri gabanta ya fad'i ganin yanda idanuwanshi suka yi jawur da jaraba a cikin dakiya tace,    "Har abada bazan tab'a canza shawarar k'in aurenka ba, kayi duk abunda kaga zaka iya yi domin cikar burinka kai da azzalumin mahaifinka."

A zabure Shu'aib ya damk'o gashin kanta tareda ciro wani hankachief aljihunshi ya Shak'a mata a hanci ba shiri izzatu ta tafi luuu ya taro ta tareda had'a ta da jikinshi ya rungumo jikinshi har rawa yakeyi ya bar wajen.

Ammi dake kallon abunda yake faruwa a cikin tashin hankali, ta bar jikin window'n a guje da nufin kaiwa izzatu agaji, Garzali da  ya nufo garden  d'in yana hango Shu'aib ya shak'awa izzatu wani abu tayi luuu, a cikin tashin hankali ya zo zai tafi wajen me ya tuna ya dawo baya ya lab'e, a gabanshi Shu'aib ya wuce da izzatu tana langab'e  jikinshi, ya biyo bayansh har zuwa d'akin Shu'aib d'in inda saboda rawar jikin ya cimma burinshi, idanuwanshi sun rufe ya kasa jin motsin tafiyar Garzali da ke biye dashi a baya, yana shiga d'akin ya banko d'akin batareda ya rufe ba ya fara tub'e kayanshi ya zama tunb'ur sannan ya fara k'ok'arin cirewa izzatu doguwar rigar dake jikinta, Garzali yana banko k'ofar d'akin idanuwanshi suka kai inda Shuaib ya zaro wandon izzatu zai cire,  a cikin d'imaucewar ganin kyakkyawar  halittar da Ubangiji ya azurtata da samu.

Cire wandon yana daidai da wani naushi da Garzali ya kai masa a kumatu, ba shiri sai ga hakoranshi biyu sun biyo hannunshi a dalilin bala'in azabar naushin da ya kai masa, wanda yayi daidai da shigowar Ammi kamar an jefota d'akin, ganin dukan da Garzali yake yiwa Shu'aib yasa ta isa wurin izzatu da gudunta, a cikin d'imaucewa ta jawo bedsheet d'in  dake shinfid'e kan gadon ta rufe mata jikinta, sannan ta fara wani gunjin kuka a cikin tashin hankali.

Garzali kuwa dukan shu'aib yake yi kamar wani tsohon zaki kafin kace me yayi masa jinajina, zuciyar Ammi a cike take da farin cikin jin dad'in dukan da ake yiwa Shuaib, K'arar dukan da Garzali ke yiwa Shu'aib ne yaja hankalin Ammaah dake k'ok'arin wucewa ta k'ofar Shu'aib, a cikin mamaki ta bud'e k'ofar ta lek'o abunda idanuwanta suka gani ya girmi tunaninta, ba shiri ta k'araso ta nufi izzatu dake kwance tamkar wata matacciya, ba shiri amaaah ta k'walla k'ara sai ga Abbaaah da wasu security's mata da maza sai rige rigen zuwa d'akin Shu'aib akeyi, inda kai tsaye kuwwar Amaah ta karad'e rabin gidan.

Abunda Abbaah yayi arba dashi ya bugi zuciyarshi sosai, wanda ya kasa motsi balle ya k'araso d'akin ya tabbatarwa zuciyarshi abunda yake zargi, jikinshi yana rawa ya ciro wayar dake aljihunshi ya kira yayanshi Alhaji sani, saboda dimaucewar da yayi ya rasa me ya dace ya aiwatar, da sassarfa ya k'arasa wurin da Ammaah take rungume da izzatu sai zuba kuwwa takeyi ba k'ak'k'autawa, don ita Ammi a lokacin shiru tayi saboda ganin halin da Ammaah ta shiga ma ya shalle nata, duk da ita kanta dauriya ce kawai take yi domin jin takeyi kamar taje ta shak'e shu'aib ta kashe shi kowa ma ya huta.

Kafin minti biyar sai ga Alhaji ya k'araso gidan saboda ko gida bai riga yaje ba, yana ganin kiran yaji wani farin ciki saboda a tsammaninshi ko Abbaah ya canza shawawa ne, shiyasa ya kirashi ya bashi hak'uri a daidaita ayi auren, ganin yanda security's da sojojin da 'yansandan da ke gidan sukayi dandazo ne yasa shi fargabar kodai Shu'aib ya sakawa Abbaah gubar da ya bashi ne, shine Abbaah ya kirashi suyi sallamar bankwana?, aikuwa ya k'ara jin wani k'arfi a zuciyarshi saboda hango kanshi da yayi yana birgima a cikin dalolin nera, aiko sai gashi kwatsam abunda ya tarar ya saka shi aza hannu a kai ya kwantsama wata mahaukaciyar k'ara tareda kiran sunan shu'aib, jikinshi yana rawa  ya fiddo 'yar k'aramar bindigar dake hannunshi ya saita Shu'aib da ita sai ji kake yi d'waaaaaaa!!!
Ya sakarwa Shuaib ita wajen k'ok'arin ya harbe shi a kai ne halbin ya sameshi a hannu.

Gaba d'aya wurin ya runtume da ihuuuu.

Nima dai wlh bazan tsaya ba wallah nikam na fece🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️

Akafta 🏃‍♀️

D/Auta ce⛹️‍♀️
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI 🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*
*Bakan Gizo*
Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏻*

*PAGE SIXTY*

**********************

Alhaji fuskarshi a murtuk'e alamun ba wasa ya mik'awa Shu'aib wani abu ga wata 'yar kwalba, a cikin mamaki Shu'aib ya zaro idanuwa tareda fad'in "poison"ya k'are maganar tareda dafe bakinshi, ba tareda ya karb'i kwalbar ba, Alhaji a cikin zaro idanuwa tareda k'ara tamke fuskarshi babu alamun rahama ko kad'an yace da shi, "Karb'i nace."

Shu'aib ya zula hannu ya karb'i kwalbar amman fuskarshi har izuwa lokacin mamakin bai gushe ba, a cikin wata murya Alhajin ya fara magana kamar haka, "Guba ce ka ajiye ta a hannunka muddin Alhaji Yahaya ko 'yarshi basu amince da aurennan ba, to na baka umurnin kayi gaggawar saka masa a abinci, ka bi duk hanyar da zaka bi domin ka tabbatar ya ci, saboda mutuwarshi itace zata kawo muna komi a cikin ruwan sanyi, don zan tursasa 'yarshi ta aureka ko bata so kaga daga lokacin shikenan dukiyar gaba d'aya zata dawo k'ark'ashin ikonmu nida kai, saboda har matanshi duk zan aure su muyi kwanciyarmu a kan dukiyar muna birgima, saboda haka da zarar kaga ba'a yi nasara ba a wannan zaman da zamuyi yanzu dashi, to ka aiwatar da abunda na saka kawai domin cikar burinmu yana cikin wannan kwalbar, da zarar Alhaji yahaya ya bak'unci lahira to komi zai zo muna da Sauk'i, shikenan munyi winner saboda wad'annan 'yan k'auyen munafukai da shirinsu suka zo, muddin ba muyi wani yunk'uri ba to mu ne zamu tashi a tutar babu."

Shu'aib idonshi akan na mahaifinshi har ya k'are maganar hannunshi a sage, saboda har lokacin bai janye hannunshi daga ansar maganin da yayi ba, domin tsabar tsananin mamakin da Alhajin ya bashi, Alhaji a cikin d'aga murya yace da Shu'aib, "Umurni nike baka ba shawara na nema ba, kuskurewa a cikin wannan Umurni nawa shine hatsarin da zaka shiga babba a wurina, domin kuwa akan k'in cikar gurina na mallakar dukiyar Alhaji yahaya, wallahi kai kanka ba zaka tsira a hannuna ba saboda tsaf zan iya kawar da kai a doron k'asa."

Shu'aib ya zaro idanuwa Alhaji ya d'aga masa kai alamar tabbatarwa, Shu'aib jikinshi yana rawa ya saka kwalbar aljihu, saboda ya razana da lafuzzan da mahaifinshi yake furzowa, tamkar wanda baya cikin hayyacinshi jikinshi yana rawa ya bar wurin, yayin da shima Alhajin ya yi wani murmushi mai sauti sannan ya bar wurin, daga nan video'n ya k'are.

Alhaji sani ba shiri ya fad'i k'asa yana rok'on Abbaah akan don ALLAH yayi hak'uri sharrin zuciya ne, Abbaah saboda tsananin mamakin da ya kama shi, k'anzil bai iya furtawa ba amma idanuwanshi akan Alhajin hawaye suna ta kwaranya wasu bayan wasu akan fuskarshi, ya fara taku zai bar wurin a cikin dakiya yace da sojojin, "arrest him"ai kuwa suka k'ara cafko Alhaji sani suna janshi a k'asa tamkar basu san matsayinshi a wurin Abbaah ba, saboda dukan da suka yi masa tun a kan hanya har suka jefa shi mota, Alhaji ko sai kururuwar kiran sunan Abbaah yake yi akan ya yafe masa, wai ba laifinshi bane sharrin shed'an ne.

Bayan an wuce da Alhajin ne Ammaah ta kalli Garzali a cikin sanyin murya tace,

"Lalle kaine ka cancanci ka auri izzatunmu domin munada yak'inin cewa, ko bayan ranmu zaka zamo bango abun jinginawarta taji sanyi, saboda haka kasa aranka ma tamkar ka auri izzatu, ALLAH ubangiji ya taya ka ri'ko, mungode mungode da wannan bajintar da kayi, zuwanka gidannan ya zamo muna alkhairi tunda har ka gano muna kumurcin macijin, da yake ta sumamenmu domin ya tarwatsa muna farin cikinmu, tabbas na k'ara yarda da karin maganar hausawa wadda suke cewa, makashinka yana tare da kai sannan munafukinka yana gindinka, ALLAH yayi maka albarka Garzali kuma ya saka maka da gidan aljannah."

Izzatu da ke lafe jikin ammaah itama tace "Ameen" saboda tunda ta samu ta saka kayanta take son ta shi tsaye amma jikinta yayi sanyi k'alau saboda rashin k'arfin jikin, amma tana jin albishir d'in da amma take yiwa yayanta, taji wani kuzari ya zo mata ba shiri, a take ta mik'e taje da gudu ta rungume shi tana wani irin kuka gwanin ban tausayi, shima ba wani tunani ya k'ara manne ta jikinshi tareda sauke wata katuwar ajiyar zuciya, yana bubbuga bayanta alamar lallashi.

Ammi kam tsam tayi ta fito d'akin saboda tsananin kunyar da ta kamata, Ammaah kam wani murmushin jin dad'i tayi itama ta bi bayan Ammi, har da guzurin jawo masu k'ofa ta rufe sannan suka yi sashen Abbaah dukansu, domin suje su bashi hak'uri saboda sun san cin amanar da d'an uwanshi yayi masa dole ne ta bugi zuciyarshi sosai.

Suna fita Garzali ya b'anb'areta a jikinshi ba don yana so ba, ya zaunar da ita akan gadon hannunshi cikin nata, ya fara bata hak'uri, izzatu kuwa k'ara narke masa tayi tana ta kukanta, duk da batasan me Shu'aib yayi mata ba amma ganin yanayin da taga kanta, da tarzomar da aka yi a gaban idonta ya tabbatar mata da zargin da take yi, saboda tuno lokacin da Shu'aib ya shak'a mata wani abu, aikuwa ba shiri ta k'ara fashewa da kuka, a cikin kukan take cewa, "Wayyo yayana Shu'aib ya yi man fyad'e ya raba ni da mutuncina."

manage plss 🤗

Wai ina su iya kulu ya labarin Amina da Dr?za kuji a next page insha Allah

Akafta😃

D/Auta ce🥰
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏼 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI 🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*
*Bakan Gizo*
Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏼*

*PAGE FIFTY NINE*

*********************

K'arar bindigar ya saka mutane da dama a firgici, saboda su kansu sojojin dake harabar gidan a guje suka k'araso wurin kowane bindigarshi a hannu suna muzurai,  ganin Alhaji sani da bindiga rik'e a hannu ne yasa suka ja burki, amman duk da haka ransu a b'ace suna jiran umurni daga mai girma Gwamna.

Abbaah a cikin d'inbin mamaki ya saka hannu ya karb'e bindigar sannan ya kalli Alhaji sani, saboda abunda ya aikata ba k'aramin mamaki ya bashi  ba, tabbas shu'aib yayi laifi amma laifinshi bai kai na a saka bindiga ayi k'ok'arin  kashe shi ba, domin shi daman ya kirashi ne domin yaga halin shu'aib d'in da yake k'ok'arin had'awa aure da izzatu, shin ta ina ma ya sami bindigar da har yake b'oyo a jikinshi?,shin  wa yake hari da bindigar? a cikin damuwar da ke kwance akan fuskar Abbaah ya kalli Alhajin yace,      "Haba Alhaji ba wannan hukuncin ya dace ace ka yanke ba a matsayinka na babba."

Alhaji sani idonshi jawur saboda bak'in cikin abunda Shu'aib yayi, saboda ganin duk ya rushe masa tsarin da ya dad'e yana yi shekara da shekaru, sai yanzu a na gaf da cimma buri  yace zai kawo masa cikas saboda rashin hankali irin nashi.

Aiko a cikin d'aga murya yace,    "Miye amfanin rayuwar wanda yake k'ok'arin yiwa 'yar uwarshi wannan aikin?, ai gara a shafe labarinshi a doron k'asa da kallon fuskar maciyi amana irinshi."

Shu'aib da ke kwance cikin jini yana murk'ususun wahala, jin lafuzzan da ke fita bakin mahaifinshi da bak'in cikin abunda yayi masa yace,     "Duk wa ya janyo matsalar ba kai ba ina zamana ka tura ni aikata abunda kai ka kasa aiwatarwa tsawon shekarru, akan mi ka saka ni a ciki daman ashe jiran kake in yi kuskure  domin ka kashe NI kamar yanda ka fada?, ashe da gaske zaka iya kashe ni saboda abin duniya? wallahi ALLAH ya isar man a kanka ban yafe maka ba, tun da ka ke k'ok'arin kasheni na tabbata Abbaah ma bazai tsira da mugun nufinka ba, matuk'ar ba mataki aka d'auka akanka ba yasa a kashe ka kamar yanda kaima  kake yunkurin kashe s........ "

Jinin da ya buge shi ne yasa ya sume ba shiri, Abbaah ya bada umurnin a kaishi asibiti haka aka kwashi Shu'aib cikin jini aka fice dashi d'akin, yayin da  Alhaji ya fara borin kunyar maganganun da Shu'aib ya yi yana fad'in cewa   " kaji shegen yaro ni zaka yiwa k'azafi?, domin ka had'ani fad'a da d'an uwana to ALLAH ba taka ba bak'in munafuki, Wallahi naso na kashe ka kowa ma ya huta."

Abbaaah da Ammaah da AMMI da izzatun kanta da k'arar bindigar ta farfad'o da ita daga nannauyan baccin da ta tafi, dukansu suka tsura masa idanuwa zuciyoyinsu suna mai tantamar abunda yake fad'a, saboda ganin ba har zuciyarshi maganganu suke fitowa ba, Garzali da yake kallonshi a cike da reni ya yi taku hannunshi a aljihu ya k'araso gabanshi yayi masa wata dariyar mugunta, sannan ya dawo gaban Abbaah a cikin ladabi yace,    "Ranka ya dad'e idan har ka bani dama akwai maganar da nike so inyi, kafin Abbaah yayi magana Alhaji yayi caraf yace,      "Me zaka fad'a kai kuma bak'in bak'auya wannan rigima ta cikin gida ce,  ba wani bare

da ya isa ya shigo cikinta yayi muna iyayi da kilbibi irin na tsofaffin kwad'ayayyu, kun zata bansan asirin da kuka yiwa d'an uwana ba?, wanda yasa aka sakarwa d'iyarmu dukiya tana yi maku wacaka, kai munafuki ai ina sane ko manyan kud'in da ta dunk'ula ta baka sai da kuka tsafe ta sannan kuka samu, amman duk da haka abun bai isheku ba sai da kayi mata asiri ta nace wa sonka, don kawai ka mallaketa ka cenye dukiyarta to ta ALLAH ba taku ba 'yarmu tafi k'arfin d'an k'auye irinka  wad'anda suka yi gadon tsiya gaba da baya, to ahir d'inka ka sakarwa 'yarmu kurwa haka nan abun ya isa. "

Garzali ya yi murmushi har sai da hak'oranshi suka bayyana, sannan ya dawo gaban Alhajin ya cira hannu ya maka masa wani wawan  mari har sau biyu, gaba ki d'aya kowa a wurin ya zaro ido, musamman Abbaah da yaji zafin abun sosai amma ya kasa d'auke  idanuwanshi akan Garzali, wanda  ya fara magana kamar haka yace,      "ALLAH wadaran jahilci da rashin tunani tabbas yanzu na gano d'an k'auyen da ya shigo birni daban yake da haifaffen garin, tun da har kwakwalwarka ta koma irin ta kifi wadda babu komi a cikinta sai dusa, kasani duk wani k'ulle k'ullen da kake da d'anka duk a tafin hannuna yake, kuma yanzu zan tona duk wani mugun nufin da kake bibiyar Abbaah da shi da ahalinshi gaba d'aya."

Yana k'are maganar ya ciro wayarshi dake aljihu ya kunna videon da yayi masu ya karawa Alhajin a fuska, aiko  Alhaji yana ganin abunda ke ciki ya zabura zai ruga sojoji suka cafkeshi, sai gashi ya fara rantse rantsen sharri Garzali zai k'ulla masa.

Garzali yaje ya jona wayar da kayan kallon shu'aib da ke d'akin, aiko sai ga muryar shu'aib tartar lokacin da yake waya da Alhajin, sannan ya k'are ya kunna videon sai ga photon Alhaji da Shu'aib a tsaye rumfar motoci inda suka fara magana kamar haka,

🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️🏃🏻‍♀️

Akafta😝

D/Auta ce👍🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI 🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*
*Bakan Gizo*
Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏻*

*PAGE SIXTY TWO*

*********************

Garzali kuwa zuwanshi gidan keda wuya yana k'ok'arin parking d'in motarshi ne, ya hango Abu da Mari a wani d'an lungu suna tsutsar bakin junansu, hankalinsu ya d'auku basu ma ji shigowar motarshi ba, saboda shigowar Abu kenan gidan bayan yayi sati biyu baya gida, to ko da ya dawo Malam yana sashen iyar shiyasa ya jawo ta nan lungun suna tanbad'ewarsu domin su rage zafi.

Aikuwa fitowar Garzali daga motar ne yasa hankalinsu ya dawo suka shiga taitayinsu, saboda buga murfin motar da yayi da k'arfi shine ya jawo hankalinsu, suna had'a idanuwa dashi suka yi tsuru tsuru alamun rashin gaskiya suka bayyana garesu, domin Mari jikinta har rawa yake yi ta bar wurin ta shige gidan da gudu, Abu kuwa kallon Garzalin yayi sama da k'asa ya zubar sannan ya yi fuu ya fice gidan, yana gyara zaman wandonshi mai d'auke da k'ananan makamanshi, Garzali ya bishi da kallo ya girgiza kai sannan ya nufi sashen Iya kulu, tuno farin cikin da yake ciki ne yasa ya janye damuwar Abu a zuciyarshi, ya shiga da bakinshi a washe har kunne kai tsaye falon Malam ya nufa, inda yake zaune tareda d'iyan Inna hure suna lissafin kud'i, Garzali yana shiga kafin ya zauna sai da ya basu hannu suka gaisa, sannan ya zauna a k'asan k'afar Malam ya fara kai gaisuwarshi gareshi a cikin ladabi, sannan yayi murmushi yace "Alhaji Malam."

Dukansu suka yi dariya Malam yana murmushi yace, "Mai niyya dai."

Garzali ya gyara zamanshi yace,   "Magana nazo muyi da kai amman naga kuna aiki."

Malam ya ajiye lissafin yace da Su suci gaba da lissafin ya tashi tsam yace da Garzali,   "Zo muje daga ciki to."

Garzali ya k'ara bajewa yace,   "Zauna abinka ai mu da su isyaku duk abu d'aya ne, daman nazo ne in fad'a maka sak'on mai girma Gwamna, yace in sanar da kai gobe zai ZO gidannan ya nema mani auren 'yarka Izzatu."

Ba shiri Malam yace,   "ALLAHU AKBAR Dada kin tafi ba ki da rabon ganin wannan rana, ALLAH ya jik'anki da rahama ya kyautata makwancinki, maganarki ta zamo gaskiya izzatu alkhairi ce a wurinmu, yau gashi ta sanadinta mun zama abunda ko a mafalki bamu tab'a tunanin gani hakan ba."

Garzali ya k'ara gyara zamanshi yana kallon malam a cikin murmushi  ya kwashe komi da suka yi da Abaah ya sanar da shi, har badak'alar da aka yi da su Alhaji Sani da Shu'aib duk ya sanar da shi, MALAM saboda tsananin farin ciki ya k'wallawa Iya kira, Jikinshi yana rawa ya jawo wayarshi ya kira Mama hassatu,sai ga iya afujajan ta shigo yanayin da taji Malam ya kirata ne ta shigo da sauri gabanta yana fad'uwa, Saboda yanzu duk abunda zata yi ace bai yi ba ta son shi, saboda ganin shi kanshi malam d'in yanzu  arzik'i sai b'ub'b'ugowa masa yake yi, saboda daman cen shi ya k'ware da kasuwanci sosai, yasan salon ya maida kwabo ya koma sisi a cikin harkar saye da siyarwa.

Malam yace da ita ta zauna albishirr ne zai yi masu ita da Mama, aiko ba musu ta zauna sai ga Mama ta shigo fuskarta d'auke da Murmushi, saboda taga motar Garzali zuciyarta ta tabbatar da lalle ya zo gidan, aikuwa zamanta keda wuya ko gaisawa ba'ayi ba MALAM yace da Garzali ya sanar dasu komi, aiko ya tank'washe k'afa ya fara yi masu bayani, komi, bakinshi a bud'e yana dariyar farin cikin ya dinga yi masu bayanin  abunda ke faruwa, Iya kulu tana jin zancen hajjinsu bana da auren izzatu ba shiri ta yi zaman dirshan, sannan ta tashi da sauri ta bud'e d'an k'aramin  firjin d'in Malam ta jawo ruwa ta zuba k'asan tyles d'in, aikuwa sai ga Iya ta duk'a tana zuk'e ruwan har ta shanye, sannan ta taso tareda rafka wata uwar gud'a har sai da dukansu suka dad'e kunnuwansu, aikuwa ta fara rafka kirari na nuna jin dad'inta bayan ta k'are ne tace, "ALLAH sarki Hajiya 'yar kuluwa mai k'ashin arzik'i."

Ai kuwa gaba d'ayansu suka sa mata dariya, sannan suka yi ta sakawa izzatu da iyayenta albarka, addu'a ko sun shata tafi million iya kulu har da kuka saboda tuno irin abubuwan da tayi wa izzatu, sannan suka yi ta taya juna Murnar abin farin cikin da ya samesu, a nan baje  suka tsara yanda zasu shirya tarbon babban bak'onsu da zai zo gobe, bayan sun k'are ne ya kalli Mama yace,    "Ina Amina.?"

Mama tana murmushi mai sauti tace dashi,   "Tana cen na baro ta waya take Dr hashim, kasan yanzu kanta ya dawo jiya ma yazo wurin Malam sun gaisa, ya nemi alfarmar a bashi izinin shigowa neman aurenta, Malam ya amince masa to shine fa tun jiya suke lik'e sai waya suke."

Dr yayi murmushi yace, "Suyi abunsu lokaci ne kafin mu zo kansu su ma."

Dukansu suka yi dariya sannan Iya tace, "Ina Abu ya shiga ne ya zo yaji wannan abun farin ciki da ya same mu?"

Malam ya b'ata fuska Garzali yace, "Na ganshi da zan shigo amma ya k'ara fita."

Iya cikin damuwa tace, "bari in tafi in ga ko ya dawo"

Ta fice falon Garzali ya biyo bayanta yace da ita "ina Mari" iya tace "wa yasanar mata wannan shashash k'ila tana cen tana bacci bari in tado maka ita ku gaisa."

Garzali ya sami kujerar falon iya ya zauna, sai ga Mari iya ta sakota gaba tana yi mata fad'a.

Garzali zai yiwa Mark ne da ya tambayeta???

Akafta 😆😆

D/Auta ce👍🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI 🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*
*Bakan Gizo*
Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏻*

*SIXTY ONE*

*********************

Ya saka hannu biyu ya tallabo fuskarta ta k'ura masa idanuwa hawaye suna ta kwaranya a kan kyakyawar fuskarta da tayi ja saboda kuka, ido cikin ido yake kallonta sannan ya saka fuskarshi yana goge mata hawayen dake ta zuba ba k'ak'k'autawa, fuskarta har tashi sun jik'e sharkaf da hawayen, Garzali ya k'ara rik'o kanta da hannuwansa ya saita bakinshi saman idonta ya fara lashe mata hawayen, saukar halshenshi a fatar idonta ya saka ta jin wani yarrrr a jikinta wanda har taji tsikarta tana tashi,  ba shiri ta janye kanta tareda k'ura masa wani kallo da jajayen idanuwanta tace,   "bakaji abunda na fad'a bane yayanah!? Shu'aib fa yayi man fyad'e yaci amanar zumunci, ya k'unsa mani bak'in cikin da har na koma wa mahallicina bazan tab'a manta wannan bak'ar rana ba."
Hawayen da ke idanuwanta sai tserarra sukeyi kan fuskarta, Garzali yayi murmushi tareda rik'o hannunta yace,   "Taya kika san yayi maki fyad'en?."

Izzatu ta k'wace hannunta tareda galla masa wata  harara tace,

"Sakeni tunda abun ma bai dame ka ba daman ai nasan yanzu dole ne ka daina sona tunda an yi watsi da mutuncina."

Ta k'are maganar tare fashewa da wani sabon kuka mai sauti, tareda yunk'urin tashi a zuciye, cikin zafin nama Garzali ya yi saurin rik'o hannunta,  sannan ya saka hannunshi d'aya ya zaunar da ita akan gadon, ya duk'a tareda kai Gwiwoyinsa k'asan carpet d'in dake shimfid'e a tsakiyar d'akin, sannan ya kira sunanta tareda d'ago fuskarta da hannunshi idanunta cikin nashi hawayenta suna sauka, ya jawo hannunta ya d'ora shi a  saitin zuciyarshi, a hankali ya fara magana     "Duk wani bugun numfashin da kike ji yana gudu a cikin zuciyata, to ki sani da sonki yake tafiya sonki a kullum dad'a yad'uwa yakeyi a cikin zuciyata, haka ma k'aunarki a cikin jinin jikina dake gudana yake tafiya, zuciyarki ta daina baki cewa zan iya gudunki don wata k'addara ta sameki, wadda sam ko da alama hakan ma bata faru ba, saboda wannan lambun nikad'ai ne aka halittawa shi, don haka babu wani wanda ya kai matsayin da ko hangenshi ya yi ballantana ya rab'u jikinshi, nine kad'ai zan shiga in sha ni'imar dake tattare da shi, ke tawa ce har abada babu abunda zai rabani dake sai ikon ALLAH wanda shi ba'a isa AYI jayayya dashi ba wato

mutuwa, ko ita d'in ina fatan Ubangiji ya karb'i rok'ona ya ara mani lokaci,  ya barni har sai na shiga wannan lambun nasha danshin ni'imar  da ke tattare da shi."

Izzatu kam gabaki d'aya kalaman Garzali sun k'ara dulmiyata a kogin k'aunarshi, haka zalika wata kunya ta ziyarceta ba shiri da sauri ta k'wace hannunta ta rufe fuskarta da tafukan hannayenta, Garzali yayi murmushi mai sauti tareda lakuce mata hanci yace,    "Hankali ya kwanta ba abunda ya sami lambuna,  ALLAH bai nufa da aci zalina ba."

Izzatu ta tashi da gudu zata fita sai kawai taci karo da Ammaah da ke k'ok'arin shigowa dakin, Ammaah tayi saurin rik'o hannunta tana murmushi tace,

"Yi a hankali kar ki fad'i kinsan amarya tsotsai ne da ita."

Ta k'are maganar tareda shigowa d'akin ta kai kallonta wurin Garzali tace,   "To ango tashi kaje Abbaah yana nemanku, amma kafin nan sai ka bani albishirina."

Garzali yana murmushi ya lalaba aljihunshi ya fito da sweet biyu ya mik'awa Ammaah yana dariya yace,     "Gashi."

Dukansu suka YI dariya Ammaah tana dariya tace,    "Nak'i wayon je dai kuji kiran amman nikam na biyo bashi."

Dukansu suka k'ara saka dariya a tare suka fito Amaaah tayi sashenta yayin da Garzali  da izzatu suka wuce wurin Abaah.

Suna kan hanyar zuwan ne izzatu a gaba sai juya mazaunai take yi cikin doguwar rigar robar da ta lafe a jikinta, ba shiri Garzali ya rik'o hannunta yace,

"wannan k'walele da yawa yake tsaya ni mu tafi tare."

Izzatu tayi dariya duk da bata gano inda maganarshi ta dosa ba, suka jera suna tafiya har suka je sashen, atare suka shiga babban falon Abaah da sallamarsu a baki, da murmushi a kan fuskarshi ya amsa masu sallamarsu, sannan suka zauna tareda kai gaisuwarsu ga Abbaah  a cikin ladabi, musamman dai Garzali da sai a lokacin yake jin kunyar marukan da ya zabgawa Alhaji Sani a gabanshi.

Abbaah ya fara yiwa Garzali godiyar irin bajintar da ya yi wajen gano green snake under the grass,wato mugun nufin da d'an uwanshi Alhaji sani yake shirya masa bai sani ba tsawon shekaru,  sannan ya fara yi masu albishir kamar haka,     "Alhmdllh daman ance komi yayi farko to zai yi k'arshe, gaskiya tayi halinta  yanzu duk wani shakku ya k'are, kai d'in dai ne ba canji daman wani bai isa ya auri matar da ba tashi ba,  kai ne Mijin da daman cen ALLAH ya zab'awa izzatu shine dalilin da yasa ta fita hannunmu tun tana cikin zanen goyonta, domin kawai ka zama mijinta don haka dole ne mu aurawa izzatu mijinta, da kaina zan taka k'afata har gidan

Malam Ayuba in nema maka auren Izzatu da hannuna."

Ba shiri Garzali yaje wurin Abaah tareda dafa k'afafunshi ya fashe da wani irin kukan farin ciki, Abbaah sai bubbuga bayanshi yake yi yana bashi hak'uri, bayan ya lafa da kukan ne Abaah yace, "Akwai wani tanadi da ka yiwa kanka na Muhallin zama ko kuwa?."

Garzali ya share hawayen fuskarshi yace, "Eh akwai gidan da na fara ginawa yanzu haka ma ankusa karasawa."

Abbaah yayi murmushi mai sauti yace, "Ba damuwa duk da daman cen ba wani zama ne zakuyi anan ba, zaku zauna ne tsawon sati d'aya da aurenku, sai ka d'auki matarka ku wuce London inda zaka yi karatunka, itama idan kana da ra'ayin karatun sai a sakata ta fara karatun a cen, duk da kai karatun naka ba mai tsawo bane shekara biyu ce zaka yi ka fito cikakken Doctor mai zaman kanshi kafinnan an gina maka asibitin da zaka dinga taimakon al'umma, fatanmu kawai ALLAH ya shiga cikin lamarinmu, dangane da zuwan su Malam makkah ma idan lokaci yayi ko kuna cen za'a yi komi insha Allah ."

Daga izzatu har Garzali farinciki ya lullub'e su, daga nan Garzali ya fara kukan murna goma da ishirin yana yiwa Abaah godiya har sai da Abaah ya hanashi, sannan yace da shi yaje ya sanar da su Malam zuwanshi gobe da safe wajen nema masa auren Izzatun.

izzatu kam saboda farin ciki rungume Abbaah tayi itama tana kuka, Abbaah yana ta aikin lallashi ne Amaaah ta shigo tana yi masu tsarguwar kukan da suke yi, sannan Abaah ya basu umurnin tafiya suka fito kowane idanuwa sunyi ja saboda kukan farin ciki.

Bayan sun fito ne Izzatu taje ta rungume Garzali shima gam ya manneta jikinshi a tare suka sauke wata k'atuwar ajiyar zuciya, Garzali kanshi a kafadarta yace, "Ba nida bakin da zan gode maku K'anwata kun gama yi mani komi a rayuwa addu'a d'aya ce zan dinga yiwa Abaah a duk lokacin da na kai goshina nayi sallah, akan ubangiji ya saka masa da gidan aljannah, ya k'ara tsareshi da sharrin mak'iya da mahassada da sharrin mutum da sharrin aljan, ko wani abun halitta mai cutarwa da shi da ahalinshi gaba d'aya duniya da lahira."

Ammi da ke bayansu tace "Ameeñ" da sauri suka saki junansu saboda muryarta da suka ji a cikin kunnuwansu ba shiri, jikin Garzali yana rawa saboda kunyarta ya sunne kai yana gaidata, itama ta amsa a cike da jin kunyar surukantaka sannan ta yi wurin Abaah da yake nemanta.

Garzali da izzatu suka kalli juna suka yi murmushi, sannan suka yi sallama tayi masa rakiya har gindin had'ad'd'iyar motarshi, ya ja suna yiwa juna bye bye ya nufi gidansu zuciyarshi cike fam da murna had'e da farin cikin da ya mamaye masa kafatanin zuciya. Motarshi ce da ya saya a cikin miliyoyan kud'in da izzatu ta mallaka masa, sannan ya fara aza dank'areren gida naji da fad'i bayan ya bud'a k'aton shago ya zuba yara Malam yana jagorantar komi, tareda taimakon d'iyan INNA hure maza da yake ji dasu tamkar d'iyan da ya haifa, wad'anda suma malam ya nema masu muhallin zama da matayensu a cikin birnin, domin kawai su tallafa masa tunda shi

Abu ya fand'are masa  dole ya zuba masa idanu don sai yayi wata ma bai saka shi a idanuwanshi ba.

Akafta 🏃🏻‍♀️

D/Auta ce🤝🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI🔥*

*KAR KU MANTA LITTAFAN HADIZA D/AUTA*

*Tartsatsi*
*Ruwa da kanra*
*Bakan Gizo*
   Sai
*🔥BAKON YANAYI🔥 mai take da nashi kalar salo kar ku bari a baku labari sayen nagari maida kud'i gida🤝🏻*

*PAGE SIXTY THREE*

**********************

Mari ta k'araso ta zauna sai sunne kai take yi tak'i bari su had'a idanuwa da Garzali, ko gaisuwa a cikin tsoro tayi masa ita saboda tana jin tsoron ya tona ta iya Kulu ta koreta, ita ko yanzu a

duniya ba abunda ta tsana irin ta koma k'auyensu.

Garzali ya kafe idanuwanshi a kanta yace, "Meye tsakaninki da Abu?"

Mari ta fara inda inda tana susar kai, Garzali ya daka mata wata tsawa tareda zaro mata idanuwa yace, "Meye tsakaninku nace?"

Mari ta fara kuka tana bashi hak'uri tana fad'in bazata koma ba, Iya kulu ta zura mata idanuwa saboda alamun rashin gaskiyar da taga sun bayyana gareta ran Garzali a b'ace yace da ita, "Ki kiyayi abunda zaisa in saka hannu in doke ki, ke wace wawuya ce da baki san 'yancin kanki ba?, to bari kiji mutuncinki darajarki idan kika yi sake kika rasa su ke ce a wahale, saboda shi namiji ba ruwanshi tsaf zai iya zubar maki da mutuncinki a banza matuk'ar kika yi sake, duk kusancinki da shi ko wallahi zai maki sakiyar da babu ruwa ko d'ige a ciki, sai daga baya k'i dawo kina cizon hannu bayan kece kika bada k'ofar komi, in kunne yaji to jiki ya tsira ni dai na fad'a maki gaskiya har ga ALLAH mun fita hak'k'inki, ruwanki ne ki ji ki yi amfani da maganata ki kama kanki, haka ma ruwanki ne ki watsar duk wanda yak'i ji to fa ba zai k'i gani ba."

Yana k'are maganar yace da ita ta tashi ta bashi wuri, Iya ko da take cike da mamakin maganganun Garzali ta kai kallonta gareshi tace, "Me marin tayi ne?"

Garzali bai b'oye ba ya sanar da Iya abunda ya gani sannan ya k'ara da cewa, "Sai kin saka ido sosai akan Mari da Abu, in ba haka ba su jawo wa mutane abun magana."

Iya kulu hankalinta ya tashi ta fara banbamin fad'a, ta iske Mari har d'aki tayi ta jibgarta sannan tace da ita ko kallon Abu ta sake yi sai ta bar gidannan, ta tsorata sosai shima da Abun ya dawo tayi ta b'ab'atunta amman shi ko kallo bata ishesa ba, balle yaji tsoron fad'anta k'arshe ma da ya gaji da kwakwazonta taso mata yayi kamar zai doketa a zuciye ya jawo jakarshi ya bar mata gidan, Iya kulu ta fashe da kuka tareda yin danasanin gatan da ta nuna masa a cen baya tana kuka tace, "ALLAH ya jik'anki Dada ashe duk fad'an so kai ne kike yi mani, yau ga gaskiyarki da kike fad'a mani ta fito fili, ashe haka ne da kika ce kaso naka duniya ta k'i shi, ka k'i naka sai duniya ta so shi".

Garzali dai bai k'ara cewa komi ba ya ficewarshi d'akinshi da ke farkon sashen Mama hassatu, yayi wanka sannan ya fito wajen Malam suna tsara yanda zasu tarbi Abbaah gobe, Malam ya d'aga waya ya kira mai unguwa ya sanar da shi duk abunda ke faruwa, mai unguwa yaji dad'i sosai don shima yana cikin mahajjatan, suka yi ta taya juna murnar wannan karramawa da Abaah yayi masu, sannan suka yi sallama akan shima gobe tun da sassafe zai zo ayi komi dashi.

Aikuwa da safe k'arfe goma cif Abbaah ya yi tattaki zuwa gidan Malam, domin nemarwa Garzali auren IZZATU tareda rakiyar wasu mutanenshi, saboda danginshi wad'anda suke d'aki d'aya da Alhaji sani, sun ce ba ruwansu da shi da auren 'yarshi tunda ya tozarta masu d'an uwa, mutum d'aya ne daga cikinsu ya fahimci illar abunda Alhaji sanin yayi, wanda tare dashi ma

aka yi wannan tafiyar don yace baya goyon bayan rashin gaskiya.

Tarba ta mutunci su Abbaah suka samu wurinsu Malam da mai unguwa da wasu dattijan k'auyen  wad'anda Malam yayi zaman lafiya dasu a cen, bayan an k'are 'yan gaishe gaishe ne Abaah ya fara gabatar da abunda ya kawo su, a cikin tsantsar farin ciki  Malam ya amince da had'in  auren 'yarshi izzatu da Garzali, Abbaah ya YI umurni da a kawo masa wata jaka, jikin wani scurity yana rawa ya ajiye jakar a gaban Abbaah a cikin ladabi, Abbaah ya saka hannu a jakar ya d'auko bandur d'in 'yar dubu har guda biyar ya ajiye a gaban Malam yace,      "Ga sadakin yarona Garzali mun takaita  ne saboda muyi koyi da sunnar ma'aiki, idan kuma ance sai mun k'aro za mu cika su zamo 1.million don bama son uban amarya yaga kasawarmu."

Gabaki d'aya wurin aka saka dariya sannan Malam cike da farinciki yace,      "Tunda abu ne na gida tuwo na maina a barsu haka ma sun isa, fatanmu kawai ALLAH Ubangiji ya sanyawa auren Albarka."

Dukansu suka ce,    "Ameen."

Daga nan Abbaaah ya gyara zamanshi yace,    "Muna neman alfarmar a saka muna rana, amma fa da wuri muke so kada aja muna lokaci."

Malam yana murmushin jin dad'i yace,     "Wata d'aya yayi maku?."

Abaaah yana murmushi yace,    "Yayi muna tsawo amman tunda har haka uban Amarya ya saka dole ne muyi hak'uri, ALLAH ya nuna muna lokacin lafiya kuma ya sanya alkhairi a cikin lamarin."

"Ameen Ameeñ " kawai kake ji tana tashi a bakunansu, dukansu kowa ya tofa albarkacin bakinshi tareda yiwa auren fatar alkhairi, Garzali har k'asa ya duk'a yana yiwa Abbaah godiya saboda karamcin da yayi masu saboda ba kowane mutum ne zai iya yin hakan ba,  amman shi duk da girman matsayinshi sai gashi ya yi abunda ko wasu  na k'asa da shi ba zasu iya yin hakan ba.

Suka rabu a cikin mutunci da girmama juna kowa sai sambarka yake yi, bayan ya yiwa su malam da mutanen k'auyen tasu kyauta ta musamman, ya dunk'ulo kyauta mai tsoka yace a baiwa iya kulu da mama, sannan aka YI masu rakiya tareda yiwa juna fatar ALLAH ya nuna wa kowa lokacin.

Bayan sun tafi ne mai unguwa da wad'anda suka zo suma suka koma k'auye, suna  cike da farin cikin abun alkhairin da suka samu, sannan da jinjina wannan karamci na mai girma Gwamna, bakunansu sai addu'ar gamawa lafiya suke yi masa ba gajiyawa.

Bayan kwana biyu da saka rana Garzali ya koma wurin bautar k'asarsa, wadda bai wuce kwana uku da su kammala ba, amman yana lik'e da 'yar amaryarsa a waya sai soyewarsu sukeyi

hankali kwance, saboda yanzu sun tabbatarwa zukatansu sun zama mallakin juna babu wata fargaba .

**
Saura kwana biyu da saka ranar auren ne SUDEIS da SADIS suka dawo gida, saboda sun kammala karatunsu na secondary gaba d'aya, bayan anje d'aukosu ne Amaaah tace da izzatu tayi shigar manyan mata taje falon Ammi ta zauna, don ayi masu surprise aga ko zasu iya banbance Ammi da ita, aikuwa izzatu tasha kayan Ammi ta hakimce saman kujera, sai ko gasu sun shigo da gudunsu har suna haki suka zube a jikin izzatu suna fad'in "Ammi oyoyo."

Izzatu ta fara bubbuga bayansu tana shafa kawunansu tana murmushi, su kuma saboda jin da suka YI Ammi bata ce masu komi ba yasa SUDEIS ya d'ago yana fad'in,

"Ammi ko mu koma har sai kinyi dokin ganinmu ne?."

SADIS ya d'ago fuskarshi ya k'are mata kallo zuciyarshi cike da mamakin ganin Ammin ta k'ara zama yarinya, a cikin mamaki yace, "Gaskiya Ammi wannan yanayi yayi maki dad'i kinga yanda kika koma.?"

Izzatu tace, "Sannunku da zuwa 'yan yarori anzo lafiya? ya hanya?" tana k'are maganar ta fashe da wata k'atuwar dariya harda rik'e ciki, dukansu suka bita da kallo a cikin mamaki,saboda muryarta da suka ji ta banbanta da Ammi, sai ga Ammaah da Fahat da Ammar sun fito suma sunata yi masu dariya, Amma tana dariyar tace,

"Ku d'aga man 'ya kar ku tsofar man da ita tun kafin zuwan lokacin, kuje ku nemo Amminku wannan kam 'yata ce izzatu kuma yayarku."

Ammi ta fito itama tana dariyar yayinda suma suka fara yiwa kansu dariyar, Ammi ta kallesu tace , "Ku in banda abinku baku sheda ta ba ne halama? duk photunanta da kuka yi ta shan gani."

SUDEIS yana dariya yace, "Ni fa na gano ba ke bace Ammi na dai yi shiru ne kawai, amman SADIS nasan shi kam bai gane ta ba kam."

SADIS ya harareshi yace, "Kaji yaro ni da kai wa ya fara ganowa ba ni ba?."

Daga nan suka ci gaba da zolayar junansu, sannan suka nutsu suka fara gaisawa tareda firar yaushe gamo, aikuwa fira ta b'alle a tsakaninsu musamman da suka ji an kusa bikin izzatu, suma sai suka fara tsara yanda zasu yi nasu bikin.

**
Anfara tsara shirye shiryen bikin ta kowane b'angare, lefe ma Abaah ne ya baiwa Ammaah kud'i taje da kanta har dubai ita da Mama hassatu suka lafto wa izzatu kaya tamkar ba za'a bar

duniya ba, haka kuma  tamkar basu tab'a sanin zafin neman kud'in ba, komi yaji ta kowane b'angare saboda idan nace zan tsaya fad'in abunda ke ciki sai an d'auki dogon lokaci ban gama lissafin kayan ba.

 Ana saura sati biyu bikin ne aka kwashi lefe himili guda aka kai gidan Malam d'akin uwar Amarya wato mama hassatu.

Wannan ahali biyu da suka dunk'ule suka zamo d'aya kwatanta irin farin cikin da suke ciki ma ba zai misaltu ba, domin kuwa sun had'e kansu waje d'aya sai nunawa juna karamci suke yi ba banbanci, b'angaren kayan k'arin ni'ima kuwa bayan Ammaah tayi nata Mama hassatu ma takanas ta samo, wata  wadda ake kira  hajiyar jin dad'i ta zo ta dinga gyara izzatu ta ko'ina ciki da wajenta, har sai da Ammaah taga za'a kassara mata 'ya sannan  ta rok'i alfarmar akai izzatu Niger domin taje ta gano dangin mahaifiyarta, aiko ba musu aka shirya izzatun tareda rakiyar Ammah da  Garzalin domin shima ya kai gaisuwarshi wurin dangin Ammi.

A cen d'inma hakan ce takasance domin kuwa duk wani nau'in abunda suka san zai saka ango manta sunanshi, to sai da suka bata na ci ta canye na sha ta shanye na tsugunnawa ma haka, tun izzatu tana jin dad'in abun har ta kai ita kanta abun ya fara damun jikinta, ta zama wata lazy bata da aiki sai kwanciya saboda abubuwan sun ratsa jikinta sosai, Garzali kwananshi biyu acen ya juyo gida Nigeria saboda shirye shiryen da ke gabanshi,duk da ya samu an kammala ginin gidan komi yaji babu ce kawai babu a ciki.

Ammaah da izzatu  satinsu d'aya a cen suka dawo aka ci gaba da hidimar biki, wanda aka tsara Kamu a ranar laraba Alhamis Aje k'auye gidan mai unguwa ayi wani shagalin bikin irin nasu na k'auye, wanda mutanen garin suka shirya domin taya Izzatu da Garzali farin cikin wannan aure, Jumu'a ayi walima asabar ayi yinin biki gidan malam wato mother's Day,  da k'arfe biyar na marece a d'auki amarya izzatu zuwa gidan angonta Garzali.

Bayan ankaita gidan mijinta da k'arfe takwas daidai a shiga had'ad'd'iyar dinner'r da mai girma Gwamna zai had'awa ango da Amarya,ta taya su farincikin wannan aure,  wadda manyan mutane da dama zasu halarta, domin taya Abbaah murnar aurar da 'yarsa ta farko da yayi.

Rigiji gabji fan's Ruwa da k'ank'ara ku matso kar ayi bada mu ba 💃💃💃💃💃🏃‍♀️🏃‍♀️na tafi in had'a jakar kayana🤣😝
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏼 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI 🔥*

*'yan mata da kwarya suna kidansu zasu kai amarya 💃🏾💃🏾💃🏾💃🏾💃🏾 shawara na baki cikin gidanki kiyo biyayya💃🏾💃🏾💃🏾sannu zan yo maki domin yanzu kin zamo amarya 💃🏾💃🏾💃🏾💃🏾 jin dad'i rashinsa sai kin jure sannan zaki samu so da rahusa💃🏾💃🏾💃🏾*

*SIXTY FOUR*

*********************

Ranar laraba ranar da aka tsara ce za'ayi kamu,  tun kafin lokacin mutane suka fara isa k'aton hall d'in da aka tanada domin wannan bikin kawai, wanda aka gayyato makid'a da mawaka domin su zo su taya mutane gwangwaje wannan biki, an tsara wurin yayi masifar kyau saboda takanas aka keta hazo domin lodo kayan k'awata duk wani events da za'ayi a bukin har a k'are.

Da misalin k'arfe biyar na marece ne manya manyan motoci suka fara parking a bakin harabar hall d'in, inda zuk'a zuk'an mata suka yi ta b'ulb'ulowa tamkar wad'anda injin ke yiwa wanka, duk wanda ka kalla ya kur'e adaka tamkar bazasu taka k'asa ba, mutane sai tururuwar shiga k'aton hall d'in sukeyi suna samun muhallin zama suna hakimcewa tareda shan k'amshi, masu kid'a sai aikinsu kawai sukeyi,nima dai naci kayan sallata na sami kujera na zauna sai kallon mutane nikeyi d'ai d'ai,  don kar a gano 'yar lek'en asiri ce ni a kora ni waje,  ina nan hakimce akan tawa kujerar sai ga Mc ya fara bayanin cewa ga amarya da ango zasu shigo, aikuwa na k'ara baza idanuwana domin in basu abinci, cen na hango wasu manyan Alhazawa suna shigowa inda masu kid'a suka sauya wak'a zuwa wake  iyayen amarya da ango,  d'aya bayan d'aya suna ta shigowa tareda samun wurin zama su hakimce, cen na hango Mama hassatu da Amaah fuskarsu sai annurin   farinciki ke fita ,cen na hango wata hajiya taci arniyar kwalliya sai taku take k'wask'was, ta sagala wata jaka a hannu tana wani d'agiyar hanci sama,  abun mamaki tana k'arasowa na gano ashe iya kulu ce, na k'ara gwalalo idanuwana domin in tantance shin itace d'in kuwa KO mai kama da ita?, ai kuwa idanuwa na suka tabbatar man ita d'in ce ba tantama, suma suka sami wurin zama suka zazauna, daga nan aka k'ara sanarwar ga ango da amarya nan zasu shigo, tareda canza salon kid'an da wak'ar  aiko naga kowa ya bazawa k'ofar idanuwa, yayinda wasu suke ta jawo wayoyi suna jiran shigowar Amarya izzatu da angonta

Garzali.

Aikuwa sai gasu sun shigo Amina da Dr hashim a gaba suna taka rawa a hankali suna shigowa, sannan wasu 'yanmata da samari bayansu a jere sai ga Izzatu da Garzanta suna biye  bayansu rik'e da hannun juna, yayin da wasu yanmatan da samari suke biye da su abaya, wani kid'an music mai bala'in dad'i yana tashi dukansu tafe suke suna d'an taka rawa ahankali har suka shigo tsakiyar hall d'in sai da aka yiwa Amarya da ango rakiya zuwa wurin zamansu, sannan kowa ya sami wurin zama ya zauna daga nan aka fara gudanar da shirye shiyen da ke gaba, aka kira k'awar amarya d'aya da abokin ango d'aya da su fito su nunawa mutane farin cikinsu, aikuwa sai ga sunan Amina da Dr ankira suka fito tsakiyar fili aka saka masu wak'ar auren suka fara taku, Amina ta saki jiki ta gwangwaje sosai Dr sai lik'i yake yimata, bayan sun fita ne aka umurci babbar aminiyar amarya da ta fito ta bada biography d'in amarya, aka saki wani kid'a cool music aiko sai ga Amina ta fito tana taku a hankali tana rausaya har taje ta karb'i microphone d'in, sannan ta fara watso tarihin amarya a cikin harshen turanci, sai kace daman cen a cikin turawan ta tashi ta burge mutane sosai a wurin, Mama hassatu taji dad'in ilimin da aka yi tsaye kai da fata akan sai Amina tayi, tayi ta saka albarka ga lesson teacher d'in da ya jajirce wajen koya mata karatun,don daman cen Amina tun a k'auye ta kusa hardace alk'ur'ani, shiyasa karatun bokon bai wani bata wahala ba.

Iya kulu sai jinjina kai takeyi sabosa jinjina irin turancin da taji Amina tayi, Mari da ke kusa da ita bakinta a bud'e tana kallon Amina saboda burgetan da tayi, iya kulu ta zungurota tareda saka talkaminta mai tsini ta taketa,  saboda haushin da ta bata na ganin zata kwabsa mata, mari tayi saurin kai kallonta ga Iyar tace,     "Me nayi kuma iya?"

Iya ta harareta tace, "wannann baki naki da kika saki inda da k'aton k'waro anan ai sai ya fad'a, haka kawai aje nuno uwar ango a television kisa a hasko ni tare dake ki rage mani martaba"

Mari tayi mata wani kallo tana gunguni tace,    "Nifa iya banga ma dalilin da yasa kikazo wurinnan ba,  sai da aka ce karkizo kika nace sai kinzo don kawai ki takurani"

Iya ta yi saurin buge mata baki tace,   "Me kike fad'a ne don ubanki yanzu insa masu tsaro su rufe man ke muga k'aryar zuwa cin arzik'i, wallahi na gaji da matsalarki ana k'are biki zan maidaki k'auyenku kije cen kici gaba da k'auyancin"

Mari ta bud'a baki zata baiwa iya hak'uri taji ance da abokin ango ya fito ya bada tarihin ango, tana ganin Dr ta tsura masa kallo, ya fito yayita watsa turancinshi bayan ya k'are ne aka ce da Amarya da ango su fito tsakiyar fili su cashe.

Mari tayi tsalle tace, "Wayyo dad'i"iya kulu ta maka mata harara tareda buga tsaki ta jawo jakarta tace,

"Shegiyar yarinya zata sa in kasa ganin komi."

Aikuwa Izzatu da Garzali suka fito hannunsu rik'e da juna gam, sunci kwalliyar da idan na tsaya siffanta ta zan d'auki lokaci ban gama ba, aka saka masu kid'a na musamman Garzali ya rungumota jikinshi suka fara rausayawa, yana mata lik'i tana yimasa, daga nan mutane suka dinga fitowa suna ta zuba masu ruwan lik'i, Amma da mama hassatu ma sun nuna tasu bajinta, iya kulu ma da jakarta a hannu ta dinga zaro kud'i tana ta yimasu lik'i, da abun yayi mata dad'i sai ga Iya kulu da shan d'amara da gyalenta, jakarta a hannu tana ta tik'ar rawa aiko kallo ya koma gareta, sai lik'in kud'in ya koma kanta ina zura kaina wajen lek'enta, aiko garin gulma wajen rawar iya kulu ta saka jakarta ta buge man kai da sauri na kauce gefe ina sosa wurin, haka na daure na dawo yin tsalle,Saboda cincirindon masu lik'i ya hana inji dad'in kallon.
Daga nan aka ci gaba da cashewa har lokacin tashi yayi aka watse taron, Mota ta musamman Garzali da Izzatu suka shiga,izzatu tana shiga ta makure gefe tana maida numfashin gajiya tareda yin wata hamma mai cike da kasala, Garzali ya saka hannu ya janyota jikinshi ya rungume k'amk'am, tareda sauke ajiyar zuciya izzatu ta lafe jikinshi kamar wata mussa, Garzali ya kai kallonshi gareta a cikin wata kasalalliyar murya yace, "Duk gajiyar bikin ce haka kanwata?, ko yanzu fa akwai sauran aiki a gabanki ko kinmanta gobe zamu je k'auyenmu?."

Izzatu ta k'ara narke masa a hankali tace,

"Bansan me ke damuna ba yayana wallahi bana jin dadin jikina, sai in ta jin banida wani kuzari"

Ta k'are maganar tana hawaye, Garzali yayi murmushi mai sauti yace, "Wannan duk aikin su Ammaah ne kiyi hak'uri kinji, da ank'are bikin an kaiki gidanki a hankali zaki ganki kin dawo normal."
Izzatu ta d'aga idanuwanta tana kallonshi, ya d'aga mata kai sannan ya yi mata wani shu'umin kallo ba shiri ta janye idanuwanta tana murmushi,tareda k'ara sunne kanta a cikin jikinshi, suna manne da juna har suka kai gidan Malam inda nan izzatu ta dawo tun lokacin da suka dawo Niger, a cikin sanyin jiki ya rik'ota suka fito direct sashen Mama ta wuce, bata dire ko'ina ba sai k'uryar d'akin mama hassatu ta kwanta, saboda gajiyar da tayi uwa uba jikinta da bata jin kuzari ko kad'an.

Tana nan kwance Amina ta shigo d'akin ta fad'a kan gadon tana fad'in "wash na gaji da yawa fa"

Izzatu ta saka k'afa ta shurota tace, "Kedai anyi k'atuwar raguwa yasin Dr zai sha fama ."

Amina ta galla mata wata harara tace, "Wai kwando ke cewa rariya mai yoyo, ai ni duk son jikina ban kaiki ba, keda tun da kika zo gidannan kwanciya ce aikinki, yarinya in zaki ware ki ware don wallahi baki isa ki cutar da yayanmu ba, haka kawai ba zaki hanashi angwancewa ba."

Izzatu ta tashi zaune a hankali tace da Amina,
"Wallahi Amina duk jikina ya canza gaba d'aya na kasa gano kaina, wannan kayan wahalar da aka ta cusa man duk sun sakani bana jin dad'in jikin, bansan me suke nufi da wannan cushe cushen da suke yiman ba."

Amina ta k'yalk'yale da dariya tace, "me kike ci na baka na zuba hajiyata?,ai ke zaki bada labarin ma'anarsu da kanki, har kinsa na tuna Mama tace da mun dawo in baki cup d'aya"

Tana k'are fad'a ta janyo wani galam ta tsiyayo abunda ke ciki ta mik'a mata tana dariya tace, "Karb'i kisha hajiya tun kafin raina ya b'aci fuskata ta d'oro hadari."

Izzatu ta maka mata wata harara tareda yin kwanciyarta tace, "Wallahi ba zaku kashe ni ba."

Amina ta ajiye cup d'in tace, "Bari in kira mamar tunda ni kin rena ni."

Izzatu ta gyara kwanciyarta tareda juya mata baya tace, "Tunda baki da imani ai kije ki fad'o."

Amina ta b'ata fuska tace, "Jirani minti biyu yanzu zaki ga rashin Iman......"

Shigowar Garzali ne ya katse mata maganar tana dariya tace, "Yawwa yaya Garza don ALLAH ka saka ta tasha dole tunda ni ta rena tsayina."

Tana k'are maganar ta fice tana dariyar mugunta, Garzali ya k'araso idonshi akanta har ya zauna ya saka hannu ya d'auko cup d'in yana murmushi mai sauti yace, "K'anwata daure kisha kinji tun kafin mama tazo tayi fad'a."

Izzatu ta tashi zaune tana hawaye tareda turo baki tace, "Yanzu yayana da kai za'a had'a kai a kasheni ko?"

Yayi saurin gimtse dariyar da tazo masa ya tashi tsam da kofin a hannu ya je kusa da ita ya zauna, tareda kiran sunanta a hankali yanayin kiran da yayi mata yasa ta d'ago fuskarta ba shiri ta kalleshi, ido cikin ido yace da ita "karb'i kisha ko in taya ki shan ne"

Izzatu da sauri ta d'aga masa kai ya kai kofin abaki yana murmushi ya kurb'a, da sauri ya janye bakinshi tareda cewa,
"Cab yarinya kinji dad'inshi kuwa? lalle mama tana sakantaki duk wannan dad'in ke kad'ai, sha kiji akwai dad'i sosai."

Ya kai cup d'in a bakinta ba musu ta kurb'a ya saita gefen bakinta ya k'ara kurbawa, ya maida mata, haka suka dinga yi har suka shanye ba tareda sun tantance ba.

Amarya da ango sha lugude🤣🤣🤣

Akafta😝

D/Auta ce👍🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

*🔥BAKON YANAYI🔥 book ne da ke tafe da zafin shi kada ku bari abaku labari salonshi daban yake da saura 200 kacal👌🏻 zata sa ki kasance d'aya daga cikin member ta 🔥BAKON YANAYI🔥*

*PAGE SIXTY FIVE*

*********************

Sannan ya ajiye kofin yace,   "Ko ke fa ba gashi kin shanye ba?"

Ta wani turo baki zata yi kuka sai ga Mama ta shigo, tana shirin yin fad'a sai taga ba komi a kofin sannan tace,   " To Ki tashi ki tub'e wad'annan kayan kije ki yi wanka, watak'ila ma ko sallah baki yi ba  kin wani zo kin nad'e cikin d'aki, anya izzatu wannan raggancin zai fiddaki kuwa? "

Izzatu ta fara kuka mara sauti tace,   "To duk ba kune kuka janyo man ba, wallahi ni nagaji da shan wad'annan abubuwan "
Mama tana murmushi ta fara tafiya  tace,    "mun ji dai tashi kije kiyi wankan kai kuma ka tashi kaje ka zo nan ka nanuke ana cen ana ta nemanka."

Tana k'are maganar ta fice Garzali ya kai kallonshi gareta sai faman sharar hawaye take yi, yana 'yar dariya yace,   "Haba k'anwata wai miye abun kuka ne?, nidai in don wannan abun ne zan yiwa mama magana abarshi haka wanda aka yi ma ya isa, yi shiru kinji tashi kije kiyi

wankan ko zaki fi jin k'arfin jikinki."
Sai da ya lallab'ata ta daina kukan sannan ya fita, ta tashi tana gunguni ta fara tub'e kayan, ta fad'a toilet ta sullo wankanta sannan ta yi sallah tana karewa ta haye gado sai bacci, don ko abinci sai da mama ta saka baki sannan taci Amina sai dariya take yimata.

*****

Koda safiya ta waye tun da safe suka d'unguma sai k'auye, ba'a zame da izzatu ko'ina ba sai gidan mai unguwa, yayinda su Mama da iya suka yi gidansu inda suka sha mamakin ganin yanda aka k'awata gidan kamar a birni, Iya kulu da ta yi tirjiya akan rashin zuwa k'auyen, sai gata ta washe tana wani shan k'amshi saboda ganin gidan ya k'ara sakata jin ita wata ce.

Takanas aka gayyato masu kid'an k'warya suka zo gidan suka yita baje kolinsu, aiko mata sai tud'ud'uwar zuwa gidan suke yi suna kashe k'eyar idanunsu, yayin da wasu suka baje suna ta tik'ar rawa abinsu, Iya da mama hassatu sunyi b'arin kud'i sosai tareda rabon turame, don kuwa duk wadda taje bukin da turmin atamfarta mai rai da motsi, bayan sauran tarkacen biki da aka yi masu d'auke da suna da kuma photon ango da amarya, anci ansha mutanen k'auyen sai sambarka sukeyi tareda sakawa auren albarka.

Da k'arfe hud'u 'yan tauri suka fara baje hajarsu a k'ofar gidan mai unguwa, wanda a cen cikin gidan nashi ma taron bikin ne akeyi, tunda safe aka saka amarya tsakiyar gida tayi d'aurin kirji, duk wadda tazo sai ta d'ebo lallen da aka kwab'a ta murza mata a jiki, anata shafa mata ana gud'a ana addu'o'i, inda a gefe d'aya masu kid'an kwarya na garin suka dinga buga k'warya suna darzar rawa, izzatu tun tana dauriya tana danne dariyarta har ta fito fili itama tana d'an murmusawa, saboda yanda matan suka baje sai gurzar rawa sukeyi iya karfinsu.

Bayan an k'are bikin saka lallen ne taje ta sullo wanka ta cab'a kwalliya sosai da irin shigarsu ta k'auyawan, aka aza masu kujera a bakin k'ofar fadar mai unguwa ita da Garzali da shima yayi shigar suna ta kallon yanda ake ta sharu da wasar tauri.

Sai marece sakaliya ana gaf da magriba sannan aka watse taron, bayan ansha ruwan lik'in kud'in da aka yi ta yi tamkar ba'a san zafin neman kud'in ba, sannan suka tattaro tareda rakiyar security's suka garzayo gida.

Saboda gajiyar da izzatu ta yi suna dawowa ta baje sai bacci, safiya tana wayewa wadda ta kasance ranar jumu'a ana saukowa daga masallaci, a babban masallacin jumu'ar garin dandazon mutane suka shaida d'aurin auren MUHAMMADU GARZALI AYUBA da Amaryarsa NANA AISHA YAHAYA BADAWI (IZZATU).

Daga nan k'arfe hud'u na yamma aka je walima, wadda shahararrun malamai suka bada fatawowi masu taken SOYAYYA DA RAYUWAR AURE A MUSULUNCI, wadda ta had'a manya manyan mutane mata da maza da suka taru suka yita baiwa amarya da ango shawara.

Ranar asabar rana ce da gidan malam ya so ya kasa d'aukar d'inbin jama'ar da suka taru,

domin su nuna farin cikinsu ga wannan aure na tsofaffin masoya biyu.

K'arfe biyar na yamma aka d'auki amarya Izzatu zuwa gidan angonta Garzali, bayan tasha nasihohi ta kowane b'angare.

Ammaah ce rik'e da ita tana kuka lokacin da za'a shiga da ita cikin katafaren falonta, Mama hassatu tazo da sauri ta duk'o saitin kunnenta tace,

"Ki shiga da k'afarki ta dama tareda bisimillah"

Aikuwa kukan da take bai hanata yin abunda Mama tace ba, bayan ankaita har k'uryar d'akinta sannan aka k'ara jaddada mata hud'ubobin da suka yi ta ratsa gangar jikinta, wad'anda suka k'ara kashe mata dukkan gangar jikinta tana ta kuka gwanin ban tausayi..

K'arfe bakwai cif aka fara shirin zuwa dinner, mata sai had'ewa sukeyi kamar wasu masu wankan injin, gurin kowace dai kar a barta a baya.

Nima dai na tafi inyi nawa gayu 🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️mai zuwa tazo muje kar ayi bamu😝.

Akafta 🏃‍♀️

D/Auta ce⛹️‍♀️⛹️‍♀️⛹️‍♀️⛹️‍♀️
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*PAGE SIXTY SIX*

**********************

K'aton Hall ne wanda aka k'awata da  kayan ado kalar ash masu masifar kyau, ta ko'ina sai walwalniya ke tashi saboda ankon shiga dinner d'in kanshi ash color ne, Amarya da ango sun had'e iya had'uwa wanda a duba d'aya idan angansu sai a zaci mutanen K'asar hindu ne, Izzatu ce banza ko had'ad'd'en d'an saurayi Garzali wanda shi kanshi anyi foolish d'inshi sosai, haskenshi ya fito tamkar wata d'an daren goma sha biyu,'yan mata da yawa sun k'yasa saboda ganin santalelen jarumi a cikin mazaje, saboda ta ko'ina Garzali ya had'u masha ALLAH to bale in angangaro wajen sha kundum Uwar biki fasa taro,  IZZATUn Malam d'iyar mama hassatu yar gaban goshi wurin Ammaah gilashin Ammi da Abbaah,  abun alfakhari wurin Yayanta angonta uban 'ya'yanta  Garzali.

 Wannan had'ad'iyar dinner ta tara manya manyan mutane na cikin jaha da kewayenta, har mutanen da suka shigo jirgi suka keta hazo musamman saboda wannan dinner, dinner ce ta musamman wadda sai wane da wane ne a cikinta, don in baka da get pass kai da ita sai daga nesa don ko get d'in shiga  wurin baka kai matsayin da zaga tab'a ba, saboda security's da aka baza birjik masu uniform  kala kala,  sai mu zarar idanuwa sukeyi tareda muzurai bindigarsu a saite suna jiran ko ta kwana.

Nidai ALLAH ya taimakeni da get passed d'ina a hannu, ina tafe naci kwalliyata sab'e da jakata da kud'in Napep kawai ne a ciki,  amman idan ka ganni zaka d'auka wata Alhajiya ce saboda tsananin canyewar da nayi, a zahirance ko ni  ko filin jirgi sau d'aya na tab'a zuwa 😛ina tafe ina yafk'i sai ga goribaty itama abun ba sauk'i don ni sai naga kamar ma tafini had'ewa, bayan mun gaisa muka jeru muna tafe muna fira har bakin get d'in, goribaty tayi caraf zata shige wani soja ya buga mata tsaya tareda tambayarta ina get pass d'inta?, aikuwa ta daburce jikinta yana rawa ta shiga lalaben jakarta, ina tsaye ina kalonta iya lalabe ta lalaba ko'ina ba shi ba samatarshi, aikuwa jikinta ya d'auki hazon rawa ta fara rok'on don ALLAH ayi hak'uri abarta ta shiga ta mantoshi a gida, sam sojan ya ce da ita k'arshe ma korata suka yi tana gudu suna biyarta, har saida ta fad'in bakinta yaci k'asa ya koma sai kace bata tab'a shafo janbaki ba, ture kaga tsiyan da tayo sai gashi a k'asa ya turje cikin k'asa, ta tashi a rud'e  ta bazama da gudu soja ya saka k'afa yayi ball da d'ankwalin sannan ya dawo kaina, jikina yana rawa na fiddo nawa da nawa na mik'a masa, ya karb'a sannan aka bud'e mani get na shige kud'um amman  zuciyata kwata kwata naji ba dad'i saboda goribaty na da aka hana shiga abun ya man zafi ba kad'an ba.

Ina shiga da tak'amata kalar mutanen da nagani a cikin hall d'in sun saka ni raina kaina a lokaci d'aya, saboda ganin had'ad'd'un mata shafaffu da mai da na gani a  ciki sun saka  jikina  yayi sanyi k'alau, a hankali na fara taku nayi wurin wasu kujeru da na hango cen baya, ina k'ok'arin kaiwa wurin ne na hango my Ambash da Mmn Abdulwahab suna k'usk'us, ina k'ok'arin kaiwa wurinsu ne naji an tab'o hannuna waigowar da zanyi sai ga Mummyta mmn 3H tareda Mmn 3S, nayi tsallen murna zanje wurinsu sai naji na taki k'afar wata 'yar gayu, ina k'ok'arin bata hak'uri ne wai sai naga ashe ma mmn Abdul ce bayan mun gaisa , ina yunk'urin  zagayawa inje wurin

Mummyta naji an k'walla kuwwar kiran "Mamana" waigawar da zanyi nayi arba da d'iyata Ummu Muhammad tareda daughterta Rufaida, a d'ari naje muka rungume juna.

Na zo zan zauna naji ance kira sunana waigawar da zanyi na hango Ramatu Sanusi ta hakimce saman kujera, kusa da ita naga kamar Nurse dinmu fati Ghana, ina k'arasowa na ga ko ita d'ince kuwa ashe bama ita kad'ai ba harda ummin zarah wato k'anwata Humayya, tareda fatima Abdullahi 'yar saulawa da k'awayena Ruk'ayya habibu da Mardiyya, sai Zee skt da mmn twin's da kuma hinde Ibrahim.

Bayan na zauna na ji an tab'o ni ta baya waigawar da zanyi nayi arba Aisha yola tareda Ussainata da Rahila Abba tareda d'iyata Hamida.

Abun fa ba sauk'i domin kuwwa wuri ya d'auki sowar kiran sunan D/Auta, a zabure na waiga gefen da naji ankira sunana, aikuwa mamaki fal raina domin kuwa nayi arba da mutane na kuma fan's na ruwa da k'ank'ara sai d'ago man hannu suke yi, a cikin farin ciki nima na dinga d'aga masu nawa hannu fuskata cike da tsatsar farin ciki, saboda mutane masu d'inbin yawa da a lokaci d'aya bazan iya kawo sunayensu ba, saboda MATA RAHAMA GROUP da D/AUTA NOVEL, tareda MASARAUTAR D/AUTA duk suna wajen, k'wansu da kwarkwata duk sunzo nuna farin cikinsu akan wannan aure mai d'inbin tarihi.

Bayan kowa ya natsu ne aka fara gudanar da shirye shiryen, mawaka da 'yan films d'in da aka gayyato sun baje sai nuna kwarewarsu sukeyi, bayan ank'are warwasawa ne Amarya da ango suka dinga bin manyan mutanen da ke wajen suna kai gaisuwa, sai Albarka ake ta saka masu tareda yi masu fatar zaman lafiya ga aurensu, sannan aka Umurcesu da su je su yanka cake bayan sun ciyar da junansu ne suka koma a tsakiyar fili, inda manya manyan mutane 'yan siyasa da sarakuna tareda wasu attijirai suka yi ta zuwa suna ta baiwa Amarya da ango kyautuka, daga mai basu zuzurutun kud'i sai mai yimasu kyautar motoci tareda kadarori, duk kyautar da aka bada sai wurin ya d'auki sowa da tafi, bayan ank'are ne aka fara services d'in abinci da abin sha, muna jere a sahu munata jiran layi yazo kanmu ina bayan Mmn Abdulwahab, duk abunda aka saka mata nima shi ake sanya man a nawa plate d'in, aikuwa ana kaiwa wajen pepe cheken ai kuwa Mmn Abdul an zuba mata na farko tak'i janyewa, macen hotel d'in da suke rabon abincin ta kalleta tayi Murmushi ta k'ara zuba mata wani har sai da plate d'inta yayi tsini, sannan ta wuce tana jin dad'in ganin yau kura ta sami nama, nima kam ina ganin abunda tayi na mak'ale na kasa d'agawa har sai da aka yiman irin nata sannan na ja tunga na bararraje ina kwasar gara, na fizgo wata tsoka ne idona yakai kan fuskar goribaty muna had'a idanuwa ta galla man harara, ba shiri na tuntsure da dariya saboda tuno fad'uwar da tayi har da su cin k'asa, naja plate d'ina nayi wurinta nace da ita, "Anya goribaty bakinnan naki zai iya cin wannan gara kuwa?, wannan fad'uwar da kika yi fa dole ne idan mun koma gida kije k'i tambayi likita in zaki iya cin wani abu dashi, don haka ki kawo kawai akwai leda ajakata in juye maki kayanki,in muka koma har gida zanje in kaimaki kayanki idan kin tambayo likitan kinji gaskiyar zancen, saboda ina gudun ki jazawa kanki matsalar da baki ji ba baki gani ba." na k'are maganar tareda k'ume dariyata ina ta Alla Alla ta bani da ko taga tsiya don kaf zan cenye ko k'ashi bazan bar mata ba, ashe ashe ta ranfo ni ta maka man wata jar harara tace, "Oloshi

buruku dadani, yanzu kwakwanuty  ni zaki yiwa 419?, ai koda bakin nawa zai radaddage sai na ci kinga sai  inji dad'in ganin likitan da kyau."

Na fashe da wata jarumar dariya nace,

"shin wai ya aka yi ma kika sami sa'ar shigowa ne?"

Ta cisgar naman har sai da ta cika bakinta fam sannan tace

"ALLAH ya soni ina komawa gida na ganshi na d'auko, da yanzu wannan shagalin fa duk bada ni ba ansha dani."

Niko sai dariya nike ta yimata, mutane sun baje sai shan gararsu suke yi, kowa ka gani bakinshi da maik'o sai cakam cakam da ake tayi da bakuna.
Da k'arfe goma dam aka tashi dinner'r taro ya watse kowa sai sambarka yake yi, Ango ya sulale da Amaryarshi ba tareda kowa ya sani ba, saboda yanda yaga tayi matuk'ar  gajiya, ko kyautukan da suka samu sai wasu security's ne suka biyo su dasu.

Shagalin biki bidiri bired'e💃💃💃💃💃💃💃💃💃💃

Akafta🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️

D/Auta ce⛹️‍♀️⛹️‍♀️⛹️‍♀️⛹️‍♀️⛹️‍♀️
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*PAGE SIXTY EIGHT*

*********************

Ita ta fara falkawa motsin da yaji tana yi na k'ok'arin mik'ewa da take yi, yasa ya falka shima saboda wawar rungumar da yayi mata take ta so ta zare kanta daga jikinshi, aiko ya k'ara manneta tsam a jikinshi ta saka hannuwanta biyu tana ture shi, da dai yaga da gaske tashin take son yi sannan ya bata damar mik'ewa, tana gunguni ta tashi tsaye da hanzarinta sai gata ta kai zaune ba shiri saboda zafin da taji ya ziyarceta ba shiri, da sauri yazo kanta yana murmushi ya duk'a tareda YI mata alamun ta hau bayanshi ya goya ta, ta makawa bayan nashi harara sannan ta fara yunkurin tashi tana taku a hankali tana cizon leb'o, waigawar da zai yi ya hangota har ta kusa shigewa toilet da sauri ya isa wurinta tareda taimaka mata suka shiga bayin, duk tirjiyarta da kumbure kumburen fuskarta bai hana ya yi mata gashi irin na masu jego ba, saboda abunda yake ta k'ulafuci akanshi wanda yake so ya ya hilace ta ya koma jik'a alk'alaminshi da taddawa, tun a toilet d'in ya saki jiki ya dinga binta da salo salo wanda tun tana turjiya har ta ware dolenta, bayan sunyi wankan ne ya janyota d'aki da dabara irin tashi da wayo har ya koma samun kanta, ya dinga kwasar ganimarshi hankali a kwance ba tareda tayi masa bore ba, sai dai kukan wahala da take yi a hankali yayin da shi kuma yake hawayen farin ciki, a hankali yake bi da ita har sai da ya maida k'walamarshi, sannan ya k'yaleta amman badon yaso hakan ba sai don tausayinta da yake ji, Albarka ko tasha ta tafi a k'irga sannan ya lallab'ata suka je suka yo wani sabon wankan, sai da ya rakata har d'akinta sannan ya dawo ya shirya tsaf sai tashin k'amshi yake yi, ango Garzali kam har wani k'yallin goshin sabon ango naga yana yi, murmushi a kan fuskarshi ya kasa b'oyuwa saboda tsantsar farin cikin da yake a ciki yafi k'arfin a kwatanta, ya nufi d'akinta sai zuba k'amshi yake yi koda yaje ya tarar da ita ta yi kwalliyarta simple kamar yanda ta saba saboda ita ba gwanar kwalliya ce ba, iya kacinta powder sai d'an lip a baki, ta saka wasu riga da siket na wata tsadaddar atamfa, d'inkin ya hau jikinta sosai tana tsaye gaban mirror tana murza d'aurin d'an kwali, hankalinta ya d'auku bata ma ji shigowarshi ba kasancewar a bud'e d'akin yake, ya tako a hankali yayi tsaye bayanta yana k'arewa halittarta kallo tun daga saman kanta har zuwa k'afafunta, ba shiri yaji tsikarshi ta k'ara tashi yarrrr!, ya sauke k'atuwar ajiyar zuciya, ya k'araso wurinta sannan ya zagayo hannunshi ya rungumota ta baya, tareda kai mata kiss kiss a wuyanta idanuwanshi a rufe yana sauke numfashi, sai shak'ar daddad'an turaren da ta saka a jikinta mai masifar k'amshi yake yi, ita kam lamo tayi kamar ruwa sun cita saboda abunda take jin yana yawo a jikinta, hannunshi da taji a cikin rigarta ne yasa tayi saurin bud'e idanuwanta da ke rufe, tareda saukar wasu hawayen da batasan ko na minene ba akan fuskarta, shehshekar kukanta da yaji shiyasa yayi saurin birkito ta a firgice yake kallonta, a cikin wata siririyar murya yace da ita,

"Me aka yi maki ne kuma yanzu?"

Tana murzar idanuwanta kamar wata k'aramar yarinya tace,      "Duk ba kai bane NI miye ma baka yiman ba?, kwana d'aya da kawoni gidanka ka saka ni kuka yafi a k'irga, ashe daman haka kake bansani ba?da ina ganin Shu'aib ne kawai d'an iska ashe kaima d'in dai sai a hankali."

Garzali yayi wata dariya mai sauti yace,

"Ai ni d'an guguwa ma ne in dai akan wannan fannin ne, yarinya kima gode ma Allah a hakan ma ina tausayinki da sai kin gane shayi ruwa ne, don ni duk abunda nayi bani da laifi saboda Mama da Ammaah ne suka janyo komi, saboda sune suka ce in yi ta nanuke maki kar in yarda in d'aga maki k'afa."

Da sauri ta d'ago idanunta ta kalleshi fuskarta d'auke da alamun mamaki,ya d'aga mata gira yana murmushi yace,   "Yes don sune suka yi ta baki abunda zai sa ni in yi ta  zaucewa a kanki, to ko kinga dole ne kiyi juriyar duk halin da kika sami yayanki, tunda ai kema kinsan ba halina bane ba ko?"

Izzatu ta maka masa wata jar harara sannan tace,

"To ai yanzu kafi man kola shafawa ai NI bansani ba wallahi da ban biye su nasha ba, don gashi sun jaman za'a kassarani da ka bari munyi ta aurenmu hankali kwance, baka bijiro muna da wannan katuwar matsala ba."

Garzali ya lakuce mata hanci sannan yace,   "To meye auren halan?nidai zo ki maida man kwalliyata da kika goge wajen rakinki."

Ta zunb'uro baki tana gunguni yayi 'yar dariya sannan yace,

"Yanzu kuma inyi wani abu ace na zama d'an iska,yanzu dai zauna in maki kwalliyar muje muyi break fita zanyi fa ."

Ya k'are maganar tareda zaunar da ita a kan 'yar kujerar madubin, ya saka cleanser ya goge mata fuska tass sannan ya fara shafa mata powder, ya d'auko eye liner ya zira mata sannan ya shafa mata janbaki ya gyara mata girarta dake kwance cike fam da gashi gata bak'i k'irin tamkar anyi mata jagira, sannan ya shafa mata eye shadow kalar atamfar da ke jikinta, idonta a rufe yace,    "Ko ke fa yanzu naga amarya ta fito tsaf amman haka kawai da gata na ki dinga yiman kwalliyar masu takaba?."

Tana bud'a idon taga yanda tayi kyau masha ALLAH a cike da mamaki tace da shi,    "A ina ka iya wannan kwalliya yayana?"

Yana dariya yace "tayi kenan"

Tayi masa wani kallo tace,   "Tayi amman kad'an."

Yace      "To akawo tukuici ko ince sai an biyani ma."

Tayi 'yar dariya sannan tace     " ka biyo  bash.......... ."

Kafin ta Kai k'arshen maganarta yace,   "Ai ko ni kam ba zan yarda ba wallah."  caraf ya jefa bakinshi a nata duk mutsu mutsun da takeyi bai k'yaleta ba har sai da ya shanye janbakin tass, sannan ya saketa tana maida numfashin wahala, tana k'ok'arin yin magana ne yayi mata alamar tayi shiru da hannunshi, sannan ya janyota suka fito k'aton falonsu dake mak'are da kayan more rayuwa, kai tsaye suka nufi diny da yake cike fam da abun breakfast, wanda Ammaah da Mama suka yi sammakon aiko masu dashi, don tun dawowarshi Masallaci ne wani d'aya daga cikin scuritys d'in dake tsaron gidannasu, ya  ke sanar dashi  Ammaah tace kar su tanadi komi su jira za'a kawo masu abin kari, lokacin da suke bacci ne security d'in ya kira wayarshi yana sanar dashi sak'on ammaah ya iso har da na Mama ma yazo da ba'a san da zuwanshi ba, ya fita ya bada Umurni aka shigo da kayan sannan ya koma ya mak'alk'ale matarshi, wadda yake jin sonta tamkar ranshi.

Wajen cin abincinma bai barta ba haka yayi ta jagulata ita ko ta  biye shi  suna ta zuba soyayyarsu, ta sukurkurce masa sai shagwab'a take ta  zuba masa, shi ko abun nema ya samu ya shiririce ya manta ma da fitar da yace zai yi, sun ciyar da junansu sosai sunci sunyi k'at don ita duk da rashin son cin abincin da bata yi, shauk'in soyayyarshi  da ya jata yasa ta saki jiki ta ci sosai, bayan sun kammala ne ya sake zuwa yayo wani wankan sannan yayi mata sallama ya nufi gidansu Abaaah domin yayi masu godiya.

Ita ko fitarshi ke da wuya ta shige d'akinta nikam ina ganin haka na haye diny d'in inata kwasar gara ta, ina tsaka da yagar wata k'atuwar cinyar kaza ne naga wasu ma'aikatan gidan masu uniform iri d'aya sun nufo ni, da sauri na cisgi naman na cika bakina sannan na d'auko ledar dake jakata na juye sauran na kular duka na b'oye a jikina, aiko suna zuwa suka fara tattara kayan suka kwashe duka naga sunbi wata hanya, na bisu da harara nace "Baku yi man bak'in ciki ba ai tunda na yagi rabona."

Na k'are maganar da yi masu gwalo sannan na k'ulle namana tamau na jefa jaka na fito ina yauk'i nayi gida abuna.

🤣🤣🤣🤣

Akafta😛

D/Auta ce👍🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*PAGE SIXTY SEVEN*

**********************

A gajiye lik'is suka isa gida wanda shi kanshi angon ya gaji sosai saboda jiganiyar  hidimar bikin da suka sha, to bale Amarya Izzatu da sai angaje takeyi tun a cikin mota har suka k'araso gida, saboda a lokacinma wani bacci ne mai dad'i yayi awon gaba da ita, yana yin parking ya tarairayo abarshi ya rungume suka shige cikin gida, in da direct d'akinshi yayi da ita ya samu ya lallab'ata taci kazar amarcin, sannan suka je suka yi nafilar godiyar ALLAH tareda addu'ar nemarwa aurensu zaman lafiya mai d'orewa, sannan ya taimaka mata ta sullo wanka tana ta mashalon bacci wanda duk rabi a cikin mayen bacci tayi shi shiyasa ma ko d'ar bata ji ba lokacin da yana taya ta wankan, bayan ta fito ta shirya cikin wata arniyar rigar bacci tareda shafa turaruka a jikinta sannan ta baje kan gado sai bacci, shima yayo wankan yabi lafiyar gadon tareda janyo abarshi a jiki ya mak'alk'ale, ya sauke ajiyar zuciyar da ta kai goma saboda farin cikin jin dad'in ganin wannan rana, da ALLAH ya mallaka masa k'anwarshi  Izzatu a matsayin matar aurenshi halalinshi, K'amshin turaren dake jikinta ya saka shi shiga wani yanayi yayi k'ok'arin rage zafi ta hanyar k'ara  cusa kanshi cikin jikinta yana sauke numfashi sama sama, ya dinga sarrafata a hankali saboda baya son ta tashi daga baccin da ya fahimci tana jin dad'inshi sosai, domin kuwa ta baje sosai sai sauke numfashi takeyi a hankali, amman sabon yanayin da ya tsinci kanshi a ciki ya sanya shi  bin jikinta da wani kalar salo,  wanda ita kanta sai da  taji abun har tsakiyar kwanyarta a cikin baccin, wanda itama ta fara maida masa da

martanin nata kalar salon, don ita a tsammaninta duk mafarkan da tasha yine a 'yan kwanakin, shiyasa ta baje sai karb'ar sak'on da yake aika mata takeyi tana sauke numfashin jin dad'in yanayin, wanda shi kanshi a lokacin ya d'imauce sosai duk da yaso ya d'aga mata k'afa amman yanayin da yaganta yasa ya kasa jurewa, wasa tayi nisa ne yana gaf da cimma buri sai kawai hankalinta ya dawo jikinta, ba shiri ta fara kukan ceto a firgice tana kiran sunanshi akan yazo ya taimaketa Shu'aib zai yi mata fyad'e, wannan magana da ya ji ta fad'a ita ce ta kare masa gwiwa akan k'ok'arin da yake na son cimma cikar muradinshi, ya koma lallashi tareda ban baki yana kwantar mata da hankali yana lallaminta har ta koma bacci, shi kam baccin kwata kwata kasa d'aukarshi ya yi saboda abunda yake ji yana yawo a jikinshi, musamman mararshi da ta rik'e ta k'ulle  tamau sai numfashin wahala yake fitarwa, tareda cije lips yana runtse idanuwanshi saboda daman cen ya dad'e yana fama da wannan lalura wadda dole sai yasha lemun tsami yake jin sauk'i, to amman na yau yafi YI masa illah sosai gashi ba wani lemun tsamin da ya yi tanadi balle yaje ya d'auko ya sha yaji 'yar sa'ida, tun yana d'aukar abun wasa har sai gashi da yin zufa sharkaf yana murk'ususu saboda tsananin azabar da yake sha, da dai yaga idan bai d'auki wani mataki ba zai hallaka kanshi a kan abunda yake lalinshi ne, ya janyo ta jikinshi tamkar wani bajimin zaki ya fara aika mata da manya manyan sak'una, wanda ta kasa jurewa sai gata tana karb'ar yanayin itama a zafafe saboda abubuwan da aka ta d'irka mata sun tsimata sosai,wasa sai moving takeyi cikin zak'uwar cimma manufa ai lokacin da ya zo neman hanyar da zai b'ullewa ne, ta k'walla wata k'arar azaba shiko duk da ya riga da ya d'imauce amman kuwwar ta shiga k'wak'walwarshi sosai,sai dai ya kasa dainawa ne  domin jin yake yi idan har ba sauke nauyin wahalar yayi ba to a ganinshi bazai rayu ba, aikuwa ya saki jiki ya YI ta neman hanyarshi sai cen kuma naji Izzatu ta daina kuwwar sai kukan da take ta rerawa,  ina lab'e jikin k'ofar na zuro kaina zan lek'a ne domin inga meke faruwa ai kuwa sai Garzali ya zo da hanzari ya rufo k'ofar d'akin da ya mance bai rufe ba da k'arfi, sai akan fuskata aikuwa na yi baya da sauri saboda azabar da naji ta ziyarceni ba shiri,  idona a rufe na ji saukar d'imi a kussawar hancina a firgice nayi saurin shafa wurin aikuwa da sauri na bud'e idanuwana sai ga jini nayi arba dashi, na bud'a baki zan k'walla k'ara ne naji Izzatu ta riga ni fasa tata kuwwar, da sauri naje jikin k'ofar na lafe domin inji me take yiwa Kuwwa, sai kawai naji tana ta kiran,
"Wayyo Yayana kayi hak'uri Izzatunka ce fa k'anwarka Wayyo mutuwa zanyi wayyo Mama kuzo ku gani yayana zai kasheni."

Da sauri na fad'i zaune dab'as saboda tsananin tausayin Izzatu da ya kamani, ba shiri naji saukar hawaye akan fuskata na saka hannu na shafo fuskata, zafin da naji ya ziyarceni ne a lokacin na tuna da fasa man hanci da Garzali yayi wajen tsegumi.

Tsananin Kukan da naji tana yi da magiya ne  ya saka ni kwanciya a wurin ban shirya ba, ina nan kwance nayi shiru ina saurare naji ta daina kuwwar cen kuma sai naji muryarshi yana bata hak'uri, a raina nace,   "Haba dai d'an air sai yanzu kasan da ka bada hak'uri, bayan ita ka kasa jin nata hak'urin da tayi ta baka?, ai wallahi sai ALLAH ya saka mata."

Ba shiri na dafe baki saboda tuno da nayi ashe fa ba laifi yayi ba, a raina na k'ara cewa,
"Ku kuka jiyo ni miye nawa ma a ciki ne?"

Daga nan bacci yayi awon gaba dani anan wurin ba tareda na tantance ba, ina cikin baccina mai dad'i ne naji anyi ball dani, a zabure na mik'e tsaye ina waige waige jikina sai rawa yake yi saboda tsananin firgicin da nayi, aikuwa idanuwa na suka sauka akan Garzali da ya ke sanye da jallabiyya bak'a yana sauka k'asa da saurinshi,  na duba agogon hannuna sai naga asuba ma ashe tayi a raina nace,   "Kila masallaci zai je  shine ya yi man wannan halbin d'an renin hankali."

A zabure na fad'a d'akin aikuwa sai ga Izzatu naga tana fitowa daga toilet da alamu ma wanka ta fito sai taku take a hankali tana cizon leb'e, kamar wata mai koyon tafiya  haka naga tana tafiya, hawayen idonta kuma  har lokacin basu daina tsiyaya akan fuskarta ba, a daddafe ta zura doguwar riga tareda saka hijab ta tada  sallah, nima da sand'a naje bayin nayo arwallah na lab'e gefen akwatunanta a gurguje nayi sallahta, ina nan zaune ina kallonta bayan ta k'are addu'o'i ne tayi kwanciyarta akan carpet d'in sallahr sai sharar k'wallah take yi tana sharb'ar kuka a hankali, sai ga Garzalin ya bud'e k'ofa ya shigo aiko na k'ara makurewa jikin akwatunan, kai tsaye wurinta yazo ya kira sunanta yana wani Munafukin murmushi yace   "k'anwata tashi kije kan gadon ki kwanta kiyi baccinki kinji."

Madadin ta tashin kamar yanda yace d'in ko kuma tayi magana sai kawai ta fashe masa da kuka, da sauri ya tallabota ya had'ata da jikinshi yace,   "Nasan nayi maki laifi amman don ALLAH kiyi hak'uri kinji wallahi nima naso nayi dauriya amma na kasa, kiyi hak'uri ki yafe man kinji ba laifina bane ni'imar da ke cikin lambunki ne tasa ni d'imaucewa, na hak'ura ne kawai ba don na so datse shan  zumar ba sai dai kawai tsananin tausayinki da naji, amman har ga ALLAH ba don naso hakan ba saboda ke mace ce da idan antara dubu ba za'a fiddo kamar ki ba, yanzu na gano ashe ni d'in ba k'aramar gata  aka yi mani ba, don wannan zuma da kika lasa man ba zanso ace nayi missing d'inta ba koda na minti biyu ne, idan ta ni ne ma mu dawwama a hakan ina ta zuk'ar zumarki duk tsawon second ko awa ko yini ko kwana balle sati zuwa shekara,  to kisani  bazan tab'a gajiyawa da ke ba saboda ke mace d'aya ce amma tamkar da miliyan a wurina, Ubangiji ALLAH yayi maki albarka ALLAH ya saka maki da gidan aljannah firdausi, Iyayenki Kuma yanda suka farantaman Ubangiji ALLAH yayi ta faranta masu a kullum safiya har zuwa ranar tashin k'iyama, tashi muje kiyi baccinki kinji."

Izzatu ta k'ara nok'ewa tareda zubowar wasu ruwan hawayen tace,

"Barni a nan nafi jin dad'i."

Garzali yayi wani murmushi tareda shafa d'an k'aramin gemunshi yace,    "To ai ko anan zan iya k'ara shiga lambuna tunda ba kya son cen."

Aiko zumbur ta Mik'e daga jikinshi tana jan baya har ta kai jikin gini ta makure tana kuka mai sauti, Ya danne dariyar da yake son yi ya b'ata fuska yace,    "Oya to muje ki kwanta idan ba kya so ni ba zan takura ki ba."

Ya k'are maganar tareda rik'o hannunta ta mik'e tsaye jikinta sai rawa yake yi, da yaga ma takun

zai bata wahala ya rungumota ajikinshi ya kaita kan gadon, sannan ta kwanta jikinta cure waje d'aya tana kyarma saboda tsananin tsoronshi da take ji, ya YI murmushi tareda yi mata wani kallo sannan ya gyara mata kwanciyar, ya zagaya ya kwanta sannan ya janyota ya had'a ta da jikinshi ya sauke k'atuwar ajiyar zuciya,  don ya kwantar mata da hankali ma yayi magana mai kama da rad'a yace mata,    "YI baccinki ba abunda ni zan yi maki wannan ma da na samu na gode ALLAH yayi albarka."

Sannan ta saki jikinta ta yi shiru minti biyu a tsakani tayi bacci, ya k'urawa fuskarta kallo yana jin soyayyarta tana k'ara shigewa a cikin duk wani lungu da sak'o na zuciyarshi, haka ma duk wata k'ofar gashi dake cikin jikinshi sai mik'ewa yakeyi, bai san lokacin da ya kai mata wani zazzafan kiss a kumatu ba, tareda runtse idonshi yana jin wani NISHADI a birnin zuciyarshi, Murmushi akan fuskarshi har shima wani  bacci mai dad'i yayi  awon gaba da shi.

Ina ganin haka na lallab'a na bud'e k'ofar d'akin a hankali na fito, saboda nima inje in d'an runtsa in biya bashin baccin da naci wajen ganin K'wak'waf kafin su tashi daga baccin, tareda jinyar hanci da bakina da ya suntume suntum🤣🤣🤣🤣🤣.

Akafta😂

D/Auta ce👌🏻
[8/23, 1:54 PM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*Barka da SALLAH all da fatar ALLAH ya maimaita muna ya nuna muna ta bad'i lafiya💃💃💃 amman fa ni har ynz banga nawa k'ullin naman ba😔saura kuma kuce man kun cenye 🙄yasin da mun had'u sunnah TV da yarinya😏🤣*

*PAGE SIXTY NINE*

*********************

Kai tsaye gidan Gwamnati ya nufa tareda rakiyar wasu scuritys da suka mara masa baya, a cikin tsananin jin nauyi ya dinga gayar da Abba, kanshi a sunkuye saboda wata sabuwar kunyarshi da ta lullb'eshi , Abbaah ya kalleshi yana murmushin jin dad'i yace, "Yau ni yarona yake jin kunya?, ALLAH yasa ba surukuta ce kake so kayi dani ba?."

Garzali ya k'ara sunkuyar da kanshi yana murmushi, Abbaah ya saka hannu ya danna wani Abu har sau biyu sai ga Ammaah da Ammi sun shigo, saboda kiran da suka ji Abbaah yayi masu ya tabbatar masu da cewa abu mai muhimmanci ne yasa ya kira sun a tare, suna shigowa suka tarar da Garzali Ammi ta d'an ja birki ta kasa k'arasowa, yayin da Ammaaah ta k'araso ta zauna sannan fad'ad'a murmushinta saboda jin dad'in ganinshi idonta a kanshi tace, "A'a wannan ango ne nake gani haka?to sannu da zuwa ina ka baro man 'yata?."

Garzali ya k'ara sunne kai ya waske da tambayar Ammaah ya koma gayar dasu,don baya son yayi abunda zasu ranfo shi, Ammah ta amsa fuska cike da jin dad'in ganin wannan girma da yake basu, Ammi kam gefe ta samu ta zauna a cikin jin nauyin ganin Garzali.

Bayan sun gaisa ne Abbaah yace dashi su fara shiri saboda tafiyarsu tana nan kamar yanda aka tsara, Garzali ya tank'washe k'afafu ya fara zuba godiya a cikin kalamai masu dad'i, wad'anda ba Abbaah kawai ba har Ammi da Ammaah sunji dad'in yanda ya saki jiki yanata zuba masu addu'o'i, bayan sun k'are tattaunawar ne Garzali ya yi sallama da su, har yazo zai tafiya ammaah tace, "Jirani in zo in baka sak'o ga 'yata."

Ta k'are maganar tana 'yar dariya ta biyo bayanshi suka fito waje sannan suka tsaya, Ammaah ta sassauta dariyarta tace, "Daman sak'on naka ne ba nata ba don ALLAH alfarma nike nema a wurinka akan ka tausayawa 'yata ka bita a hankali har ta saba."

Garzali ya dafe baki a cikin jin nauyin maganar sannan yayi murmushi ba tareda ya yi magana ba, Ammaah ta k'ara da cewa " don ALLAH Ka bita sannu a hankali kaji ALLAH ya baku zaman lafiya tareda hak'uri da juna, kuma ya yiwa aurenku albarka ya kawo zuri'a d'ayyiba."

Garzali yana sosa kai yake ta fad'in "Ameen Ameeñ."
Sai ga su Su SADIS nan ya biye su suna ta zuba fira, kamar daman cen sun san juna har lokacin SALLAH yayi.
Sai da yayi SALLAHr azahar tareda su SUDEIS sannan ya koma suka k'ara yin sallama bayan ammaah ta bashi sak'on ya gayar mata da IZZATUn, sannan ya fad'a motarshi scuritys suka raka shi har gidan Malam, amma a cikin zuciyarshi sai nanata zancen Ammaah yake yi yana murmushi tareda shafar gemu wanda shi kad'ai yasan ma'anar murmushin.

Kai tsaye sashen Mama ya fara shiga wanda har lokacin wasu 'yan uwanta da suka zo bikin suna nan basu tafi ba, tun a kan hanya ya fara gaisawa da mutane don kafin yaje wurin Mamar

har tasan da zuwanshi, saboda muryarshi da ta jiyo yana gaisawa da mutane, bayan ya shigo ne ya zauna suka fara gaisawa sannan yace,   " Ilham da Amina fa? Ban gansu ba ko duk gajiyar bikin ce ta b'oye su."

Mama tana y'ar dariya tace,      "Halan ba daga gidan ka fito ba? ai suna cen ita da Amina saboda Izzatun ce ta matsa akan su zo , to shine Amina taja ilham d'in suka je  don dai ta matsa kawai amman da basu je sun takurata ba."

Garzali ya fara 'yar dariya yace,    "Gara da suka je Mama don tun d'azu na fito ina gidansu Ammaah."

Mama ta fad'ad'a murmushinta sannan tace    "Masha ALLAH daman zancen da nike son inyi maka kenan gara da kaje hakan yayi sosai."

Daga nan Mama tayi ta yimasa nasihar hak'uri da iyali tareda fahimtar dashi amfanin hak'uri a wurin magidanci, Nasiha sosai tayi masa sannan suka yi sallama ya tambayi Malam tace dashi yana sashen Iya Kulu aikuwa ya fito ya nufi sashen.

Abun mamaki koda yaje sashen ya tarar da ba kowa gidan tsit kamar ba anan aka yi kacaniyar biki ba, sai iya kulu da ya tarar falo tana kallo Mari zaune k'asan carpet  tana yi mata wankin k'afa a cikin wata roba mai fad'i  da ke ajiye gabanta da ruwa a ciki,  Garzali ya kalleta yanda tayi ture ka ga tsiya tana latsar remote tana canza tashoshi, sallamar shi da taji ne yasa ta yi saurin kai kallonta gareshi tareda ajiye remote tana fad'in,

"Ango kasha k'amshi sannu da zuwa ina ka baro man 'yar tawa ne?. "

Garzali ya zauna yana murmushin jin dad'in yanda Iya ta ke nuna k'aunarta ga izzatun, ya fara gaidata a cikin ladabi itama Mari ta gaidashi  sannan taci gaba da aikinta, Garzali yana 'yar dariya  yace,   "Naga gidan ba kowa ina 'yan bikin ne? ko har sun wuce gida haka da sauri?."

Iya ta yi wani mere sannan ta k'ara d'age dankwalinta sama tace,     "Ni na kora su saboda na gaji da bak'ar kazantar da suke yi muna a gida."

Garzali ya d'an b'ata rai yace,   "Ai da kin barsu nazo munyi sallama sannan."

Iya ta fara hurar hanci tace    "Ai Malam ya basu kud'in mota to kai miye na wahalar da kanka akan mutanen da suka nuna man K'iyayyar sai yanzu da suka ga ALLAH ya rufa man asiri sannan zasu zo suce sona suke yi?ai ni wallahi kar nike kallonsu babbak'un Kwad'ayayyu, da sun d'auka banda k'ashin arzik'i shiyasa suka yi ta wulak'anta ni, to ai yanzu gashinan nayi masu fintinkau shiyasa aka ce d'an hakin da ka rena shi zai tsone ma idanuwa.  "

Malam da ke fitowa yace,    "Tabbas ko don gashi kema hakin da kika ta renawa a baya yayi maki rana, gashi kina ta cin arzik'in d'iyar da kika sheganta, yau gashi iyayenta sunyi maki ranar

da har ki mutu ba zaki daina cin gajiyarsu ba, don haka ki daina gori wurin wad'anda kika san sune k'ashin bayanki, don ba ke kika baiwa kanki ni'imar ba ALLAH ne ya baki har kika ci albarkacin wasu amma ba don halinki ba."

Iya Kulu ranta ya b'aci sosai amman duk da haka jikinta yayi sanyi da bugun gorar da MALAM yayi mata, tana shirin bashi amsa taga Mari ta saki baki hanci da ido tana kallonsu, Iya ta d'aga hannu ta kwad'a mata mari sannan tana huci tace, "Munafuka ta saki hanci da baki tana kallon Mutane, tashi ki kwashi kayan munafuccinki ki fice tunda ke bakida wayon in kinga d'ana yazo ki bamu wuri mu tattauna, algunguma a samu abun nad'a a fad'awa Uwa ita ko taje tana bazawa K'auyawan mata irinta."

Malam yayi mata wani kallo sannan ya koma babban falonshi, saboda daman cen a cike yake da iyar don bada son ranshi ta kori 'yan uwanta ba, ya dawo wurin SALLAH ne ya had'u dasu kowace da kayanta nik'i nik'i suna yimasa sai watarana, yace dasu su jirashi yazo aiko koda ya shigo gidan ya tarar da Iyar sai banbamin fad'a take yi, tun daga nan ya fahimci itace ta koresu ashe, bai bi ta kanta ba yaje d'auko kud'in ba tareda ya kulata ba ya kai masu su shiga mota, sunata godiya sannan suka wuce ya dawo yaga iya tana lek'enshi aiko ta buge da borin kunyar fad'in, "Me yasa ka basu kud'in ai da ka barsu su je cen su k'arata. "

Malam yayi banza da ita har sai da zai shige falonshi sannan ya waigo yace, "Kije ki karb'o kud'in tunda baki so aka basu ba."

Iya ta zunb'uro baki ta d'age d'ankwali tana girgizar jiki ta k'walawa Mari kira tareda sauran 'yan aikin da ke mata hidima, ta tasa su a gaba sai da suka gyara gidan tsaf sannan aka feshe gidan kaf da freshner mai mugun k'amshi lungu da sak'o , bayan an had'a da turaren wuta sannan ta hakimce falo tasa Mari ta wanke mata k'afafu, shine Garzali ya tarar da su sai gashi Malam ya kwafsa mata a gaban Mari shiyasa bata yi watawata ba ta sauke fushinta akan Marin saboda tasan MALAM yafi k'arfin reninta yanzu.

Bayan malam ya shige ne Iya tace, "Ai dai komi ya wuce kuma na nemi yafiyar yarinya to tone tone nami za'azo ana yiman nikam?"

Ta k'are maganar tareda murgud'a baki kamar wata yarinya, Garzali ya k'ume dariyarshi ya tashi k'yam ya bi bayan Malam, yana yar dariya marar sauti saboda ganin yanda take magana tana d'aga ido sama tana hurar hanci tareda turo lab'b'a kamar wata k'aramar yarinya.

Bayan sun fara gaisawa da malam ne Garzali ya gyara zamanshi yace, "wani tunani nayi MALAM shiyasa nace bari in sanar da kai sai inji naka ra'ayi akai.
"

Malam ya nutsu da kyau sannan yace, "Ina saurarenka me ke tafe da kai?."

Malam yace, "Dangane da kyautukan da muka samu nida Izzatu, nayi nazari akan mu

sadaukar da dukiyar ayiwa k'auyenmu k'aton masallacin Jumu'a sannan a gina makarantar islamiya a k'ara fad'ad'a makarantar bokon da ke garin sannan a saka Bohol Bohol na ruwa domin a raya k'auyen amman kai me ka gani a kan lamarin?."

Malam ya sauke k'atuwar ajiyar zuciya sannan yace,   "Kayi tunani mai kyau amman wani hanzari ba gudu ba ka yi maganar da Matarka? Koko gaban kanka kayi?"

A cikin ladabi yace  "A'a bamuyi maganar da ita ba gaskiya."

Malam yayi murmushinsu na manya sannan yace,  "To ka tuntub'eta kaji ta bakinta duk shawarar da kuka yanke sai ku sanar da Mahaifinta ka bar masa komi a hannushi, ni iyakaci na addu'a Ubangiji ALLAH ya baku ladar niyyarku ta alkhairi, kuma ya k'ara had'a kanku ku yi zamanku lafiya Ubangiji ALLAH ya albarkaci aurenku."

Sai "Ameen Ameeñ" Garzali yake ta fad'i sannan suka k'ara tattauna maganar bayan sun k'are ne suka yi SALLAH tareda MALAM sannan ya fito gidan tareda yi masu sallama dukansu sannan yayi gida.

Koda yaje tun kafin ya shiga ya jiyo K'amshi yana tashi saboda wani masifaffen turare ne da Amina ta turare gidan dashi, aiko gidan ya k'amsashe ga k'amshin sabon fenti da sababbin kaya sai suka gauraye suka bada wata kala, sannan ita kanta Amarya IZZATU Amina ta saka ta sai da ta sake sabon wanka, sannan takanas ta kira wata gwanar kwalliya ta tsantsara mata had'ad'd'iyar kwalliya, ta shirya cikin wata tsadaddar shadda da tasha stone work wanda aka k'awata da kristone stone kaloli sai walwalniya sukeyi, mai kwalliyar ta saki jiki ta murza mata d'aurin d'ankwali, sannan ta zuba gwalagwalai kunne da wuya sannan da abin hannu tareda agogo da zobensu, turaren da Ammi ta baiwa Mama taba Amina ta kawo mata shi tabi lungu da sak'o na jikinta ta murza, saboda taji dad'in k'amshin don ita sam batasan amfaninshi ba shiyasa ta saki jiki ta mulke jikinta da shi.

Aiko suna jin shigowar Garzali Amina tace taje tayi masa sannu da zuwa, a cikin jin kunya ta fito suka yi arba da juna tun daga nesa turaren ya fara kaiwa Garzali sak'o, a cikin mayen sonta ya k'araso ya kai mata wata wawuyar runguma tamkar zai maidata cikin jikinshi, ba shiri tace wasshh! Ba shiri yayi saurin d'ago ta ya kalli fuskarta, tsananin kyawon da tayi masa yasa ya k'ara gigicewa ya k'ureta da kallo tamkar a ranar ya fara ganinta, shirun da taji ne yasa ta d'ago fuskarta ta kai dubanta gareshi, ba shiri gabanta ya fad'i saboda yanayin idanunshi da ta gani sun canza launi zuwa ja, saboda tsantsar jarabar da turaren ya takalo wadda ke k'unshe cikin jikinshi wadda idanuwanshi suka fallasa komi, a cikin dakewa tace "sannu da zuwa ya.... y. a... n....." maganar ta mak'ale ne a sanadiyyar wata gawutacciyar runguma da ya k'ara yimata tareda jefa bakinshi cikin nata yana tsotsa tamkar ya sami wani sweet, tun suna tsaye har tsayuuwar ta fara gagararsu tayi luu zata fad'i ya tarota ya k'ara manneta jikinshi, sai da ya gamsu don kanshi da tsotsar sannan ya d'auketa cak kamar wata 'yar yarinya ya shige d'akinshi tareda turo k'ofa da k'afa tace garam!!!!!!.

Ya direta akan gado zuciyarta sai bugawa take yi saboda tsananin tsoronshi da take ji, ta fara hawaye tana fad'in  "Su.. Ami... na.. fa.. suna..... n.. " yayi saurin d'aura yatsanshi a bakinta yace shiiiiiiii!!!! aiko tayi gum ba shiri, shiko ya shiga sarrafata tareda  mamayeta da soyayyarshi mai zafi  don ko sai ganin d'ankwalin da aka sha wahala wajen d'aurashi nayi ak'asa anyii cilli da shi, a rud'e yake fara aika mata da sak'o sai da ya tabbatar tazo hannu sannan ya yi k'ok'arin shigewa lambunshi mai d'auke da wani daddad'an k'amshi da dausayi mai dad'i , yayi ta aiki a cikin k'arfi tareda jarumta Izzatu tun tana muk'us har ta fara kukan neman ceto, tun tana YI a hankali har ta b'are baki zata yi kuwwar neman agaji, aiko da sauri ya rufe bakinshi da nata yayi ta aiki tamkar wani bajimin zaki.

Kuka da buge buge ba wanda batayi ba amman bai masan tana yi ba, Su Amina kam da suka ji shirun yayi yawa ne ta ja Ilham tareda mai kwalliyar suka bar masu gidansu.

Amina sai dariya takeyi k'asa k'asa saboda ta tabbatar anyiwa Izzatu kamun kazar kuku shiyasa suka ji ta muk'us.

Nima dai na gaji da ganin k'wam 🤣🤣🤣nayi nan tun kafin Oga Garzali ya ganni ya k'ara buge man fuska.

Akafta🙈

D/Auta ce🤝

[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *🔥RUWA DA KANKARA🔥*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

_Yawan comment yawan typing🙄_

*PAGE SEVENTY*

*********************

Garzali kam sai da ya sha romonshi sosai sannan ya saurara mata, domin turaren har lokacin yana jinshi har tsakiyar kanshi saboda k'arfin aikinshi, ganin yanda ta dunk'ule wuri d'aya tana kuka yasa hankalinshi ya tashi sosai, saboda tuno irin sukuwar dokin da yayi mata tausayinta ya kama shi matuk'a, cikin tattausar murya ya fara ban baki da lallami da dubara har ya shawo kan abarsa, ya manneta jikinshi yana sanya mata albarka saboda irin lagwadar dad'in da ta jiyar dashi, domin shi a ganinshi tafi kowace mace zak'i a kaf fad'in duniyar gaba d'aya, duk da kasancewarshi mutum nutsatsatse wanda bai tab'a mu'amala da kowace mace ba sai ita, amman jikinshi yana bashi ita d'in special ce ko a cikin jerin dubban mataye, a hankali ya fara share mata hawayen da suka b'ata tsadaddiyar kwalliyar da aka murza mata wadda minti biyar da suka wuce ta maidata tamkar wata ba indiya, amman yanzu gashi duk ta had'e waje d'aya saboda tsananin kukan rakin da tasha.

A cikin tattausar lafazi yace "My sugar Kiyi hak'uri da yayanki kinji, nima bansan haka halina yake ba sai a yanzu amma insha ALLAH zan dinga controlling d'in kaina, don bana son ganin ina saka ki kuka nafi so ki saki jikinki dani kodon mu k'ara samun armashin wajen tarayyarmu."

Ta zunburo baki sannan cikin murya irinta shagwab'abbi tace "ba wani ni Ammaah zan fad'awa tunda na gano tausayin iya kan fatar bakinka ya tsaya."

Ba shiri ya zaro ido tareda ri'ko hannunta saboda tuno jan kunnen da Amaaah tayi masa, a cikin wata marainiyar murya yace

"Yayanki ne fa Wify yanzu zaki iya fad'awa amma wannan sirri namu? Haba dai ai nasan kema wasa kike yi, kiyi hak'uri kinji bazan sake ba amman fa ba alk'awali ne nayi ba, kada in mance in sake kwatawa kice na sab'a alk'awali."

Izzatu tayi saurin tashi zaune tace "Ni kasa ma duk yunwa nike ji gashi daman ko abincin ni ban ma ci ba."

Yana murmushi ya shafa cikinshi sannan yayi gyatsa a cikin siririyar murya yace,
"Ni ko kinga k'at nike saboda kin k'osar dani bama sai naci abincin ba."
Ya k'are maganar tareda kanne mata ido d'aya da sauri ta rufe fuskarta tace, "Yayana wai yaushe ka koma haka?."

Yana dariya yace "Nima bansan lokacin da kika sa na koma hakan ba, sai na fad'awa Mama ince kin lalatani."
Izzatu tayi saurin dirowa daga kan gadon tareda janyo bedsheet d'in da ke shinfid'e a gadon, sai da ta kai bakin k'ofar toilet sannan ta fara harararsa tace "idan kaje kace fyad'e nayi maka."

Tana k'are maganar ta fad'a toilet da gudu  Shima ya diro yana dariya zuciyarshi fara k'al saboda NISHADIn da ke tattare da ita, ya bita toilet d'in a cen ma sai da suka ja lokaci suna soyewarsu,  sannan suka fito izzatu ta maida kayanta ta fito a kunyace saboda tunaninta duk har lokacin su Amina  suna gidan, aikuwa a cikin jin nauyin abunda zata fad'a ta d'an tsaya jikin k'ofar tareda gyara natsuwarta, sannan ta murd'a hannun k'ofar ta shiga sai gashi taga d'akin wayam ba kowa a ciki, ta yi mamakin ina suka shiga ta lek'a wani d'akin da ke cikin wannan shima wayam, a take zuciyarta tace

_kira wayar Amina kiji_

aikuwa ba musu ta d'auko wayarta kira d'aya biyu a na uku Amina ta d'auka tareda gimtse dariyarta, saboda a gaban Mama take Izzatu tace   "Wai ke kuna ina nazo ban ganku ba?"

Amina tana dariya  ta tashi tsam ta nufi d'akinta don bata son Mama taji abunda zata fad'a sannan tace

"Ai mu tuni mun tsufa a gida."

"Ya akayi kuka tafi bansani ba."

Izzatu ta tambaya cikin damuwa  Amina tayi dariya mai sauti sannan tace    "Taya zaki sani kam tunda soyayya ta rufe maki idanuwa turare ya fara aiki."

Izzatu ta kai zaune ba shiri tace    "Ke fa yar renin hankali ce wane turaren."

Kit Amina ta kashe wayar sai dariya take tayi saboda a kunnuwanta taji lokacin da Ammi take waya da Mama dangane da amfanin turaren, Izzatu tayi ta kira tak'i d'aukar wayar sai dariyar mugunta take ta yi ita kad'ai, sai da taga ta dameta da kira ne ta tura mata text dangane da amfanin turaren, aikuwa ba shiri ta dafe kai tace   "Ya salam."

Wanda fad'in maganar yayi daidai da shigowar Garzali a d'akin sai zuba k'amshi yake yi, tana ganinshi ta tashi a guje ta fad'a toilet tareda murza key, yabita da kallo cike da mamaki ya kai kallonshi ga wayar da ta ajiye, ba shiri ya zauna ya d'auki wayar ya duba sai ga text d'in Amina yana karantawa yana murmushi, sai a lokacin ya gano abunda yasa ta gudu ba shiri aikuwa ya fara yimata dariya, ya ajiye wayar yaje bakin toilet d'in yace   "Wai Yau ni k'anwata take gudu?to shikenan ki fito ni falo ina jiranki a diny muci abinci."

Ya fita yana dariyar wautarta waton dai da gaske ta tsorata da halinshi, ita ko sai da ta sake sabon wanka har sai da  ta tabbatar ba k'amshin sannan ta fito tareda sake sabon shiri cikin wasu tufafin da ta canza a gurguje sannan  ta fito.

Yawan comment's yawan typing 😔

Akafta🙄

D/Auta ce🤝
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*PAGE SEVENTY ONE*

*********************

Jiki a sanyaye ta isa wurinshi inda ya ke zaune a kan d'aya daga cikin kujerun diny d'in, ya raja'a sosai wajen mayar da reply ga 'yan uwa da abokan arzik'in da suka ta turo masa da text's na taya shi murnar auren da yayi.

Har tazo ta zauna ba tareda ya d'ago kanshi ba, aikuwa taji haushi a cikin dabara ta wafce wayar, sannan ya d'ago ba shiri yana kallonta, ganin yanda ta had'e rai tareda maka masa wata harara, ya yi murmushi tareda jifarta da wani kallo ya kama kunnuwanshi da hannunsa duka biyu ya marairece yace,

"Am sorry."

Ta kashe wayar ta ajiye kan table d'in sannan ta tashi ta fara saving d'insu, a cikin plate d'aya d'aya ta yi ta zuba kalolin abincin sannan ta saka spoon d'aya tareda d'ebo abincin izuwa bakinshi, wanda shi tuni ita ya k'urewa manejin kallonshi komi da take burgeshi yake yi, shiyasa tana kai abincin bakinshi ya rik'e hannun sannan ya bud'a bakin tareda taimaka mata suka juye abincin abakinshi, sannan ya karb'i spoon d'in ya d'ebo itama ya kai mata bakinta, aiko ba musu ta karb'a ta cenye saboda daman cen cikinta wayam yake, aikuwa yana ganin haka yayi ta loda mata abincin har SAI da tayi k'at sannan shima ta dinga bashi, suna ci suna 'yar firarsu k'asa k'asa suna dariya har suka k'are.

Bayan sun koma falo ne yake nuna mata tulin texts d'in da ake ta turo masa na taya su murnar aurensu, tana jikinshi mak'ale tana kallon yanda yake ta maida reply, sannan ya jawo wata k'atuwar envelope mai d'auke da photunan bikinsu sunfi guda dubu, suka shiga dubawa d'aya bayan d'aya suna sharhi akan photunan inda zasuyi dariya su dara wajen yabawa su yaba, har suka kai inda Iya kulu ke zaune ta hakimce gata tasha d'aurin d'ankwali mai fanka, ga jaka a hannunta tasha ado masha ALLAH, Izzatu ta kalli pic d'in tayi murmushi sannan tace "yayana ya kaga iyar mu."
Ya kai dubanshi ga pic d'in yayi murmushi ba tareda yace komi ba,sai cen ya ajiye photunan yana kallonta a cikin tsantsar sonta da ke fudo duk wata kofar gashi da ke jiinshi, a hankali ya k'ara janyota jikinshi ya sauke mata kiss a kumatu tareda sunne kanshi cikin wuyanta yana shak'ar turaren da ta fesa, a k'ok'rinta na gusar da wancen maganad'isun jarababben turaren, ya zagayo hannunshi ta k'asa sai kawai jinsu tayi damk'e da na shanunta yana wasa da su, ba shiri ta zabura tareda watsar da photunan da ke hannunta, sai ga hawaye sharr akan fuskarta, da sauri ya saketa tareda saukowa k'asa yana kallonta ido cikin ido yace, "haba my sugar k'anwata raki dai raki dai yanzu shikenan ni bazan yi abunda nike so ba? Ni ne fa."

Ta zunb'uro baki ya had'iye dariyarshi yace

"Ba kya so?"

Ta d'aga masa kai ba shiri ya kai zaune tareda yin tagumi da hannunshi biyu yace

"Na shiga goma ni Garzali."

Ba shiri ta k'yalk'yale da dariya ya bita da kallo gwanin sha'awa amman ya fuske alamar yayi fushi, sai gata ta sauko itama tareda shigewa jikinshi ta lafe a hankali ta furta cewa

"Kayi hak'uri yayana kaji zan jure bazan koma kuka ba, amman kai ma ka daina yin wasu abubuwa sai in ta ganin kamar muma mun zama 'yan iska, ni kuma bani son mutane su ganmu su zarge mu."

Garzali ya k'ume dariyarshi sannan yace

"Ina abunda na tarar da ke kina sha d'akin Mama kin tuna?"

A hankali tace "Eh"

Yace "kinsan amfaninsu?"

Tace "A'a nidai kawai bani ake yi."

Yana 'yar dariya yace

"To amfaninsu kawai don wannan abun da kika ga munayi ne, kuma idan ba na cire maki abun ba, to kisani maganin zai yi ta damunki a jiki ne ke k'arshe ma zai iya sakar maki wani kurji a cikin ciki har sai cikinki yayi girman filon nan da kika gani"

Ya k'are maganar tareda nuno mata wani katon filon kujera da ya fad'o daga kan kujerar, ba shiri ta zato idanuwa ganin hankalinta ya tashi yayi saurin cewa,    "Amma idan kika saki jikinki zan taimaka maki yanda cikn ba zai yi girman filon ba, ke idan ma kika bi  sharud'd'an da zan gindaya maki ko?, to ina tabbatar maki da ko girman cikin ba zakiyi ba balle har yazo yayi k'ato ya fashe mu shiga uku."

Da sauri ta tashi zaune tace   "fad'a man Yayana wallahi bana son cikina ya k'ara girma balle har ya kai girman wannan pilon nikam na shigesu, yanzu shikenan su Ammaah sun san da haka suka yi ta d'irka man ina sha.""  ta fashe da kuka ya juya fuskarshi yayi dariyashi marar sauti sannan ya dawo gabanta yace,    "Miye na kuka gashi ni nace zan taimake ki?, kiyi shiru kiji abunda zan fad'a maki wanda idan kin kiyaye shikenan cikinki zai yi ta zamanshi a haka ba zaki shiga matsalar komi ba."

Tana sharar hawayen tace   "Fad'a man yayana wallahi zan kiyaye."

Ya zauna da kyau sannan ya fara magana fuska ba wasa yace

"Kinga na farko duk abunda kika ga NAYI kar kiyi k'orafi balle kiyi kuka, na biyu kuma koda wasa kada ki fad'awa kowa,  na uku kuma dole ne ki dinga saka turaren nan da kika sanya d'azu duk lokacin da zamu kwanta bacci koda kad'an ne, abu na k'arshe kuma a duk lokacin da na k'are shiga lambuna wajibi ne kice man kin gode."

Tayi shiru na minti biyu kamar ba zata yi magana ba sannan tace    "yanzu idan nayi duk abunda ka lissafo shikenan bazanyi k'aton cikin ba?"

Yace    "Shikenan kin gama naki aikin sauran kuma ni ne zan yi ta iya kokarina har sai na tabbatar da cewa maganin ya fita a jikinki."

Ta rungumeshi tana sharar hawaye tace

"Nagode yayana, amman yanzu shikenan idan su bani  bazan koma karb'a ba ko? "

Da sauri yace    "A'a karb'i abunki kisha ai ni nasan yanda zanyi bazan bari maganin ya cutar da ke ba."

Ta fara k'ok'arin tashi daga jikinshi tace

"gara dai in barsu da kayansu yafi kawai."

Yace "To dama yafi amman duk da haka da kin daure kin karb'a ko wannan don yana na farko ne."

Bata ce komi ba ta tashi tsam zata bar falon saboda ta k'uduri aniyar wad'anda ma aka had'ota da su duk a floshing zata zuba su, har ta fara tafiya zata bar falon ya kirata ta dawo ya janyota ta fad'a jikinshi, a cikin dabara yasata dole ta ware har da su k'yalk'yala dariya, sannan ya gyara zamanshi yace "Magana ce nike so muyi dake."

Ta natsu sosai tana saurarenshi a cikin hikima ya sanar da ita shawarar da ya yanke, taji dad'i sosai tayi farin cikin jin wannan tunanin mai kyau da Yayanta yayi, ta goyi bayan k'udurinshi na alkhairi sosai ta jinjina masa matuk'a akan wannan zurfin tunani da yayi.

Basu tashi firar ba har sai da aka yi magriba sannan suka je suka d'oro arwllah ya ja madu SALLAHr, sun dad'e sosai a wurin suna addu'o'in neman zaman lafiya ga aurensu, Garzali ya saki jiki yayi ta yiwa Iyayenshi da iyayenta addu'a sannan suka koma karatun AlQur'ani har aka yi isha.

Har tara da rabi suna falo Garzali yana wani bincike acikin computer, tana mak'ale dashi kamar wata mage tana kallon yanda yake aikin cikin k'warewa, ganin yanda ta fara bacci ne yasa shi ajiye aikin dolenshi yaja abarshi suka shige d'aki, ya shimfideta shima ya kwanta tareda rufa masu bargo, bacci yaci idonta sosai sai hamma take zubawa kafin kace me bacci yayi awon gaba da ita, yana kallonta cikin shauk'in sonta yana yi masu addu'ar bacci ne, sai gata ta tashi zumbur zata sauka gadon da sauri ya rik'o hannunta tareda tambayar "lafiya"

A cikin rawar jiki tace na mance ban shafo turaren ba, ya janyota jikinshi yana 'yar dariya yace "Kwanta abunki ai sai gobe sharud'd'an za su fara aiki."

Cikin sanyin jiki ta kwanta ido cikin ido tace dashi "da ka bari na shafo."

Yana murmushi yace

"Na yafe na yau kiyi baccinki hankali kwance ba abunda zai same ki kinji?"

Sai a lokacin ta sami natsuwa kafin kace me tayi baccinta, shima cike da annushuwa ya fara baccinshi mai d'auke da mafalkai kala kala tareda amaryarshi.

***

Ai kuwa tsakanin kwanakin ya darji amarcinshi hankali kwance zuciya zaune, duk da bai cika zama gidan ba ai dare.
Bayan kwana biyu da maganarsu da Izzatu yajewa Abbaah da maganar shima yayi farin ciki sosai har ma ya k'ara da tashi gudunmuwa a matsayinshi na Gwamnan jahar, ya yi masa bushara da cewa makarantar boko da bohol bohol shi zai d'auki nauyin aikinsu, Masallaci da

islamiya ce kawai za'ayi cikin kadararsu, sai Company buga robobi da yake so a kafa cikin garin, wanda yake so matasa da masu sauran k'arfi na garin da kewaye su zo afafata da su, saboda a rage yawan zaman banza ga marasa k'arfin da ke yankin, aikuwa Garzali yaji dad'i sosai yayi ta godiya.

Bayan kwana biyu suka fara shirye shiryen tafiya, wanda izuwa lokacin mutane sunyi ta zuwa ganin Amarya, daga k'auyen cikin garin tsakanin 'yan uwan Abbaah masu goyon bayanshi tareda abokan arzik'i ta kowane b'angare, saboda tafiyar da zasu yi ne mutane suka YI ta tud'ud'uwar zuwa ganin gidansu tareda yi masu bankwana.

Daren da zasu tafi tun da safe Garzali ya d'auki izzatu ya kaita gidansu Malam domin tayi masu sallama, Mama da Malam sun saka su a gaba suna ta yimasu jan kunne sosai akan suyi hak'urin zama da junansu, iya kulu kam tsakaninta da izzatu ALLAH ya baku zaman lafiya kawai take fad'i, saboda wani girma da take ganin Izzatu tayi mata a ido, har wani jin kunyarta ta fara ji lokacin da izzatun ta shiga sashenta, ko idanuwa bata so su had'a saboda jin kunyar abunda tayi mata a baya, Izzatu kam banda dariya ba abunda take yi a cikin ranta, saboda ganin wai itace yau Iya kulu ke jin kunya?duniya juyi juyi.

Har k'arfe biyu Izzatu tana gidan, sannan Mama tace yaje ya kaita wurinsu Ammaah, aiko har bakin motarshi suka yo mata rakiya kaf gidan har Iya kulun, Abu kanshi duk bak'in halinshi sai da ya fito ana yi masu bankwana dashi kasancewar jirgin asuba zasu bi.

Amina ta janyota gefe tace, "Wai ko kinga yanda kika koma cikin kwanaki shida da aurenku? cab lalle yayanmu baya wasa, nasan nan gaba idan mun sake ganinki ma kasa gane ki zamuyi."

Izzatu ta kai mata duka tace "Rawar jikin me kike YI ai kema kin kusa zama kamar ni har ki fini, amman in kin matsu sai a yi kome cikin sati d'aya a kai masa kowa ya huta."

A tare suka k'yalk'yale da dariya Mama ta k'walla mata kira sannan tazo ta d'auki ilham ta sakar mata kiss a kumatu, sannan ta ajiyeta ta shiga motar ilham ta fasa kuka sai ta bita dole ta janyota ta aza kan cinyarta sannan tace

"Mama zanje da ita don ALLAH "

Mama tace "Aje lafiya"

Ta rufo motar suka fara tafiya tana d'aga masu hannu suna d'ago mata sai ga wasu hawaye shaaaa akan fuskarta, Ilham ta kalleta tace

"Aunty kuka kike yi?"

Izzatu ta k'ara rungumeta jikinta sai sharar hawayenta take yi, bayan sun d'auki hanyar gidansu

Ammaah ne ya yi saurin kai kallonshi gareta, saboda sheshekar kukanta da ya jiyo ga kunnenshi duk da k'ira'ar sudes da ke tashi a cikin motar, yayi ta bata hak'uri har suka kai gidan da gudu ta b'alle murfin ta fito d'auke da ilham tana gudu zuwa sashen Ammaah sai k'wallawa su Ammar kira take yi, sai gasu sun fito dukansu har su SUDEIS da SADIS suka rungumeta, kowa sai murnan ganinta yake yi Ammaah da Ammi ma ba'a barsu a baya ba, nan suka dawo a main falon gidan suka yada zango suna ta murna da d'okin ganin juna, Ammi taji dad'in ganin yanda Izzatu ta sauya cikin 'yan kwanaki, ta wayance da fad'in ina Yayan naki ko yana wurin Abba....... , kafin ta rufe bakinta sai ga Abbaah Garzali biye dashi a baya sai sunne kai yake yi.

Nan ya zube yana ta kwasar gaisuwa wurin surukanshi, daga nan yayi masu sallama ya tafi da nufin zuwa dare zai dawo ya d'auketa, aiko ta baje cikin 'yan uwanta sai fira suke yi, sai daga baya Ammaah ta jata d'akin Ammi tace taje  cen ta huta tabar biyewa  su SADIS kar su saka ta ciyon kai, wanda ita tayi hakan ne don Ammi ta sami damar ganawa da 'yarta, don ta fahimci kawaici ne kawai take yi amman soyayyar 'yarta bayyane take akan fuskarta , aiko suna kulewa tayi ta bata shawarwarin da zasu amfaneta, tareda koyar da ita yanda zata yi juriya da halin mijinta a fakaice, don ta fahimci Garzalin ba k'aramin jarumi bane shiyasa da wayo tayi ta bata dubarun zama da miji.

Sai daga baya Ammaah tazo aka ci gaba da ita, inda har ta k'ara kawo mata wata kaza da tasa takanas aka dafo mata wadda taji kayan had'i sosai, cikin wayo suka yi ta hilatarta har ta cinyeta tas bata sani ba, sannan ta koma gunguni saboda tuno abunda yayanta ya fad'i, taso ta tambayi Ammaah domin taji k'arin bayani akan lamarin sai kuma ta tuna yace kar ta fad'awa kowa dole tayi gum ba don taso ba, Abbaah ya kirata takanas yayi ta yi mata nasihohi akan juriya da hak'uri, tana tareda da k'annenta har  dare zuwa lokacin da ya zo d'aukarta anan ta bar ilham wurin Ammi suka tafi gida.

Daren dai Garzali ya d'aga mata k'afa bai nemi shiga lanbum ba saboda tunanin tashin asubar da zasu yi, aiko tayi baccinta mai dad'i hankali kwance har hud'u na asuba  inda suka tashi suna ta kimtsawa har aka yi asuba, ana sallame SALLAH scuritys suka zo tafiya da su airport.

Koda suka je sun tarar da su Ammaah da Abbaah tareda Mama da MALAM da iya kulu Ammi dai cewa tayi bazata je ba, aiko Izzatu sai da tasa dukansu kuka, saboda yanda ta rikice gaba d'aya saboda ganin za'a rabata da kasarta iyayenta 'yan uwanta tareda abokan arzik'i, akaita inda bata san kowa ba kuma ba wanda ya Santa.

Dak'yar aka b'anb'areta jikin Mama hassatu da Ammaah tana wani irin kuka gwanin ban tausayi,
Su ammaaah suna tsaye har jirginsu ya d'aga, sannan suka juya gida kowa jiki  sanyi k'alau saboda rabuwa da da 'ya'yansu  kuma surukansu.

Nidai na mak'ale a tayar jirgin don yasin bani bari ayi babu ni.💃💃💃💃💃💃😝

Akafta😆

D/Auta ce🤝
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*PAGE SEVENTY TWO*

**********************

Jiki a sanyaye su Malam suka wuce gida yayin da su Ammaah da Abaaah suka wuce nasu gidan suma, zuciyoyinsu cike da alhini rabuwa da su Izzatu.

Iya kulu kam shigarta gidan keda wuya ta fara jin sautin nishi a d'akin Abu, wanda da ta kashe kunnuwanta ne ta jiyo ashe ma ba shi kad'ai bane har da muryar mace, abunda ta ji wa kunnuwanta yasa gabanta ya k'ire ya fad'i ba shiri, saboda idan ba kunnuwanta bane tabbas ta juyo Abu yana fad'in,

"Ashhh washhhh mari tsotsa man sosai wayyo dad'i, Mari ci.... ga... ba cen.. ye... ni..... gaba d'a..... ya.... "

Iya kulu a cikin wani zafin nama ta banki k'ofar da k'afa, aka yi dace ma ashe ba ko rufe take da key ba, aikuwa sai gashi idanuwanta sunyi mata mugun gani, domin kuwa Abu da Mari ne tumb'ur haihuwar uwarsu suna aikata masha'a.

Iya kulu ba shiri ta gwalalo idanuwanta kamar su fad'o a cikin rud'ewa tace

"Abu Mari daman abunda kuke aikatawa kenan?" a cikin kuka ta k'are maganar tareda yi cikinsu da duka, da taga abun baiyi mata ba ta jawo extension d'in dake mak'ale da socket tayi ta watsa masu, Mari sai kuwwa take yi tana tsalle har ta sami sa'a ta ture Iya ta fad'i ta shige d'akinta a d'ari ta dantse da key, Abu kam ko gezau bai yi ba, ya dai ja kayanshi ya shige toilet, Iya ko da tunda Mari ta tureta ta fad'i bisa hannunta dab'as aiko hannu yace " k'as!!" alamun ya karye,  ba shiri tace

"Wayyo ALLAH ta karye ni shegiya karuwa wallahi sai kin bar gidannan nan yau,Kande ma da ta haifo ki ALLAH ya tsine mata tunda ta haifo bala'i ta kawo man cikin gida."

Iya kulu kuka take kashirb'in dak'yar ta samu ta Mik'e hannunta d'aya  tallabe da hannun da ya kare, ta fito sai k'ara tsinewa Mari take yi Abu kam yana ganin ta fita ya had'a inashi inashi ya bar gidan, Mari  tana d'aki cike da tashin hankali jikinta sai rawa yake, saboda duk bala'in da iyar take yi a kunnenta don ko bata ce sai ta bar gidan ba, ita tasan dole ne ta barshi tunda har ta kamata hannu dumu dumu da Abu suna tanbad'ewaesu da suka saba.

Iya kulu ta dannawa Malam da ke sashen Mama kira tana kuka take sanar dashi ta karye a nemo mata mai gyara, a cikin tashin hankali Malam da Mama suka shigo sashen suna tambayarta garin yaya ta karye?.

Ita ko sai kuka kawai take yi takasa maida bayanin abunda ya faru, saboda bak'in cikin da yayi mata yawa a zuciya, Malam ya d'aga waya ya kira wani Mai gyaran kariya na K'auyensu, sannan suka ci gaba da lallashinta, Iya kulu sai kuka takeyi kamar wata k'aramar yarinya tana k'ara tsinewa Mari.
Mari kam itama ta had'a kayanta kaf ta dinga lodawa a jakunkuna, tana lab'e jikin k'ofa tana sauraren Iya har mai gyaran yazo, tana jin an fara gyaran hannun iya kulu tana ta zabga kuwwa, ta fito sad'af sad'af hannunta duka biyu jaye da jakunkunan da ta ciko fam da kayanta had'e da na iyar da take ta sacewa idan ta sami garara, har ta fita gidan tana jin sautin kuwwar Iyar ana gyara mata hannun, shiyasa hankalinsu Malam ya d'auku basu ma san fitarta ba, tazo bakin gate ne Amina ta fito daga sashen Mama zuwa sashen iyar saboda jin kuwwar da take yi wadda ta karad'e kaf gidan saboda tsananin azabar da take sha wajen gyaran.

Amina ta bita da kallo batareda tace da ita k'anzil ba, itama Mari ta bita da harara tareda murgud'a baki saboda 'yar tsama ce a tsakaninsu basa shiri, Amina ta d'auke kanta tayi sashen Iyar inda ta tarar har ank'are gyaran, idonta sunyi ja sosai sun kunbure yayin da hannun ya haye yayi suntum a  lokaci d'aya, amma har lokacin bata daina Kuka tana tsinewa Mari ba, saboda ganin take YI itace taja raayin Abu ta koya masa wannan masha'a, shiyasa tak'i fad'awa su Malam ainahin abunda ya faru, ta dai ce masu Mari ce ta tureta ta fad'i.

Mari kam tana fita ta tari adaidaita ta kaita inda ake shiga motar garinsu, minti goma sha biyar sai gata a k'ofar gidansu, aiko k'annenta da yaran unguwar suka fara murna suna fad'in

"Ga mari ga mari"

Suka rik'a mata kayan har cikin gidansu, Kande kam sai rawar kai take ga 'yarta mai arzik'i ta zo, aiko ta shiga rawar k'afar ganinta tareda sauran 'yan k'annenta sai haba haba ake yi da ita, ita kam sai murmushin yak'e take yi duk da izuwa lokacin zuciyarta bata tsoron asirinta ya tonu ace ga abunda tayi, tsoronta d'aya ne Iya kulun ta turo mata 'yansanda su tafi da ita, tun tana cikin zullumi kwana d'aya biyu har zuwa uku har ta gyagije ta ci gaba da sha'aninta, saboda tace da su kanden Iyar ce tace tazo taga gida ta koma.

Wasa wasa Mari sai gata da kwashe wata d'aya a k'auyen, izuwa lokacin duk zama garin ya gundureta ga zazzab'in da ya sata a gaba kullum sai amai take kelayawa, shiyasa ma Kanden ta matsa mata akan ta koma don ita tunaninta ko cimar da suke ci ce take sakata amai saboda sabon da tayi da jin dadi a birni, Ita ko ta kafe akan bazata koma ba sai taji sauk'i, aiko Kande taja wata budurwar 'yarta mai suna indo suka nufi gidansu Malam, saboda Indon ta maye gurbin Mari kafin ta mirmije ta dawo bakin aikinta.

Iya kulu tana zaune a falo abun duniya ya sha mata kai sasai saboda Abu tun da ya fita har zuwa ranar bai dawo ba ko a waya bai kirata yaji ya lafiyarta ba, saboda tana da tabbacin yaji lokacin da take kururuwar Mari ta karye mata hannu, amman sai gashi har lokacin bai waiwayo gida ba, don ita ko kad'an tafiyar mari bata dameta ba don koda bata tafin ba ita sai ta korata dole ta bar gidan.

Iya kulu tana k'yalla ido ta hango Kande aiko ta fara balbalin bala'i, duk da hannun da take tallabe dashi wanda har lokacin tana fama dashi, Kande ta marairece duk da batasan laifin da Mari tayi ba sai bada hak'uri take yi, Iya ta rufe ido taciwa kande Mutunci tsaf amman Kande ko a jikinta saboda gurinta d'aya ne iyar ta d'auki  Indo aikin Madadin Mari, aiko dak'yar ta shawo kanta ta amince amman da sharad'in daga ita har Marin kada ta sake ganin k'eyarsu a gidan, in don kud'in aikinsu zata sa akawo masu har gida, Kande kam ko ajikinta tunda buk'atarta ta biya don bata son arzik'in da suke samu ta k'ark'ashin iyar ya sub'uce masu, haka ta baro gidan Iya ko k'wandala bata bata ba balle kud'in mota,har sai da ta biya sashen Mama sannan ne taci abinci Mama tayi mata alkhairi duk da tasan Munafucci ne da kwad'ayi yasa ta zo wurinta.

Mari kam cikin wata biyu alamomi irin na masu ciki ya fara bayyana a wurinta, amman daga ita har Kanden ba wanda ya gano hakan har sai da cikin ya kai wata biyar sannan ne suka fara ganowa, saboda tsirfar masu ciki kala kala da take yi aiko abu ga k'auye labari ya bazu gari akan Mari tayi cikin shege, kyara da tsangwama babu wadda bata sha ita da Kande da 'yan kannenta, don ko shima kanshi baban nasu sai da fita ta gagareshi a k'auyen.

Da abu yayi yawa sai ga labari yakai har fadar mai unguwa, yasa kirata da mahaifanta aka saka Mari a gaba tareda yi mata titsiyeta akan sai ta fad'i inda ta samo cikin shege, tana kuka ta fad'i cewa Abu ne gaba d'aya wurin kowa jikinshi yayi sanyi, mai unguwa yace taje gida shi zai yi magana da Malam sannan suka fito, yara da manya suka biyo su duuu  mutanen gari sai wak'a suke yimata ana amshi,

"Duk garinnan wa yayi cikin shege?"

Sai yara su amsa suce

"Mari d'iyar Kande"

Mari me ya kaiki cikin shege?"

Yara su ce

"Kwad'ayi"

Haka aka raka SU ana wak'a har gida, sai da Mai unguwa yasa aka kora mutane sannan suka watse, amman fa garin ko'ina ya d'auka Mari tayi cikin shege.

Dad'i na da gobe saurin zuwa, ashe da gsk ne da aka ce rana dubu ta b'arawo, rana d'aya tak ta mai kaya shin ya wannan rikici zai kaya🤔shin wai ina bak'in london ne🤣🤣🤣🤣.

Akafta

D/Auta ce🤝
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*PAGE SEVENTY THREE*

*********************

*Mutanen london*

Amarya izzatu da angonta Garzali kuwa suna cikin jirgi sai aikin lallashinta yake yi,  saboda  jirgi yana tashi sautin kukanta ya k'aru dak'yar ya samu ta daina kukan ta koma ajiyar zuciya, ta lafe jikinshi yana ta aikin lallaminta har ya samu  tayi bacci, sannan ya sauke ajiyar zuciya tareda k'ara rungumeta gaba d'aya a jikinshi, kanshi a saman fuskarta bai damu da kallon da ake yimasa ba, shi dai gurinshi kawai ta sami natsuwa aiko sai da tasha bacci sosai sannan ta falka,ta d'an ci abinci kad'an ta koma baccin yayinda shima baccin yaci idonshi suka had'a kai wuri d'aya suna yin abunsu gwanin ban burgewa, har sai da wata mai service d'in abinci tazo zata wuce ta gansu tayi murmushi tace

"Luv bird's"

Gaba k'i d'aya wurin aka saka dariya saboda mutane da yawa soyayyarsu ta burge su, saboda yanda Izzatu ta narke masa tana ta rigima shi kuma Og Garzali sai lallashi yake yi kamar wata yarinyar goye.

Saukar jirginsu keda wuya sai ga wani driver da wani d'an katako wanda aka yi zanen photon izzatu da Garzali sai d'aga shi yake yi sama yana warar idon ta ina zai gansu, aiko idanuwan Garzali ya kai a kan photonsu ya nufi mutumin,  yayin da shima baturen ya hango su da sauri ya k'araso wurinsu yana farin ciki, bayan sun gaisa yake sanar dasu shine zai kaisu masaukinsu wanda Abaaah ya tanadar masu tun kafin suje, aiko suka shiga mota sai gidan.

Tsarin k'asar da muhallinsu da suka gani sun k'ayatar da su sosai, gidan da zasu zauna gida ne had'ad'd'en gaske don Abaaah babu abunda bai sa aka tanada a gidan da ta b'angaren abubuwan more rayuwa.

A gajiye tib'is suka shiga mutumin yayi ta nuna masu abunda ya kamata ace sun sani na kan gidan sannan ya tafi, sai ga abinci yayi masu Oder bayan sun yi wanka tareda salloli suka baje suka CI suka sha, sannan suka k'ule d'aki sai bacci mai cike da gajiya.

Koda safiya ta waye a gurguje suka yi breakfast wannan baturen yazo ya d'auke su sai School d'in da zasu fara karatu, don itama izzatun Garzali ya yi magana da Abbaah akan ya amince itama tayi karatun, aiko a tare suka je aka k'arasa 'yan cike ciken da za'ayi aka nuna masu inda zasu je, sannan suka koma gida da akan gobe zasu fara zuwa School d'in.

Shigarsu keda wuya k'ayataccen falon ya rungumota jikinshi yace,

"Azo a biya ni bashi na da aka cinye."

Izzatu tayi saurin zaro ido tareda turo baki tace,

"Ni nazata ma ka d'auki hutu ne har sai mun koma Nigeria."

Garzali ya zaro ido a waje tareda lakuce mata hanci sannan ya fara yamutsata yana lumshe idanuwa saboda shak'ar k'amshinta da yake yi, sai sunsunarta yake yi tamkar wani bunsuru, gaba ki d'aya ya kashe mata jiki sosai da salonshi, har sai da ya tabbatar ta zo hannu sannan amman duk da haka tak'i sakin jiki dashi, a cikin wata shak'ak'kiyar murya yace da ita,

"Hutu kike so."

Ta d'aga kai saboda yanayin da take ciki bazata iya magana ba, aiko ya fara k'ok'arin zare jikinshi ranshi a b'ace yace

"OK to ki huta d'in tunda ke bakida tausayi."

Ya tashi tsam ya shige d'akinsu izzatu kirjinta ya fara bugawa saboda ganin yayanta yaji haushin maganar da tayi, ba shiri sai ga hawaye shaaaa suna gangarowa a kan fuskarta, jiki a mace ta yunk'ura ta tashi tsam tabi bayanshi koda taje ta iske shi kwance yana kallon ceiling, jiki ba kuzari ta zauna gefenshi tareda aza kanta saman k'irjinshi,sannan ta saka hannu ta fara wasa da d'an k'aramin gemunshi cikin siririyar murya a hankali tace,

"Am sorry my husby ka yafe mani bazan sake ba kaji yayana?."

Yayi banza da ita kamar bai jita ba, ranta a jagule ta yunk'uro gaba d'aya ta fara kashe masa jiki da kalamai tareda tsokano shi lungu da sak'on da duk tasan zata kamo tashar shi, a cikin nata salon tareda kwarewar da shi bai ma san ta iya wasu abubuwan ba, tun yana juriya har ta ciyo galabarshi ya fara mayar mata da martani da soyayyarshi mai zafi, don daman cen fushin bai kai zuci ba aiko suka shiga nunawa juna k'auna sai nishinsu kawai ke tashi, saboda salo salon da suka dinga yiwa juna wanda dukansu sun hargitsa tunanin juna, har suka zo magangara inda a lokaci d'aya Garzali ya fara ihun dad'i tareda sambatu kala kala, sai zuba aiki yake yi yana kuwwa har sai da Izzatun ta rufe masa baki, sannan ya d'an rage aiko sai hakarta yake yi a cikin rud'ewa tareda rikicewa, saboda tsananin bala'in ni'imar da ke tattare da jikinta don duk abunda Ammaah ta yi mata bai hana Ummi saka ta d'aki ta mik'a mata wani abu a kofi tace ta shanye ba, aiko ta gane barno gabas take don kuwa tun tana cikin shauk'in har ta koma kuka tareda neman agaji, bai ma san tana yi ba dole ba don taso ba ta hak'ura har sai da ya mayar da k'walamarshi sannan ya saurara mata, yana ta saka mata albarka babu k'ak'k'autawa yana sambatun ganimar da ya samu, ita ko sai kumbure kumburen fuska take yi, yayi murmushi mai sauti sannan yayi mata rad'a a kunne yace,

"Kiyi hak'uri k'anwata kinji saboda zumar da nike sha a wurinki wallahi bansanim lokacin da nike rikicewa, kiyi hak'uri da halina kinji don ALLAH kar ki gaji kullum kiyi ta bani ina lasawa, saboda zumarki kullum k'ara zak'i take yi haka ma lambun sai k'ara naso mai cike da sanyin dad'i yake, ga rab'a da take sauka har tsiyaya take yi ki tausaya man k'anwata, bani da kowa sai ke idan

kin hana man ina kike so inje?"

Aiko sai ga kuka shaa ga idon Garzali ba shiri Izzatu ta fara lallashinshi tace

"Kayi yanda kake so da ni taka ce yayana inma sau hamsin ne kayi abunka nayi alkawali zan yi juriya dad'i ko wuya bazan juya maka baya ba."

Aikuwa ya k'ara manne ta jikinshi a cikin farin ciki suka koma sarrafa juna tareda jiyar da juna dad'i kamar wasu mayunwata, sai da suka tabbatar sun gamsu da juna sannan suka YI bacci mai cike da annushuwa da farin ciki.

Haka rayuwarsu ta ci gaba da gudana a kullum basa gajiya da tarairayar  juna,  a gefe d'aya kuma sun maida hankalinsu sosai akan karatunsu.

Suna da wata biyu da aure Izzatu ta sami ciki aiko farin ciki a wurin Garzali kamar ya take kan jariri, sab'anin ita da ko kad'an bata so samun cikin ba a lokacin, saboda tunanin matsalolin ciki zasu hana ta yin karatunta cikin natsuwa, shiyasa tayi  wauta wajen rok'arshi alfarmar  akan ya bari su zubar da cikin kawai wai in ta k'are karatun sai ta fara haihuwar.

Aiko ta ga b'acin ranshi a lokacin don kuwa hannunshi har rawa yake yi wajen sakin k'wanji ya mazga mata mari, tareda yi mata gargad'i mai tsanani akan duk abunda ya sami cikinshi wallahi sai ya bata mamaki, aiko taji tsoro sosai ta koma bashi hak'uri amman sai da ya kwashi sati d'aya kafin ta shawo kanshi, gaba d'aya ya k'aurace mata ko magana baya yi mata har sai da yaga ta jigata sosai sannan ya yafe mata suka koma kula da lafiyar d'an tayin cikinsu, don ko kad'an bai bari karatunta ya sami wata matsala ba ya k'arfafa mata gwiwa sosai akan tallafa wa karatunta.

*Nigeria*

Mai unguwa ya kira malam a cikin tsanaki yayi masa bayanin abunda ke faruwa, malam banda fad'ar innalillahi wa inna ailaihirraji'un ba abunda yake fad'a, saboda tashin hankalin da ya shiga a cikin da d'imaucewa a kid'ime ya dawo gida, saboda da safe ne lokacin ya fita kasuwa kenan, aiko sai gashi dole ya dawo gida ba shiri bai zame ko'ina ba sai sashen Iya tun a bakin k'ofa ya fara dannawa Abu kira, saboda anyi dace ranar gidan ya kwana kuma anyi sa'a bai fita ba, sai gashi ya fito yana yamutsa fuska alamun daga bacci ya taso sai wani cin magani ya ke yi, Malam yana zuwa ba tareda wani jinkiri ba ya fara wazga masa mari tareda kai masa wani naushi a ciki sai ga jini yana fitowa ta bakinshi, wanda yayi dai dai da zuwan iya kulu wurin tareda indo da tana ganin abunda ke faruwa tasha jinin jikinta a zuciyarta tana ta jin dad'i, saboda abunda yayi mata bazata tab'a yafe masa ba.

Aiko iya kulu ta fara salati tareda kururuwar azo a taimaketa Malam zai kashe mata yaro, Malam kam bai daina dukan Abu ba har lokacin da iya k'arfinshi, iya kulu ko da taga ba wanda ya zo cetonsa taji tsoron ya kashe mata shi ta nufi malam kamar wata zakanya da nufin ta hanashi

dukan Abu, aiko ya saka hannu ya kai mata wani wawan Mari har sai da ta wuntsila, hannunta karyayye ya bugu da gini ta k'ara k'walla wata katuwar kuwwa, sai ga Mama hassatu da Amina tareda masu aiki da masu gadin gidan duk sunyo caa, kowa ya shigo ya tarar da Malam yana dukan Abu sai yayi turus dole, sai Mama ce kawai tayi jarumtar zuwa ta sha gaban Abu tareda rik'e hannun Malam akan kar ya dake shi, aiko sai a lokacin Malam ya dawo daga hayyacinshi ya fara zuba masa ruwan bala'i, sauran mutanen da ke wurin suna ganin haka suka fara baiwa malam hak'uri, Mama hassatu tace da masu aikin kowa ya tafi zuwa bakin aikinshi sannan suka fice, amma zuciyoyinsu suna ta tunanin me Abu yayi ne da zafi haka wanda har ya janyo fushin ubangidansu mai kirki da hak'uri?.

Malam ko ta inda yake shiga ba tanan yake fita ba sai cisgar fad'a yake yi har yana cewa dashi sai ya bar masa gida, Abu jini yana zuba ta hanci da baki ya shiga ya tattaro kayanshi yazo zai fita ne Iya da ke rungume da hannu tana kuka tace

"Wallahi na rantse da ALLAH bazai fita ba haka kawai zaka korar mani yaro kana ganin halin da ka saka shi a ciki, jini fa ta hanci da baki yake fito masa to WALLAHI sai dai in nima in bar maka gidan mu tafi tare dashi gaba d'aya."

Malam cikin tsananin fushi yace

"Idan baki bishi BA ALLAH ya kwashe maki albarka bak'ar munafuka annamimiya ai duk ke kika jawo komi daman cen tun farko ke kika b'ata shi, to ai yanzu gashinan gurinki ya cika ya dirkawa d'iyar mutane ciki idan ta haife sai akawo maki kiyi rena, amma kisani wallahi ba a gidannan ba sai dai ki koma cen k'auye kici gaba da renon shegun, don gidana gidannan gumin tsalkakakkun mutane ne ba d'an zinar da zai zauna muna a ciki ."

Iya kulu ta aza hannu akai tareda zaro ido a waje tace

"Ciki? wane irin ciki ba dad'in ji?"

Malam ya zo kamar zai kai mata naushi Mama ta tare shi a cikin zafin rai yace

"Da kin bari na lallasata sannan in yi mata bayanin sakacin da tayi da har ya janyo muna wannan bala'i a zuri'armu, don itace tsanin da har Abu yayiwa Mari ciki a gaban idonta, saboda rashin tarbiyyar da ita kanta bata mallaka ba balle har ta baiwa wani."

Ya kalli indo da tayi tsuru tsuru tana rabon ido yace,

"Ke kuma don Ubanki had'o kayanki kema yanzu muje in kaiki gida, don wallahi yaran kowa sun gama zama a hannunki tunda bakisan yanda ake tarbiyyar 'ya'ya ba."

Indo ta shiga d'aki hankalinta a kwance saboda daman cen zama gidan ya gundureta tun ranar da Abu ya keta mata rigar mutunci, saboda tsoratar da ita da yake aduk lokacin da zai

kusanceta da wata sharbebiyar wuk'a, akan duk tayi kuwa ko ta fad'i wallahi sai ya kasheta, dole tayi muk'us har yayi abunda zai yi ya fita saboda tsoron da take ji akan kar ya kasheta.

Iya kulu tana kuwwar wayyo hannunta Malam ya tsallaketa ya fita kai indo K'auye, inda kai tsaye gidansu ya direta sannan ya nufi gidan mai unguwa, bayan sun gama gaisawa ne suka fara tattauna maganar, aka yo kiran mijin kande wato Baban Mari Malam ya bashi hak'uri sosai yana kuka gwanin ban tausayi, Baban Mari yace ba komi k'addara ce Malam ya ciro kud'i masu yawa ya baiwa mijin kande, yace a baiwa Mari ta kula da cikinta har zuwa lokacin da zata haihu, sannan ya koma gida zuciyarshi cunkushe da bak'in cikin da misaltashi abu ne ba kad'an ba, saboda yafi ta'allaka laifin komi akan Iya Kulu don saboda itace tayi sakacin da har hakan ta faru, duk da bawa bai isa ya tsallakewa k'addararshi ba.

Koda yaje gida ya tarar da Mama ta kira mai gyara ya k'ara gyarawa  Iya hannun,  tana kuka tana sambatun ankori d'anta cikin mawuyacin hali, Malam ya ce da Mama ko sannu ta koma cewa da iya kulu wallahi bai yafe mata ba, sannan ya k'ara da cewa ko sashen Iyar ta sake shigowa bada izininshi ba to bai yafe mata ba, aiko hankalinta ya tashi ta fara bashi hak'uri ya yi banza da ita ya shige sashenshi ya barta anan.

Iya ta k'ara b'arkewa da kuka tana sambatun daman cen ai MALAM ba sonta yake ba yafi son Hassatu da ita, to ai in ta mutu sai ya zuba ruwa k'asa ya sha,  a tak'aice  dai yinin ranar gidan haka kowa ya yini zuciya ba dad'i, don ko Mama tana son ganin Malam ta lallashi abunta saboda yana sashen Iyar,  amma kashedin da taji yayi mata ne yasa ta jin ba dad'i, dole dai a waya ta kirashi tana bashi hak'uri tareda kwantar masa da hankali.

Koda safiya ta waye Malam da kanshi ya kira Dr hashim yace dashi ya turo iyayenshi a saka masu rana nan da sati biyu akai masa matarshi, aiko daman Dr a k'age yake shiyasa ba wani jinkiri ya turo Iyayenshi aka saka ranar biki kamar yanda malam yace, ba b'ata lokaci aka shiga hidimar biki Dr ya kawo sadakinshi tareda lefenshi duka a lokaci d'aya, ba tareda wani wasu manyan shagulgula ba aka yi biki aka kai Amarya Amina gidan Angonta Dr Hashim.

Dr kam abun nema ya samu ya baje ya gane k'ofar amaryarshi cikin natsuwa tareda nuna mata shi ma fa ba k'yalle bane a fagen, domin kuwa ya nuna mata lalle shi d'in Dr ne na gaske ko a wannan fannin, yayi ta zuba godiya ga Ubangiji da ya Musanya masa Izzatu da Amina har ta zamo alkhairinsa, domin kuwa duk da d'an gajeren lokacin da aka saka bai hana Mama tsayawa kai da fata ba wajen gyara Amina, shiyasa Dr ya k'ara zaucewa da niimarta da ya d'and'ano,zaman lafiya suke yi sosai tareda soyayya mai k'arfi da suke nunawa junansu.

Wata d'aya tsakanin wannan hargitsin lokacin zuwan mahajjata yayi duk wad'anda Izzatu ta biyawa Makka suka garzaya k'asar saudiyya, inda suma Izzatu da Garzalin suka tafi suka had'u acen k'asa mai tsalki, zuwa lokacin Izzatu ta k'ara murjewa tayi kyau sannan ta k'ara yin 'yar k'iba saboda cikinta ya shiga wata na hud'u a lokacin, cikin ya k'ara yi mata  kyau sosai gwanin sha'awa da burgewa.

ALLAH ya bada zaman lafiya Amina da Dr Hashim 👏🏻

Shin wai ina Alhaji sani da Shu'aib?me zai biyo baya ga indo sakamakon fyad'en da Abu yayi mata???wane mataki malam zai d'auka akan Iya idan Mari ta haihu???.

Akafta💃

D/Auta ce🤝🏻
[8/22, 1:56 AM] Auntyna: *💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*PAGE SEVENTY FOUR*

**********************

Ammaah da Ammi sunji dad'in ganin yanda dukansu suka gansu, saboda Garzali ma kanshi har wata 'yar k'iba ya aza, don kowa ya gansu yasan suna cikin kwanciyar hankali kuma suna jin dad'in aurensu, musamman hango da suka yi Izzatu ba ita kad'ai bace, don Izzatu ta hana Garzali ya fad'a wa kowa tana da juna biyu, a wautarta wai kunya take ji shi kuma ya biye ta suka yi gum abunsu, Mama hassatu tayi masu fad'a sosai akan b'oyewar da suka yi, a cewarta idan banda wannan had'uwar da sukayi kenan sai dai su jiyo ta haifu, Iya kulu kam duk ta kalli Garzali da Izzatu tareda albarkar cikin da ALLAH ya albarkace su dashi, sai ta ji kunyar abunda tayi masu a cen baya,  musamman ganin yanda wanda take so d'in gashi shine silar shigarta duk wani k'unci da take a ciki, shiyasa tayi ta kuka tana rok'on ALLAH akan ya yafe mata akan zaluncin da ta yiwa izzatu.

Amina da Dr ma dasu aka zo aikin hajjin sunji dad'in ganin junansu tsakanin izzatu da Amina da Garzali da Dr, Amina sai tsarguwa take yiwa izzatu saboda cikin da ke jikinta ya d'an turo kad'an

har ana ganinshi, Garzali kam kai tsaye yake cewa Dr ya jawa matarshi kunne akan ta daina matsawa matarshi, su had'e suyi ta barkwancinsu gwanin burgewa, Inna hure ma da mijinta tareda mai unguwa da mahaifiyar Mama hassatu da Ummaru dandan inna hure duk suna cikin mahajjatan.

Sunyi aikin hajjinsu lafiya sun k'are lafiya sannan suka yi kukan rabuwa da juna, Musamman Izzatu da tasha kuka sosai har sai da Ammi tayi ta yi mata fad'a, Ammaah kam lallashinta ta dinga yi akan tayi hak'uri nan da wata biyu ita zata zo ta zauna da ita har sai ta haihu, sannan ne aka samo kanta taji sanyi ta daina kukan, sun rabu cikin kewar juna Izzatu da Garzali suka wuce London, yayin da su kuma suka dawo gida Nigera.

Malam da Iya kulu da Mama hassatu sunyi tsaraba sosai ga 'yan uwa da abokan arzik'i na k'auye, takanas suka je k'auyen sai da suka kwashe sati d'aya a cen, mutane sai turuwar zuwa yi masu barka da arzik'i suke yi, sannan suka dawo gida cike da takaicin abunda suka tarar acen, domin kuwa Indo ma ciki ya bayyana a jikinta da aka tambayeta ina ta samo shi, kai tsaye tace Abu ne yayi mata fyad'e bak'in ciki yasa Malam fad'uwa aka kwashe shi sai asibiti, Iya kulu ma in jininta ya kai d'ari uku to duk ya haye, saboda ba k'aramin cin mutunci Kande da mijinta suka yi mata ba, tana ji tana gani dole tayi gum don bata da ta cewa, don kuwa kande har k'ok'arin dukan Iyar tayi aka shiga tsakaninsu, shiyasa taji haushi ta saki jiki tayi ta tsinewa Iya kulu itada iyayenta tareda bak'in d'anta Abu, Mama hassatu dai sai bada hak'uri take yi saboda in har b'era da sata to ko daddawa da wari, don kuwa da Kwad'ayi bai ja kande ba da duk hakan bata faru ba.

Malam dai yayi jinyar sati d'aya sannan aka sallomoshi, da k'udurin idan safiya ta waye ya kora iyar ta koma cen k'auye da zama har sai d'iyan Kande sun haifu, don yayi rantsuwa ba zai zauna gida d'aya da d'iyan shaggu ba.

Aiko cikin dare sai ga gangar 'yan fashi sun dira gidan. Malam da niyyar su ta Kashe shi, anyi bata kashi tsakaninsu da masu gadi da scuritys d'in dake tsaron gidan, amman duk da haka sai da suka ci nasarar shiga sashen iya kulu, a tsammaninsu Malam d'in a cen yake aikuwa sai ga jami'an tsaro anturo masu mota mota, da suka ga basu sami sa'ar ganin Malam ba iya kulu tana fitowa a rud'e tana kuwwa, wani daga ciki ya saita bindigarshi ya sakarwa Iyar bullet a k'afa, saboda jin sautin jiniyoyin motar 'yan sanda da sojoji, sun tabbatar da an ritsa su shiyasa d'aya yaji haushi ya sauke fushinshi gareta, ba shiri ta fad'i k'asa tareda k'walla k'ara wanda yayi dai dai da shigowar dubban sojojin, Abu dake cikin gangar 'yan fashin ya cakumo wanda ya halbi iyar a cikin karaji yace, "Mamata ce fa"

A cikin zafin nama ya saita d'an fashin ya halbeshi a k'irji, halbin yayi daidai da k'arasowar jami'an tsaron suka saita shi da bindigogi ba shiri ya yi hand's up, suka tasa keyarshi tareda sauran 'yan fashin suka tafi dasu, aka bar wasu suka ciccib'i iyar da take a some suka fito da ita.

Malam da ke lab'e tareda Mama hassatu sai jibin wahala tareda tsoro suke yi, musamman da

suka Ji yo k'arar halbe halbe, Ilham ta fasa k'ara sauran ma'aikatan da ke gidan suma suka k'ara tsurewa, zuwan jami'an tsaron yasa hankalinsu ya d'an kwanta, Malam yayi k'arfin halin fitowa ya lek'o aiko sai yaga an taso k'eyar 'yan fashin a gaba hannuwansu a sama, sai kuma ga wasu jami'an sun d'auko iya kulu ranga ranga, ai afujajan ya iso wurinsu hankali a tashe yake kiran sunanta a rude dashi aka shiga motar wasu 'yansanda suka ja motarsu da k'arfi suka nufi asibiti mai zaman kanta da ita, yayin da wasu suka tafi da 'yan fashin wasu suka tsaya tsaron gidan.

Da k'yar aka samu jinin da ke zuba a k'afar iyar ya tsaya, sabida ga tsintsiyar k'afa aka halbeta gaba d'aya k'afar ta ragargaje, dole Malam yasa hannu akan za'a yi mata aiki a cire k'afar don ta tashi aiki kwata kwata gaba d'aya , an d'auki awanni kafin a fito da ita kwance sambal kamar matatta, an saka bandeji an nad'e gundulalliyar k'afar da aka yanke.

Koda safiya ta waye labari ya bazu a ko'ina akan b'arayi sun shiga gidan surukan d'iyar Gwamna, Gidan TV gidan Radio tareda jaridu duk baza labarin ake yi, sai dai an b'oye sunan Abu don kare martabar gidan Malam da gidan Gwamnati, saboda gudun zubewar mutuncinsu.

Iya sai da tayi sati bata farfad'o ba tasha gorunan jini tareda gorunan ruwa sunfi a k'irga, koda ta falka ta ganta da gundulalliyar k'afa taci kuka kamar ranta zai fita, musamman idan ta tuno ganin da tayiwa Abu a cikin gangar 'yan fashi, a take hawan jini ya rufe ta har sai da bakinta ya karkace, ko Malam kanshi k'arfin hali ne kawai yake yi amma da za'a aunashi da ance shima jinin nashi ya haye saboda bak'in cikin jin sana'ar da Abu yake yi wadda har yayi amfani da damar yazo da mutanenshi akan a kashe shi.

Malam yayi kuka yayi kuka musamman idan ya tuno irin bala'o'an da ya haddasa, d'iyan Kande biyu duk ya d'irka masu ciki, gashi yazo har gida da nufin ya kashe Malam ALLAH bai nufa ba sannan gashi sanadin hakan Iya ta rasa k'afarta d'aya, kuma duk akan sakaci tareda son zuciya wajen gurbata tarbiyyar Abu da Iyar tayi, yanzu gashi an b'ata goma biyar bata gyaru ba, shiyasa Malam ya rok'i Abbaah akan hana sanarwa da su Garzali abunda ya faru, don dole ne idan yaji zaice sai ya dawo to kuma gashi karatun nashi mai zafi ne, wanda shekara d'aya ce kacal zai yi karatun acen.

Bayan wata biyu Iyar taji sauk'i aka sallamota tareda k'afar roba da aka yi mata, wadda kullum ta kalleta sai tayi kuka tareda rok'on gafarar Ubangiji don tasan hak'k'in Izzatu ne yake bibiyarta.

Cikin Mari a lokacin watanshi takwas yayin da na Izzatu yake cikin wata na shidda, Indo kuma nata yana wata hud'u.

Iya kulu ta koma ta ALLAH kullum da carbi a hannunta tana lazumi tareda istigfari tana rok'on ALLAH akan ya yafe mata abunda tayi a baya, kullum bata da aiki sai kuka saboda an yanke wa su Abu hukuncin daurin rai da rai a gidan maza, saboda sassaucin da aka nemar masu don farko hukuncin kisa aka yanke masu ta hanyar rataya.

Watan haihuwar Mari yana kamawa Malam ya maida Iya k'auye aka dawo mata da indo da Mari a wurinta, ita aka barwa kula da su da komai nasu duk da itama ba wata lafiya ce da ita ba, aiko wani dare nak'uda ta kama Mari aka kwasota zuwa asibitin birni, zuwansu bai fi minti biyar ba ta haifo d'anta k'ato guda amman ko shurawa baiyi ba ya rasu, asubar farin aka nemi Mari sama da k'asa aka rasa ba'a ganta ba ta tsere, hankulan mutane ya k'ara tashi aka bazama nemanta lungu da sak'o na  garin ba'a ganta ba, dole aka zubawa sarautar ALLAH ido, wata d'aya a tsakani sai ga labari yazo anga Mari gidan Karuwai na garin, ta fetsare iya fetsarewa bata kunya kuma bata shayin kowa akan sana'arta ta karuwanci da ta fara, dole aka zuba mata idanuwa don ta riga da ta fitsare k'afafunta.

Cikin Izzatu yana Wata takwas Ammaaah taje cen London ta zauna tareda da ita har sai da ta haihu, saboda cikin yayi girma sosai kamar ba haihuwar farin ba, gashi yana bata wahala matuk'a  don ko k'afafuwanta sun kumbure suntum, ga k'afarta d'aya da ta mak'ale dak'yar take iya tafiya, tayi ta kuka tana rok'on ita dai acire mata cikin hakanan ta gaji, Ammah da Garzali suyi ta aikin lallashi da ban baki.

Aiko ranar haihuwa ba k'aramar azaba tasha ba tun safe ta fara nak'uda har marece, tun ana tsammanin zuwan haihuwar har aka yanke shawarar ayi mata CS, Garzali yana kuka saboda tsananin tausayinta ya saka hannu, ana shirye shiryen shiga da ita d'akin tiyata ne nakudar tazo gadangadan, likitoci suka rufu a kanta cikin ikon ALLAH sai ga d'anta ta haifo k'ato guda, ana cikin murna ta k'ara santalo wani yaron sai dai shi bai kai girman na farkon ba, murna wajen Garzali da Ammaah abun ba magana.

Bayan an shirya yaran ne aka mik'awa Garzali su duka biyu ya karbesu ya rungume a jikinshi yana shak'ar kamshinsu, sai godiya yake yiwa Ubangiji da ya azurtashi da samunsu, a take yayi masu hud'uba da sunan AYUBA da YAHAYA waton dai sunan Malam da Abbaah, sannan ya mik'a su ga Amaaah ya fita cike da murna tareda  tsananin farin cikin, sai kiran wayoyi yake yi yana sanar da mutane abun alkhairin da ya same shi.

Bayan kwana biyu da sallamosu ne jirgin 'yan Nigeria masu zuwa ganin jarirai ya isa London, kowa sai Murnar ganin jariran yake yi, Iya kulu yaran rungume a jikinta ta fashe da kuka tana rok'on Izzatu ta yafe mata, Izzatu ta ce da ita ai ita tuni ta yafe mata duk abunda tayi mata, don ALLAH ta daina dawo da hannun agogo baya, Iya kam duk ta motsa bata fasa rok'on yafiyar Izzatun ba, saboda a ganinta iftila'o'an da duk suka sameta suna da nasaba da zaluncin da tayi mata, sai a lokacin ne ake yimasu bayanin abunda ya faru da wanda yake kan faruwa, Izzatu tayi kuka sosai da taji abubuwan da suka faru bayan basu nan, tayi ta nanata yafiyar da tayi wa iya Kulu ko don ALLAH ya tsayar da sakamakon iya hakanan, Kwanan Iya biyu jirgi ya juya da ita Nigeria saboda Indo da ta baro ciki ya tsufa don a lokacin watanshi bakwai.

Ta bar sauran wad'anda zasu tsaya ayi bikin sunan dasu, Amina ma duk da cikin da take dashi d'an wata biyar bai hanata halartar ganin jariransu ba, dangin Abbaah ma da suke ganin lafinsa akan hukuncin da ya yanke wa ALHAJI sani da shu'aib, da suka gano gaskiya daga baya duk sun bi don ma da yawansu sun zo ganin jariran, anyi shagalin bikin suna cikin natsuwa da

kwanciyar hankali sannan suka dawo tareda kewar juna.

Bayan sati d'aya da suna IZZATU ta kammala jarabawar k'arshen shekararta ta farko Ammaah ta kwasota suka baro London tareda 'yan jariranta da suka ci sunan AMIR da AMMAR, HASSAN shine AYUBA wanda ake yiwa lak'abi da AMIR sai HUSSAINI shine YAHAYA wanda ake cewa AMMAR, suka garzayo k'asa Nigera da zummar idan shima Garzali ya kammala karatunshi da ya rage saura wata biyu zai biyo bayan su.

Akafta💃

D/Auta ce🤝

*💦RUWA DA KANKARA⛈️*

*NA HADIZA D/AUTA*

https://www.facebook.com/106584514455096?referrer=whatsapp

*⭐⭐⭐TAURARI WRITERS ASSOCIATION⭐⭐⭐*

(We entertain and educate according to our religion and ethnics)

*PAGE SEVENTY FIVE*

🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚🔚

******************

Ammi da Abaaah sunji dad'in ganin 'yan biyun jikokinsu, SUDEIS da SADIS dasu fahat sai murnar ganin jarirai suke yi, Ammar kam yafi kowa jin dad'i saboda sunanshi da aka sakawa mai sunan Abbaah, a kullum yana nanuke da mai sunanshi ko daukarsa baya so ayi, Ammaah da Ammi kam sai kula da 'yan jikokinsu suke yi tareda mahaifiyarsu Izzatu mai jego, Mama tana iya k'ok'arinta wajen zuwa ta gansu ko tasa akawo mata su su yini wurinta, soyayya da kulawa

fa mai jego da 'yan yaranta suna samu sosai, wata d'aya da haihuwarsu sunyi b'ulb'ul da su gwanin sha'awa, itama kanta tayi jiki abunta saboda ba wata wuyar wahalar reno take sha ba, iyakacinta da su idan zata basu nono kuma da sun sha za'a karb'esu, shiyasa take bajewa tana ta shan soyayyarta da angonta na k'arni, Pic d'inta da na jariran kullum safiya sai ta tura masa sannan idan tana shayar dasu video call suke yi yana ta kallo yana jin dad'i, ya matsu sosai ya dawo gida yaga matarshi da 'yan yaranshi, a gefe d'aya kuma yana so yazo yaga Iya kulu da ta koma k'auye tana jinyar Kanta tareda kula da Indo da duk dawainiyarta ta koma kanta, ya damu sosai da jin halin da yaji d'an uwanshi ya ke a ciki, waton zama gidan kaso na tsawon rai da rai.

Indo kam watan cikinta yana shiga tara ta fara nak'udar tsaye, har zuwa lokacin da nak'udar gasken ta zo aiko cikin k'ank'anin lokaci ta haifi 'yar d'iyarta  salun alun,  tun kafin ma ace za'a kaita asibiti, aikuwa Iya kuu tayi Murna ganin yarinyar sosai, saboda kama sak da take yi da Abu lokacin da ta haife shi, sai dai abun bak'in da ta tuno da bafa ta hanyar sunnah aka same shi ba, bayan angyara yarinyar da Mahaifiyarta Iya tana rungume da Jaririyar ta fashe da kuka, saboda ta tuno lokacin da MALAM ya tsinto Izzatu tana jaririya,ta tuno da Kalaman da tayi ta jifar IZZATU da su lokacin da Kande ta zugata, tareda maganganun da Dada tayi mata a cikin b'acin rai sunata yi mata  amsa amo cikin kunnuwa, ba shiri ta rungume 'yar jinjirar tana ta wani masifaffen Kuka, indo dake rakub'e tana kallonta itama sai kukan take yi gwanin ban tausayi, Sai ga sallamar Kande asama ba tareda ta jira an amsa mata ba ta hankad'e labulen ta shigo idonta akan indo tace,      "Tunda kin haife mata cikin to taso muje gida kin gama naki aiki, sai susan yanda zasuyi da abunda aka haifa ke kuma ALLAH ya isar maki akan cutar da aka yi maki."

Ta jawo indo kiii zasu fita Iya ta ajiye jaririyar da take ta wutsil wutsil cikin towel tana tsutsar hannu alamun tana neman nononta, Iya ta yunk'ura da lafiyayyar k'afarta taje ta rik'o hannun indo,tana kuka wanda har ya ta kasa yin magana,  Kande ta saka hannun cikin zafin nama ta fusgo Indo sai ga Iya kishim k'asa ta fad'i, Kande bata tsaya kula da abunda tayi ba ta fice gidan tana ta bala'i rik'e da hannun indo.

Iya ta yi k'ok'arin tashi zaune saboda kukan da jaririyar ta canyara, jiki ba kuzari taje ta d'auketa tana girgizata tareda k'arin sautin kukanta, a zuciyarta sai Istigfari take yi tareda nadamar abunda ta aikata a baya, tana cikin Kukan sai ne sai ga Indo ta shigo d'akin da gudu tana kuka, saboda a tsammaninta Iyar tana nan kwance har lokacin, tana ganin Iyar rungume da yarinyar taji tausayin iyar ya kamata matuk'a, taje tasaka hannu ta karb'i yarinyar a hannun Iyar ta zauna tareda d'ora yarinyar a cinyarta, Iya tana kallo ta fiddo nono ta fara shayar da yarinya, iya ta sauke ajiyar Zuciya sannan ta zauna tana kallon indo da yarinyar tausayinsu ya kamata, ta dafe baki ta shige k'uryar d'akin tana wani irin gunjin kuka zuciyarta cike da nadama tareda danasani akan rayuwarta ta baya, tana ina ma za'a iya maido hannun agogo baya da ta gyara miyagun halayenta da a kullum Dada take kuka akansu,acikin kukan tace,    "Dada  uwa tagari ALLAH ya jik'anki da rahama, yau na gano abunda kika dad'e kina nusar dani, ashe ita k'addara zuwa take yi babu wanda yafi k'arfinta sai wanda ALLAH ya tserar, yau gashi 'yar da nike shegantawa tayi mani rana Iyayenta sun zamo silar arzikinmu, amman duk da haka ALLAH ya mayar man da mugun nufina akaina,  nida mai zugani muna sheganta 'yar mutane wadda ta zamo tsatson

sunna mai kyakkyawan asali,sai gashi hak'k'inta yau yana ta bibiyarmu har gashi mune a yau rungume da abun kunyar, Ya ALLAH ka yafe muna nida Kande "

Ta k'ara fashewa da wani kukan sai ga Indo ta shigo goye da 'yar jinjirarta da tayi bacci, ta zauna tareda share hawayenta tace da Iyar, "Na rungumi k'addarata ALLAH ya yafe muna kurakuranmu duka, kema kiyi hak'uri ki rungumi kaddararki haka ALLAH ya tsara mutum bai isa yayi jayayya ba, da ke da Innarmu kuyi tuba ga Ubangiji akan abunda kuka yi abaya, ALLAH maji rok'on bayi ne zai yafe maku laifukanku. "

Kande da ke lab'e tana saurararsu ta shigo hawayen nadama suna zuba akan fuskarta, saboda shigarta bayi Indo ta sulale ta dawo gidan, koda ta fito bata ganta ba tayo tsinke gidan, tun a bakin k'ofar d'akin ta jiyo kukan Iya Kulu da sambatunta, jikinta yayi sanyi tana k'ok'arin shigowa ne taga Indo ta shiga d'akin goye da 'yar jaririyarta, imani ya k'ara kamata musamman da taji kalaman Indon, ta sami wuri ta zauna tana kuka ta fara magana, "Lalle yau na yarda da hak'k'in IZZATU ne yake bibiyarmu, munyiwa yarinya k'age mun shegantata yau ga shege an haufar muna muna kallo ba yanda zamuyi, asanadin haka ma yau Mari ta shiga duniya duk akan sanadin alhakin yarinyar Mutane da muka d'auka, yau ga Abu cen gidan yari d'aurin rai da rai tareda horo mai tsanani, ALLAH ka yafe muna saboda wannan izna ne ga duk mai halaye irin namu, yaji tsoron ALLAH ya daina ya tuba ga ubangijinsa sannan ya nemi yafiyar wad'anda ya zalunta, tun kafin zuwan ranar nadamarshi."

Gaba d'aya suka runtume suna ta kuka gwanin ban tausayi aka rasa mai lallashin wani, har sai da suka in sallamar wata matar Mai unguwa sannan suka tsayar da kukansu.

Bayan an bata Umurni ta shigo take sanar dasu sak'on mai unguwa da yace tazo taga abunda aka haifa kafin yazo.

Kafin kace me gari ya d'auka Indo ta haife cikin shegenta, aikuwa sai 'yan gutsuri tsomar gulma kawai ke tashi gungu gungu na tsofaffi da matasan gari, har ma da matan cikin gida masu zuwa ganin k'wak'waf, har sai da mai unguwa ya yi kashedi akan kada wanda ya sake zuwa gidan, sannan ne aka sami sauk'in masu zuwa barkar Munaficci, Malam kam baizo ba kuma ya hana kowa yazo sai dai ya aiko da komi da ake buk'ata na jaririya da mai jego, tsakanin kayan barka dana abincin da zasu ci da abubuwan da zasu buk'ata sai da ya aiko , don kuwa har ragon kauri sai da ya aiko aka soyawa mai jego, ranar suna yarinya taci sunan Iya Kulu wato Hauwa'u ina kiranta da suna jidda, 'yan gulma sunyi iya yinsu har sun gaji sun bari don kansu.

Izzatu tayi arba'in taso tazo k'auyen amman Malam ya hana, iyakacinta gidajen 'yan uwa da abokan arzik'i da ke cikin birnin, duk da aranta taso taga Iyar da abunda aka haifawa Abu amman Malam ya hana, sai dai a sace taje ita da Amina gidan yari sun gano Abu, yayi bak'i ya rame jikinshi gaba d'aya shatin buloli ne sun yi masa tambo tambo, kallo d'aya idan kayi masa bazaka so k'ara kallonshi ba, har k'asa ya duk'a yana rok'on IZZATU gafara akan abunda ya yi mata a baya, tana kuka tace dashi ba komi ita tuni ta yafe masa, ya nemi da ta bashi yaran ya gani Amina ta harareta alamar kar ta bada amman tayi mata kamar bata gani ba, ta mik'a masa

yaran duka duk da warin da ke tashi a jikinshi, yana kuka ya dinga kallonsu yana yaba tsantsar kyawon da ALLAH yayi masu, sannan ga kuma kamar d'an uwanshi sak shi suka biyo kamar an tsaga kara, Amina ta saka hannu ta karbesu saboda kukan da taga yaci k'arfinshi, sai nanacin yake yi Izzatu ta yafe masa kuma tace don ALLAH Malam da iya su yafe masa, duk dauriyar Amina sai da ta yi hawaye saboda tausayin da ya bata.

A cikin kukan yace da Izzatu idan taje ta cewa d'iyan  Kande Mari da indo su yafe masa keta masu rigar y'anci da yayi, a nanne  ma  Amina take sanar da shi abunda ya faru bayan baya nan, waton k'afar Iya da aka cire da tserewar da mari tayi bayan Haifu abun baizo da rai ba, sannan yanzu Haihuwar 'yar da Indo tayi masa mai suna Jidda, Abu ya k'ara fashewa da kuka gwanin ban kuka yana rok'arsu su kawo masa yarinyar ya gani tareda Indo ya nemi yafiyarta, yana cikin kukan ne lokaci ya cika aka jashi kamar wata dabba aka shige dashi, Izzatu da Amina da Kuka kashirb'in suka fito gidan Yarin.

Kai tsaye gidan Malam suka nufa suna kuka suke sanar da Mama abunda ke faruwa, anyi sa'a Malam baya gida Mama tayi ta lallashinsu tareda yi masu alk'awalin zata shawo kan Malam yayi hak'uri ya yafewa Abu da Iya, don ita kanta hukuncin da ya yanke wa Iya bai yi mata dad'i ba.

Garzali kam yana cen yana fama da exam's wadda itace ta k'arshe da ya k'are ta zai dawo gida, duk da damuwar da yake a ciki ta kewar matarshi da 'yan  yaranshi, tareda bak'in cikin matsalolin da gidansu ke fuskanta bai hana shi dukufa wajen jajircewa akan jarabawar ba, don kuwa koda suka k'are resul ya fito a tashi d'aya suka rik'e shi saboda k'wazon da suka ga yayi akan yayi aiko da su a manyan asibitocin dake k'asar na tsawon shekara d'aya, aiko yayi farinciki sosai da wannan ci gaba duk da yaso ya dawo itama kasarshi ta amfana da iliminshi, amman idan ya tuna shima aikin wani k'arin ilimin ne sai yaji dad'i kuma yayi godiya  ga ALLAH da hakan ta  kasance.

Aiko kai tsaye ya garzayo k'asarshi ta gado waton Nigeria zuciyarshi cike da kewar k'asar da mutanen kirkin da yayi acen.

Mama ta nemi alfarmar Izzatu ta koma gidanta domin ta tarbi mijinta, aiko ba Musu aka tattarata aka  mayar da ita tareda masu aikin da zasu dinga kula da su Amir bayan an yi mata sabon gyara ciki da waje.

Garzali kam tun daga Airport da su Abbaah da malam ammaah da Mama da suka je tarbarsa ya gaisa dasu a cen  kai tsaye gidanshi aka wuce dashi, zuciyarshi cike da farin cikin dokin son ganin Matarshi da yaranshi, aikuwa suna yin arba da gudu ta je ta rungume abunta sai kace wad'anda suka YI shekara basu ga juna ba, cike da murnar ganinta yace

"Where is my kid's?"

Tayi masa nuni da d'akin da suke ya saketa da gudu ya nufi d'akin, yana yin arba dasu kwance akan gado Ammar yana bacci Amir kam sai wutsil wutsil yake YI da k'afafuwa da hannu a cikin

shawul, yayi saurin bud'e idonshi yace,  "What a amazing?"  da sauri yaje ya d'auki Amir dake ido biyu tareda bashi peck a goshi yana jin dad'in ganin yanda suka yi b'ulb'ul gwanin burgewa, Ammar ya fara mutsu mutsu zai tashi yayi saurin d'aukarshi yace,  "Come and seeing your daddy."

Aikuwa ya d'auko shi shima ya had'asu waje d'aya ya rungumesu a jikinshi zuciyarshi fari k'al da ganin 'yan biyunshi, yayita lallashinsu har dukansu suka yi bacci ya lallab'a ya ajiye su, sannan ya sauke ajiyar zuciya, idonshi suka kai akan fuskar Izzatu da suna had'a ido tasha mur, tana tsaye jikin k'ofa tana kallonsu cike da burgewa amman a fuska tayi fushi, da sauri ya taso yace

"Na shiga d'ari me nayiwa my sugar take fushi dani?"

Ta bud'e d'akin ta fito ya biyo bayanta tareda rungumeta yana shak'ar numfashinta ido a rufe yace,

"Muje a bani hak'k'ina wallah."

Yanayin da yayi magana ya bata dariya sosai, amman ta mazge tace  "Yanzu kasanni bayan kafi son yaranka dani."

Da sauri ya zaro ido yace,  "Sharri da rana haka za'a likamun kashin kaji?"

Yanayin da yayi maganar ne yasa ta k'yalk'yale da dariya  ba shiri, aiko ya fara sarrafa kayanshi duk magiyar da take yimasa akan ya bari yaci abinci ya huta amman ina, har sai da ya jik'a alkalaminshi sannan hankalinshi ya  kwanta, sannan yaje yayi wanka ya dawo falo yana cin abinci suna firar yaushe gamo.

Kasancewar dawowar dare ce yayi takanas ya kaiwa masu aiki yaran ya k'ule da matarshi ya darji amarcinshi, har sai da yaran suka yi ta kuka sannan Izzatu ta karb'osu suka dawo wurinsu, suka ci gaba da Reno.

Aiko koda safiya ta waye ya nufi gudansu Abaabh bayan sun gaisa yayi wa Abbaaah bayanin da zai yimasa dangane da abunda ya shafi karatun da aikin da aka daukeshi, Abbaah yayi murna sosai kuma  ya jinjinawa kwazonshi nan ne yake yimasa bayanin Asibitinshi da ake ginawa wadda saura k'iris a k'are, sannan da alkawullan da yayi masa akan ci gaban k'auyen duk anyi wasu anfa wasu kuma har an kammala, yaji dad'i sosai yayi murna, aka kira su Ammaah da Ammi suka zo suma suka gaisa tareda taya shi murna, sannan ya fito zuwa gidansu Malam.

Malam yaji dad'in ganin Garzali cikin natsuwa tareda hutu da kwanciyar hankalin da ya bayyana gareshi, yayi hamdala ya godewa ALLAH da ya albarkace shi da samun d'a irinshi, sun dad'e suna tattaunawa da Malam akan ya yafewa Abu da Iya dak'yar ya shawo kanshi, don ita Mama har tayi maganarta ta k'are k'anzil baice da ita ba, dole ta hak'ura ta bar maganar tunda ta

fahimci ya hau da yawa, yanzunma don yana shi d'in shiyasa ya amince akan zasu je k'auye gobe, sannan kafin suje su biya gidan yari su gano Abu.

Aiko tunda sassafe suka shirya dukansu Malam da Mama Izzatu da Garzali tareda Ammmah Ammi Amina da tsohon cikinta tareda Dr suka dunguma mota mota suka rafi ganin Abu, ba b'ata lokaci aka fiddo masu shi yanayin da suka ganshi yasa dukansu jikinsu yayi sanyi, anan take Ammaah ta bada umurnin a sake shi, aikuwa aka cire masa ankwar dake hannunsa da k'afa, aka kaishi wani tsabtataccen toilet yayi wanka aka bashi kaya ya saka sannan aka badeshi da turare, sannan suka shiga mota zuwa k'auyensu Malam, kowa zuciyarshi cike da alhinin ganin Abun, don ko baka da Imani ka ganshi sai ka tausaya masa, kai tsaye gidansu Malam aka nufa aka bud'e k'aton falonshi kowa ya zauna,  mai unguwa da mukarrabanshi suka zo aka had'a Abu da Indo tareda su Iya da kande da mijinta, sannan Garzali ya fara magana kamar haka,

"Wannan taro anyi shine saboda a had'u a yafewa juna abunda ya faru a baya, saboda haka don ALLAH dukanmu muyi hak'uri mu yafi juna ALLAH ubangiji ya yafe muna gaba d'aya "

Gaba d'aya falon aka ce "Ameeñ"   Iya kulu ta fashe da kuka tana rok'ar Izzatu ta yafe mata abunda tayi mata, Izzatu tace ai ita wallahi tuni ta yafe mata saboda daman cen bata kullaceta ba ita, kande ma rarrafo ta kama k'afar izzatu tana rok'on ta yafe mata, itama tace ta yafe mata Abu kam fashewa yayi da kuka gwanin ban tausayi yaje wurin Malam ya rik'o hannunshi yana rok'arshi akan ya yafe masa, shima yace ya yafe masa sannan ya dawo wurin kande itama ya rok'eta sannan idonsh suka tsaya akan Indo da take ta sharar hawaye, yana kuka yana rokonta yafiya itama sai kukan take, ba kunya yace

"ina 'yata indo"

Indo ta sunne kai tareda yi masa nuni da Inda Iya da ke rungume da yarinyar, yaje ya durk'usa gaban Iya yana kuka yace ta yafe masa itama tana kuka tace ta yafe, ya saka hannu ya karb'i 'yarshi wadda yake jinta har cikin jininshi, ya rungume yana kuka daganan Malam yayi gyaran murya yace,     "Alhmdllh tunda har Indo ta haifu lafiya  ina nemawa Abu neman aurenta ALLAH ubangiji ya yafe masu laifukan da suka aikata dukansu muma ya yafe mu gaba d'aya  "

Kowa yace Ameen Babansu Mari cikin jin dad'i yace,      "a matsayina na mahaifinta Na ba Abu auren Indo duniya da lahira."

Gaba d'aya wurin ya d'auki kabbara, Garzali ya fito da kud'i aljihunshi rafar 1k ya ajiye, sannan yace,   "Ga sadakin idan ba damuwa ko yanzu za'a iya d'aura masu aure."

Kowa yayi na'am su Ammaah suka fito suka shiga sashen Mama hassatu, Mai unguwa yasa aka kawo dabino aka rarraba a tsakaninsu ba b'ata lokaci  aka d'aura auren Abu da Indo akan sadaki nera dubu d'ari, sannan taron ya watse sai ALLAH sanya alkhairi ake yiwa auren.

A cen sashen Mama kuwa Iya kulu da kande basu daina neman yafiyar IZZATU ba, Ammah cike da mamaki ta tambaya abunda ya faru ba wata  kwana Iya ta fayyacewa su Ammaah da Ummi duk abunda ya faru, tun daga ranar da Malam ya tsinto Izzatu har lokacin da iftila'o'an da suka yi ta faruwa ga rayuwarsu da suka sani da wanda baije kunnuwansu ba, aiko a take itama Ammaah ta fashe da kuka saboda tuno itace tsanin komi, don itace tayi sanadin raba izzatu da gidansu har wasu suka dinga shegantata, ta rik'o hannun Ammi da Izzatu tana ta rok'arsu yafiya tana kuka, Ammi ma duk taji zafin sheganta mata 'ya da aka yi amman bata kullace kowa ba ta yafewa kowa, har itace ke basu baki akan su daina kuka komi ya wuce, Izzatu kam daman cen ta riga da ta yafewa kowa itama ta shiga aka dinga basu baki akan suyi hak'uri su daina kuka.

Ammaah da Ammi suka koma gida zuciyoyinsu cike da alhinin abunda ya faru, su malam kam kwanansu biyu a garin bayan anyi d'an shagalin biki sama sama, sannan suka bar Amarya da angonta tareda surukarsu Iya kulu,don Malam yaso su koma cen birnin abar Abu da matarshi da 'yarshi anan, amman tace a barta nan kawai zata zauna dasu.

Auren Abu da wata d'aya Amina ta haifu, ta sami d'anta k'atoto ranar suna aka saka masa sunan Baban Dr.

Su Ammar suna da wata biyar Izzatu ta sami wani cikin lokacin ma har sun koma London inda Dr Garzali yake aiki a wata k'atuwar asibiti, ita kuma take  ci gaba da karatunta ga yara biyu ga d'an tayin ciki, abubuwa suka runtumewa Izzatu taso a zubar da cikin amman yak'i bari,  da taimakonshi na matsayinshi na mijinta da taimakinshi da shawarwarinshi na babban Dr ta sami yaranta suka gyagije sunada wata tara suka iya tafiya, ko ina suna zuwa da gudunsu amman yak'i bari a yaye su har sai da ta haifu, sannan aka cire su daga Nono, ta ci gaba da shayar da yarinyar da ta haifa mai sunan Ammaah wadda suke kira Mimi.

****

ALHAJI sani kam sai da yasha gwalwgwale sannan ya YI bayanin duk tuggun da ya had'a da bakinshi, wanda laifin Shu'aib kad'an ne fiye da rabi duk nashi ne, yasha wuya a hannun sojoji har sai da suka makanceshi saboda azaba, sannan ne Abbaaah yace su kyaleshi aka kaishi asibiti yayi jinya sosai amman idanuwa sun tsiyaye dole sai na roba aka saka masa, sannan ne yayi nadamar abunda yayi yana sanar da sauran 'yan uwanshi komi,  tiryan tiryan yayi masu bayanin duk makircin da ya k'ulla don su daina ganin laifin Abaaah, aikuwa dukansu sunyi nadamar cin zarafin da suka yi masa, kacokam suka d'aura lefin kanshi Musamman saboda halbin da yayiwa Shu'aib wanda asanadin hakan hannunshi ya daina motsi, duk da yasha jinya yaji sauk'i amman jijiyoyin hannunshi duk sun katse, yanzu haka hannun ajiye kawai yake baya amfana masa komi, daga shi har Alhajinshi sunyi nadamar abunda suka aikata sunyi ta neman yafiyar Abbaaah, lokacin da Izzatu tayi arba'in taje gidansu sunyi ta rok'onta akan ta yafe masu, ta tausaya masu halin da suke ciki a take ta yafe masu.

Yarinyar Abu kam tana 'yar shekara biyu ta fito k'ofar gida tana wasa ne wani d'an shayeshaye yayi mata fyad'e, a take a wurin ta mutu ko shurawa bata yi ba kuma Ya tsallaketa ya tafiyarshi.

Sai da yaran unguwa suka kawo ta gida matacciya iya kulu tana yin arba da ita tareda jin abunda ya faru,  jininta ya haye ta  fad'i tun kafin aje asibit tace ga garinku nan, ALLAH ya karb'i ran Iya Kulu a sanadiyyar fyad'en da aka yiwa jidda d'iyar Abu.

Anyi sadakar sati d'aya da rasuwarta sannan su Malam suka koma gida su Garzali ma suka koma london tareda yaransu.

Shima kanshi Abu tashin hankalin da ya shiga ba kad'an ba, saboda ba k'aramin so yake yiwa 'yarshi ba shiyasa yayi ta rok'on ALLAH tareda istigfari akan abunda ya aikatawa Mari da Indo, ashe haka iyaye suke ji idan an b'ata masu yaransu, ya jinjinawa iyayen da hakan take faruwa dasu saboda shi kanshi da aka yiwa 'yarshi da ba ma ta hanyar aure aka sameta ba yaji zafi balle 'ya'yan sunna, ALLAH ya k'ara tsare muna yaranmu gaba d'aya matan da mazan duka.

Bayan shekara biyar  GARZALI da IZZATU sun k'are karatunsu sun dawo gida an kammala masu ginin k'atuwar asibiti mai zaman kanta mai suna MARYAM HOSPITAL HOSPITAL, waton sunan Dada bayan itama aka yi wata acen k'auye aka zuba maaikatan likitoci Doctor GARZALI da Dr IZZATU sun duk'afa ceton rayuwar al'umma a birni da k'auyensu da ya zama wata alkarya saboda abubuwan ci gaban da aka kawo masu suna amfana.

Anan na kawo  k'arshen LITTAFINa mai suna RUWA da KANKARA, abunda nayi kuskure Ubangiji ya yafe mani inda nayi daidai ALLAH ya bani lada, ina k'aunarku masoyana aduk inda kuke kusani HADIZA IBRAHIM  D/AUTA K'AURA ZAMFARA STATE  tana k'aunarku Son so fisabilillah  alkhairin ALLAH ya kai maku a duk inda kuke NAGODE 🤝🤝🤝

Mu had'u a book d'ina mai suna BAKAN GIZO kar ku bari abaku labari kuma kuzo a kafta da ku🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️🏃‍♀️

Tammat bihamdullah👏👏👏👏👏